# Tauhidi

# Ginshiƙin Musulunci

Sharhin Littafin:

## *Al-Usul Ath- Thalatha*

**"Shika-shikan Aƙidar Musulunci Guda Uku"**


Wallafar:

**Dr. Abdulmuhsin Ibn Muhammad Al-ƙasim**

Babban Limamin Masallacin Madina

Fassarar:

**Cibiyar Ahlulbaiti da Sahabbai ta Nijeriya**

# تيسير الوصول شرح ثلاثة الأصول

لفضيلة الشيخ الدكتور عبد المحسن بن محمد القاسم

إمام وخطيب المسجد النبوي

حفظه الله

بلغة الهوسا – لغة المائة مليون إفريقي

*Masu Fassara*:

**Dr. Muhammad Mansur Ibrahim**
Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci
Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, Sokoto

**Aliyu Rufa'i Gusau**
Hukumar Bincike da Bunƙasa Shari'ah,
Zamfara

*Masu Bita*

**Farfesa Haruna Abdullahi Birniwa**
Sashen Harsunan Najeriya,
Jami'ar Bayero ta Kano

**Dr Sani Yusuf Birnin Tudu**
Babban Manazarcin Harshen Hausa a
Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci
Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, Sokoto

Bugu na Farko 1436H/2015M
ISBN
Haƙƙin Mallaka
@ **Cibiyar Ahlulbaiti da Sahabbai ta Nijeriya**
ahlulbaitiandsahaba@gmail.com

## *Gabatarwar Mawallafi*

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Ubangijin talikai. Tsira da aminci su ƙara dauwama bisa ga Annabinmu Muhammadu, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya. Bayan haka:

Ko shakka babu littafin ***"Shika-shikai Uku na Aƙidar Musulunci"*** wanda shugaba mai daraja, mujaddidin addini; Sheikh Muhammad ɗan Abdilwahhab - Allah ya ƙara masa dubun rahama da jinƙayi - ya wallafa, yana daga cikin mafi amfanin wallafe-wallafen da aka yi a wannan fanni na Shika-shikan Addini. Sakamakon haka ne ma da yawa daga cikin ɗaliban ilimi da fararen hula a wannan fage suka karɓi aikin nasa hannu bi-biyu. Suka kuma ba da himma sosai wajen karanta shi da nazarin shi da hardace shi. Ba don komai ba, sai domin kasancewar waɗannan shika-shikai wani babban sharaɗi ne, wanda aƙidar Musulmi ba ta karɓa sunanta sai da shi. Wannan ba abin mamaki ba ne saboda, da ma Tarihi ya tabbatar da irin yadda Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya yi ma wannan malami baiwar ƙwarewa a fagen wallafa, da kyakkyawan tsari, da kafa ƙwararan dalilai da hujjoji tare da kaifin lafazi, duk a cikin kyawawan kalmomi. To, sai ga shi waɗannan shika-shikai guda uku, sun haɗa gaba ɗayan waɗannan siffofi da sigogi da kamanni, kamar yadda jikansa Sheikh Abdurrahman ɗan Hasan *Rahimahullah* yake cewa: *"Amfanin wannan littafi ga masu neman shiriya, ba ya ƙidayuwa, tattare da zamansa taƙaitacce".*[1]

Tabbas haka abin yake. Saboda littafin ya ƙunshi duk abin da saninsa yake wajaba a kan ɗan Adam, wanda ya danganci sanin Ubangijinsa, da nau'ukan ibadun da ya yi umurni da su, da yadda bawa zai san makamar addininsa, da matakai da zanguna da martabobinsa, da rukunan kowane mataki. Kazalika, da sanin Annabin Allah ta hanyar sanin wani abu daga cikin tarihin rayuwarsa, da hikimar da take tattare a cikin aiko shi a matsayin Manzo, da imani da tayar da matattu, da manyan Rukunan Tauhidi guda biyu, wato kafirce ma Ɗagutu da imani da Allah Mahalicci.

[1] *Ad-Durar-Assaniyya* 4/733

Matsayin da waɗannan Shika-shikai Uku suke da, na zama sharaɗin ingancin aƙida, ya sa Shehun Malamin ya mayar da hankali wajen laƙanta ma ɗalibai da sauran mutane su. Shi ya sa Sheikh Abdulaziz bn Baz *Rahimahullahu* yake cewa: *"Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya kasance yana laƙanta ma ɗalibai da sauran jama'ar gari waɗannan shika-shikai domin su nazarce su da kyau, su kuma hardace su, har a wayi gari sun zauna daram a cikin zukatansu saboda zamansu sharaɗin ingancin aƙida."* [2] Sarkin Malamai Sheikh Muhammad bn Ibrahim *Rahimahullah,* shi kuma sa yake yi ana karanta wannan littafi yana sharhinsa a kowace rana.[3]

A farkon wannan littafi akwai wasu muhimman saƙonni guda uku, masu matuƙar amfani da Malamin ya yi shimfiɗa da su. Ga su kamar haka:

***Saƙo na Farko:*** Wajabcin neman ilimi da aiki da shi, da kira zuwa gare shi tare da haƙurin cuta a kan wannan tafarki.

***Saƙo na Biyu:*** *Tauhidin Rububiyyah* da *Uluhiyyah* da kuma so da ƙi don Allah.

***Saƙo na Uku:*** Bayani a kan *Tauhidi* da kishiyarsa.

Da wannan cikakken tsari sai wannan littafi na Shika-shikai Uku ya zama wani aiki da ba ya da tamka idan ana zancen tuwasun addini. Masu ƙoƙari kuma a fagen ibada da kaɗaita Allah Mahalicci, suka samu ja-makafi mai haske. Shi ya sa Sheikh Abdul'aziz bin Baz *Rahimahullah* ya ce: *"Wannan littafin yana da matuƙar amfani a ɓangaren aƙidah."*[4]

Saboda irin muhimmanci da tarin amfanin da waɗannan saƙonni suke da su, da tsananin buƙatar da musulmi suke da ita da su, ya sa malamai sanya ma shugabanni ƙaimi a kan wajabta ma talakawansu karatun su da fahimtar su. Tabbacin hakan shi ne abin da Sarkin Malamai Sheikh Abdurrahman ɗan Hasan *Rahimahullah* yake cewa: *"Ya zama wajibi a kan kowane shugaba ya umarci gaba ɗayan malamai da limamai su riƙa halartar wuraren da ake karantar da darussan addinin Musulunci. Ya kuma wajabta musu karatu da nazarin littafin* ***'Kitabuttauhid"*** *wanda Malaminmu ya wallafa, wanda yake*

---

[2] *Sharh Thalathat al-Usul,* na Sheikh bn Baz, shafi na 21.
[3] *Fatawa Ash-Shaikh Muhammad bn Ibrahim* 1/21.
[4] *Sharh Thalathat al-Usul,* na Sheikh bn Baz, shafi na 21.

*ƙunshe da hujjojin Alƙur'ani da Sunna yana bambance ƙarya da gaskiya. Tabbas! Wannan littafi, tattare da zamansa taƙaitacce, ya ƙunshi alheri mai tarin yawa sakamakon irin yadda Malamin ya ƙawata shi da hujjoji a kan kaɗaituwar Allah Subhanahu wa Ta'ala, irin waɗanda suke wadatar duk wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi ma gam da katar. Kamar kuma yadda a cikinsa ya kawo hujjoji da dalilai a kan Shirka irin wadda Allah Subhanahu wa Ta'ala ba ya gafartawa. Bayan haka, wajibi ne kuma a kan shugaba ya wajabta ma wannan rukuni na mutane, yin bitar waɗannan tuwasu na addini guda Uku bisa hujjoji da dalilai, da kuma ƙa'idoji guda huɗu".* [5]

Sarkin Malamai Muhammadu ɗan Ibrahim, Allah ya jiƙan sa, har takarda ya rubuta ma limamai yana umurtar su, su karantar da masallata waɗannan Shika-shikai guda Uku. A cikin wasiƙar ne yake cewa: *"Ya zama wajibi a kan ku ku karantar da mutane al'amurran addini da yi musu jarrabawa a kai kamar yadda aka kawo a taƙaice cikin littafin* ***"Shika-shikai Uku na Aƙidar Musulunci".*** *Domin wajibi ne a kan kowane limami ya isar da wannan ilimi ga masu halartar masallacinsa, ya kuma ware wani lokaci a kowace rana, wanda a cikinsa zai riƙa tambayar su al'amurran addininsu. Abin da ya shige musu duhu kuma a wannan ɓangare, sai ya sanar da su".* [6]

Saboda muhimmanci da amfanin wannan littafi ne, ni kuma na himmatu wajen yi ma sa wannan sharhi, wanda na ba shi suna: ***Tayseer Al-Wusul, Sharh Thalathat Al-Usul***[7]. Iyakar abin da na yi shi ne kusantowa da abin da mawallafin yake nufi, da madogararsa, tare da ƙara kafa hujjoji da maganganun magabatan wannan al'umma, waɗanda suka ƙare rayuwarsu wajen hidimar ilimin addini da bunƙasa shi musamman dai *Shaikhul-Islami* Ibnu Taimiyyah da almajirinsa Ibn Al- Kayyim. Allah ya jiƙan su.

A ƙarshe ina roƙon Allah Maɗaukakin Sarki ya sa wannan aiki nawa ya amfani jama'a, ya kuma zama wata taska da za mu amfana da ita gobe ƙiyama.

---

[5] *Ad-Durar-Assaniyya* 4/733

[6] *Fatawah Ash-Shaikh Muhammad Ibrahim* 2/277.

[7] Fassara wannan larabci a yadda yake da harshen Hausa ba zai bayar da cikakkiyar ma'anar da mawallafin yake nufi ba. Don haka muka raɗa ma littafin suna da harshen Hausa kamar haka: ***Tauhidi Ginshiƙin Musulunci*** *Sharhin Littafin* ***Al-Usul Ath-Thalatha "Shika-shikan Aƙidar Musulunci Guda Uku".*** Masu Fassara.

*Wa sallallahu ala Nabiyyina Muhammad, wa ala álihi wa sahbihi ajma'in.*

***Dr. Abdulmuhsin Ibn Muhammad Ibn Abdirrahman Ibn Kasim.***
Limamin Masallacin Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam,*
Kuma Alƙali a KotunYanki ta Birnin Madina Mai Alfarma.

*Bismillahir-Rahmanir-Rahim*

## *SAKONNI MASU MUHIMMANCI GA MAI KARATU*

### *SAKO NA ƊAYA*

### Mas'aloli Guda Huɗu

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ce:*

*"Da sunan Allah, Mai Rahama, Mai Jinƙai. Ka sani* [8] Allah *ya yi maka rahama, ya zama wajibi a kanmu, mu yi karatun wasu mas'aloli guda huɗu, ta farko : Ilimi. Shi ne sanin Allah, da sanin Annabinsa, da sanin Addinin Musulunci bisa dalilai. Ta biyu: Aikida, sai. Ta uku: Kira zuwa gare shi. Ta huɗu: Haƙuri a kan haɗuwa da cutarwa a cikinsa. Dalili kuma a kan haka shi ne, faɗar Allah Ta'ala:*

> *"Da Sunan Allah Mai rahama Mai Jinƙayi.*
> *Ina rantsuwa da zamani.*
> *Lalle ne mutum yana cikin hasara.*
> *Face waɗanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, kuma suka yi ma juna wasiyya da bin gaskiya, kuma suka yi ma juna wasiyya da yin haƙuri".*[9]

*Imamu Shafi'i Rahimahullah ya ce: Ko da Allah bai saukar da wata hujja ba, ga halittarsa, sai wannan Sura, to, ta ishe su.*

*Shi kuma Imamul-Buhari Rahimahullah a cikin ingantaccen littafinsa, ya ƙulla babi kamar haka: "Babin Ilimi Kafin Magana da Aiki". Ya ce: Dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ka sani ba*

[8] Da wannan kalima ce Malam ya buɗa waɗancan saƙonni guda uku, waɗanda suka share ma shika-shikan Aƙidar Musulunci fage.

[9] Suratul Asr: 1-4

***Ubangiji sai Allah, ka kuma nemi gafara a kan zunubanka. Ka ga a nan ya fara gabatar da ilimi kafin magana da aiki".***

Mawallafin, Allah ya jiƙan sa, ya buɗe wannan littafi nasa da *Bisimillah* yana mai neman taimakon Allah, da albarkar sunansa Maɗaukaki. Yana cewa, ina fara wannan aiki: ***"Da sunan Allah"*** domin koyi da abin da yake cikin littafinsa Maɗaukakin Sarki, da kuma kwaikwayon Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a cikin wasiƙunsa da sauran rubuce-rubucensa.

***"Allahu"*** babban suna ne na Maƙagin halitta, mai girma da ɗaukaka, wanda gaba ɗayan sunayensa suke biye da sawunsa a daraja da martaba. ***"Ar-Rahmanu"*** kuwa, suna ne daga cikin sunayensa *Subhanahu wa Ta'ala,* wanda ya keɓanta da shi shi kaɗai; babu wani abu a faɗin ƙasa komai daraja da ɗaukakarsa, da ya isa a kira shi da wannan suna balle ya karɓa. Ma'anarsa ta ƙunshi yadda Maɗaukakin Sarkin ya sifanta da mayalwaciyar rahama da cikakken tausayi ga dukkan bayinsa.

***"Ar-rahimu"*** shi kuma suna ne daga cikin sunayensa Allah. Sai dai ana iya kiran wani mahaluki da shi ya kuma karɓa abinsa gaba gaɗi. Sunan yana nuna kasantuwar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ma'abuci rahama mai saduwa da bayinsa. Bambancin ***Rahmanu** da **Rahimu*** shi ne, na farko na maganar yalwatar jinƙayinsa, na biyun kuma na alaƙantar da jinƙayin ga bayi. Bisa wannan ma'anar ne Shehun Malami Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa: *"Arrahmanu sifa ce ta jinƙayi da Allah Subhanahu wa Ta'ala ya sifaitu da ita. Arrahimu kuma na nuna saduwar jinƙayin nasa ga bayinsa".* [10]

Daga nan sai mawallafin ya ci gaba da cewa: ***"Ka sani…"*** Ba ya kamata ka jahilci al'amurran addininka. Saboda haka zan lissafo maka waɗansu muhimman mas'aloli da suka shafi shika-shikan aƙidar wannan addini, waɗanda kuma tabbas! Ya zama wajibi a kanka, ka kula da su matuƙar kulawa ta hanyar mayar da hankali a kan su. Kafin haka ina roƙar maka jinƙayin Allah *Subhanahu wa Ta'ala* da cewa: ***"Allah ya yi maka rahama".*** Da waɗannan kalmomi kuma, mawallafin yana fadanci ne ga Allah Maɗaukakin Sarki a

[10] *Bada'iul-Fawa'id* 1/24

madadin mai karatu; ya saukar da rahama da jinƙayinsa gare shi, wadda a sanadinta zai sami biyan buƙatunsa. Duk wani abu kuma da yake tsoro da fargaba a wayi gari ya tsere ma sa. Irin wannan salo kuwa na fatar alheri, da shi waɗanda suke kira zuwa ga shiriya suka saba. A haka sai a wayi gari bayan matsayinsu na masu karantarwa, sun kuma ɗauki wani matsayin na masu addu'a da roƙon Allah. Wannan salo kuwa ɗaya ne daga cikin nagartattun hanyoyin da mawallafin Allah *ya jiƙan sa* ya yi amfani da su, waɗanda suke nuna tsananin kulawarsa da al'amarin bayin Allah muminai, da kuma kyakkyawar manufar da yake da ita bisa ganin alherin ya zama hantsi a duniyar Musulunci.

***"Ko shakka babu, ya zama wajibi"*** irin wanda bai bar kowa ba: ***"A kanmu",*** masu hankali, maza da mata, yara da manya: ***"Mu yi karatu"*** domin mu san: ***"Wasu mas'aloli guda huɗu",*** waɗanda suka haɗa da:

1. Sanin Shiriya bisa hujjoji da dalilai; ba sanin shanu ba. Hakan kuwa ta haɗa da sanin Allah, da Manzonsa, da kuma addininsa na Musulunci. Mawallafin ya tsaya ga ambaton waɗannan al'amurra ne guda uku kawai saboda kasancewarsu Shika-shikan aƙidar Musulunci, waɗanda aƙida ba ta kammala sai da su. Musamman, da yake su ne abubuwan da za a tambaye shi su a cikin ƙabarinsa. To, da zarar kuwa bawa ya gane Ubangijinsa, da Annabinsa da addininsa bisa hujjoji da dalilai, addininsa ya gama cika da kammala.

Su kuwa sauran abubuwan da aiki da su yake wajaba a kan bawa, sanin su shi ma wajibi ne. Kamar Shika-shikan Imani, da na Shari'o'in Musulunci, da abubuwa na haramiya, da nisantarsu take wajaba, da wasu abubuwan kuma na ilimi daban-daban, waɗanda yake da buƙata da su, da makamantansu. Haka kuma ya wajaba ne ya san su a kan hujja domin ya ji daɗin bauta ma Ubangijinsa *ala basiratin,* ya kuma samu kusanci zuwa gare shi bisa hujja. A kan haka yake wajaba a kan sa tilas, ya tuntuɓi malamai don su waye ma sa kai a kan abin da bai sani ba. Imamu Ahmad *Rahimahullah* yana cewa: *"Ya zama wajibi a kan musulmi ya nemi ilimin da addininsa ba ya inganta sai da shi. Sai*

*aka tambaye shi kamar me? Sai ya karɓa da cewa: Irin abubuwan da bai kamata a ce musulmi ya jahilta ba, kamar Sallah da Azumi da masu kama da su".* [11]

Sauran abubuwan da waɗannan ba sukan zama farilla ne ta hanyar wakilci kamar ilimin Rabon Gado, da yadda ake Wankan Gawa da sauran su. Irin waɗannan da zarar wani rukuni na jama'a sun san shi, to, sun wadatar kuma sun ɗauke ma saura laifi.*

Ilimin: ***"Kuma"*** da nemansa yake wajaba a kanmu, ***"Shi ne sanin Allah", Subhanahu wa Ta'ala.*** Ma'ana, bawa ya san shi ta hanyar sanin abubuwan da ya sifaita kan sa da su *Subhanahu wa Ta'ala*, a cikin littafinsa, Mazonsa kuma *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya karantar, waɗanda suka haɗa da sunaye da siffofi da ayyukansa Maɗaukakin Sarki. Tabbas, gane ko waye Allah, ɗaya ne daga cikin muhimman abubuwa na wannan addini. Rashin sanin sa a irin wannan hanya, ko shakka babu, wani nau'i ne na wasa da addini. Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Haƙiƙa Allah Ta'ala ya zargi duk wanda bai ba shi girman da ya cancance shi ba, bai san shi yadda ya kamata a san shi ba, bai kuma ba shi siffofin da suka dace da shi ba".*[12]

Ai, ba yadda za a yi addinin mutum ya karɓa sunan addini matuƙar bai san Ubangijinsa sani na haƙiƙa ba. Saboda haka ne tushen wa'azin gaba ɗayan Manzanni – Amincin Allah ya tabbata a gare su - ya ginu a kan sanar da mutane Allah Maɗaukakin Sarki ta hanyar sunaye da siffofi da ayyukansa. A kan wannan kuma Malam Ibnl Kayyim yana cewa: *"Mabuɗin kira zuwa ga addinin Allah shi ne laƙanta ma duniya masaniya da Ubangiji Maɗaukakin Sarki".*[13] Saboda haka duk wanda yake kan hanyar neman yardar Allah Ta'ala, to, wajibi ne ya nemi sanin sa sani na haƙiƙa. Domin ba zai iya girmama shi ba fiye da yadda masaniya da shi take ƙunshe a cikin birnin zuciyarsa. Duk wanda kuwa ya san Allah Maɗaukakin Sarki irin haka, to, soyayya za ta shiga tsakanin sa da shi. Malam Ibn Al-Kayyim ya ƙara da cewa: *"Duk wanda ya san*

---

11 *Alfuru'u* na Ibn Muflih 1/525
12 *Madarij As-Salikin 2/495.*
13 *Madarij As-Salikin* 3/17.

*Allah ta hanyar sunaye da siffofi da ayyukansa, ko shakka babu soyayya za ta shiga tsakanin sa da shi".* [14] Kuma sanin Allah Maɗaukakin Sarki da bauta masa shi kaɗai, shi ne sanadin samun arzikin duniya da Lahira, kamar yadda Shehun Musulunci Ibnu Taimiyya *Rahimahullah* yake cewa: *"Duk wani jin daɗi da farin ciki da karsashi da annashawa, da ni'ima irin wadda yawun baki ba zai iya bayyanawa ba, sun tattara a cikin sanin Allah Subhanahu wa Ta'ala da kaɗaita shi, da kuma imani da shi".* [15]

Wani ilimin: ***"Kuma"*** da nemansa yake wajaba a kan kowane mukallafi, shi ne, ***"Sanin Annabinsa"*** Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, saboda shi ne jekada tsakaninmu da Allah, wanda ya isar da saƙonsa zuwa gare mu. Saninsa kuma ba zai kammala ba, a ma'auni na wajabci, sai an ƙanƙame tare da aiki da duk abin da ya zo da shi daga wurin Allah, na addini da shiriya ta gaskiya.

Wani abu kuma da yake wajaba a kan kowane mukallafi, shi ne: ***"Sanin Addinin Musulunci bisa dalilai"*** waɗanda suka zo a cikin Alƙur'ani da Sunna, saboda shi ne kawai, addinin da Allah Maɗaukakin Sarki ya wajabta mana bauta masa ta hanyarsa. Babu kuma wata hanya ta shiga Aljanna face ta sanin wannan addini tare da biyarsa sau da ƙafa. Jahiltar sa da yi masa riƙon sakainar kashi shi yake kai mutum Wuta. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Cika da kamalar mutum sun dogara ne a kan waɗansu tuwasu guda biyu: bambancewa tsakanin gaskiya da ƙarya, da fifita ta a kanta. Ba wani abu ne ya fifita waɗansu halittu a kan waɗansu ba a wurin Allah a duniya da Lahira illa bambancin da suke da shi a tsakaninsu a cikin waɗannan abubuwa guda biyu".* [16]

Hasali ma, nauyin masaniyar da bawa yake da ita, da Allah Maɗaukakin Sarki, da Annabinsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, da kuma addinin Musulunci, su ne farkon abin da za a tambaye shi a kai a cikin ƙabarinsa. Tabbacin wannan shi ne abin da ya zo a cikin hadisin Bara'u ɗan Azib *Radhiyallahu Anhu,* daga

[14] *Assawa'iƙ Al-Mursalah 1/151*
[15] *Fatawa Al-Islam 27/31.*
[16] *Al-Jawab Al-Káfí* shafi na 99.

Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* A cikinsa yake cewa: *"Sai Mala'iku biyu su je ma mumini, su zauna, su ce masa: Wa ye Ubangijinka? Sai ya karɓa da cewa: Ubangijina shi ne Allah. Sai su ce masa: Mene ne addininka? Sai ya karɓa da cewa: Addinina shi ne Musulunci. Sai kuma su sake ce masa: To, mene ne matsayin bawan Allah ɗin nan da aka aiko zuwa gare ku? Sai ya ƙara karɓawa da cewa: Manzo ne na Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam".* Ahmad ne ya riwaito shi.[17]

Duk wanda kuwa Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya yi wa gamon katarin fahimtar waɗannan shika-shikai tare da hujjoji da dalilansu, to, ya fi kowa cancanta da iya karɓa waɗannan tambayoyi na waɗannan malakilu guda biyu a cikin ƙabarinsa. Wasu mutane kuwa, ta tabbata a cikin wannan hadisi cewa, bakin kawai za su saki, suna iina, suna faɗin: *"Ban sani ba".* [18]

Sai dai sauran mutane, fararen hula a duniyar ilimi, idan sun yi imani da kaɗaituwar Allah Maɗaukakin Sarki, da zaman duk wani abin da ake bauta wanda ba shi ba, abin banza, to, sun tabbata musulmi ko ba za su iya kare hakan da hujjoji da dalilai ba. Malam Abdullahi ɗan Abdurrahmani Abá Biɗin *Rahimahullah* yana cewa: *"Farilla ne a kan kowane musulmi ya nemi ilimin Tauhidi da Rukunan Musulunci bisa dalilai da hujjoji; dogara da wani a wannan fanni ba ya halatta. Sai dai farar hula, wanda bai san waɗannan hujjoji da dalilai ba, amma ya ƙudurce zaman Ubangiji Allah Makaɗaici, ya yi imani da Manzancin Annabi Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam, da tashi bayan mutuwa, da Aljanna da Wuta. Ya kuma yi imani da kasancewar gaba ɗayan ayyukan Shirka, waɗanda ake aiwatarwa a irin waɗannan wurare, duk, ɓata ne da ɓarna. Da zarar dai ya yi imani da haka, imani maras tazgaro, to, ya zama musulmi, ko da kuwa ba ya iya tabbatar da hakan ta hanyar hujjoji da dalilai. Ai daman mafi yawan fararen hula a duniyar Musulunci ko an laƙƙana musu waɗannan dalilai da hujjoji, ba za su iya fahimtar ma'anarsu ba a mafi yawan lokuta".* [19]*

---

[17] *Al-Musnad,* Hadisi na (17558) 4/278 daga Bara'u ɗan Azib *Radhiyallahu Anhu.*
[18] *Al-Musnad,* Hadisi na (17558) 4/278 daga Barra'u ɗan Azib *Radhiyallahu Anhu.*
[19] *Ad-Durar Ath-Thasaniyya* 4/339

Tabbas babu wani aiki da ya kama ƙafar neman ilimi. Imamu Ahmad *Rahimahullah* yana cewa: *"Babu wani abu da yake iya kafaɗa da kafaɗa da ilimi".* [20] Shi kuma Ibn Al-Kayyim ga abin da yake cewa: *"Ilimin Shari'a shi ne ne rayuwar zukata, hasken idanu, sanyin ƙirji, mahutar hankula, warwarar rayuka, wurin ɗebe kewar makaɗaita, jamakafin masu ɗimuwa. Shi ne ma'aunin da ake auna ayyuka da zantuka da halaye da shi. Sai da shi ne ake gane Allah Subhanahu wa Ta'ala har a bauta masa, a tuna shi, a gode masa, a kuma girmama shi. Da ilimi ne masu ƙwazo a fagen bauta suka samu isa fadar Allah Subhanahu wa Ta'ala. Ta hanyarsa ne kuma duk wanda ya kai wane a wannan bigire, ya kai. Masu guri da fata shiga wannan sahu kuma, ta ƙofar ilimi ne suka samu shiga. Kazalika, ta hanyarsa ne ake gane Shari'o'i da hukunce-hukunce, a iya bambancewa tsakanin halas da haram. Sai da shi ne ake iya sadar da zumunci. Shi ne liman kuma jagora, aiki kuwa mamu kuma mabiyi. Duk wanda ba ya cikin dangi kuma, idan yana da ilimi ya huta. Shi ne abokin magana idan an kaɗaita, mai ɗebe kewa a yayin da aka shiga tasku. Shi ne ruwan kashe gobarar shubuha. Duk wanda ya mallaki taskarsa kuma, ba ya talauci har abada".* [21]

Amfanin ilimi yana gaba da na abinci kamar yadda Imamu Ahmad *Rahimahullah* yake cewa: *"Buƙatar da mutane suke da ita da ilimi ta fi wadda suke da ita da abin ci da abin sha. Dalili kuwa shi ne, iyakar buƙatar da mutum yake da ita, da abin ci da abin sha, sau ɗaya ne ko biyu a wuni. Shi kuwa ilimi yana da buƙata da shi adadin numfashinsa na wuni, kullum".*[22] Kai daraja da matsayin neman ilimi, sun ma yi wa na jihadi fintinkau, kamar yadda aka riwaito daga bakin Ibnu Abbas *Radhiyallahu Anhu,* cewa: *"Kwana da tashi a cikin hidimar neman ilimi ta fi girma a wurin Allah bisa jihadi wajen ɗaukaka kalmar Allah*".[23] Haka kuma Imamu Ahmad *Rahimahullah* yana cewa: *"Neman ilimi da karantar da shi, ya fi lada bisa ga jihadi da duk wani abu wanda ba shi*

---

[20] *Al'-Adábu Ash-Shar'iyya* na Ibn Muflih 2/45.
[21] *Madarij As-Salikin* 2/467
[22] *Madarij As-Salikin* 2/467
[23] *Al-Firdaus bi Ma'asur Al-Khiɗab,* Hadisi na (4303) 3/109

*ba".* [24] Shi kuma Imamu Abu Hanifa *Rahimahullah* cewa ya yi: *"Mafi girman ibada ta taɗauwu'i ita ce neman ilimi da bayar da shi".* [25] A yayin da shi kuma Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa: *"Matsayin jinin shahidai a wurin Allah bai wuce na tauwadar da malamai ke rubutun ilimi da ita ba".* [26]

Ba wannan kawai ba, ilimi shi ne mafi girman abin da ake iya raya lokuta a ƙawata su da shi. Babu kuma wani abin da numfashin mutum zai yi gudunmawa da shi a ɗakin duniya, ko jinin ƙoƙon zuciya ya yi baiwa da shi, kamar sa. Ga abin da Imamun-Nawawi *Rahimahullah*[27] yake cewa a wannan ma'ana: *"Magabata sun haɗu a kan cewa, shagaltuwa da neman ilimi ya fi shagaltuwa da sallolin nafila, da azumi, da tasbihi, da matara kama da su daga cikin ibadojin da ake yi da gangar jiki, lada".* Shi kuma Sayyidi Ali ɗan Abi Ɗalib *Radhiyallahu Anhu* ya ce:

*Ka rayu a kan neman ilimi kar ka nemi canjinsa,*
*Mutane matattu ne; ma'abuta ilimi kuwa rayayyu.*

Haka kuma babu wata nasiha da malamai suke cika kunnuwan duniya da ita, tsawon zamuna, kamar nema ilimi. Misalin wannan shi ne, Ibnl-Jauzi *Rahimahullah* da yake cewa: *"Ban gushe ba ina kwaɗaitar da mutane a kan neman ilimi saboda matsayin da yake da shi na hasken da ake gane makamar rayuwa duniya da Lahira da shi".* [28]

Babu wani wuri inda arziki ya yi sansani sai cikin ilimi kamar yadda Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa: *"Gaba ɗayan abin da ake cewa arziki ya tattara ne a cikin ilimi da abin da yake haifarwa. Sai dai ba kowa ne ke iya samun sa ba sai wanda Allah ya yi ma gamon katar; babu mai iya hana abin da ya bayar, kamar yadda babu mai iya bayar da abin da ya hana. Ba wani abu ne ya hana mafi yawan mutane fantsama a cikin gulbin neman ilimi ba illa*

---

[24] *Al-Insaf* na Mawardi 2/162
[25] *Minhaj As-Sunnah* 6/75.
[26] *Al-Furusiyyah* na Ibn Al-Kayyim shafi na 157
[27] *Al-Majmu'* 4/6.
[28] *Ahkam An-Nisa',* na Ibnl-Jauzi shafi na 7.

*wahalar da ke ciki da wajensa, da ɗacin zangunan mabuɗansa, da irin yadda sai gumi ya zuba a goshi kafin a same shi. Tabbas! Ko ana samun sa sai an kai ruwa rana".* [29] Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, da kan sa sai da Allah ya umarce shi da dagewa bisa neman ilimi, inda yake cewa masa: *"Ka ce: Ya Ubangiji! Ka ƙara mani ilimi".* Duk mahalukin da Allah Maɗaukakin Sarki ke son sa da alheri, to, sai ya sanar da shi makamar addininsa. Tabbacin wannan kuwa shi ne faɗar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: *"Duk wanda Allah yake so da alheri yana sanar da shi makamar addininsa".* [30]

Duk wanda ya san cewa, duniya gida ce na gwagwarmayar neman darajoji da manyan abubuwa, duk kuma lokacin da aƙaluman matsayin mutum a fagen ilimi da aiki da shi suka ɗaukaka a duniya, sai matsayinsa a gidan Lahira ya ƙara ɗaukaka. Duk wanda ya san haka, kamata ya yi a taras da shi mai kula da lokaci; ba zai ɓata ko minti nasa ba. A maimakon haka zai zama mai matsanancin haƙuri da kowace irin jarabawa da talauci, har a wayi gari ya samu biyan buƙata; hutu ba ya samuwa ta hanyar hutu. Ga abin da Fudhailu yake cewa:

*Ka yi wa kanka tanadi da gaske, kafin mutuwa,*
*Tabbas! Riba da hasara na bayyana ne idan an motsa.*

Kafin kuma ilimi ya samu, lalle ne mutum ya kyautata niyya a cikin nemansa. Idan kuma ya samu, ya tabbata ya yi aiki da shi, ya kuma kiyaye alfarmarsa, domin da bai neme shi don Allah ba, to, babu abin da ya yi illa ɓata lokaci da hasarar sakamako. Wanda kuma aiki da ilimin ne ya kasa tabbatar wa, to, zai zama babbar hujja a kan sa ta azaba.

Wannan ilimi kuma da muke ta magana, muna nufin ilimin Shari'a ne, irin wanda yake zama sanadin sanin abubuwan da suka wajaba a kan *mukallafi*, na addininsa, waɗanda rayuwarsa ba za ta inganta ba sai da su, saboda matsayin da suke da shi na zama dalilin jin tsoron Allah *Subhanahu wa Ta'ala.*

[29] *Miftah Dar As-Sa'adah* 1/111.
[30] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (181) 1/24, *Sahih Muslim,* Hadisi na (1037) 2/717 daga Mu'awiyya *Radhiyallahu Anhu.*

Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"Malamai ne kaɗai daga cikin bayinsa suke tsoron Allah".* A kan wannan ma'ana ne Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa: *"Babu yadda za a yi a bauta ma Allah shi kaɗai, a kuma gode masa, a yaba a kuma girmama shi, sai da ilimi. Ba za a iya gane fifikon Musulunci a kan wani addini da ba shi ba, sai da ilimi. Ba za a iya sanin halas da haram ba sai da ilimi. Ba kuma za a iya fifita Musulunci a kan sauran abubuwa ba sai da ilimi".* [31]

Kai! Ba fa yadda za a yi, a iya samun fada a wurin Allah Maɗaukakin Sarki, ko a samu shiga Aljanna, sai an tsaya a kan Littafin Allah da Sunnar Manzo. Nagarta kuwa ga bawa, har abada ba za ta taɓa samuwa ba a duniya da Lahira, matuƙar ba gane Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya yi ba. Idan kuma aka wayi gari jahilci da rafkana sakamakon yin biris da sha'anin ilimi, sun yi masa ƙawanya, to, babu abin da zai sauka gare shi sai gushewar ni'ima da saukar azaba. Bisa haka ne Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa: *"Ba wani abu zai sa a wayi gari duniya da tarwatse ba, illa jahilci. Rayuwarta kuma ba za ta taɓa tabbata ba, sai da ilimi. Saboda haka ake ganin da zarar ilimi ya samu ga gari ko unguwa, sai a samu ƙarancin sharri ga mutanensu. Da zarar kuwa an neme shi an rasa, sai sharri da fasadi su bayyana".* [32] Saboda haka bai kamata ga duk mai hankali ba, ya ɓata lokutan rayuwarsa da awannin zamaninsa ba, a cikin abin da ba neman ilimi mai amfani ba.*

Mas'ala ***"Ta biyu",*** wadda saninta yake wajaba a kanmu, ita ce: ***"Aiki da Ilimin".*** Yin haka wajibi ne saboda babu wani amfani ga ilimin da ba a aiki da shi. Hasali ma wata rana za a neme shi a rasa; ya yi ko sama ko ƙasa. Wasu daga cikin magabatan wannan al'umma sun bayar da shaida a kan haka da cewa: *"Duk hadisin da muke son hardacewa sai mu tsare yin aiki da shi".* [33] Tabbas! Duk wanda ya tsare aiki da abin da ya sani, Allah zai tsare masa iliminsa ya kuma buɗe masa ƙofofin samun wasu ilmuka da bai sani ba. Haka kuma aiki da abin da aka sani yana taimakawa ga ƙaruwar imani. Tabbacin

[31] *Miftah Dar As-Sa'adah* 1/314
[32] *I'ilam Al-Muwaƙƙi'in* 2/752.
[33] *Iƙtidha' Al-Ilm Al-Amali* na Khaɗib Al-Bagdadi shafi na 90.

wannan shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Kuma waɗanda suka shiriya, (Allah) zai ƙara musu shiriya ya kuma azurta su da taƙawa".* Imamush-Shaukani ya ce: *"Wannan aya tana nufin Allah Subhanahu wa Ta'ala zai ƙara musu imani, da ilimi, da basira a cikin addini".* [34] Duk wanda kuwa ya yi arzikin samun ilimi da ikon aiki da shi, to, ya tabbata mai arziki kamar yadda Imamun-Nawawi *Rahimahullah* yake cewa: *"Hikima ita ce ilimi, wanda ya haɗa sanin Allah, da kaifin basira, da kamun kai, da tabbatar da gaskiya domin aiki da ita, da kame kai daga kishiyarta. Ba kowa ne mai hikima ba, illa wanda ya tabbatar da waɗannan abubuwa".* [35]

Idan aka wayi gari mutum yana aiki da iliminsa, ta hanyar tsare alfarmar duk abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya farlanta masa. Ya tsare nafilfili, kamar sallolin sunnoni, da Shafa'i da Wutiri, da karatun Alƙur'ani, da Istigfari a kowace safiya, ta hanyar keɓance wani lokaci ya zauna a cikin masallaci yana zikiri kullum, musamman bayan sallar safe har zuwa hudowar rana. Bayan haka, ya kuma nisanci majalisun da babu abin da ake yi cikinsu sai wasanni da sharholiya. Ya ƙaurace ma duk wani mazauni da ya san babu masu cika shi, sai maciya naman mutane da miyagun maganganu. Ya kuma kiyaye harshensa daga abin duk da bai shafe shi ba. Duk wanda ya zama haka, to, ana lissafa shi a cikin masu aiki da iliminsu. Shi kuwa duk wanda ya kasa aiki da abin da ya sani, to, ba kuwa yadda za a yi ya ɗanɗani zaƙin ilimi balle na jin tsoron Allah. Ba kuma da wani ɓata lokaci ba za a wayi gari Allah Maɗaukakin Sarki ya shafe duk abin da ya sani, ya mayar da shi cikin sahun jahilai. Malam Fudhailu ɗan Iyadh yana cewa: *"Komai ilimin malami, ba ya da bambanci da jahili, matuƙar ba ya aiki da iliminsa. Da zarar ya fara aiki da shi kuwa, to, a lokacin ne ya zama malami".*[36]

Wanda duk ba ya aiki da iliminsa, to, ranar ƙiyama zai zama hasara gare shi. Tabbacin hakan kuwa shi ne faɗar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: *"Ba za a bari bawa ya ɗaga ƙafarsa ba a ranar Kiyama, sai an tambaye*

---

[34] *Fath Al- Kadir* 5/35
[35] Sharhin Imam Nawawi a Kan Sahihu Muslim 2/33.
[36] *Tarikh Madinat Dimashƙ* na Ibn Asakir 48/428.

*shi a kan shekarunsa; ya ya ƙaras da su, da iliminsa; aikin me ya yi da shi, da dukiyarsa; ya ya same ta, ya kuma ya kashe ta, da gangar jikinsa; a kan wane aiki ya kaɗar da ita".* Tirmidhi ne ya riwaito shi.[37]

Wata tabbatacciyar magana kuma ita ce, sharrin wanda ba ya aiki da iliminsa ya fi na jahili tuburan. Irin wannan mahaluki kuwa yana ɗaya daga cikin mutane uku, waɗanda za a yi makamashin Wuta da su ranar Kiyama.[38] A kan wannan ma'ana ne Ibn Raslan yake cewa:

*Duk malamin da bai yi aiki da iliminsa ba,*

*Za a azabtar da shi kafin masu bautar gumaka.* [39]

Duk kuwa wanda ya san wata mas'ala ƙwaya ɗaya daga cikin mas'alolin addini, to, ya zama malaminta, za a kuma kama shi da hujja a kanta ko da ba ya cikin jerin sunayen malamai sha fannona. Ga abin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake cewa a kan wannan: *"Alƙur'ani yana zama hujja ga mutum ko ya zama hujja bisa kan sa".* Muslim ne ya riwaito shi.[40] Shi kuwa duk wanda ya yi aiki bisa jahilci, to, da shi da Nasara ba bambanci. A yayin da shi kuwa wanda ya sani ya ƙi aiki da sanin, yake kankankan da Yahudu. Malami na sosai shi ne wanda ya sani, ya kuma yi aiki da saninsa, ko da kuwa ilimin nasa bai taka kara balle ya karya ba. Babu wani abin da Shari'a ke nufi a cikin umurni da neman ilimi, face aiki da shi. ba kuwa domin komai ba, sai don hakan na haifar da tsoron Allah Mahalicci da samun kusanci gare shi.*

---

[37] *Sunan At-Tirmidhi* Hadisi na (2417) daga Abi Barzata Al-aslami *Radhiyallahu Anhu.* Ya kuma ce: Wannan hadisi ne kyakkyawa kuma inganyacce.

[38] Waɗannan mutane uku su ne: Mayaƙi, da Mai neman ilimi, da Mai ciyar da dukiyarsa, waɗanda ba yardar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* suke nema ba; mutane kawai suke so su yabe su. haka wannan magana ta zo a cikin hadisin da Muslimu ya riwaito a cikin ingantaccen littafinsa, Hadisi na (1905) 3/1513 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

[39] *Az-Zubad* na Ibnu Raslan shafi na1.

[40] *Sahih Muslim,* Hadisi na (223) daga Abu Malik Al-Ash'ari *Radhiyallahu Anhu,* ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce: *"Tsarki shi ne rabin imani, faɗin Alhamdu lillahi na cika ma'aunin aiki, cewa Subhanallahi Walhamdu lillahi na cika abin da ke tsakanin sama da ƙasa. Sallah kuma haske ce, sadaƙa kuma hujja ce, haƙuri kuma haske ne. Shi kuma Alƙur'ani hujja ce gare ka ko bisa kanka. Dukan mutane suna wayuwar gari, wani ya sayar da rayuwarsa, wani kuma ya 'yantar da ita, ko ya halakar da ita."*

Mas'ala ***"Ta Uku"*** da neman saninta yake wajaba a kanmu, ita ce ***"Kira zuwa ga tafarkin Allah"*** Maɗaukakin Sarki tare da karantar da mutane, da shiryar da su, da kuma yi musu adalci.

Kira zuwa ga tafarkin Allah *Subhanahu wa Ta'ala,* ɗaya ne daga cikin mafi girman ayyuka masu girma da ɗaukaka, kasancewar ta hanyar da gaba ɗayan Manzanni suka rayu a kai, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki yake ba mu labari cewa:

*"Ka ce: Wannan ita ce hanyata. Ina kira zuwa ga Allah ala basiratin, ni da wanda ya rufa mani baya. Tsarki kuma ya tabbata ga Allah, ban kuma zama daga cikin mushrikai ba".*

Shaihin Malami Ibnu Kasir ya yi sharhi a kan wannan aya da cewa, *"Allah Maɗaukakin Sarki yana gaya wa Manzonsa ne Sallallahu Alaihi wa Sallam ya sanar da mutane da aljannu cewa, wannan tafarki da yake a kan sa, na kira zuwa ga Kalmar shahada ita ce hanyarsa. Yana kuma wannan aiki ne bisa cikakken tsari, da yaƙini, akan hujja. Duk kuma wanda ya yi imani da shi, to, za a same shi, shi ma, yana kira zuwa ga abin da, shi Manzon, yake kira zuwa gare shi. Shi ma kuma ba zai kasa zama ala basiratin ba, da sakankancewa da kuma hujja irin ta hankali da Shari'a".* [41]

Bisa wannan dalili, maganar da za ta fito daga bakin malami mai kira zuwa ga Allah ita ce mafi kyawon zance da tsarki a wurin Allah. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*:

*"Anya akwai mafi kyawon zance fiye da na wanda ya yi kira zuwa ga Allah, ya kuma yi aiki na ƙwarai, ya kuma ce, lalle ni ina daga cikin musulmi?".*

Saboda haka duk musulmi na ƙwarai, wanda Allah Maɗaukaki ya yi ma sa muwafaƙar gane Ubangijinsa, da Annabinsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, da addininsa, da kyau. To, babu shakka za a same shi yana ƙoƙarin gayyato wasu mutane zuwa ga wannan tafarki. Ga abin da Ibnu Taimiyya *Rahimahullah* yake cewa game da haka: *"Babu wata manufa a cikin kiran da Annabawa suka yi, Kai! Halitta gaba ɗayanta, Allah bai samar da ita ba, ya saukar da littattafai, ya*

[41] *Tafsir Al-Kur'an Al-Azim,* na Ibn Kathir 2/766.

*kuma aiko Manzanni, sai kawai domin a bauta masa shi kaɗai, wato kiran gaba ɗayan halittu zuwa ga mahaliccinsu".*[42]

Ita kuwa da'awah, mafi girma da ɗaukaka daga cikin matakanta, shi ne kira zuwa ga kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki, wato *Tauhidi,* da kore Shirka. Dalili kuwa shi ne, babu wani Manzo da Allah ya aiko zuwa ga mutane face ya kira su zuwa ga yi masa ɗa'a da kaɗaita shi da bauta. A lokaci ɗaya kuma yana yi musu kashedi da Shirka da duk wani abu da yake da alaƙa da ita, babba ko ƙarami. To, bayan haka sai mai da'awah ya ci gaba da nuna ma mutane sauran ayyukan ibada, ɗaya bayan ɗaya, ta hanyar farawa da mafifici, sai mai bi masa daga cikin shari'oin Musulunci; haka-haka. Tare da haka kuma yana yi yana saka hikima a cikin duk wata kalma da zai furta, da wani aiki da zai yi, saboda koyi da abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya ce:

*"Ka yi kira zuwa ga tafarkin Ubangijinka a cikin hikima da wa'azi kyakkyawa. Ka kuma yi jayayya da su da abin da yake shi ne mafi kyau".*

Duk kuwa wanda ya zama ba shi da aiki sai kira zuwa ga tafarkin Allah Maɗaukakin Sarki, a cikin kyakkyawar niyya, da yi bisa koyarwar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, to, yana daga cikin mataimakan Manzon Allah na gaskiya. Bisa wannan ne Malam Ibnu Taimiyya *Rahimahullah* yake cewa: *"Magada Manzanni kuma halifofin Annabawa, na gaskiya, su ne waɗanda suka tsaya a kan tafarkin raya addini a baki da aikace ta hanyar kira zuwa ga tafarkin, na Allah da Manzo. Irin waɗannan mutane su ne mabiya Manzo na gaskiya. Misalinsu kamar wani nagartaccen sashe na ƙasa ne mai albarka,wanda mamakon ruwan sama ya samu gurbi a cikinta, aka wayi gari ta fitar da ciyawa mai tarin yawa; ta yi albarka a karan kanta, mutane kuma suka amfana da ita".* [43]

Wani abin ban sha'awa kuma shi ne, irin yadda babu wani lokaci da ladar mai da'awa za ta yanke matuƙar iskan duniya na kaɗawa. Dubi abin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake cewa: *Duk wanda ya yi kira zuwa ga shiriya, zai samu lada irin ta wanda ya yi aiki da kiransa, ba tare da su, tasu*

[42] *Al-Fatawa* 2/464.
[43] *Maj'mu' Al-Fatawa* 4/92.

*ladar ta samu raguwa ba. Haka duk wanda ya yi kira zuwa ga ɓata, zai samu zunubi irin na wanda duk ya yi aiki da kiransa, ba tare da su, nasu zunubin ya samu wani tasgaro ba".* Muslim ne ya riwaito shi.[44]

Ka ga a haka kenan babu wani abu na ƙawace-ƙawacen duniya, wanda matsayinsa ya kama ƙafar gwagwarmaya a cikin ƙoƙarin shiryar da halitta. Tabbacin wannan shi ne, abin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake gaya ma Sayyidi Ali ɗan Abu Ɗalib *Radhiyallahu Anhu,* cewa: *"Haƙiƙa, Allah ya shiryar da mutum ɗaya ta hannunka, ya fi alheri gare ka bisa ga garken jajayen raƙuma".*[45]

Saboda haka ne, Annabawa ba su da wata manufa, illa shiryar da mutane zuwa ga gane Ubangiji Allah Maɗaukakin Sarki kamar yadda ya kamata, da kuma bauta masa, a matsayinsu na waɗansu abubuwa guda biyu, da suke zama sanadiyyar samun arzikin duniya da Lahira. Shehun Musulunci Ibnu Taimiyya *Rahimahullah* yana cewa: *"Malamai Magada Annabawa, su ke ɗauke da nauyin bayanin abin da Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam, ya zo da shi, da mayar da martani a kan abin da ya saɓa masa".* [46] Kuma ai buƙatar da mutane suke da ita, da da'awah domin gane addini, ta fi wadda suke da ita, da abin ci, da abin sha. Harwayau, Ibnu Taimiyya na cewa: *"Tabbas rayukanmu sun fi buƙatuwa zuwa ga sanin abin da Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam da mabiyansa suka zo da shi, a kan abin ci, da na sha. Dalili kuwa shi ne idan an rasa abin ci da sha, mutuwar tsaye kawai za a yi a nan duniya. Rashin sanin addini kuwa azaba madawwamiya yake haifarwa".* [47]

Ita kuma Da'awan nan da muke magana tana da fannona da dama. Karantarwa, da yi ma wanda ya kama daji hannunka mai sanda, da faɗakar da gafalalle, da yawaita nasiha da gargaɗi da tunatarwa, da nuni zuwa ga aikata alheri. Duk waɗannan abubuwa Rukunai ne na kira zuwa ga addinin Allah. Ga abin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ke cewa a kan haka: *"Duk wanda*

---

[44] *Sahihu Muslim,* 4/2060, Hadisi na (2674) daga abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

[45] *Sahih Al-Bukhari,* 3/1077, Hadisi na (2783) da *Sahih Muslim*, 4/1872, Hadisi na (2406). Daga Sahlu ɗan Sa'ad *Radhiyallahu Anhu.*

[46] *Al-Fatawa* 27/316.

[47] *Al-Fatawa* 1/5.

*ya zama sanadin wani alheri, to, zai sami lada daidai da ta wanda ya yi shi".* [48] Duk kuwa wanda ya yi watsi da wannan aiki na shiryarwa da karantar da mutane al'amurran addininsu, to, ya gitta kan sa ga haɗarin azaba da narko. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*:

*"Haƙiƙa, waɗanda suke ɓoye abin da muka saukar na hujjoji bayyanannu da shiriya, bayan Allah ya bayyana su ga mutane a cikin littafi. Waɗannan, Allah yana la'antarsu, masu la'anta kuma suna la'antarsu. Sai kawai waɗanda suka tuba, suka gyara. To, waɗannan, ina karɓar tubarsu, kuma ni mai yawan karɓar tuba ne, mai jinƙayi".*

Ibn Al- Mubarak *Rahimahullah* yana cewa: *"Duk wanda ya yi rowar ilimi, Allah zai jarrabe shi da ɗayan abubuwa guda uku: ko dai ya yi saurin mutuwa, ilimin ya yi ko sama ko ƙasa, ko a wayi gari shi da jahili ba bambanci; ya mance komai, ko kuma duk inda masu mulki suka yi ya bi su".* [49]

Saboda haka ya zama wajibi a kan kowane musulmi ya zama mai kira zuwa ga tafarkin Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, da nasiha ga mai raggon kaya, da gwagwarmayar gyara halin zaman jama'a, kowa gwargwadon halinsa da matsayinsa.*

## 4. Haƙuri

Mas'ala ***"Ta Hudu"*** daga cikin mas'alolin da neman sani da aiki da shi, yake wajabta a kanmu ita ce ***"Haƙuri da Cuta a kan wannan tafarki"*** na Allah Maɗaukakin Sarki.

Hakan ya zama wajibi ne saboda farfajiyar da masu Da'awah ke ƙoƙarin cin nasara a kan ta, ita ce ƙirazan mutane. Wannan sashe na halitta kuwa daban-daban yake, kamar yadda fuskoki da zahirinsu, na mutanen, suke daban-daban. Saboda haka duk wanda ya zaɓi riƙo da addini, da kiran mutane zuwa gare shi, to, kamar ya ɗauki birnin Kano ne ba gammo, ya kuma saka takalmin da Annabawa suka bari, na kira zuwa ga tafarkin Allah Ta'ala. A wannan

---

[48] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (1093) 3/1506 daga Abi Mas'ud al-Ansari *Radhiyallahu Anhu.*

[49] *Almadkhal Ila As-Sunan Al-Kubra,* na Baihaƙi, Hadisi na (587) shafi na 350.

matsayi kuwa na shiga tsakanin mutane da ƙudurce-ƙudurcen zukatansu, munana, babu mamaki su cutata masa. Saboda haka, lalle ne ya sari sandar haƙuri da neman lada. Saurari abin da Imamu Malik *Rahimahullah* yake cewa a kan haka: *"Kar ku yi murna ga wanda bai gamu da wani bala'i ba a kan wannan tafarki".* [50]

Shi kuwa haƙuri yana nufin jajircewa da jurewar zuciya a lokacin da mai ita ya haɗu da matsaloli. To, shi kuwa addini, cikinsa da waje, yana da buƙatar sanadarin haƙuri. Asalin kalmar ta haƙuri, a harshen Larabci shi ne, turkewa da dabaibayewa. Saboda haka, kenan haƙuri yana nufin turke rayuwa da dabaibaye ta, da hana ta shiga da'irar girgiza da tsoro da fargaba. Shi kuwa harshe, a hana shi raki da yakwaci, da jinini. A yayin da gaɓoɓi kuwa, ake hana su yin laifi, kamar mutum ya ɗaga hannu ya mari fuska ko ya tsage wuyan riga, da matara kama da waɗannan. Wannan fa muna maganar ma'anar haƙuri kenan a harshen larabci. To, a Shari'ance idan aka ce haƙuri, ana nufin wata ɗabi'a ce, maɗaukakiya, wadda take hana ka aikata duk wani abu da bai dace ba. Malam Ibnu Taimiyya *Rahimahullah* na cewa: *"Ba yadda za a iya gane gaskiya sai ta hanyar ilimi. Ita kuwa shiriya sai da haƙuri take samuwa".* [51] Da haƙurin nan kuma ne, da yaƙini, abubuwa biyu, waɗanda su ne ginshiƙan tawakkali, ake samun shugabanci a duniyar addini". Bisa wannan ma'ana ne, har wa yau, Malam Ibnu Taimiyya *Rahimahullah* ke cewa: *"Duk wanda aka azurta shi da haƙuri da yaƙini, to, Allah ya yi nufin sa shi shugaba a duniyar addini".* [52]

Saboda haka, kirana gare ka, ya kai ɗan'uwa musulmi! Shi ne, kar ka fasa shiga sahun masu kira zuwa ga addinin Allah ko ka samu kanka cikin sahun waɗanda aka jarraba da wani abu. Ai, haɗuwa da matsaloli bisa wannan tafarki, abu ne da da aka saba da shi a tarihin ɗan Adam. Saurari abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ke gaya ma Annabinsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam*:

*"Haƙiƙa an ƙaryata Manzanni tun kafinka, amma, suka yi haƙuri a kan ƙaryata su da aka yi, aka kuma cutar da su, har taimakonmu ya je musu".*

---

[50] *Al-Fatawa* 4/50.
[51] *Al-Fatawa* 10/40.
[52] *Al-Fatawa* 6/215.

Manzanni da kake ji, babu irin cutarwar da ba su haɗu da ita ba; ta magana da ta aiki. Dubi abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake labarta mana:

*"Kuma lalle ne, haƙiƙa, an yi izgili da Manzanni a gabaninka. Sai waɗanda suka yi izgilin, abin da suka kasance suna izgili da shi, ya faɗa musu".*

Kai daga cikin Manzannin nan ma akwai waɗanda suka rasa rayuwarsu, kamar yadda Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ke cewa:

> *"Yanzu za a zauna duk lokacin da wani Manzo ya je muku da abin da rayukanku ba su sha'awa, sai ku kangare, sashensu ku ƙaryata, wani sashe kuma kuna kashewa".*

Ashe babu mamaki don abin da ya samu Manzannin nan, ya samu duk wanda ya saka rigarsu. Tabbacin hakan kuwa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki:

*"Kuma haka nan, muka sanya maƙiyi ga kowane Annabi; shaiɗanun mutane da aljannu, sashensu na wahayi ga sashe, da ƙawataccen zance bisa ga ruɗi".*

Sai dai a duk lokacin da haƙuri da tsoron Allah suka samu ga mai da'awah, to, babu abin da sharrin maƙiya zai yi da shi, bisa alƙawarin Allah:

> *"Idan kuka yi haƙuri, kuka kuma yi taƙawa, makircinsu ba zai cutar da ku da wani abu ba. Haƙiƙa Allah, mai kewayewa ne ga abin da suke aikatawa".*

Sai dai magana guda, wadda ba ta tashi, ita ce, babu makawa sai Allah ya jarrabi mai kira zuwa ga tafarkinsa. Wani mutum ya tambayi Imamu Shafi'i *Rahimahullah* da cewa: *"Ya baban Abdullahi! Shin da a jarrabi mutum, ko a share masa hanya, wane ne mafifici? Sai ya karɓa masa da cewa: Ai ba zai taɓa yiwuwa a share maka hanya ba har sai an jarrabe ka. Ka tuna cewa, Annabi Nuhu, da Ibrahimu, da Musa, da Isah, da ɗungurungum Muhammadu, salawatullahi wa salamuhu alaihim, duk an jarrabe su. Amma, da suka yi*

*haƙuri sai aka share musu hanyar. Saboda haka kada wani mai da'awa ya taɓa zaton cewa, zai tsira daga raɗaɗin hanyar". [53]*

Wani abin kuma shi ne, da zarar mutum ya saba da haƙuri, to, maƙiyansa za su riƙa shakka da jin tsoronsa. Wanda kuma ya kasa saka rigar haƙuri, to, nan take ne maƙiya za su koɗa wuƙaƙe suna jiransa. Saboda haka yana da kyau kowane musulmi, ya saba ma kan sa da haƙuri, tare da sakankancewa da cewa, Allah *Subhanahu wa Ta'ala* zai ba shi lada a kan haka. Tabbatacciyar magana ce cewa, duk wanda yake da yaƙinin samun lada, to, babu wani abin da cutarwa za ta yi da shi. Da ɗai mumini, babu abin da yake gabansa illa aikata abin da aka umarce shi da shi, da nisantar wanda aka hane shi, da haƙuri a kan abin da aka hukunta masa. Da zarar kuwa mutum, koma waye shi, ya kasa haƙuri, to, nan take zai faɗa a cikin abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya haramta masa, ko ya ƙetare wanda aka wajabta masa.*

Hasali ma, babu abin da ya fi dacewa da wanda ya yi karatu, yake aiki da shi, ya kuma kama hanyar wa'azi, kamar haƙuri. Da zarar kuwa ya kasa zama mai haƙuri, to, wawayen mutane kuma jahilai, za su wofintar da shi. Dalili kuwa shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Saboda haka ka yi haƙuri domin kada waɗanda ba su da yaƙini su wofintar da kai".* Kai ka san matsayin haƙuri ba ɗan ƙarami ne ba, tunda har aka umurci Manzanni *alaihimussalamu,* da yin ado da tufan haƙuri inda Allah ke cewa:

> *"Ka yi haƙuri kamar yadda manya-manyan Manzanni suka*
> *yi haƙuri; kada ka yi musu gaggawa".*

Hanyoyin tabbatar da wannan ɗabi'a ta haƙuri sun haɗa da, jure ma cutarwa, da haɗe fushi, da gafarta ma mutane, balle ga mai karantar da mutane. Wannan ita ce mafi girman hanyoyin da dole sai an yi haƙuri a kan su, an kuma kai matuƙa a cikin ƙoƙari da tsarkake niyya domin kwalliya ta biya kuɗin sabulu. Duk kuma lokacin da cutarwa ta yi tsanani, to, sa'annan ne nasara ta kawo jiki, bisa ga shaidar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da yake cewa: *"Kuma haƙiƙa nasara tana tare da haƙuri".* Ahmad ne ya riwaito shi.[54] Shi

---

[53] *Alfawa'id,* shafi na 407

[54] *Al-Musnad,* Hadisi na (2804) 1/307 daga Ibn Abbas.

kuwa Sayyidi Ali *Radhiyallahu Anhu* cewa ya yi: *"Haƙuri wani abin hawa ne da ba ya raggon kaya, wadatar zuci kuma takobi ne da ba ya giɓi".* [55]

Sai dai ya kamata a lura, ba lalle ba ne don mutum ya yi haƙuri, sai haƙarsa ta kai ga ruwa nan take. Ko alama, nasarar wannan haƙuri nasa tana iya tabbata ko bayan ya kwanta dama. Sai kawai a wayi gari Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya sanya so da ƙaunar abin da ya yi kira zuwa gare shi a cikin zukatan mutane; su kama su riƙe ba ji ba gani. Ka ga a haka, mutum mai haƙuri ya ci ribar duniya da Lahira a lokaci ɗaya, saboda ya samu yardar Allah da kusantarsa, kamar yadda Buwayayyen Sarkin yake cewa: *"Lalle Allah yana tare da masu haƙuri".* Shi kuwa Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* sai yake cewa: *"Ma'aunin ayyuka kan yi nauyi ne sanadin biyar gaskiya da haƙuri a kan haka, da sakin hannu idan an roƙa, da kuma tsakaitawa idan an yalwata".* [56]

Haka kuma babban rabo ba ya samuwa sai an yi haƙuri, an kuma ji tsoron Allah. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa:

> *"Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku yi haƙuri kuma ku yi juriya, kuma ku yi zaman dako, kuma ku yi taƙawa, tsammaninku za ku ci nasara".*

Ta kuma tabbata cewa Allah Maɗaukain Sarki ya yi ma masu haƙuri bushara da abubuwa guda uku, waɗanda kowane daga cikinsu alheri ne, kuma mutane na faɗi tashin samunsu a wannan gida na duniya. Ga abin da Allah yake cewa:

> *"Kuma ka yi bushara ga masu haƙuri. Waɗanda idan wata musiba ta same su, sai su ce: Lalle ne mu ga Allah muke, kuma lalle mu zuwa gare shi masu komawa ne. Waɗannan akwai albarka a kan su daga Ubangijinsu da wata rahama. Kuma waɗannan su ne shiryayyu".*

Ba kuma kowa ne yake da rabon shiga Aljanna ba, matuƙar bai kasance ɗaya daga cikin masu haƙuri ba. Dalili a kan haka kuwa shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*:

---

[55] *Muhadarat Al-Udaba',* na Abul Kasim Al-Asfahani 2/ 524

[56] *Ijtima' Al-Juyush Al-Islamiyya,* na Ibn Al-Kayyim, shafi na 78.

*"Lalle haƙiƙa ni, na saka musu ne yau saboda haƙurin da suka yi. Tabbas, lalle haƙiƙa, su ne kawai masu samun babban rabo".*

Tabbatar da ganin rayuwa ta tsare alfarmar waɗannan mas'aloli guda huɗu, da aka tattauna a sama, wato, ilimi, da aiki da shi, kira zuwa gare shi, da kuma haƙurin cutarwa. Waɗannan na daga cikin manya-manyan abubuwa masu nauyi ga rayuwa, kafin ta samu nagarta, har ma maƙwabta su ci albarkarta. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ya bayyana wannan matsayi da cewa: Yaƙar zuciya na da matakai guda huɗu. Kuma ya kawo su kamar haka:

**Na Farko:** A yaƙe ta a kan neman ilimin shiriya da addini na ƙwarai, irin waɗanda babu yadda za a yi mai ita, ya samu babban rabo da arzikin gidan duniya da Lahira sai da shi. da zarar kuwa rayuwa ta kasa samun irin wannan ilimi, to, ta tashi aiki tun a nan duniya.

**Na Biyu:** A yaƙe ta a kan aiki da ilimin da aka samu. Idan kuwa ba haka ba, to, a sani wannan ilimi da aka samu, idan har bai zama guba ya halaka mutum ba, to, babu fa yadda za a yi ya zama mai amfani.

**Na Uku:** A yaƙe ta a kan kira zuwa ga wannan ilimi ta hanyar karantar da duk wanda ba ya da shi. Idan kuwa har samun hakan ya faskara, to, mutum ya zama cikin sahun masu ɓoye abin da Allah ya saukar na shiriya bayyananna. A haka kuwa wannan ilimi nasa ba zai amfane shi da komai ba, balle ya tserar da shi, daga azabar Allah.

**Na Huɗu:** A yaƙe ta a kan haƙuri da wahalhalun kira zuwa ga tafarkin Allah, da cutarwar da za ta haɗuwa da ita daga sauran halittu. Mai rai ya ɗauka cewa duk wannan daga Allah ne. To, da zarar mutum ya gama

taka waɗannan matakai, to, ya zama ɗaya daga cikin manyan bayin Allah "*Rabbániyyun".** [57]

Kalmar: ***"Dalili"*** kuma, malam ya yi amfani da ita ne a matsayin share fage ga shimfiɗa hujjoji da dalilai masu ƙarfafa wajabcin tsare alfarmar waɗannan mas'aloli guda huɗu tare da kiyaye ta, ta hanyar neman sani da laƙantarsu, wato, ilimi, aiki da shi, kira zuwa ga hakan, da kuma haƙuri bisa cutar da za a haɗu da ita a kan wannan tafarki. Dalili a kan haka a cewarsa shi ne: ***"Faɗar Allah Ta'ala: Bismillahir Rahmanir Rahim".*** Wannan *basmala* ya kawo ta ne kawai a matsayin mabuɗin sura, amma ba ta daga cikin hujjojin.

Cewar da Allah ya yi: ***"Ina rantsuwa da zamani"*** yana nufin awowi da mintuna da daƙiƙoƙin zamani, waɗanda a cikinsu ne mumini yake samun riba ta hanyar aikata ayyuka na ƙwarai. Waɗanda kuma suka bijire su sami hasara da taɓewa. A cikin kwarkwaron lokaci ne, bayin Allah suke ayyukansu daban-daban, kuma a cikin sane abubuwan ban mamaki suke ta faruwa. Shi kuwa Allah Maɗaukakin Sarki yana da ikon rantsewa da duk abin da ya ga dama daga cikin halittarsa. Wannan ba wata matsala ba ce. Sai dai yin haka ba dole ba ne gare shi, tun da ba ya tayar da magana. Yana dai yin rantsuwar ne domin ƙarfafa mana sani da fahimtar girman al'amurra da muhimmancinsu.

***"Lalle ne mutum",*** kowane irin jinsi ne a bisa doron ƙasa: ***"Yana cikin hasara",*** da halaka da tawaya. Hasara kuwa kishiya ce ta riba, sa'annan mataki-mataki ce. Saboda haka tana yiwuwa wanda wannan ƙaddara ta faɗa ma, ya yi babbar hasara ne, ta duniya da Lahira; ni'imomin gidajen biyu sun yi masa ƙanshin ɗan goma, azabobinsu kuma sun yi kamun mayunwacin zaki. Tana kuma iya yiwuwa hasarar ba gama-gari ce ba. Saboda haka ne Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya saka kowane ɗan Adam a ciki lamirin. ***"Face",*** waɗanda Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya toge a cikin wannan Sura, waɗanda suka sifanta da waɗansu siffofi guda huɗu, waɗanda suka haɗa da imani da Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, kamar yadda ya ce, sai fa: "***Waɗanda da suka yi***

---

[57] *Zád Al-Ma'ad Fi Hadyi Khair Al-Ibád* 3/10.

***imani",*** ya kuma zauna a cikin zukatansu. Shi kuwa imani ba ya tabbata sai ta hanyar ilimi. Su kamar ƙadaga ce mai fuska biyu.

Bayan imani: ***"Kuma suka aikata ayyukan ƙwarai",*** da gaɓɓansu, suna yi suna komawa, suna kuma yi ma aikin nasu zubi da tsoron Allah da tsarkake aikin domin sa. Suna kuma biyar sawun koyarwar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a cikin gaba ɗayan ayyukan nasu; na zahiri da na baɗini, waɗanda suka jiɓinci haƙƙoƙan Allah da na takwarorinsu bayi, na wajibi da na mustahabbi. ***"Kuma suka yi ma juna wasiyya da bin gaskiya".*** Gaskiyar nan kuwa ita ce imani da aiki na ƙwarai. Wato, har koyaushe sashensu yana yi ma sashe hannunka mai sanda, ɗorawa tare da kwaɗaitarwa a kan wannan sha'ani. ***"Kuma suka yi ma juna Wasiyya da yin haƙuri"*** a kan musibu da ƙaddarori da nau'ukan cutarwa, daga waɗanda suke umurni da aikata alheri, suke kuma hanin su aikata sharri. Sai aka kuwa yi sa'a suka jure ma ɗa'ar Allah suka kuma jure ma nisantar saɓon sa.

To, duk wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi masa arzikin tsare waɗannan ɗabi'u, ya tsira daga hasara. Ya tashi daga zama gama-garin bawa, ya shiga sahun bayi masu babban rabo. Su, waɗannan siffofi guda biyu na farko, wato, imani da aiki na ƙwarai, suna zama sanadin cika ne da kamala ga mutum a karan kan sa. A yayin da biyun na ƙarshe kuma, wato, wasiyya da gaskiya, da wasiyya da haƙuri suke ba shi damar bayar da gudunmawa a cikin gyaruwar waninsa. To, da zarar kuwa hancin waɗannan siffofi guda huɗu sun haɗu ga mutum, to, ya gama samun tsira daga hasara. A hannu ɗaya kuma ya samu babbar riba wadda yawanta ba shi ƙirguwa.

Da ma kuma, ba komai ne addini ba, illa imani, da aiki na ƙwarai, da da'awah, da kuma haƙuri, kamar yadda Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ya bayyana cewa: *"Magabatan wannan al'umma sun haɗu a kan cewa, malami ba ya cancanta a kira shi na Allah, sai idan ya san gaskiya yana kuma aiki da ita, da karantar, da ita. Ko shakka babu duk wanda ya yi ilimi, ya yi aiki da shi,*

*ya kuma karantar da wasu shi, ya tabbata cikin manya-manyan bayin Allah a cikin sammai da ƙassai".** [58]

Wannan Sura; *Suratul Asri* da abin da ta ƙunsa, wani gargaɗi ne da tunatarwa ga jinsin ɗan Adam baki ɗaya, cewa lalle fa yana cikin hasara. Wanda kawai ba haka ba, shi ne wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya toge, wato, wanda nauyin ƙarfin imaninsa da Allah da ɗa'arsa zuwa gare shi, a sikelin ilimi, ya kai ko'ina. A haka ya kammala ke nan a karan kansa. Wasiyyar da ya tsare kuma zuwa ga 'yan'uwansa, ta ƙara ba shi wata kamala. Ginshiƙin kuma da yake ɗauke da gaba ɗayan waɗannan matakai, shi ne haƙuri. Da an taka matakinsa, to, an ƙure maleji kenan a fagen cika da kamala irin ta ɗan Adam. Malam Ibnl-Kayim *Rahimahullah* na cewa: *"Masu hankali, ƙwansu da kwarkwata, sun ce: Ni'ima ba ta samuwa ta hanyar ni'ima. Haka kuma hutu, ba ya samuwa ta hanyar hutu. Saboda haka duk wanda ya zaɓi shagali, to, za a yi wani shagalin ba da shi ba".*[59]

Duk mai hankali da basira, da zarar wannan Sura ta shiga kunnuwan basirarsa, to, ba abin da zai yi illa ya yi gaggawar kuɓutar da kan sa daga zama cikin masu hasara, ta hanyar sifantuwa da waɗannan siffofi guda huɗu. Sura ce mai matuƙar girma da ɗaukaka, wadda waɗannan siffofi guda huɗu da take ƙunshe da su, su ne ginshiƙan da rayuwar musulmi ke tafiya a kai.

Imam Ash-Shafi'i ***Rahimahullah***[60] yana cewa - game da wannan Sura: ***"Ko da Allah bai saukar da wata hujja"*** da gargaɗi, da tunatarwa, da hannunka mai sanda a cikin Alƙur'ani: ***"Ba, ga halittarsa",*** mukallafai: ***"Sai wannan sura",*** mai girma, bakandamiya: ***"To, ta ishe su",*** [61] zama hujja da dalilin tsare martabar addini, da aikata ayyuka na ƙwarai, da kira zuwa ga tafarkin Allah

---

[58] *Zád Al-Ma'ad Fi Hadyi Khair Al-Ibád* 3/10.

[59] Sifa'ul Alil shafi na 250.

[60] Allah ya yi masa rasuwa a shekara ta 204H.

[61] Ibnu Kathir a cikin Tafsirinsa (1/63) cewa ya yi, wannan magana tabbas daga bakin Imamus Shafi'i aka samo ta, amma ba a cikin wannan siga baƙi da baƙi ba. Ga abin da yake cewa: *"Inda mutane za su yi ma wannan Sura karatun ta natsu, to, da ta wadatar da su".* Haka Kuma Ibn Al-Kayyim ya ambata a cikin *Attibyan* shafi na 53, da kuma cikin *Miftah Dar As-Sa'adah* 1/58, da kuma a cikin *Al-Istiƙama* 2/259, da kuma a cikin *Uddatus-Sabirin* shafi na 60, riwaya daga bakin shi Imamu Shafi'i ɗin kuma, cewa: *"Da mutane za su zurfafa tunani a cikin wannan Sura, da ta ishe su riga da wando."*

*Subhanahu wa Ta'ala*, da kuma haƙuri a kan haka. Ba kuwa domin komai ba, sai don irin yadda Surar ta haɗa gaba ɗayan matakan cika da kamala ga ɗan Adam. Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* na cewa a kan haka: *"Abin da ake ce ma cika da kamala a cikin haƙƙin ɗan Adam, shi ne, ya zama kammalalle a haƙƙin kansa, mai kuma taimaka ma waninsa ya kammala. Saboda haka wannan Sura, tattare da zamanta taƙaitacciya, ta fi kowace Sura ta Alƙur'ani tattara bayanin alheri a cikinta".* [62]

Wannan Sura kuma wata babbar bushara ce, mai gargaɗi ga bawa. Manufarta ita ce, jawo hankalinsa ya tsaya da kyau ya yi ma kan sa hisabi. Wannan ma'anar ce Malam Ibnu Rajab *Rahimahullah* yake bayyanawa inda ya ce: *"Wannan Sura wani ma'auni ce, wanda mumini yake auna nauyin ayyukansa da shi, domin ya gane shin riba ya samu ko faɗuwa".*[63] Tabbas wannan Sura ta cancanci duk abin da malamai suka faɗa game da ita sakamakon girman daraja da ɗaukakar sha'aninta.

***"Kuma",*** saboda muhimmacin da neman ilimi yake da shi ne, kafin yin duk wani aiki, domin gudun bawa ya bauta ma Ubangijinsa cikin duhun kai, hakan ta sa: ***"Imamul-Buhari Rahimahullah",*** [64] ***A cikin ingantaccen littafinsa,*** [65] ***ya ƙulla babi a wannan fage, ya ce: "Babin Bayanin Ilimi Yana Gaban Magana da Aiki".*** Ya kuma ƙara da cewa: ***Dalili a kan haka; Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ka sani babu Ubangijin da ya cancanci bauta Sai Allah, Ka kuma nemi gafara a kan zunubanka".***

Sai kuma Imamul-Buhari *Rahimahullah* ya ƙara da cewa: ***"Ka ga a nan, Allah Maɗaukakin Sarki ya fara gabatar da ilimi a kan magana da aiki".*** Dalili kuwa shi ne, abu ne mawuyaci mutum ya yi ilimi, a kuma same shi yana aiki ba bisa shiriya da haske ba. Duk aikin da ba ilimi ne yake yi masa jagora ba, to, babu abin da zai zama ga ma'abucinsa sai sharri da cuta. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Ilimi shi ne shugaban aiki, kuma mai yi*

---

[62] *Miftah Dar As-Sa'adah* 1/58.
[63] *Laɗa'if Al-Ma'arif,* shafi na 313.
[64] Allah ya yi masa rasuwa a shekara ta 156H.
[65] A sashen da ya keɓe ma a kan ilimi, sai ya raɗa masa suna: *"Babin Ilimi Kafin Magana da Aiki."* Hadisi na (5) 1/37

*masa jagora. Shi kuwa aiki matsayinsa gare shi, shi ne na mabiyi da mai koyi. Duk aikin da bai zama a kan sawun ilimi ba, mai koyi da shi, to, ba ya da wani amfani ga ma'abucinsa. Hasali ma, zai cutar da shi ne kawai, kamar yadda wasu daga cikin magabatan wannan al'umma suke cewa: Duk wanda ya bauta ma Allah bisa jahilci, to, ɓarnar da ya yi ta fi gyara yawa".* [66]

Ashe kenan matsayin ilimi shi ne mafifici a kan na aiki. Sa'annan kuma sharaɗi ne sai da sanadarin ilimi a cikin kowane irin aiki, da kowace irin magana ne, suke inganta. Tabbas ilimi shi ne shugaban waɗannan abubuwa guda biyu, saboda duk ingancin niyya shi ne ingancin aiki.*

---

[66] *Miftah Dar As-Sa'adah* 1/ 85.

## SAKO NA BIYU

### Sani Kafin Aiki

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ce:*

***"Ka sani, Allah ya yi maka rahama, ya zama wajibi a kan kowane musulmi namiji, da mace, neman sanin abin da waɗannan mas'aloli guda uku suka ƙunsa, da kuma aiki da su. Ta farko: Cewa Allah ne ya halicce mu, ya azurta mu. Bai bar mu haka nan ba, sai da ya aiko Manzo zuwa gare mu. Duk wanda ya yi masa ɗa'a, zai shiga Alhjanna. Wanda kuma ya saɓa masa zai shiga Wuta. Dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Ta'ala: "Lalle ne mu, mun aika, zuwa gare ku, wani Manzo mai shaida a kanku, kamar yadda muka aika wani Manzo zuwa ga Fir'auna. Sai Fir'auna ya saɓa ma Manzon, saboda haka muka kama shi kamu mai tsanani.***

Bayan mawallafin ya ƙare magana a kan waɗannan mas'aloli guda huɗu, waɗanda sanin su da imani da su, suke wajaba a kanmu. Sai ya shiga wata maganar kuma, a kan wasu mas'alolin guda uku, su ma, da sanin su da aiki da su, suke wajabi. Ga abin da yake cewa a kan su:

***"Ka sani, ya zama wajibi",*** irin wanda wani ba ya ɗauke ma wani nauyinsa: ***"A kan kowane musulmi",*** mukallafi: ***"Namiji da Mace: Neman sanin abin da waɗannan mas'aloli guda uku suka ƙunsa".*** Na farko: Tauhidin *Rububiyyah,* na biyu: *Tauhidin Uluhiyyah,* na uku: *Wala'a da Bara'ah* (So da ƙi don Allah). Mawallafin ya bayyana waɗannan abubuwa da cewa su ne ginshiƙan addinin Musulunci. To, kafin komai, kamata ya yi mu kalli waɗannan lafuzza da kyau, mu yi ƙoƙarin gane abin da suka ƙunsa na ilimi da aiki.[67] ***"Da kuma aiki da su",*** da duk abin da suke karantarwa, saboda su ne ginshiƙan addini, kuma tushen aƙidarsa.

Mas'ala: ***"Ta farko",*** ita ce *Tauhidin Rububiyyah,* ɗaya daga cikin mas'aloli guda uku da saninsu yake wajibi a kan mu, sanin: ***"Cewa Allah ne ya halicce mu",*** a da can babu mu. Kamar yadda Allah yake cewa:

---

[67] *Ad-Durar As-Saniyya,* 1/117

*"Lalle ne wata mudda ta zamani ta zo a kan mutum, bai kasance kome ba wanda ake Ambato".* Bayan haka, kamar yadda Maɗaukakin Sarki ya ce a wata ayar, sa'annan sai muka halitta shi a cikin kyakkawar kama: ***"lalle, haƙiƙa mun halicci mutum a cikin kyakkyawar sifa".*** Shi ne kuma: ***"Ya azurta mu",*** ya yi mana ni'imomi daban-daban; bai bar mu da yunwa ko ragga ba. A maimakon haka sai ya ba ko wane mahaluki nasa arziki gwargwadon hali, ya kuma ci gaba da ɗaukar wannan nauyi. Tabbacin wannan shi ne abin da Allah yake cewa a wata ayar:

*"kuma babu wata dabba a cikin ƙasa face arzikinta na wurin Allah".*

Tsarki ya tabbata ga wannan Sarki, wanda ya samar da mu daga babu. Ya yi mana ni'imomi domin mu bauta masa, shi kaɗai. Ga abin da Allah Maɗaukakin Sarki ke cewa game haka:

*"Kuma ban halicci aljannu da mutane ba, face domin su bauta mani. Ba ni buƙatar wani arziki daga gare su, ba ni kuma buƙatar su ciyar da ni. Haƙiƙa Allah shi ne mai azurtawa, mai cikakken ƙarfi".*

***"Bai bar mu haka nan ba",*** a kara zube, ba tare da wani dabaibayi na umurni da hani ba. Wannan shi ne abin da yake jan hankalinmu zuwa gare shi, da ya ce:

*"Shin ko kuna tsammanin cewa, lalle haƙiƙa, mun halicce ku ne a banza, kuma cewa, lalle haƙiƙa ku, ba masu komawa ne zuwa gare mu ba".*

A wata ayar kuma ya ce:

*"Ashe mutum yana tsammanin a bar shi haka nan sake?"*

Tabbas, Allah Ta'ala bai bar mu cikin ɗimuwa ba ta yadda ba za mu iya gane gaskiya ba, da inda take, da yadda za mu iya isa wurin har mu yi tozali da ita.

A maimakon hakan ***"Sai dai ya aiko Manzo zuwa gare mu",*** ɗauke da wannan gaskiya a cikin siga mafi sauƙi, a matsayinsu na malamai masu karantarwa da shiryarwa zuwa gare ta. Suna kuma yin haka ne domin mu iya kama tafarkin shiriya ta hanyar yin aiki da umarce-umarcen da suke cikinsa. ***"Duk wanda ya yi masa ɗa'a , zai shiga Aljanna",*** saboda yi masa ɗa'a, yi ma

Allah Maɗaukakin Sarki ne. Ga abin da *Subhanahu wa Ta'ala* yake cewa, a kan haka:

*"Duk wanda yake biyayya ga Allah da Manzonsa, zai sa shi gidajen Aljanna, ƙoramu na gudana daga ƙarƙashinsu, suna masu dauwama a cikinsu, kuma wancan shi ne babban rabo".*

Mafi girma da ɗaukakar halitta, da kusanci a wurin Allah shi ne wanda ya bauta masa kamar yadda ya yi umurni. Shaikhul-Islam *Rahimahullah* yana cewa game da haka: *"Cika da kammalar girma sun tattara ne a cikin cika da kammalar mizanin ɗa'a ga Allah Subhanahu wa Ta'ala da kuma Manzonsa Sallallahu Alaihi wa Sallam, fai da ɓoye.*[68] Da ma kuma su Manzanni, Allah bai aiko su ba sai domin a yi musu ɗa'a a cikin duk abin da suka zo da shi. ***"Wanda kuma",*** sunansa ya kasance a cikin jerin marasa arziki na har abada, to, sai a taras yana saɓa ma wannan Manzo. Ba abin da zai hana faruwar haka tunda wanda duk: ***"Ya saɓa masa lalle ne zai shiga Wuta".*** **Allah** Maɗaukakin Sarki yana cewa a kan haka:

> *"Duk wanda ya saɓa ma Allah da Manzonsa. To, lalle haƙiƙa, makomarsa ita ce wutar Jahannama, suna masu dauwama a cikinta har abada".*

Shi kuma Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce: *"Babu wani mahaluki daga cikin al'ummata, da ba zai shiga Aljanna ba, sai wanda ya ƙi".* Sai aka tambaye shi da cewa: *"Wa kuwa zai ƙi ya rasulallahi?* Sai ya karɓa da cewa: *"Duk wanda ya yi mini ɗa'a, zai shiga Aljanna. Wanda kuma ya saɓa mini. To, shi yaƙi".* Buhari ne ya riwaito.[69]

***"Dalili"*** kuma a kan tsoratarwa daga saɓa ma Manzo *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Shi ne faɗar Allah Ta'ala da ya yi, cewa: "Lalle ne mu, mun aika, zuwa gare ku wani Manzo, mai shaida a kanku kamar yadda muka aika wani Manzo zuwa ga Fir'auna. Sai Fir'auna ya saɓa ma Manzon. Saboda haka muka kama shi, kamu mai tsanani".*** Hakan kuma ta faru ne ta hanyar nutsar da shi, da

---

[68] *Al-Fatawa*

[69] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (6851) 6/2655 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

rundunarsa, a cikin kogi, ba tare da ko ɗaya daga cikinsu ya tsira ba. Bayan haka kuma za su gamu da wata azabar a cikin ƙaburburansu har zuwa ranar tashin Kiyama. Daga nan kuma azabar wuta ta karɓa. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: ***"Wuta ana gitta su a kanta",*** lokacin da suke cikin ƙaburburansu; za a azabtar da su da wannan wuta: ***"Safe da maraice, kuma a ranar da Sa'a take tsayawa, ana cewa: Ku shigar da mutanen Fir'auna a mafi tsananin azaba".*** Wannan shi ne ƙarshen duk wanda yake saɓa ma Manzanni, kuma sakamakon masu ƙin biyayya ga umurninsu.

Saboda haka, lalle ne wannan al'umma ta Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ta yi kaffa-kaffa da saɓa ma Manzon nan nata, domin kada irin abin da ya samu Fir'auna ya same su, inda Allah Maɗaukakin Sarki ya kama su, kamu irin na mai isasshen ƙarfi. Malam Ibnu Kathir *Rahimahullah* ya ce: *"Wannan al'umma ta Annabi Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam, ta fi kowace al'umma cancanta da halakarwa idan ɗaiɗaikunta suka ƙaryata Manzonsu, saboda Manzon nasu, daraja da ɗaukakarsa sun fi na Annabi Musa ɗan Imrana".* [70]

Tirƙashi! Ashe kenan alheri gaba ɗayansa yana cikin biyayya da ɗa'a ga manzanni, kamar yadda saɓa masu ta tattara kowane irin sharri. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa:

> *"Wanda ya aikata aiki na ƙwarai; namiji ne ko mace, alhali yana mumini, to, haƙiƙa, muna rayar da shi, rayuwa mai daɗi. Kuma haƙiƙa, muna saka masu ladarsu da mafi kyawon abin da suka kasance suna aikatawa".*

Shaihul- Islami *Rahimahullah* ya ce: *"Imani da Allah da kuma Manzo shi ne cibiya kuma tushen arzikin duniya da Lahira".* [71]*

---

[70] *Tafsir Al-Alƙur'an Al-Azim,* na Ibn Kasir 4/395
[71] *Al-Fatawa,* 20/193

## TAUHIDIN ULUHIYYA

***Sheikh Muhammad bn Abdil Wahab ya ci gaba da cewa:***

***"Mas'ala Ta biyu: Cewa Allah ba ya lamunta a haɗa shi da wani a cikin bauta; Mala'ika ne makusanci ko Manzo ne aikakke. Kuma dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma lalle ne, wuraren sujada na Allah ne, saboda haka kada ku kira kowa tare da Allah".***

To, kasancewar mas'ala ta farko, wadda ta gabata, tana magana ne a kan *Tauhidin Rububiyyah*, wanda shi kuma yana share ma *Tauhidin Uluhiyyah* fage, da sauran abubuwan da ke ƙarfafa shi. Bisa wannan dalili, sai mawallafin ya shiga bayani a kan sa, a cikin wannan mas'ala ta biyu.

Eh! Wannan mas'ala tana magana ne a kan imani da Allah Maɗaukakin Sarki a matsayinsa na abin bauta. Ɗaya ce kuma daga cikin mas'aloli guda uku waɗanda sanin su da ƙudurce su ke wajaba a kan kowane musulmi. Ma'ana, kamar yadda Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake shi ne Mahalicci, mai azurtawa, wanda ya halicce ka, ya kuma azurta ka, ta hanyar yi maka baiwa da wasu ni'imomi da alherai. To, ka sani kuma: ***"Cewa Allah ba ya lamunta",*** hasali ma yana tsananin ƙyamar: ***"A haɗa shi da wani a cikin bauta; Mala'ika ne makusanci ko Manzo ne aikakke.*** To, bale wani, wanda ba su ba. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa: *"Lalle ne Allah ya amince muku abubuwa uku, a yayin da ya ƙyamatar muku wasu uku. Ya aminta ku bauta masa ba tare da haɗa shi da wani abu ba, ku kuma yi riƙo da igiyarsa gaba ɗayanku; kada ku rarraba, kuma ku tausaya ma wanda ya shugabantar a gare ku. Ya kuma ƙyamatar muku ka-ce-na-ce, da ɓata dukiya, da yawan roƙo".* Muslimu ne ya riwaito shi.[72] Kuma Allah Ta'ala ya ba mu labarin cewa, lalle fa, ba zai lamunci bayinsa su kama tafarkin kafirci da, inda yake cewa:

---

[72] *Sahih Muslim,* Hadisi na (1715) 3/1340 daga Abu Hurairata.

*"Idan kun kafirce, lalle, haƙiƙa, Allah Mawadaci ne daga gare ku, kuma ba ya lamunce ma bayinsa yin kafirci. Idan kuwa kuka gode zai yarda gare ku".*

A wata ayar kuma ya bayar da labarin cewa, Musulunci shi ne abin da ya yarde ma bayinsa, wato bauta masa da zuciya ɗaya, inda yake cewa:

*"Kuma na yarda Musulunci ya zama addini a gare ku".*

To, idan kuwa har Allah *Subhanahu wa Ta'ala* bai yarda bayinsa su bauta ma wani makusanci gare shi ba, kamar Mala'iku, ko Annabawa, ko Manzanni, tattare da kasancewarsu mafi girman halitta. To, rashin hakan ga wanda ba su ba shi ne mafi tsauri. Tabbas kuwa, saboda bauta, ko alama, ba ta cancanci wani wanda ba Allah ba. Kamar yadda babu wani mai halittawa, da azurtawa, da hukuntawa, sai shi. To, babu kuwa wanda ya cancanci bauta sai shi kaɗai, ba tare da abokin tarayya ba. Kenan ana buƙata ne, a wannan gaɓa, mumini ya yi imani da abubuwa biyu a lokaci ɗaya; imani da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* a matsayin Mahalicci, mai azurtawa, mai kuma hukuntawa, da imani da shi a matsayin wanda kaɗai, ya cancanci ibada, kamar yanka, da sallah, da alwashi, da rantsuwa, da matara kama da waɗannan, kuma lalle bauta ma wani wanda ba shi ba, ya zama babbar ɓarna.

***"Kuma dalili",*** a kan cewa Allah Maɗaukakin Sarki ba ya lamuntar a haɗa shi da wani a cikin bauta, ko ma waye shi, shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: ***"Kuma lalle ne, wuraren sujada",*** wato, masallatai da gaɓoɓan da ake amfani da su wurin yin sujada, duk: ***"Na Allah ne",*** shi kaɗai da ba waninsa ba. ***"Saboda haka kada ku kira kowa tare da Allah".*** Kar ku yi sujada a cikin waɗannan wurare da waɗannan gaɓoɓi ga wani wanda ba Allah Maɗaukakin Sarki ba, Mala'ika ne, ko Annabi, ko waliyyi, ko wani wanda ba su ba. Kiran nan na ibada ne, ko na roƙo. Irin wannan kira, ga wani wanda ba Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ba, shi ake ce ma Shirka mafi girma. Irin wannan zunubi kuwa Allah ba ya gafarta shi, sai idan an tuba, kamar yadda Allah yake cewa:

*"Lalle, haƙiƙa Allah ba ya gafartawa a yi Shirka da shi, amma, yana gafarta abin da bai kai wannan ba ga wanda ya so".*

A taƙaice dai, wajibi ne a yi imani da cewa, Allah *Subhanahu wa Ta'ala* Makaɗaici ne, Mabuwayi a kan bayinsa, mai kuma cikakken ƙarfi. Ba ya lamuncewa a bauta ma wani wanda ba shi ba, ko a haɗa shi da wani mahaluki mai rauni, a cikin bautarsa.*

## SO DA KI DON ALLAH

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:*

*"Mas'ala ta Uku: Cewa ba ya halatta ga duk wanda ya yi ma Manzo biyayya, ya kuma kaɗaita Allah, ya ƙulla soyayya da wanda ya yi ma Allah da Manzonsa tawaye, ko da ya kasance daga cikin mafiya kusanci zuwa gare shi. Dalili a kan haka kuma, shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki:*

> *"Ba za ka taɓa samun wasu mutane sun yi imani da Allah da Ranar Lahira, kuma suna son wanda ya yi ma Allah da Manzonsa tawaye ba, ko da kuwa iyayensu ne, ko 'ya'yansu, ko 'yan'uwansu, ko makusantansu. Waɗancan, Allah ya rubuta imani a cikin zukatansu, ya kuma ƙarfafe su da wani ruhi daga gare shi. Zai kuma shigar da su gidajen Aljanna, ƙoramu na gudana a ƙarƙashinsu, suna masu dauwama a cikinsu. Allah ya yarda da su, su kuma sun yarda da shi. waɗancan su ne rundunar Allah. Ku saurara, rundunar Allah su ne masu babban rabo".*

Mas'ala: ***"Ta Uku",*** tana magana ne a kan *'jiɓinta' da 'barrranta';* abubuwa biyu waɗanda su ma sanin su da laƙantar su, da ƙudurce su, da kuma aiki da su, wajibi ne a kan kowane musulmi. ***"Cewa ba ya halatta ga duk wanda ya yi ma Manzo biyayya",*** a cikin duk abin da ya yi umurni da shi, ya kuma nisanci duk abin da ya yi hani da shi. ***"Ya kuma kaɗaita Allah",*** a cikin ibadarsa. To, haramun ne ga irin wannan bawa, ya ƙulla soyayya da duk wanda ya yi ma Allah Maɗaukakin Sarki tawaye. Wannan mas'ala na ƙarfafar tabbatar da yin aiki da waɗancan mas'aloli da suka gabace ta, kamar yadda nassosan Shari'a suka nuna. A wata Hausa, kamar mawallafin yana cewa ne,

inda har aka fito, ka kaɗaita Ubangijinka, ka kuma bauta masa shi kaɗai, kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya koyar. To, ba abin da ya rage maka yanzu illa aiki da wannan ƙasaitacciyar mas'ala, wadda ke cewa, ba ya halatta ga wanda ya taka irin wannan matsayi na kaɗaita Allah, da biyayya ga Manzo *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya ƙulla soyayya da wanda ya yi ma Allah da Manzonsa tawaye".*** Hasali ma, abin da yake wajaba a kan sa shi ne yanke duk wata alaƙa da take a tsakaninsu komai ƙanƙantarta: ***"Ko da",*** irin wannan mutum da ya kangare ma Allah da Manzonsa: ***"Ya kasance daga cikin mafiya kusanci zuwa gare shi".*** Kamar mahaifinsa, ko ɗan cikinsa, ko ɗan'uwansa. Da zarar irin wannan matsala ta shiga tsakani, to, Allah Maɗaukakin Sarki ya yanke alaƙa a tsakaninku. Hakan kuma na nuna cewa, kusanci na haƙiƙa shi ne, na addini, ba na jini ba.

A haka kenan, musulmi, komai nisansa da kai, to, wajibi ne ka lissafa shi a cikin 'yan'uwanka. A yayin da shi kuwa kafiri, ko ɗan'uwanka ne na jini, to, a lissafi irin na addini, ba-ka-ba-shi.

***"Dalili shi ne: faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ba za ka taɓa samun wasu mutane sun yi imani da Allah da Ranar Lahira kuma suna son wanda ya yi ma Allah da Manzonsa tawaye",*** ta hanyar kafirci da saɓo. A taƙaice wannan matsayi da wancan ba su haɗuwa, wato, imanin mutum da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* da Ranar Karshe, ba zai karɓa sunansa ba, sai idan an taras yana aiki da abin da imanin nan ya ƙunsa, ya kuma tanada. Ɗaya daga cikin waɗannan tanade-tanade kuwa shi ne, son mumini ɗan'uwa tare da jiɓintarsa, da kuma ƙin wanda ba shi ba, da raba gari da shi. ***"Ko da kuwa",*** irin waɗannan mutane da aka ambata: ***"Sun kasance iyayensu ko 'ya'yansu ko 'yan'uwansu ko makusantansu".***

To, irin: ***"Waɗancan",*** mutane da suka tabbatar da imaninsu ga Allah da biyayya ga Manzo, suka kuma raba gari da duk wanda ya yi musu tawaye: ***"Allah ya rubuta Imani a cikin zukatansu",*** ma'ana ya samar da shi, ta yadda babu wani abu da yake iya girgiza shi, balle wata shubuha ko wani shakku ya yi tasiri a cikinsu. Zukatansu tsarkaka ne kuma masu yaƙini da sakankancewa. ***"Ya kuma ƙarfafe su da wani ruhi daga gare shi",*** a cikin sigar wahayi irin na

Ubangiji abin bauta, da kuma jinƙayi da luɗufi irin na Mahalicci mai rahama. Ya kuma hukunta musu samun cikakken arziki ta yadda babu abin da yake da girma da alfarma a idanunsu, sai imani. A taƙaice dai sun samu taimako da gudunmawar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, waɗanda kuma su ne ya ce ma *'ruhi,'* saboda shi ne abin da ba za su iya rayuwa ba sai da shi.

***"Zai kuma shigar da su gidajen Aljanna",*** a gobe Kiyama waɗanda a cikinsu, akwai abin da wata ido ba ta taɓa yin arba da shi ba. Wani kunne bai taɓa jin labari ba, zuciyar wani mahaluki ba ta taɓa ɗarsawa ba. ***"Koramu suna gudana a ƙarƙashinsu, suna masu dauwama a cikinsu;"*** Kari a kan haka ***"Allah ya yarda da su;"*** ya buga musu hatimin aminci: ***"Su kuma sun yarda da shi",*** sun so shi, sun gode ma ni'imominsa da falalolinsa. Sakamakon irin yadda suka sadaukantar da makusanta da mahaifa saboda shi sai aka wayi gari ya maye musu gurbin hakan, da yarda da amincewa.

***"Waɗancan su ne rundunar Allah",*** zaɓaɓɓu daga cikin bayinsa, waɗanda ya yi ma lamuni, masoyansa na kusa-kusa, kuma masu taimakon addininsa a bayan ƙasa. ***"Ku saurara! rundunar Allah su ne masu babban rabo",*** a duniya da Lahira.

Wannan aya tana nunawa a fili cewa, duk wanda ya yanke hulɗa da wanda ya yi ma Allah da Manzo tawaye, ya barranta da shi, to, Allah Maɗaukakin Sarki zai yi masa sakamako da abubuwa kamar haka:

1. Samar da imani tare da tabbatar da shi a cikin zuciyarsa. ***"Waɗancan, Allah ya rubuta imani a cikin zukatansu".***

2. Karfafawa tare da ba su gudunmawar haske da shiriya. ***"Ya kuma ƙarfafe su da wani ruhi daga gare shi".*** Allah ya raɗa ma wannan agaji sunan *'ruhi'* ne, saboda duk inda aka rasa *'ruhi,'* to, ba za a samu rayuwa ba. Da wannan sakamako, kuwa, da wanda ya gabace shi, duk suna kasancewa ne a nan gidan duniya.

3. Shigar da su Aljanna. *"Zai kuma shigar da su gidajen Aljanna, ƙoranmu suna gudana a ƙarƙashinsu, suna masu dauwama a cikinsu".*

4. Samun yardar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*. *"Allah ya yarda da su".* Wannan kuma wani ƙari ne a kan sauran ni'imomi, kamar yadda yake cewa a wata ayar: *"Kuma yarda daga wurin Allah ita ce mafi girma".*

5. Samun gamsuwa a gobe ƙiyama, bayan bawan ya samu kansa a cikin gidan Aljanna, da abin da yake cikinta na karamomi. *"Su kuma sun yarda da shi".*

6. Karramawar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* zuwa gare su, ta hanyar shigar da shi a cikin jerin zaɓaɓɓun bayi, kuma rundunarsa maɗaukakiya. *"Waɗancan su ne rundunar Allah. Ku saurara, rundunar Allah su ne masu babban rabo".*

Mawallafin Tafsirin da ake kira *Taisir Al-Karim Ar- Rahman* ya ce: *Shi kuwa duk wanda yake jin ya yi imani da Allah da ranar Karshe, amma kuma tattare da haka, yana ɗanyen ganye da maƙiya Allah, yana kuma son waɗanda suka yi watsi da imani a bayan bayansu. To, ko shakka babu, wannan imani nasa, imani ne holoƙo. Ai, babu wani al'amari a duniya, face yana buƙatar hujja da dalili, da za su tabbatar da shi. Amma, tutiya kawai, ai, ba abin da take tabbatarwa, balle a gaskata mai ita".* [73]

Su kuwa 'jiɓinta' da 'barrranta' waɗansu tuwasu ne manya-manya daga cikin tuwasun addini, kamar yadda Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab yake cewa: *"Ba yadda za a yi Musuluncin mutum ya karɓa sunansa, ya kaɗaita Allah ya kuma ƙaurace ma Shirka, sai idan ya raba gari da mushrikai ta hanyar*

[73] *Taisir Al-Karim Ar-Rahman Fi Tafsir Kalam Al-Mannan,* na Sa'adi, shafi na 787.

*fitowa fili ya tabbata musu cewa, lalle fa, shi da su, faufau".* [74] Wannan shi ne abin da Kalmar Shahada take nufi. Wato, Musulunci wanda ya ƙunshi miƙa wuya ga Allah Maɗaukakin Sarki ta hanyar kaɗaita shi, da janyuwa zuwa gare shi ta hanyar ɗa'a, da kakkaɓe hannu daga Shirka da masu yin ta. Shaihul Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Bara'a kishiyar jiɓinta ce. Abin da take nufi kuma shi ne nuna rashin jituwa da ƙyama. A yayin da ita kuma jiɓinta take nufin nuna soyayya da ƙauna. Saboda, da ma ba komai Tauhidi yake nufi ba illa, kada a so komai sai Allah, a kuma so abin da Allah yake so, saboda Allah. A taƙaice bawa ba zai so komai ba sai don Allah, ba kuma zai ƙi komai ba sai don Allah".* [75]

Shi kuwa musulmi, lalle ne ya so wanda Allah ke so, ya kuma ƙi wanda Allah ke ƙi. Sanannen abu ne kuwa cewa, Allah ba ya son kafiri, kamar yadda ya ce: *"Lalle haƙiƙa, shi, ba ya son kafirai".* Haka shi ma kafiri ba ya son Allah, ba ya kuma son muminai. A kan haka ne Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake cewa:

*"Ya ku waɗanda suka yi imani! Kada ku riƙi maƙiyina kuma maƙiyinku, a matsayin masoyi, kuna jefa soyayya zuwa gare su".*

Wannan yana nunawa a fili cewa, soyayyar mutum da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ba za ta kammala ba, sai idan ya tsare alfarmar *Wala'a* da *Bara'a.* Shaikhul-Islami yana cewa: *"Yana daga cikin cikar son Allah da Manzo, ƙin wanda ya yi ma Allah da Manzo tawaye, da kuma jihadi saboda Allah".* [76]

Da zarar imanin mutum ya yi ƙarfi a cikin zuciya, to, za a taras ɓangaren soyayyarsa da muminai, da ƙiyayyarsa da kafirai, shi ma zai ƙarfafa. Bisa wannan ne Shaihul-Islami *Rahimahullah* yake cewa: *"Idan imanin da yake cikin zuciya, da sani da son Allah da Manzonsa, suka ƙarfafa, to, hakan zai wajabtar da ƙin maƙiyan Allah".* [77] Idan ɓangaren *wala'u* da *bara'u* a imanin bawa suka samu tangarɗa, to, hakan ya cancantar masa da azabar Allah. Ga abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake cewa a kan haka:

---

[74] *Ad-Durar As-Saniyya* 8/331
[75] *Al-Fatawa* 10/465
[76] *Al-Fatawa* 8/361
[77] *Al-Fatawa* 7/522

*"Kada muminai su riƙi kafirai masoya koma bayan muminai. Duk wanda ya aikata haka, to, ba shi da wani matsayi a wurin Allah".*

Shaihul-Islam *Rahimahullah* ya ce: *"Soyayya tana daga cikin ayyukan zuciya. Shi kuwa imani da Allah yana wajabtar da son Allah da son Manzonsa. Ba kuwa yadda za ayi hakan ta iya haɗuwa da son wanda yake ƙin Allah da Manzonsa. Shi kuwa duk abin da ya yi ban hannun makaho da imani, to, ba abin da yake wajabta wa mai shi sai zargi da azabar Allah sakamakon rashin imani".* [78]

Kaurace ma mushrikai kaɗai ta hanyar gangar jiki ba ya wadatarwa idan ana maganar 'bara'a.' Wajibi ne bayan haka a ƙi su a cikin zuciya saboda Shirkarsu. Shaihul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Raba jahar da masoyi zai yi da mushrikai da ababen bautarsu, ba kawai yana nufin yin baran-baran da su ba. Ko alama, dole ne hakan ta kasance ta samo asali daga ƙiyayya da ƙyama irin na cikin zuciya".* [79]

Amma, tattare da wannan ƙiyayya da gaba da kakkaɓe hannuwa daga waɗannan mutane, da ababen da suke bauta, tabbas, Musulunci ya haramta kashin kafiri irin na amana, da wanda aka ƙulla alƙawari da shi, da wanda aka ba mafakar siyasa.[80] Ya kuma haramta karɓe dukiyarsa, ko zaluntarsa, ko yi masa wani ta'adi. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa a kan haka: *"Duk wanda ya kashe kafirin amana, ba zai shaƙi ko ƙanshin Aljanna ba. Shi kuwa wannan ƙanshi nata ana jin sa daga nisan tafiyar shekara arba'in".* Buhari ne ya riwaito.[81]

Sai dai kuma tattare da wannan ƙiyayya da ake nuna musu, wajibi ne a kira su zuwa ga Musulunci a cikin hikima da basira, kamar yadda Annabi

---

[78] *Al-Fatawa* 10/753

[79] *Al-Fatawa* 14/753

[80] Waɗannan mutane guda uku a Larabce ana kiran su: *Zimmi, da Mu'ahad, da Musta'aman.* Wato, kafirin da ya shiga ƙasar Musulunci da alƙawarin zai dauwama a kan kafircinsa, amma zai riƙa biyan jiziya. Zai kuma kiyaye da tsare alfarmar hukunce-hukuncen Musulunci. Da kafirin da ya shigo ƙasar Musulunci bisa aminci. Sai kuma kafirin da shi ma ya shiga ƙasar Musulunci da aminci airin na mafakar siyasa. *Mujamma'ul-Anhar 1/666,* da *Raddul-Muhtar 1/166,* da *Nailul-Auɗar 7/18,* da *Giza'ul Albab Fi Sharhi Manzumatil Adab 1/238.*

[81] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (3666) 2/409 daga Abdullahi ɗan Amru *Radhiyallahu Anhu.*

*Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi da mushrikan Makka. Wato, a taƙaice dai, shi Musulunci addini ne tsaka-tsaka a cikin abin da ya shafi wannan mas'ala ta *'wala'a* da *'bara'a';* bai wuce wuri ya ce a kashe kafirai ba, waɗanda ba su ji ba su gani ba. Kazalika, bai yi raggon kaya ba ya bar ƙofar haramtacciyar jiɓinta da haɗa hannu da waɗanda ba musulmi ba. Saboda haka ya zama wajibi a kan musulmi ya zama mai ido kifi ido bado a cikin aiwatar da wannan ibada mai girman daraja; kada ya kasa, kada kuma ya wuce wuri. A ƙoƙarin haka kuma ya zama mai cikakkiyar masaniya da ƙabli da ba'adin mas'alar gwargwadon yadda Shari'a ta shimfiɗa.*

## *Wala'ah* da *Bara'ah* Iri Biyu ne

Yana da kyau kuma ka fahimta cewa, *'wala'a'* da *'bara'a'* dangane da mushrikai sun kasu kashi biyu:

1. ***Tawallí:***

   Shi ne son Shirka da masu yin ta, ko kuma taimakon kafirai a kan muminai, ko farin ciki da haka, ko ba su wata gudunmawa da agaji a kan musulmi. Irin wannan ƙawance kuwa shi ne kafirci mafi girma, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: *"Duk wanda ya ƙulla ƙawance da su daga cikinku, to, lalle haƙiƙa, ya zama ɗaya daga cikinsu".* Imamul Bagawi *Rahimahullah* ya ce: *"Imanin mumini yana lalacewa idan yana ƙawance da kafirai".*[82]

   Haka Shaihin Malami Muhammad ɗan Abdulwahhabi *Rahimahullah* yake cewa, irin wannan ƙawance yana warware imani. Ga kalamin nasa: *"Abu na biyu da yake warware imani shi ne taimakon mushrikai da ba su gudunmawa a kan musulmi. Dalili a kan haka kuma shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Duk wanda ya ƙulla*

[82] Tafsirul-Bagwi 4/ 312.

*ƙawance da su daga cikinku, to, lalle haƙiƙa, ya zama ɗaya daga cikinsu".* [83] Na biyu kuma shi ne:

2. ***Muwáláti:***

Tana nufin abota da soyayya, waɗanda suke kishiyoyi ne na ƙiyayya da gábá. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"jiɓinta na nufin kishiyar ƙiyayya, ta kuma haɗa da soyayya da haɗuwar hankali. Ita kuwa ƙiyayya ta haɗa da ƙyama da rashin jituwa".* [84]

Hanyar kuma da ake iya ganewa tare da tantance wannan fashin baƙi, na kashi na biyu ɗin nan, ita ce soyayyar da ake nuna ma masu Shirka ta kasance saboda abin duniya ne, ba tare da wani agaji ko taimako ya shiga tsakani ba, a kan musulmi. Amma, idan haka ta kasance, to, an faɗa wani babban zunubi daga cikin Kaba'irai. Allah Ta'ala yana cewa:

*"Ya ku waɗanda suka yi imani! Kada ku riƙi maƙiyana kuma maƙiyanku, a maatsayin majiɓinta, kuna jefa soyayya zuwa gare su".*

Shaikhul-Islami *Rahimahullah* ya ce: *"Tana yiwuwa mutum ya samu kansa cikin wani nau'i na soyayya da ƙawance tsakanin sa da kafirai, sakamakon wani zumunci ko wata buƙata. To, irin wannan zunubi ne kawai wanda yake rage karsashi da alkadarin imaninsa, amma, ba zai zama kafiri ba. Wannan, shi ne abin da ya faru ga sahabin nan Khaɗib ɗan Abu Balta'ata".* [85]

A taƙaice, bambanci tsakanin *Tawállí* da *Muwálati* shi ne, na farkon kafirci ne irin wanda yake fitar da mutum daga Musulunci. Na biyu kuma zunubi ne babba daga cikin Kaba'irai. An tambayi Malam Abdullahi ɗan Abdullaɗif *Rahimahullah* a kan haka, sai ya karɓa da cewa: *"Tawállí* kafirci ne da yake fitar da mutum daga cikin Musulunci. Misalinsa shi ne, ba wa kafirai da mushrikai kariya, tare da taimaka musu da dukiya ko ƙarfin jiki ko ra'ayi. *Muwálati* kuwa zunubi ne babba daga cikin manya-manyan zunubai. Sai ya ba

---

[83] *Risalatu Nawaƙidh Al-Islam,* na Shaikh Muhammad ɗan Abdulwahabi *rahimahullahu.*
[84] *Al-Fatawa* 5/510.
[85] *Al-Fatawa* 7/523.

da misali da taimaka ma su da wasu ƙananan abubuwa kamar feƙa alƙalami, ko ma yi musu murmushi da sauran su.[86]*

*Muwáláti* da *Tawállí* kamar yadda aka fassara su a baya suna da fuskoki da dama, waɗanda Shaihin malami, Sulaiman ɗan Abdullahi ɗan Muhammad ɗan Abdulwahhabi *Rahimahullah* ya bayyana da cewa: *"Lalle haƙiƙa, Allah Maɗaukakin Sarki ya yi kashedi da jiɓintar kafirai, ya kuma tsananta a kan haka. Ya kuma bayar da labarin cewa, duk wanda ya jiɓince su, to, shi da su ba wani bambanci. Haka nan kuma an samo Hadisai daga Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam, inda ya bayyana cewa: 'Duk wanda ya so waɗansu mutane, to, za a tayar da shi tare da su".*[87]

Waɗannan bayanai da muka bayyana kai tsaye cewa, duk wanda ya aikata ɗayan abubuwa ashirin, to, waɗannan ayoyi sun hau kansa. Sakamakon haka kuma zai samu kansa a cikin narkon azabar Wuta. Kai! Allah dai ya kiyashe mu faɗawa cikin abubuwan da suke wajabta motsawar fushinsa da saukar azabarsa mai raɗaɗi. Waɗannan abubuwa su ne:

1) Kawance da Kafirai irin na gaba ɗaya.

2) Nuna musu soyayya da ƙauna ta musamman.

3) Karkata zuwa gare su komai ƙanƙantarta.

Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki:

*"Kuma ba domin mun tabbatar da kai ba, lalle ne, haƙiƙa, da ka yi kusa ka karkata zuwa gare su ta wani abu kaɗan. A lokacin, lalle ne, da mun ɗanɗana maka ninkin azabar rayuwa da ninkin azabar mutuwa, sa'annan kuma ba za ka samu mataimaki ba a kan mu".*

Ka ga kuwa idan har za a fusakanci fiyayyen halitta da waɗannan kalmomi, to, ina ga wanda ba shi ba?!

4) Yi musu sassauci da siyasa. Allah Ta'ala yana cewa:

[86] *Ad-Durar As-Saniyyah* 8/422.

[87] *Al-Mustadrak,* na Hakim, Hadisi na (4294) 3/18, da *As-Sunan Al-Kubra*, na Baihaƙi Hadisi na (18642) 9/234 daga Aliyu ɗan Abu Ɗalib da Abdullahi ɗan Amru *Radhiyallahu Anhuma.*

*“Suna fatar ka sassafta, su kuma sai su sassafta”.*

5) Yi musu biyayya a cikin abin da yake ƙarƙashin mulkinsu, da shawarwarinsu. Allah Ta’ala yana cewa:

*“Kuma kada ka bi wanda muka shagaltar da zuciyarsa daga hukuncinmu, kuma ya bi son zuciyarsa, alhali kuma al’amarinsa ya kasance yin ɓarna”.*

A wata ayar kuma yake cewa:

*“Kuma kada ka bi dukkan mai yawan rantsuwa, walaƙantacce”.*

6) Kusantowa da su a wuraren zama da shigar da su fadar Sarakunan Musulunci.[88]

7) Neman shawararsu a al’amurran yau da kullum.

8) Ba su wani aiki a cikin wani al’amari da ya shafi musulmi; kowane irin aiki ne. Kamar gine-gine, ko ƙwadago, ko rubutu, ko wani abu mai kama da haka.

9) Ɗaukar su a matsayin abokan sirri koma bayan muminai.

10) Zama da su tare da ziyarar su da shiga gidajensu.

11) Yi musu fara’a da sakin fuska.

12) Girmama su dama da hagu.

13) Ba su amana bayan Allah ya riga ya tabbatar da rashin ta gare su.

14) Taimakonsu a kan wani al’amari nasu komai ƙanƙantarsa; kamar fiƙar alƙalami, da miƙo musu tawada domin su rubuta zalunci

15) Neman shawararsu.

16) Biyar son zuciyarsu

17) Yin hannu da hulɗa da su.

18) Yarda da ayyukansu, da yin shiga irin tasu.

19) Ambaton abin da zai ɗaukaka alkadarinsu kamar ce musu ranka ya daɗe ko Alasabbene, irin yadda ake ce ma Ɗawagitai: Maigirma Wane. Ko

[88] Mawallafin yana nufin haramcin ba su muƙamai da za su zauna su yi ta-ma-tela a kan sha’anin mulki ko su yi dumu dumu cikin zartar da al’amurran jama’a. Wannan kuma bayan yana nuna *Muwáláti* kai tsaye, yana da hatsari ga rayuwar al’umma da raunana ta tare da karya lagonta. To, balle kuma damƙa ma su ragamar shugabanci gaba ɗaya. Daga Masu Fassara

wanda yake jin ya ƙoshi da ilimin kiwon lafiya misali, sai ka ji ana ce masa: Gwani, da matara kama da waɗannan.

20) Zama tare da su a ƙasashensu, kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce: *"Duk wanda ya haɗa wurin zama da mushrikai, to, lalle shi da su ba bambanci"*.[89]

Idan aka fahimci wannan, kenan babu wani bambanci idan haka za ta faru tsakanin mutum da makusantansa daga cikinsu, ko waɗanda ba su ba, kamar yadda ayar *mujadalah* ta nuna".[90]

Yin kama da mushrikai a zahiri abu ne da yake haifar da ƙauna da son su a baɗini. Akan haka ne Shaihul-Islam *Rahimahullah* yake cewa: *"Yin kama a zahiri abu ne da yake haifar da wani nau'i na soyayya da ƙauna da jiɓinta a baɗini, kamar yadda soyayya a baɗini take haifar da yin kama a zahiri. Wannan al'amari ne da ake iya ji a jika, yau da gobe kuma ta tabbatar da shi".* [91]

Amma, babu laifi idan an yi mu'amala da kafiri a zahiri, ba tare da karkata ko nuna soyayya a zuci ba, ko yin kama a zahiri. Illa dai, shi imani idan ya karɓa sunasa, lalle ne ya haifar da rashin amincewa da wanda ya yi ma Allah da Manzonsa tawaye. Haka kuma a gefe ɗaya, ya lizimtar da so da ƙaunar wanda yake son Allah da Manzonsa, da kuma jiɓintar su. Saboda haka duk wanda ya jiɓinci kafiri, to, ya bar wani babban rukuni kuma wajibi, daga cikin wajiban imani. Shaikhul-Islam *Rahimahullah* yana cewa: *"Dole ne imani*

---

[89] Sunanu Abi Dawuda Hadisi na (2787) 3/93 daga Samurata ɗan Jundub *Radhiyallahu Anhu,* ya ce: *"Bayan haka, Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ce: "Duk wanda ya haɗa wurin zama da mushrikai, to, lalle shi da su ba bambanci."* Shi ma wannan Abu Dawuda ne ya riwaito shi daga Jariru ɗan Abdullahi *Radhiyallahu Anhu,* wanda ya ce: *"Wata rana Manzon Allah ya aika wani ɗan ƙwarya-ƙwaryan kwamiti don su yaƙi Khas'am, sai wasu musulmi daga cikinsu suka fara sallah don gudun a kashe su. Duk da haka sai sojojin Musulmi suka haɗa su, suka aika su lahira. Ba su ɗauka cewa Musulmi ne ba. Da labari ya kai wa Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam sai ya umarci a biya magadansu rabin diyya. Ya kuma ƙara da cewa: "Na barranta daga duk wani musulmi da ya zaɓi zama tsakanin mushrikai." Sahabbai suka ce saboda me ya Manzon Allah? Sai ya ce: "saboda musulmai da kafirai ba sa tara mazauni ta yadda suke hangen wutar junansu". Sunan Abi dawud,* Hadisi na 2645, (3/45).

[90] *Ad-Durar As-Saniyyah* 8/154

[91] *Iƙtidha' As-Siraɗ Al-Mustaƙim,* shafi na 221.

*ya tsattsage zuciyar mai shi da son Allah da Manzonsa, da kuma ƙin wanda ya yi ma Allah da manzonsa tawaye".* [92]

To, ba kafirai kawai ba, wajibi ne yadda yake wajabta a ƙyamace su, a ƙyamaci fasiƙi saboda fasiƙancinsa. Sai dai za a jiɓince shi gwargwadon imaninsa. Shaihul-Islami yana cewa a kan haka: *"Wajibi shi ne a jiɓinci waliyan Allah masu taƙawa ba tare da nuna wani bambanci ba. a kuma ƙi kafirai da munafukai ba tare da wani bambanci ba. Shi kuwa ƙasaitaccen fasiƙi za a jiɓince shi gwargwadon imaninsa, a kuma ƙyamace shi gwargwadon fasiƙancinsa".* [93]

Saboda haka dai, abin da yake wajaba a kan mumini shi ne, ya ƙyamaci duk wanda ya yi ma Allah da Manzonsa tawaye, ya kuma ƙi shi. Amma, kuma haka ba za ta hana shi ba shi goron gayyata da yi masa wa'azi da nasiha, ya dawo ga tafarkin gaskiya ba. Mumini shi ne wanda yake son masoyan Allah, yana haɗa hannu da su cikn aikin alheri. A hannu ɗaya kuma yana ƙi da ƙyamar maƙiyan Allah saboda Allah, yana kuma kyarkyorarsu har a wayi gari sun dawo ma hanyar Allah. Ta tabbata cewa, duk wanda ya ƙi wanda Allah yake ƙi saboda Allah, Allah zai maye masa wannan gurbi da wata ƙasaitacciyar soyayya da wanda ba wancan ba. Ai, ka ga Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* lokacin da ya ƙaurace ma mahaifinsa da mutanensa saboda kafircinsu, sai Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya faranta zuciyarsa da samun Isma'ila, bayansa kuma ya ba shi jika; Ishaƙa, kuma dukkansu manzanni. Tun daga wannan lokacin kuma ba a sake aiko wani Annabi ba, sai daga cikin zuri'arsa. Shi ne Allah Ta'ala yake ba mu labari cewa:

> *"To, a lokacin da ya ƙaurace musu da abin da suke bauta ma, koma bayan Allah, sai muka yi masa tukuici da Ishaƙa, da Ya'aƙuba. kowannensu kuma mun sanya shi Manzo". **

[92] *Al-Fatawa* 7/147.
[93] *Al-Fatawa* 27/ 578.

## SAKO NA UKU:
## WAJABCIN YI DON ALLAH

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ce:*

*"Ka sani,[94] Allah ya shiryar da kai zuwa ga yi masa ɗa'a, lalle Musulunci, addinin Annabi Ibrahimu, shi ne ka bauta ma Allah da zuciya ɗaya. Wannan shi ne abin da Allah ya umarci gaba ɗayan mutane da shi, ya kuma halicce su don shi. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Ta'ala:*

> *"Kuma ban halicci aljannu da mutane ba sai don su bauta mani".*

*Ba kuma komai wannan kalma ta bauta take nufi ba, illa kaɗaita Allah Subhanahu wa Ta'ala. Babu wani abu da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi umurni da shi, wanda ya kai girma da alkadarin Tauhidi. Mafi girman abin da Allah ya yi hani da shi, shi ne kishiyar Tauhidi; Shirka, wato, kiran wani ko bautar wani tare da Allah. Dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki:*

> *"Kuma ku bauta ma Allah, kada ku haɗa shi da komai".*

Mawallafin - *Allah* ya yi masa rahama ya ce: *"Ka sani Allah ya shiryar da kai",* ya kuma yi maka gamon katar da muwafaƙa: *" Zuwa ga yi masa ɗa'a".* Irin wannan du'a'i kuwa na neman dace da kama tafarkin ɗa'a da biyayya ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana daga cikin addu'o'i mafiya alheri, mafi kuma zama kandamau. Tabbacin hakan shi ne, abin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce ma Sayyidi Ali ɗan Abi Ɗalib *Radhiyallahu Anhu: "Ya Aliyu! Ka ce: Ya Ubangiji! Ka shiryar da ni, ka kuma ɗora ni a kan tafarki madaidaici. Idan za ka nemi shiriya, ka nemi shiriya ga hanya.".* Muslim ne ya

[94] Wannan shi ne saƙo na Uku daga cikin saƙonni Uku waɗanda suka gabaci Shika-shikain Aƙidar Musulunci Uku.

riwaito.[95] Da zarar kuwa bawa ya samu tsayawa a kan tafarkin ɗa'a da biyayya ga Allah, to, ya gama samun kowane irin alheri.

Domin ka samu shiga sahun waɗanda za su ci gajiyar irin wannan alheri, ka sani: ***"Lalle Musulunci",*** aƙida wadda ta tanadi kaɗaita Allah da bautar sa kaɗai da zuciya ɗaya, ba tare da an karkata akalar wani yanki nata zuwa ga wanda ba shi ba *Subhanahu wa Ta'ala*. Duk wanda ya tabbatar da haka, idan kana neman musulmi ka gan shi, ka samu. Ya cika tam, wanda yake kan tafarkin Manzanni.

A luggance kalmar *"Hanífu,"* ta Larabci, wadda muka fassara da "addini", an tsago ta ne daga kalmar *'Hanaf,* ' wadda ita kuma take nufin "karkata" daga wani abu. Idan aka ce wa mutum "Hanífu" ana nufin wanda ya karkata daga "Shirka", ya nufi birnin "Tauhidi". A ilmance, fassarar "Hanífu" ita ce daidaitaccen mahaluki, wanda ya ƙanƙame Musulunci, ya koma ga Allah gaba ɗaya ta hanyar ba wa duk abin da ba Allah ba baya. Bisa wannan, duk wanda yake a kan addinin Annabi Ibrahim *Alaihis Salam*, sunansa "Hanífu". Shaikhul-Islam *Rahimahullah* yana cewa: *Addini Bahanafe shi ne mayar da hankali ga Allah shi kaɗai, da ƙaurace ma duk abin da ba shi ba".* [96] Idan kuma kuma aka ce *Hanafiyyah,* to, ana nufin: ***"Addinin",*** shugaban sahun Hanafawa: ***"Annabi Ibrahim",*** *Alaihis Salam,* kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki ke cewa:

*"Lalle ne Ibrahimu ya kasance shugaba, mai ƙanƙan da kai ga Allah, mai karkata zuwa ga gaskiya, kuma bai kasance daga cikin masu Shirka ba".*

Wannan addini kuma shi ne addinin da gaba ɗayan Manzanni suka zo da shi. tabbacin haka shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*:

*"Sa'annan muka yi wahayi zuwa gare ka cewa, ka bi addinin Ibrahimu, mai karkata zuwa ga gaskiya, kuma bai kasance daga cikin masu Shirka ba".*

Babu kuma wani Annabi da aka aiko bayan Ibrahimu *alaihissalm,* wanda ba daga cikin zuri'arsa ba. Saboda haka ne Allah Ta'ala ya ce: *"Addinin Ubanku Ibrahimu".* Saboda shi ne kakan gaba ɗayan Annabawa

[95] *Sahih Muslim,* Hadisi na (2725) 4/2090.
[96] *Al-Fatawa* 9/319.

*alaihimussalam,* ba kuma wani addini suka zo da shi ba, sai Musulunci. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* na cewa game da haka:

*Haƙiƙa, addini a wurin Allah shi ne Musulunci".*

Bisa haka duk wani addini, wanda ba Musulunci ba tarkace ne kawai. Allah Ta'ala yana cewa:

*"Duk wanda ya bi wani addini ba Musulunci ba, har adaba ba za a karɓa daga gare shi ba. A ranar Lahira kuma yana daga cikin hasararru".*

Shi kuwa wannan addini na Hanafawa, abin da ya tanada: ***"Shi ne ka bauta ma Allah ",*** shi kaɗai: ***"Da zuciya ɗaya",*** ba tare da gwama shi da wani abu ba a cikin bautar. Ka yi baran baran da bautar duk wani abin da ba shi ba tare da ƙudurce wannan zaman bautar da ba ta Allah ba a matsayin ɓarna. Wannan shi ne abin da Maɗaukakin Sarkin ya umarci gaba ɗayan Annabawa da shi, kamar yadda ya umarci Annabi Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da cewa:

*"Ka ce: lalle haƙiƙa ni, an umarce ni da in bauta ma Allah da zuciya ɗaya".*

Bayan haka kuma sai ya umarci gaba ɗayan mutane, da haka, yana cewa: *"Kuma ba a umarce su da komai ba, face bauta ma Allah, suna masu tsarkake addinin gare shi, masu karkata zuwa ga addinin gaskiya, kuma su tsayar da sallah, su kuma bayar da zakka, kuma wannan shi ne addinin waɗanda suke a kan hanyar ƙwarai".*

Bisa haka, babu wata hanya ga rayuwa a duniya da Lahira, da zata samu nagarta da shiriya, sai ta hanyar Tauhidi da Ikhlasi. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Babu wani abu da yake amfanin zuciya kamar yadda Tauhidi da Ikhlasi suke yi. Babu kuma abin da yake cutar da ita kamar yadda Shirka take yi".* [97]

Mawallafin ya ci gaba da cewa: ***"Wannan",*** irin ibada; bauta ma Allah da zuciya ɗaya: ***"Shi ne abin da Allah ya umarci gaba ɗayan mutane da shi",*** mazansu da mata, ***ya kuma halicce su don shi". "Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Ta'ala: "Kuma ban halicci aljannu da mutane ba sai don su bauta mani".***

---

[97] *Al-Fatawa* 10/652.

Ma'ana, ba domin wasu buƙatu ba da nake da su zuwa gare su. *"Ba kuma komai wannan kalma ta bauta take nufi ba, illa kaɗaita Allah Subhanahu wa Ta'ala",* ta hanyar daidaita niyyyar da take cikin zukatansu a cikin gaba ɗayan ayyukansu, su zama domin Allah kawai suke yin su.

Da ma kuma zuciya, koma ta waye, babu yadda za a yi ta samu babban rabo, ta tsarkaka, ta samu natsuwa, sai idan tana bauta ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* shi kaɗai. Yau da za a tattara ma mutum kowane irin jin daɗi, irin wanda kowane mahaluki yake muradi. Da zarar Ikhlasi bai samu ba gare shi da saura. Kuma bautar duk da yake ma Allah ba za ta kammala ba, balle ya wadatu daga sauran halitta. Bautar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* kuwa tana karɓa sunanta ne kawai, a lokacin da aka yi ta gwargwadon yadda ya umarta, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* kuma ya karantar. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Duk wanda ya kalli yanayin duniya da kyau, zai fahimci cewa, babu wata nagarta a bayan ƙasa, wadda ba kaɗaita Allah da ɗa'a ga Manzo ne sanadiyyarta ba. Duk kuma wani sharri a ɗakin duniyar nan, da fitina, da bala'i, da fari, da galabar maƙiya, da matara kama da waɗannan, Shirka da saɓa ma Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam ne sanadinsu. Duk wanda ya kalli wannan lamari da idon basira, zai gane lalle haka abin yake tun a kan karan kansa, da kuma waninsa, gangame da keɓance".* [98] Kai! Babu wani hali da zuciya za ta shiga ta ji ba ta da buƙata da abokan halitta, sai fa idan cike take maƙil da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* a matsayin majiɓincinta, ta yadda mai ita ba ya gamsuwa da komai sai Mahalicci, ba ya kuma dogara ga komai sai gare shi.*

Ka sani kuma: *"Babu wani abu da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi umurni da shi",* a cikin littafinsa, mafi kuma girman abin da Manzanni suka umarci al'ummominsu da shi: *"Wanda ya kai girma da alkadarin Tauhidi",* ta hanyar bauta ma Allah shi kaɗai, da zuciya ɗaya. Wannan nauyi shi ne farilla mafi girma da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya ɗora ma bayinsa, su sani su kuma aikata. Saboda haka ne kuma kawai aka aiko Manzanni, aka saukar da Littattafai, ta hanyarsa ne kuma ake samun gafarar zunubai, a cancanci shiga

[98] *Al-Fatawa* 15/25.

Aljanna, a kuma samu kuɓuta da tsira daga shiga Wuta. Duk kuwa wanda bai tsaya a kan waɗannan manya-manyan al'amurra ba, to, gaba ɗayan ayyukansa, ba za su samu karɓuwa ba a wurin Allah *Subhanahu wa Ta'ala*. Ga abin da Maɗaukakin Sarkin yake cewa: *"Kuma muka gabata zuwa ga abin da suka aikata na aiki, sai muka mayar da shi ƙura watsattsiya"*.

Kuma saboda girman Tauhidi ne aka saukar da Alƙur'ani gaba ɗayansa. Gaba ɗayan kuma abin da yake cikinsa yana hannunka mai sanda ne game da Tauhidi. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* cewa ya yi: *"Babu wata aya a cikin Alƙur'ani, face ta ƙunshi bayani a kan wani nau'i na Tauhidi, ta hanyar zama hujjar da ke tabbatar da shi, da kira zuwa gare shi. Domin kuwa gaba ɗayan Alƙur'ani, ko dai labari ne game da Allah da Sunayensa da Siffofinsa da Ayyukansa. A haka ya zama Tauhidin da aka labarta a ilmance. Ko kuma ayar ta zama kira ne zuwa ga bauta ma Allah shi kaɗai ba tare da yi masa kishiya ba, da tunɓuke duk abin da ake bauta koma bayansa. Wannan kuma ya zama Tauhidin da ake nema a aikace. Ko ka taras da ayar umurni ne da hani da wajabtar da ɗa'a ga Allah a cikinsu. Wannan shi ma haƙƙi ne na Tauhidi. Ko kuma ayar ta zama labari ne a kan karimcin Allah Maɗaukakin Sarki zuwa ga ma'abuta Tauhidi da ɗa'a zuwa gare shi, da irin tagomashin da ya yi musu a nan duniya, da karramawar da zai yi musu a gobe Lahira. Wannan kuma sakamako ne irin na masu Tauhidi. Ko duk ba wannan ba, sai ka tarar ayar tana bada labari ne a kan masu Shirka, da irin azabar da za su haɗu da ita a nan duniya, da wadda za ta saukar musu a gobe Kiyama. Wannan shi kuma hukuncin wanda ya fanɗare ma Tauhidi kenan. Saboda haka Alƙur'ani gaba ɗayansa yana magana ne a kan Tauhidi, da haƙƙoƙansa da sakamakonsa, da kuma a kan sha'anin Shirka da ma'abutanta, da kuma sakamakonsu. Ka ga: "Alhamdu Lillahi" Tauhidi ce. "Rabbil-alamina" Tauhidi ce."Ar-Rahmanir-Rahimi" ma Tauhidi ce. Haka "Maliki Yaumiddini" Tauhidi ce. "Iyyaka Na'abudu Wa Iyyaka Nasta'inu" ita ma Tauhidi ce"*. [99]

Ashe kenan, Tauhidi shi ne tubalin ginin gaba ɗayan addini. Shi ne babban dalilin da yake samar da waraka daga kowane irin ƙunci, irin wanda

[99] *Madarij As-Salikin*, 3/449.

yake taushe ƙirji da zuciya. A ƙarƙashin inuwarsa ne duk mai neman mafaka yake samun ta, wanda ya kama daji kuma ya shiga taitayinsa. Kamar yadda wanda baƙin ciki ya yi ma katutu zai samu tsira da waraka. Haka kuma wanda aka zalunta ya samu ceto. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Babu wani abu da yake tunkuɗe wahalce-wahalcen duniya kamar Tauhidi. Saboda haka ne addu'ar neman tsira daga baƙin ciki, sanadarinta Tauhidi ne. Wannan shi ne sirrin kasancewar addu'ar Annabi Yunusa "Zun-Nun", babu wani ma'abuci baƙin ciki, da zai roƙi Allah Subhanahu wa Ta'ala da ita, face Allah ya yaye masa shi da albarkar Tauhidin da ke cikin ta. Idan kuma kana neman babban abin da yake jefa ɗan Adam a cikin manya-manyan baƙƙan ciki, to, babu kamar Shirka. Irin wannan ciwo kuwa ba shi da magani sai Tauhidi. Shi ne ƙyaure, shi ne ƙofa, shi ne birni, shi ne ganɗo ga gaba ɗayan halitta, shi ne kuma matsera a ga reta".* [100]

Tauhidin da Annabawa suka gamu da cirjiya a kan sa, tsakaninsu da jama'arsu, shi ne *Tauhidin Uluhiyyah:* ***"Wanda yake nufin kaɗaita Allah Subhanahu wa Ta'ala da bauta",*** kamar yanka, da alwashi, da addu'a. Irin waɗannan ibadu ba a fuskantar wani mahaluki da wani yanki daga cikinsu, da su, wanda ba Allah ba.

Shi kuwa Tauhidi, *asalatan,* ya kasu kashi uku ne:

1. *Tauhidin Rububiyyah*, wanda yake nufin kaɗaita Allah da ayyukansa.
2. *Tauhidin Uluhiyyah*, wanda yake nufin kaɗaita Allah da ayyukan bayi.
3. Tauhidin Sunaye da Siffofi, wanda yake nufin sifanta Allah da abin da ya sifanta kan sa da shi a cikin littafinsa. Manzonsa kuma ya sifata shi da shi. A yi haka ba tare da wata canzawa, ko rusawa, ko wasaftawa, ko kamantawa ba.

[100] *Alfawa'id*, shafi na 95.

Duk mahalukin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya yi masa tagomashin tabbatar da waɗannan kashe-kashe na Tauhidi guda uku a rayuwarsa, to, idan ana neman cikakken Mumini aka gan shi, an samu.

Malam ya ci gaba da cewa, saboda haka ya zama wajibi a kan bawa, ya san cewa: ***"Mafi girman kuma abin da",*** Allah Maɗaukakin Sarki: ***"Ya yi hani da shi",*** a cikin littafinsa. Mafi girman kuma abin da Manzanni suka yi kahsedi da shi: ***"Shi ne Shirka",*** wadda take nufin karkatar da wani abu na ibada zuwa ga wanin Allah.

Sa'annan, ka ga Shirka; yi ma Allah kishiya, ta fi kisan kai nauyi a wurin Allah, ta fi fashi da makani, ta fi sata. Kai! Babu wata ɓarna a bayan ƙasa da ta kama ƙafarta. Babu kuma wata hanya ta tsira ga bayi, sai hanyar Tauhidi; kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki da bauta. Shaikhul-Islam *Rahimahullah* yana cewa: *"A taƙaice dai, ka ga Shirka da kira zuwa ga abin da ba Allah ba, da samar da wani abin bauta koma bayansa, ko wani abin koyi, wanda ba Annabi Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam ba, shi ne mafi girman ɓarna a bayan ƙasa. A hannu ɗaya kuma, babu wani magani gare ta da mazaunanta, sai idan an wayi gari ana ƙudurta babu abin bauta a kan gaskiya sai Allah, ana kuma kira zuwa gare shi, ba waninsa ba. A kuma yi ɗa'a da biyayya ga Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam".* [101]

Sa'annan, idan ba ka sani ba, mafi girman zunubin da aka saɓa ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ta hanyarsa, shi ne Shirka. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Lalle haƙiƙa, Shirka zalunci ce babba".* An kuma tambayi Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cewa: *"Wane zunubi ne wanda babu kamarsa?"* Sai ya karɓa da cewa: *"Shi ne ka sanya ma Allah kishiya alhali shi ne ya halicce ka".* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[102] A wani wurin kuma Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa: *"Ku saurara! Zan ba ku labarin mafi girman zunubai. Ko kuna so?"* Sahabbai suka karɓa da cewa: Eh! Ya

---

[101] *Al-Fatawa* 15/24.

[102] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (4207) 4/1626, da *Sahih Muslim,* Hadisi na (86) 1/90 daga Abdullahi ɗan Mas'ud *Radhiyallahu Anhu.*

Manzon Allah. Sai ya ce, shi ne: *"Yi wa Allah kishiya, da ƙin uwaye".* Buhari da Muslimu suka riwaito shi.[103]

Kai! Bari. Shirka da kake ji, kake kuma gani ya kai ɗan'uwa babban bala'i ce, da yake ruguza *Rububiyyah* ya nakkasa *Uluhiyyah,* kuma munana zato ne ga Ubangijin talikai. Saɓo ce mai tsananin muni, saboda daidaitawa ce ake ƙoƙarin yi tsakanin Allah Mahalicci, mai cika da kamala a cikin siffofinsa, mai girma da ɗaukaka. Daidaitawa ce tsakaninsa da bawa, mahaluki nakasasshe. Saboda haka duk wanda ya kasa tabbatar da kaɗaituwar Allah a matsayin Ubangiji, wato, *Uluhiyyah.* To, tauhidinsa na *Rububiyyah* ba zai daɗa masa komai ba. A wata Hausa, yau da mutum zai yi imani cikakke da zaman Allah abin bauta, *Tauhidin Rubibiyyah,* amma kuma yana zuwa wurin ƙaburbura yana roƙon na kwance, alhali su ba Uwayengiji ba. Ko, ya yi wani alwashi a wurin su a matsayin fadanci zuwa gare su. To, ko shakka babu, irin wannan mutum ya faɗa a cikin *Shirkul-akbar, Shirka* wadda babu irinta.

Shirka da Allah, ba komai take nufi ba illa: ***"Kiran wani",*** wanda ba Allah ba: ***"Tare da shi".*** Wato, a wayi gari mutum yana nema, ko roƙo ga Allah, kuma yana yi ga kuma wani wanda ba shi ba. Ko ya sanya wani waliyyi ko ƙabari, tsakaninsa da Allah ta hanyar kiran sa ko neman taimakonsa, da mayar da hankali zuwa gare shi. Kai! Da dai waɗansu nau'ukan bauta. Idan kuma ka ga dama, kana iya cewa, Shirka ita ce daidaita wanin Allah da Allah a cikin abin da yake haƙƙinsa ne shi kaɗai *Subhanahu wa Ta'ala.*

Duk wanda ya yi rashin arzikin mutuwa a kan Shirka, to, fa lalle, ya gama cancantar shiga wuta; Aljanna kuma ta haramta gare shi har abada. Ga abin da Mabuwayin Sarki yake cewa: *"Ai, yadda al'amarin yake! Duk wanda ya yi wa Allah kishiya, tabbas lalle, Allah ya haramta masa Aljanna; makomarsa kuma ita ce Wuta. Kuma babu wasu mataimaka ga azzalumai".* Mai tsira da amincin Allah kuma ya ce: *"Duk wanda mutuwa ta riska yana kiran wani, kishiya, koma bayan Allah, ya gama shiga Wuta".* Buhari ne ya

---

[103] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (5631) 5/2229, da *Sahih Muslim,* Hadisi na (87) 1/19. Daga Sayyidi Abubakar *Radhiyallahu Anhu.*

riwaito.[104] ***"Dalili a kan haka;"*** cewa, mafi girman abin da Allah Ta'ala ya yi umurni da shi, shi ne Tauhidi. Mafi girman kuma abin da ya yi kashedi da shi, shi ne Shirka: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma ku bauta ma Allah, kada ku haɗa shi da komai".*** Kada ku naɗa masa kiyoshi, ko takwarori, ko makwafai, komai girma ko ƙanƙantarsu. Ku dai ku yi nesa-nesa da Shirka da duk abin da yake haifar da ita.

Saboda haka ya zama wajibi ga bawa, ya inganta imaninsa da Allah Maɗaukakin Sarki. Ya kuma kafirce ma duk wani abu koma bayansa; kiyoshi da takwarori. Dalili kuwa shi ne, farkon abin da aka umarci bayi da shi, shi ne bauta ma Allah Maɗaukakin Sarki tare da kaɗaita shi. Farkon kuma abin da aka hane su da shi, shi ne yi masa kishiya. Karshe kuma sai Buwayayyen Sarkin ya kawo sauran wajibbai da cewa: *"Kuma ga mahaifa ku yi kyautatawa, kuma ga ma'abucin zumunta da marayu da matalauta, da maƙwabci ma'abucin kusanta, da maƙwabci manisanci, da aboki a gefe da ɗan hanya, da abin da damanku suka mallaka".* Ko shakka babu kuma, irin wannan tsari na alƙur'ani, inda ayoyi suke buɗewa da horo da Tauhidi, alama ce da take nuna muhimmacinsa, da kuma mummunan matsayin da Shirka take da shi.*

---

[104] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (3227) 1636 daga Abdullahi ɗan Mas'ud *Radhiyallahu Anhu.*

## SHIKA-SHIKAN AKIDAR MUSULUNCI GUDA UKU

### SHISHSHIKE NA FARKO: MU SAN ALLAH

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ce:*

*"To, idan aka tambaye ka shika-shikan Aƙidar Musulunci uku, waɗanda saninsu ga mutum yake wajaba. Sai ka karɓa da cewa, su ne: Bawa ya san Ubangijinsa, da Addininsa, da Annabinsa Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam. Idan kuma aka sake tambayarka cewa: Wane ne Ubangijinka? Sai ka karɓa da cewa: Ubangijina shi ne Allah, wanda ya rene ni, ya kuma reni gaba ɗayan halittu da ni'mominsa. Shi ne kuma abin bautata; ba ni da wani abin bauta in ba shi ba. Dalili kuma akan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai". Duk kuwa abin da ba Allah ba, to, yana ƙarƙashin kalmar talikai. Ni kuwa ɗaya ne daga cikinsu. Idan kuma aka sake tambayarka cewa: Ta wace hanya ce ka gane Ubangijinka? Sai ka karɓa da cewa: Na gane shi ne ta hanyar ayoyinsa da halittunsa. Daga cikin waɗannan ayoyi nasa kuwa akwai dare da wuni, da rana da wata. Daga cikin halittunsa kuma, akwai sammai bakwai, da ƙassai bakwai, da abin da yake cikinsu, da abin da yake tsakaninsu. Dalili a kan haka kuwa shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma daga cikin ayoyinsa akwai dare da wuni, da rana da wata. Kada ku yi sujada ga rana ko wata. Ku yi sujada ga Allah, wanda ya hahalicce su idan kun kasance, shi, kuke bauta wa". Da kuma faɗarsa: "Lalle haƙiƙa, Ubangijinku Allah ne, wanda ya halicci sammai da ƙasa a cikin kwanaki shida, sa'annan ya ɗaukaka a kan al'arshi. Yana sanya dare ya rufe wuni, yana nemansa da gaggawa, kuma rana da wata da taurari horarri ne da umurninsa. To, shi ke da halittar kuma shi ke da umurnin. Albarkar Allah Ubangijin talikai ta bayyana!"*

*Dalili kuma akan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ya ku mutane! Ku bauta ma Ubangijinku, wanda ya halicce ku da waɗanda*

*suke a gabaninku, ko da za ku kare kanku! Wanda ya sanya muku ƙasa ta zama shimfiɗa, sama kuma ta zama gini, ya kuma saukar da ruwa daga sama, sa'annan ya fitar da abinci daga 'ya'yan itace game da shi, saboda ku. Saboda haka, kada ku sanya ma Allah wasu kishiyoyi, alhali kuna sane". Ibnu Kathir Rahimahullah ya ce: Wanda ya halicci waɗannan abubuwa shi ya cancanci a bauta masa".*

Malamin ya ci gaba da cewa, ya zama wajibi a kan kowane *mukallafi,* namiji da mace, ya san waɗannan manya-manyan shika-shikai guda uku. Su ne farkon abin da za a tambayi bawa a kan su a cikin ƙabarinsa. Idan ya bayar da gamsasshiyar amsa, to, ya tsira. Idan kuma ya yi ɓatan kai, ya halaka.

*"To, idan aka tambaye ka: Shika-shikan Aƙidar Musulunci uku,*[105] *waɗanda saninsu ga mutum yake wajibi? " "Sai ka karɓa da cewa, su ne;":*

*Na farko: Sanin Ubangiji:*

Wannan shishike kuwa shi ne asali kuma tushe ga sauran biyun. Hakan ya zama wajibi domin bawa ya iya bauta ma Ubangijin nasa *ala basiratin wa yaƙinin.* A nan ne mutum yake sanin Ubangijin nasa ta hanyar abubuwan da ya sifaita kan sa da su a cikin littafinsa, kuma ta harshen Manzonsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, waɗanda suka ƙunshi bayani a kan kaɗaituwar Allah, da ayyukansa, da sunayensa da kuma siffofinsa.

*Na Biyu: Sanin Addini:*

Shishshike na biyu, shi ne bawa ya san: ***"Addininsa",*** wanda Allah Maɗaukakin Sarki ke son mu bauta masa ta hanyarsa. Wato, aikata abin duk da ya wajabta mana aikatawa, da nisantar wanda ya wajabta mana nisanta.

---

[105] Littafin *Al-Usul Ath-Thalatha* "Shika-shikan Aƙidar Musulunci Uku" ya soma ne daga nan. Sauran duk abin da ya gabata na saƙonni rubuce-rubuce ne da Shehin Malamin ya yi, almajiransa suka yi shimfiɗa da su a gaban littafin nasa don sharar fage. Wanda ya ba ni wannan labari shi ne babban malamin nan dattijo; Salihu bn Gusn, Allah ya jiƙan sa.

***Na uku: Sanin Annabi Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam:***

Saboda shi ne jakada tsakanin mu da Allah a cikin isar da manzanci. In kuwa ba dominsa ba, babu wata hanya da za mu iya sanin yadda za mu bauta ma Ubangijinmu da ita.[106]

Waɗannan shika-shikai guda uku, sun tattara gaba ɗayan abin da ake kira addini, wato, sani da gane ko waye Ubangijinka a matsayinka na bawa? Mene ne addinin da ya aiko maka? Wane ne kuma Annabinsa da ya aiko maka saƙon addinin ta hanyarsa? Waɗannan tambayoyi, kamar yadda aka faɗi a baya kaɗan, su ne za a fuskanci bawa da su da zarar ya samu kansa a cikin ƙabari. Sai dai sanin lafuzzansu amsoshinsu kawai, ba tare da imani da su, balle aiki da abin da suka ƙunsa ba, ba ya kuɓutar da bawa daga azaba. Abin da kawai zai tserar da shi, shi ne imani da aiki da su. Da hakan ne kawai bawa zai iya kuɓuta a lokacin waɗannan tambayoyi. Idan aka kalli Hadisin Abbas ɗan Abdulmuɗɗalabi *Radhiyallahu Anhu,* za a ga cewa, ya ambaci gaba ɗayan waɗannan shika-shikai a dunƙule, inda yake cewa, lalle ya ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa: *"Duk wanda ya yarda da Allah shi ne Ubangiji, Musulunci kuma shi ne addini, shi kuma Muhammadu Manzon Allah ne, to, ya ɗanɗani zaƙin imani".* Muslim ne ya riwaito shi.[107] Ta kuma tabbata cewa, duk wanda ya yarda da waɗannan shika-shikai guda uku, ya kuma furta su da gaske a bayan mai kiran sallah ya ce: *"Ash-hadu anna Muhammadan rasulullah".* To, an gafarta masa gaba ɗayan zunubansa. Muslim ne ya riwaito shi.[108]

Bayan haka kuma, Malam Abdullaɗif[109] ɗan Abdurrahman ɗan Hassan *Rahimahullah* yana cewa: *"Yarda da amincewa da waɗannan shika-shikai uku,*

---

[106] Idan aka lura da kyau za a ga cewa mawallafin wannan littafi *rahimahullahu* ya ambaci waɗannan shika-shikai uku jumlace a farko. Daga bisani kuma ya dawo ya yi musu ɗauki ɗai-ɗai. To, ya yi haka ne ba domin komai ba, sai domin fa'idar aikin ta zamo gamamma, mai karatu kuma ya sami nishaɗi da ƙwarin guiwa. Wato, idan ka riga ka san shika-shikan a dunƙule, daki-daki, ka kiyaye su, to, yawun bakinka zai ci gaba da tsiyaya don ƙoƙarin sanin ma'anarsu.

[107] *Sahih Muslim,* Hadisi na (34) 1/62 daga Abbas ɗan Abdulmuɗɗalabi *Radhiyallahu Anhu.*

[108] *Sahih Muslim,* Hadisi na (386) 1/290 daga Sa'ad ɗan Abi Waƙƙas.

[109] Shi ne kakan Malam Muhammad bn Ibrahim *rahimahumallahu.*

*shi ne jijiyar addini, a kan su ne kuma gaba ɗayan tabbatattun al'amurra na ilimi da yaƙini suke karakaina".*[110] *

Daga nan kuma sai mawallafin ya shiga warware zare da abawar waɗannan shika-shikai uku ɗaya bayan ɗaya, inda ya fara da shishshike na farko, wato, sanin bawa ga Ubangijinsa, ya ce: ***"Idan kuma aka sake tambayarka",*** da: ***"Cewa: Wane ne Ubangijinka?"*** wanda kake bauta, mahaliccinka, mai azurtaka, wanda ba ka da wani abin bauta koma bayansa? ***"Sai ka karɓa",*** wa mai tambayar: ***"Da cewa: Ubangijina",*** wanda nake bauta: ***"Shi ne Allah;"*** ba na bautar kowa sai shi. Ba ni kuma karkatar da wani sashe na bautar zuwa ga waninsa. Ba na ruku'u, ba na yanka, ba na alwashi, ba na ɗawafi, sai domin Allah kawai. Ya kuwa za ta yiwu in kafirce ma Allah Maɗaukakin Sarki, in bauta ma waninsa! Alhali, shi ne: ***"Wanda ya",*** samar da ni daga babu, kuma ya: ***"Rene ni",*** da ni'imominsa na bayyane da na ɓoye, Ya yaye baƙin cikina. Ya kuma maƙare rayuwata da ni'ima. Ya zazzaga mani alherai iri iri, tsarki ya tabbata gare shi da ya ce: *"Da za ku lissafa ni'imomin Allah, ba za ku iya ƙidaye su ba".*

Kai ba ni kawai ba, shi ne wanda: ***"Ya reni gaba ɗayan halittu da ni'mominsa",*** ta hanyar yi musu ƙawanya da ni'imomi marasa da iyaka. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*:

*"Kuma babu wata dabba a cikin ƙasa face arzikinta na wurin Allah".*

Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *Kalmar 'Rabbu' tana nufin mai reno, Allah Mahalicci, mai azurtawa, mai taimako, mai kuma shiryarwa. Wannan suna kuma ya fi komai cancanta da a nemi agaji da kowane irin taimako daga gare shi".* [111] Tabbas, ya fi cancanta da haka domin shi ne ya samar da mutum, bayan an ɗauki wani lokaci mai tsawo cikin duniyar babu; babu ko masosonsa. Tabbacin haka shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Lalle ne wata mudda ta zamani ta zo a kan mutum, bai kasance komai ba wanda ake ambato".* Wato, bai kasance samamme ba; yana can matsayin *lashai'a.* Daga baya ne Allah Ta'ala ya samar da shi, ya azurta shi domin ya

---

[110] *Ad-Durarus-Saniyya* 8/355
[111] *Al-Fatawa* 14/13

bauta masa shi kaɗai. Wannan Ubangiji: ***"Shi ne, kuma abin bautata",*** wanda babu wani nau'i na ibada da nake karkatarwa zuwa ga wani ba shi ba. ***"Ba ni da wani abin bauta",*** da nake ƙasƙantar da kai, da fuskanta da kowace irin bauta zuwa gare shi sai shi kaɗai. Na wadatu da shi a matsayin abin bauta macancanci.

***"Dalili kuma a kan haka",*** cewa Allah ya zuba wa mutum da sauran halittu, manya-manyan ni'imomi waɗanda ba su da iyaka: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki",*** a cikin aya ta farko a cikin littafinsa mai girma wadda ita ce Fatiha mabuɗin Kur'ani: ***"Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai",*** wato, yabo a kan abubuwan madalla tare da ayarin so da ƙauna da ban girma.[112] Sun tabbata ga Allah abin bauta bisa cancanta. A matsayinsa na: ***"Ubangijin talikai;"*** Mahalicci, mai azurtawa, mamallaki mai kuma hukunta gaba ɗayan al'amurran mutane da aljanu da Mala'iku da sauran halittu baki ɗaya.

***"Duk kuwa abin da ba Allah ba to, yana ƙarƙashin kalmar talikai".*** Allah kaɗai shi ne Mahalicci. Su kuwa 'talikai' an ambace su da wannan suna ne, saboda su alama ce da take nuna samuwar mahalicci kuma mamallaki, wanda ya samar da su. ***"Ni kuwa ɗaya ne daga cikinsu",*** haka ma sauran halittu. Dukanmu kuma muna da buƙata da Allah Maɗaukakin Sarki domin biyan buƙatunmu, da yayewar baƙin cikinmu. Shi kaɗai ne Mamallakin halitta, mai azurtawa da sarrafa al'amarinta. Saboda haka shi ne kawai ya cancanci a bauta masa, koma bayan waninsa. Wannan shi ne ma'anar *Ikhlasi.**

***"Idan kuma aka sake tambayar ka cewa: Ta wace hanya ce ka gane Ubangijinka? Sai ka karɓa da cewa: Na gane shi ne ta hanyar ayoyi",*** irin nasa waɗanda suke matsayin alamomi da dalilai, waɗanda mizaninsu yake tabbatar da kasancewar Allah Maɗaukakin Sarki Makaɗaici a matsayin Ubangiji abin bauta. Na kuma gane shi ne ta hanyar nazarin ***"Halittunsa",*** manya-manya waɗanda ya samar bayan a da can babu su, ya kuma hukunta su zama masu nuni zuwa ga samuwarsa. Sai kawai aka wayi gari babu wata halitta a bayan

---

[112] Duk wannan ana ƙoƙarin fassara ma'anar da *'alif'* da *'lam'* suke ɗauke da ita, ta kaiwa matuƙa a cikin abin da suka yiwa zagi, wato godiya.

ƙasa komai ƙanƙatarta, face tana nuni a kan kasancewarsa makaɗaici. Wani mai hikima yana cewa:

*Ka kalli zati da zubin halitta,*
*Za ka tabbata cewa wasiƙu ne,*
*Daga Sarkin Sarakuna zuwa gare ka.*
*Haƙiƙa an shirya tsarin wannan halitta,*
*A kan nuna duk abin da ba Allah ba, holoƙo ne.*

Ko shakka babu kyakkyawan nazari a cikin halittar duniya abu ne da yake daɗawa tare da ƙara ƙarfin imani, yake kuma dabaibaye zuciya a cikin son Allah *Subhanahu wa Ta'ala*. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Mafi kyawon numfashin da aka yi a rayuwa shi ne wanda aka yi ana zurfafa tunani a cikin ayoyin Allah da halittunsa masu matuƙar ban mamaki, da kuma cirata daga wannan matsayi zuwa na nutsar da zuciya da himma a cikin kogin son Allah shi kaɗai ba tare da wani abin halitta ba".* [113]

***"Daga cikin waɗannan ayoyi nasa",*** masu girma da ɗaukaka, waɗanda ake iya gani da ƙwayar idaniya, suke kuma nuni zuwa ga kaɗaitarsa ***"Akwai dare",*** da yadda yake nufatowa: ***"Da wuni",*** da yadda yake gushewa; ba su haɗuwa da juna a cikin lokaci ɗaya. A maimakon haka, sai dai su riƙa biyar sawun juna ba tare da wata tazara ba; wannan na gushewa sai wancan ya maye gurbinsa. A haka sai suka zama wasu baƙi a gare mu, ɗaya na bankwana, ɗaya na sallamar shigowa. Wannan tsari kuwa gaba ɗayansa horewa ce ta Allah Maɗaukakin Sarki zuwa gare mu.

Harwayau kuma daga cikin waɗannan ƙasaitaccin ayoyi na Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, waɗanda suke nuna kasancewarsa Makaɗaici, mai hukuncin da babu na biyunsa: Akwai: ***"Rana",*** wadda take ita ce fitilar duniya: ***"Da",*** kuma: ***"Wata",*** shi ma mai haskawa a cikin duhun dare. Su biyun nan waɗansu ayoyi ne masu gudana a kan wani cikakken tsari a sasannin halitta guda biya; wannan tana hudowa a nan, sai wancan ya faɗi a can. Babu kuma wata rana, wadda a cikinta suka sake wannan gagarumin tsari mai matuƙar ban

[113] *Miftah Dar As-Sa'adah* 1/122

mamaki da inganci; ba kasawa ba kuma wuce wuri. Ba kuma yadda za a yi wani ya taras da wani balle a samu takin saƙa. A kan haka ne Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: *"Rana ba ya kamata a gare ta, ta riski wata. Kuma dare ba ya kamata a gare shi ya zama mai tsere wa wuni, kuma dukansu a cikin sarari guda suke yin iyo".* A haka, har abada, tsarin ɗaya daga cikinsu ba zai canza ba. Saboda tsari ne na Allah Mabuwayi Mai cikakken sani.

Wannan halitta ta rana da kake gani, tattare da irin yadda take da girma, idan ta faɗi, tana sujada ne a ƙarƙashin Al'arshi. Tabbacin wannan shi ne faɗar Abu Zarri *Radhiyallahu Anhu,* cewa: *"Wata rana na kasance tare da Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam a cikin Masallaci daidai lokacin faɗuwar rana. Sai ya ce mani: Ya kai Aba Zarrin! Ko ka san inda rana take faɗuwa? Sai na karɓa masa da cewa: Allah da Manzonsa ked a sani. Sai ce: Ai ba ta zamewa ko ina sai ƙarƙashin Al'arshi tana mai sujada. Wannan shi ne ma'anar faɗar Allah Subhanahu wa Ta'ala da ya ce: "Kuma rana tana gudana zuwa ga wani matabbaci nata. Wannan ƙaddarawar Mabuwayi ne, Masani".* Buhari ne ya riwaito shi.[114] Takan kuma nemi izinin Ubangiji aduk safiya idan za ta hudo. Abu Zarri *Radhiyallahu Anhu,* yake cewa a kan haka: *"Na shiga masallaci wata rana, na taras da Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam yana zaune. Bayan da rana ta faɗi, sai ya tambaye ni: Ya kai Abu Zarri! Ko ka san inda ranar nan take tafiya? Sai na karɓa masa da cewa: Allah da Manzonsa ke da sani. Sai ya ce mani: Ai tana tafiya ne ta yi sujada ta nemi iznin Ubangijinta, sai kuwa a yi mata. Wato, kamar an ce mata: Koma ta inda kika fito. Sai kawai a ga ta sake hudowa bayan ta faɗi".* [115] A lahira kuma sai a shafe haskenta a tattara shi wuri wuri ɗaya. Wannan shi ne fashin baƙin da Malam Ibnu Jarir *Rahimahullah* ya yi ma faɗar Allah Ta'ala cewa: *"Idan rana aka shafe haskenta",* wato, aka tattara shi wuri ɗaya, aka naɗiye, a kuma ya da ita wani wurin daban. To, da zarar an yi mata haka sai hasken nata ya bice.[116]

[114] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (3027) 3/1170.
[115] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (6977) 6/2700
[116] *Tafsir Aɗ-Ɗabari* 30/2700.

***"Daga cikin halittunsa kuma",*** masu girma: ***"Akwai sammai bakwai",*** masu faɗi da girman gaske: ***"Da",*** kuma: ***"Kassai bakwai",*** masu matsanancin faɗi da yawan albarka: ***"Da",*** kuma: ***"Abin ba yake cikinsu",*** waɗanda suka haɗa da taurari manya da ƙanana, da ayoyi masu ban tsoro. Da abin da yake cikin waɗancan ƙassai bakwai, kamar duwatsu, da gulabe, da dangogin halittu, da suka haɗa da dabbobi, da tsirrai, da sauran halittu samammi. ***"Da abin da yake tsakaninsu",*** sammai da ƙassan, wanda ya haɗa da iska da wasu abubuwan na daban. Kai! Da kuma irin yadda aka tsara kaiwa da komowarsu daga wannan wuri zuwa wancan a cikin sararin samaniya. Da kuma abubuwan amfani da suka samu a gabansu ba tare da sun sansance ba, kamar musayar zance da wasu mahalukai takwarorinsu da suke wata duniya. *Fasubhanallahi Rabbil-Arshil-Azim.*

Ko shakka babu! Ya kamata ga kowane musulmi ya yi mazari mai zurfi a cikin ayoyin Allah da sauran halittunsa. Ibnu Juzayyi daga cikin Malaman Malikiyya - Allah ya jiƙan sa - na cewa: *"Zurfafa tunani shi ne albarkar kowane irin hali da matsayi. Wanda duk ya yi nazarin girman Allah, zai girmama shi albarkar haka. Wanda kuma ya kalli ƙudurarsa, kallo na basira, zai zama mai tawakkali saboda haka. Haka, wanda ya yi la'akari da azabar Allah, da kyau, to, zai zama mai tsoronsa, dalilin haka. Wanda kuma ya waiwayi rahamarsa, zai zama cikin masu tsananin fata da ƙaunar samun ta a sakamakon haka. Shi kuwa wanda ya yi tunanin mutuwa, da abin da zai biyo bayanta, to, zai zama mai ƙarancin gurin duniya, kamar yadda wanda tunaninsa ya hasko tulin tarin zunubansa, sai ka taras tsoronsa ga Allah ya tsananta, ya kuma riƙa ganin rashin girman kansa".* [117]

***"Dalili a kan haka kuwa;"*** shi ne cewa, dare, da wuni da rana da wata duk suna cikin ayoyin Allah: ***"Shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma daga cikin ayoyinsa",*** masu nuni a kan cika da kamalar iko, da zamansa Makaɗaici, da ƙarfin hukuncinsa, da faɗin mulkinsa, da mayawaiciyar rahamarsa zuwa ga bayinsa: ***"Akwai dare",*** wanda duhunsa yake da tabbataccen amfani a rayuwa, da natsuwa da sararawar da halittu suke yi a

[117] *Alƙawanin Al-Fiƙhiyya,* na Ibnu Juzayyi, shafi na 284.

cikinsa: *"Da",* kuma: *"Wuni",* shi ma wanda hasken da yake ɗauke da shi mai amfani ne ga halittu domin a cikinsa ne suke kaiwa da komowa. *"Da rana da wata",* halittu biyu da rayuwar bayi ba ta inganta sai tare da su.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ci gaba da cewa: *"Kada ku yi sujada ga rana ko wata".* Ababen halitta ne su, da aka samar domin hidima gare ku. Saboda haka babu ɗaya daga cikin su da ya cancanci a yi masa sujada. A maimakon haka: *"Ku yi sujada ga Allah",* shi kaɗai; ba ga waninsa ba domin shi ne: *"Wanda ya halicce su",* tattare da wannan girma da suke da shi. Wannan, ba yinsu ne ba; daga Mahaliccinsu ne. ku yi sujada zuwa gare shi: *"Idan kun kasance, shi",* Allah ne kaɗai *"Kuke bauta ma".* To, ku taƙaita wannan bauta taku gare shi kawai, da zuciya ɗaya.

Wani dalilin kuma da yake tabbatar da kasancewar sammai bakwai da ƙassai bakwai, daga cikin halittun Allah Maɗaukakin Sarki, da suke nuni zuwa ga samuwarsa, shi ne *"Faɗar Allah: "Lalle haƙiƙa, Ubangijinku shi ne Allah, wanda ya halicci sammai da ƙasa",* da abin da yake a tsakanin su, ya kyautata ya kuma inganta halittarsu: *"A cikin kwanaki shida",* waɗanda suka fara da ranar Lahadi, suka ƙare da ranar juma'a. *"Sa'annan",* bayan kammala halittar su, ya samar da duk abin da ya yi nufin samarwa a cikinsu, sai: *"Ya ɗaukaka a kan al'arshi",* mai girma, wanda faɗinsa ya yalwaci sammai da ƙassai da abin da yake a cikinsu, da tsakaninsu, ɗaukaka irin wacce ta dace da girmansa.

Sa'annan kuma Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Yana sanya dare",* mai tsananin duhu: *"Ya rufe wuni",* tattare da haskensa. Sai, a wayi gari duhun ya mamaye gaba ɗayan fuskar ƙasa; duk wanda yake a cikin ta ya ci gaba da rayuwa a cikin sa. Kowa kuma sai ya nemi wurin sararawa da hutawa, sauran halittu kuma, kowa ya kama nasa gaba; ya nemi masaukinsa. Kowane daga cikin dare da wunin: *"Yana neman",* ɗan'uwan: "*Sa, da gaggawa".* Da zarar wuni ya kawo jiki, sai dare ya kama gabansa. Haka idan dare ya yi sallama, sai wuni ya yi bankwana. Irin wannan take sawu da waɗannan halittu suke yi ma juna, babu ƙosawa, ba gajiya, ko kasawa a cikinsa ko *misƙala-zarratin.* Haka abin zai ci gaba da gudana har ranar da Allah zai naɗe ƙasa, gaba ɗayan bayi su cirata zuwa gidan tabbata.

Haka: ***"Kuma rana da wata da taurari",*** na tsaye da masu tafiya: ***"Horarri ne da umurninsa",*** da hukuncinsa, da ilimi da kuma hikimarsa. ***"To, shi ne da hallitar",*** gaba ɗayanta, wadda daga gare ta ne aka samu sauran halittu *jumlatan.* A cikin wannan halitta ce kuma tasa, hukunce-hukunensa na tsarin halitta, na azaliyya suke bayyana. Haka: ***"Kuma",*** shi ne: ***"Da umurnin".*** Tabbas! Gaba ɗayan al'amurra da suka shafi dokoki da Annabta ƙarƙashin ikonsa suke. A nan ne kuma gaba ɗayan hukunce-hukuncen Allah *Subhanahu wa Ta'ala* na addini da Shari'a suke ƙunshe. ***"Albarkar Allah Ubangijin talikai ta bayyana",*** a cikin irin waɗannan albarkoki na ƙarshe da ya samar. Tabbas, Allah shi ne wanda alherinsa ba ya misaltuwa ko kimantuwa. Mai girma da ɗaukaka da albarka ne a karan kansa, cikin abin da ya shafi siffofinsa, da zamansu ƙasaitacci. Wannan albarka kuma ta yi naso a cikin sauran halittu, ta hanyar saukar alheri da albarka masu yawa a cikinsu. Tabbas! Allah Maɗaukakin Sarki shi ne: ***"Ubangijin Talikai",*** wanda yake yi musu ni'ima da falala irin waɗanda ba su da iyaka.*

***"Ubangiji kuwa",*** wanda ya halicci waɗannan halittu masu girma, waɗanda suka haɗa da sammai bakwai, da abin da yake ciki da tsakaninsu, a matsayinsa na mamallakinsu, mai tsara hukuncinsu, wanda kuma ya sifantu da siffofin cika da kamala: ***"Shi ne abin bauta;"*** wanda ya cancance ta shi kaɗai, koma bayan waninsa. Duk kuma abin da ba shi ba halitta shi ya yi, shi ne kuma Ubangijinsa. Sakamakon haka kuwa, kowane mahaluki na cike da mummunan rauni, ta yadda bai iya taɓuka ma kan sa komai; samarwa ko tunkuɗewa.

Daga cikin dalilan da ke tabbatar da kaɗaicinsa da cancantarsa ga bauta akwai ***fadar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ya ku mutane!"*** mazanku da mata: ***"Ku bauta ma Ubangijinku",*** ku kuma kaɗaita shi. Ku sani shi ne wanda yake saukar muku da ni'imomi na zahiri da baɗini. Kafin haka, shi ne kuma: ***"wanda ya halicce ku",*** ya samar da ku daga babu, ku: ***"Da waɗanda suke a gabanin ku".*** Kamar irin haka ne ya halicce su, bayan a da can su ba komai ba ne. Ya kuma ja hankalinku ne, zuwa ga waɗannan ni'imomi masu girman daraja nasa na mahalicci, a wayi gari kuna biyayya ga umurninsa, kuna kuma nisantar haninsa. Shi ne kuma: ***"Wanda ya sanya muku ƙasa ta zama shimfiɗa",***

yalwatacciya domin ku iya samun natsuwa a birbishinta, ku gudanar da rayuwarku cikin aminci ba tare da fargaba ba.

***"Sama kuma",*** ya halitta ta a cikin sifar: ***"Gini",*** mai rufi wanda aka kifa a birbishinku. Bayan haka ya ƙawata shi da fitilu, da alamomi, waɗanda kuke ɗaukar hannu ta hanyarsu a lokacin da kuke tafiye-tafiye a cikin duhun dare a kan tekuna da tuddai. Ya kuma ba ta kowace irin kariya. Sai kawai aka wayi gari sama tana yi muku inuwa, ƙasa kuma tana ɗauke da ku, duk ba tare da wata ja-in-ja tsakanin ku da ɗayansu ba.

***"Ya kuma saukar da ruwa",*** mai tsananin daɗin ɗanɗano da albarka: ***"Daga",*** cikin giragizai, waɗanda suke a: ***"Sama, sa'annan ta hanyar ruwan ya fitar da abin ci daga 'ya'yan itace",*** wannan ruwa, nau'uka daban-daban, waɗanda suka haɗa da dabino, da sauran 'yan'yan itace, da shuke-shuke, masu daɗi, da matara kama da su. Duk: ***"Saboda ku"*** samu warwara da jin daɗi da waɗannan ni'imomi, su kuma zama wani agaji da taimako a gare ku, a kan yi masa ɗa'a.

Duk kuwa Mahaliccin da yake samar da waɗannan ni'imomi, to, babu wanda ya cancanci bauta shi kaɗai, sai shi. Saboda haka ku gode, yadda yake faɗa *Subhanahu wa Ta'ala* cewa: ***"Saboda haka, kada ku sanya ma Allah kishiyoyi",*** da abokan tarayya, da tamka a cikin bauta: ***"Alhali kuna sane",*** da cewa yin haka ɓarna ne; ba su cancanci bauta ba ko alama. Ah! Wai to, ya ma za a yi ku bauta masa tare da waɗansu uwayengiji, alhali kuna da wannan masaniya? Tambaya. Wannan irin tarnaƙi shi ne mafi girman dalili, irin wanda hankali komai kaifinsa ba zai iya tunkuɗewa ba, a kan kasancewar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* Makaɗaici, da zaman Shirka, ɓarna.[118]

---

[118] Wannan aya ta haɗa hancin abubuwa biyu ne; umurni da bauta ma Allah shi kaɗai, da hani ga bauta ma wanda ba shi ba. Domin tabbatar da haka ne, Buwayaayyen Sarki ya kafa ma kafirai hujja, a cikin wannan aya, da abin da suka daɗe da sani da yarda, na Tauhidin *Rububiyyah*, a kan wanda suke musu, wato, Tauhidin *Uluhiyyah.* Da yawa kuwa Allah Ta'alah, a cikin Littafinsa, yake amfani da wannan Tauhidin *Rububiyyah* domin tabbatar da wajabci da ingancin *Uluhiyyah.* Ashe kenan, Tauhidin *Rububiyyah,* shi ne makami mafi kaifi da ƙarfi da ake tabbatar da Tauhidin *Uluhiyyah* da shi. Ita kuwa ibada, duk irin yadda aka yi ƙwazo a cikin ta, matuƙar ba ta da sanadarin Tauhidi, to, aikin banza ce shafa ma darni mai. Tabbacin haka shi ne, irin yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya ambaci waɗanda suke tsarkakewa tare da bauta

Imamu Abul-Fida'i, Isma'il ɗan Umar: ***"Ibnu Kathir",*** mai Tafsiri: ***"Rahimahullah"*** ya kuma saka shi gidan Aljanna: ***"Ya ce: Wanda ya halicci waɗannan abubuwa",*** ya kuma samar da su daga babu, waɗanda suka haɗa da mutum, da ƙasa, da sama, da abin da yake cikinsu na alherai da tsirrai: ***"Shi ya cancanci a bauta masa".*** [119] Duk abin da kuwa ba Allah Maɗaukakin Sarki ba, sunansa abin halitta, kasashshe, wanda babu wata hanya da yake cancantar bauta da ita. A kan haka ne Buwayayyen Sarkin yake cewa:

> *"Kuma waɗanda kuke kira, ba shi ba, ba su mallakar ko fatar gutsin dabini. Idan kun kira su, ba za su ji kiranku ba, kuma ko sun jiya ba za su iya karɓa muku ba, kuma a ranar Kiyama za su kafirce ma shirkinku, kuma babu mai ba ka labari, kamar wanda ya sani".*

Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ya ce: *"Babu wanda ya cancanci bauta, da gaske, sai wanda a hannunsa ne amfani da cutarwa suke. Wanda kuma duk ake bauta, to, wajibi ne ya mallaki amfani da cuta a hannunsa. Saboda haka ne Allah ya ƙalubalanci waɗanda suke bautar waninsa, alhali babu wani amfani ko cuta a hannunsu".* [120]*

---

masa da zuciya ɗaya a lokacin da suka sami kansu a cikin tsanani, kuma duk lokacin da baƙin ciki ya yi musu ƙawanya, suna ƙudurce cewa, waɗannan gumaka ba bakin komai suke ba; ba su iya yaye musu wannan damuwa. Amma, tattare da gaba ɗayan haka, idan sun tsira sai su koma bin gumakan nan. Allah Maɗaukakin Sarki ya ambace su mushirikai. Kuma duk ibadar da suke yi ma Allah bai ɗauke ta bakin komai ba. *"Idan kuma suka hau jiragen ruwa sai su rinƙa kiran Allah da zuciya ɗaya. Amma, idan ya tsirar da su zuwa tudu, sai kawai a taras suna shirka."* Ashe kenan, duk wanda ya yi biyayya ga gaba ɗayan Horace-horacen Allah Maɗaukakin Sarki ta hanyar ƙin karkatar da wani sashe nasu zuwa ga waninsa, to, shi ne ma'abucin Tauhidi.

[119] *Tafsir Al-Alƙur'an Al-Azim* na Ibnu Kathir (1/88). Abin kuma da wannan fashin baƙi nasa yake nufi, shi ne: Kasancewar Allah Maɗaukakin Sarki Mahalicci, Mamallakin wannan gida na duniya da gaba ɗayan abin da yake tsugune a cikinsa, mai kuma arzutawa. Waɗannan sifofi ne suka cancantar da shi zama abin bauta shi kaɗai *wahdahu la sharika lahu.*

[120] *Bada'i' Al-Fawaid* (3/1).

# MATAKAN ADDININ MUSULUNCI

***Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ce:***

***"Dangogin ibadar kuma da Allah ya yi umurni da su, su ne: Musulunci, da Imani, da Ihsani. Daga cikin ibada kuma akwai Addu'a, da Kauna, da Tawakkali, da Kwaɗayi, da Fargaba, da Kanƙan da kai, da Tsoro, da Komawa, da Neman Agaji, da Neman Tsari, da Yanka, da Alwashi, da makamantansu daga cikin dangogin ibada waɗanda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi umurni da su. Gaba ɗayan waɗannan ibadoji, ba a yinsu ga kowa sai Allah Maɗaukakin Sarki. Dalili kuma a kan haka shi ne faɗar Allah Ta'ala: "Kuma wuraren Sujada na Allah. Kada ku kira wani tare da Allah". Saboda haka duk wanda ya karkatar da wani abu daga cikin waɗannan ibadoji zuwa ga wanin Allah, to, mushriki ne, kafiri".***

Shar'anta wasu nau'uka daban-daban na ibadoji, yana daga cikin falalar da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya yi ma bayinsa, domin su sami kusanci da shi ta hanyarsu. A haƙiƙanin gaskiya kuma mutum bai san ko wacce daga cikin ibadojin ne za ta zama sanadin shigarsa Aljanna ba. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Duk wanda ayyukansa na ibada, waɗanda Allah ya yarda da su, suka yawaita suka kuma bambanta, a nan gidan duniya. To, gwargwadon haka ne ni'imomin da zai samu a gidan Lahira za su yawaita su kuma bambanta. Kamar haka ɗin ne kuma za a riƙa yi ana yi masa ƙari gwargwadon yadda ya rayu a duniya yana ƙari yana daɗi cikin nishaɗi da jin daɗi da ɗoki da kuma annashawa. Da ma yadda al'amarin yake shi ne, Allah Subhanahu wa Ta'ala ya hukunta ma kowane aiki, wanda yake so da wanda yake ƙyama, wani naso da sakamako da ɗanɗano, da kuma raɗa na musamman wanda ya saɓa ma na saura. Bisa wannan dalili ne, jin daɗi ga 'yan Aljanna, da azaba ga 'yan Wuta suka bambanta sakamakon bambancin daɗaɗan abubuwa da azabar da take cikinsu, kowanne. Saboda haka sakamako da jin daɗi da*

*daular da, wanda ya saka hannun jari a cikin ibadoji daban-daban ta sha bamban da ta wanda ya saka hannun jarinsa a cikin nau'in idaba ɗaya tal. Haka azabar wanda ya saka hannun jari a cikin ayyukan saɓon Allah daban-daban ta sha bamban da ta wanda ya saka shi a cikin aikin saɓo ƙwaya ɗaya tal".* [121]

Haka kuma martaba da darajar bawa a wurin Allah Maɗaukakin Sarki, suna ƙaruwa ne a duk lokacin da ya ƙara ƙaimin ibada da bauta masa. Shaihul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Cika da kamala ba za su taɓa samuwa ba ga bawa, sai idan ya dage a cikin bauta ma Allah; duk lokacin da himma da ƙwazon bawa suka ƙaru a cikin ibada, lokacin ne alƙaluman cika da kamalar darajarsa za su ɗaga".* [122]

To, bayan kuma da mawallafin ya bayyana cewa, abin da yake wajaba a kanmu shi ne mu bauta ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* shi kaɗai, sai kuma ya shiga lissafa wasu daga cikin nau'ukan ibada yana mai cewa: ***"Dangogin ibadar da Allah ya yi umurni da su",*** ga bayinsa, su bauta masa ta hanyarsu, suna da yawa ƙwarai, amma ga guda bakwai daga cikinsu a matsayin misali. ***"Kamar: Musulunci, da Imani, da Ihsani".*** Waɗannan ukun kuwa su ne ƙololuwar matakan addini, babu kuma ibadar da ta kai su muhimmanci. Saboda haka ne mawallafin ya fara da su. Musulunci yana da rukunai da suka haɗa da sallah, da azumi. Duk waɗannan sunansu ibada. Haka nan imani da rassansa na zahiri da na baɗini, kamar imani da Allah, da Mala'ikunsa, da Littattafansa, da Manzanninsa, da Ranar Karshe, da imani da ƙaddara mai kyau da maras kyau. Haka nan fargaba, da soyayya, da ƙauna, da dai sauransu. Kai! Duk wani abu da ake yin sa a zuci, sunansa idaba. Hasali ma shi ne mafi girma da ɗaukakar daraja a wannan shafi.

Sa'annan matakin Musulunci shi ne mafi faɗi da yalwa a shafukan addini. Sa'annan matakin Imani yana bi masa. Daga nan sai matakin *Ihsáni.* Nasa shafin shi kuma shi ne mafi zama ƙarami bisa ga sauran. Abin nufi a nan shi ne, waɗanda suke samun damar kai wa ga matakin *Ihsáni* bayin Allah ne 'yan kaɗan. Ta wannan hauji, wannan mataki darajarsa maɗaukakiya ce, mai

[121] *Ijitima' Al-Juyush Al-Islamiyya* shafi na 77.
[122] *Al-Fatawa* 10/176.

kuma girma da tsarkin daraja. Saboda haka ba kowa ne yake samun ta ba, sai waɗanda Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓa ya kuma tsarkake. Shaihul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Ibadojin zuciya da halayenta, kamar son Allah da Manzonsa, tsoron Allah da dogara gare shi. da haƙuri da hukuncinsa, da gode masa, da komawa zuwa gare shi, da tsarkake aiki domin shi, a nan ne darajojin mutane suke sassaɓawa iyakar zarafi, sassaɓawa irin wadda babu wanda ya san miƙidarinta, sai Allah Maukakin Sarki".* [123]

Daga cikin dangogin ibada, waɗanda Allah ya yi umurni da su: ***"Akwai Addu'a",*** da neman biyan buƙata wurin Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: ***"Da Tsoro, da Kauna",*** wato kwaɗayin abin da yake hannunsa: ***"Da Tawakkali",*** ta hanyar mayar da kowane al'amari zuwa gare shi: ***"Da Kwaɗayi",*** a cikin abin da yake hannun Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: ***"Da Fargaba",*** wato, tsoronsa: ***"Da Kanƙan da kai",*** ga Allah ***"Da Komawa",*** ga re shi a cikin dukan komai: ***"Da Neman Agaji",*** wurin sa ***"Da Neman Tsari",*** ta hanyar laɓewa a wurinsa: ***"Da Neman Agaji",*** ta hanyarsa: ***"Da Yanka",*** saboda shi, shi kaɗai. Haka kuma: ***"Da Alwashi". "Da makamantansu daga cikin dangogin ibada",*** daban-daban: ***"Waɗanda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi umurni da su",*** sun kuma haɗa da biyayya ga iyaye, da sadar da zumunta, da girmama baƙo, da kyawawan halaye, da duk abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake so, yake kuma ƙauna, na zantuka da ayyuka na baɗini da na zahiri. Duk waɗannan abubuwa ibada ne. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Ibada suna ne kandamau, wanda ya haɗa duk abin da Allah yake so, ya kuma yarda da shi, na ayyuka da zantuka, na zahiri da na baɗini.*[124] *Saboda ibada ta haɗa gaba ɗayan ayyukan ɗa'a. Ta kuma haɗa da cikakkiyar ƙauna, da cikakkiyar girmamawa, da cikakken kwaɗayi da tsoro da ƙanƙantar da kai, da cikakkiyar biyayya ga abubuwan da Allah yake so, kuma ya yarda. Wannan mataki kuma shi ne mataki na ƙoli, wanda babu na sama da shi".* [125]

---

[123] *Al-Fatawa* 7/409.
[124] *Al-Fatawa* 10/149.
[125] *Madarij As-Salikin* 3/144.

***"Gaba ɗayan waɗannan ibadoji ba a yin su ga kowa sai Allah Maɗaukakin Sarki;"*** bai halatta a karkatar da wani abu daga cikin su, komai ƙanƙantarsa, zuwa ga wanin Allah. ***"Dalili kuma a kan haka shi ne faɗar Allah Ta'ala: "Kuma wuraren Sujada",*** wato masallai da gaɓoɓin jiki, gaba ɗayansu milki ne: ***"Na Allah. Kada ku kira",*** wani ko ku yi sujada da waɗannan gaɓoɓi, kada kuma ku haɗa: ***"Wani tare da Allah",*** a bisa doron ƙasarsa, ko waye shi. Saboda, gaba ɗayan ƙasar ta Allah ce shi kaɗai, sai ku kaɗaita shi, a cikinta, da bauta.

***"Saboda haka duk wanda ya karkatar da wani abu daga cikin waɗannan ibadoji",*** waɗanda mawallafin ya ambata, ko waɗanda bai ambata ba, komai ƙanƙantarsa: ***"Zuwa ga wanin Allah",*** kamar ya kira wani wanda ba Allah ba, daga cikin rayayyu, domin biyan wata buƙata, wadda babu mai iya biyan ta sai Allah. Ko ya kira wasu daga cikin matattu, ko waɗanda suke nesa, ko wasu gumaka, ko itace. Ko ya ji tsoro, ko fatar wani abu daga gare su, ko ya roƙe su biyan wasu buƙatu, ko yayewar wani baƙin ciki, ko wani abu mai kama da haka: ***"To, ya yi Shirki da Kafurci".*** Ya yi Babbar Shirka, da kafirci irin wanda yake fitar da mutum daga Musulunci. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Haƙiƙa kan musulmi ya haɗu sakamakon abin da suka sani maras makawa, a addinin Musulunci, cewa, lalle bawa, ba ya halatta gare shi, ya bauta wa, ko ya kira wani, ko ya nemi taimako daga wani, ko ya dogara ga wani, wanda ba Allah ba. Haka kuma duk wanda ya bauta ma wani Mala'ika makusanci ga Allah, ko wani Annabi da Allah ya aiko, ko ya kira shi, ko ya nemi taimakonsa, to, ya faɗa a cikin Shirki".* [126]

Bambanci tsakanin *'Shirka'* da *'Kafirci'* shi ne, kafirci ya fi faɗi. Wato, duk mushriki kafiri ne, amma ba duk kafiri ne mushriki ba. Wanda duk yake ɗawafi ga ƙabari, ko yake kiran wani ba Allah ba, to, ya zama mushriki. Ana kuma iya kiransa kafiri. Amma. wanda ya tozarta wani abu na addini, sunansa kafiri, amma ba a ce masa mushriki, saboda a haƙiƙanin gaskiya bai yi ma Allah kishiya ba a cikin wannan aika-aikar tasa. Amma, ko shakka babu wannan tozartawa da ya yi ma addini, kafirci ce. Sai dai a Lahira, makomar

[126] *Al-Fatawa* 3/272.

kafiri da mushriki duk ɗaya ce; dukansu za su dauwama ne a cikin Wuta. Allah ya kiyashe mu! Ga hukuncin kowanen su nana a cikin littafin Allah mai girma. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce game da kafirai:

> *"Lalle haƙiƙa, Allah ya la'anci kafirai, ya kuma tanadar musu Wutar Sa'irah".*

Dangane kuma da mushrikai, sai yake cewa:

> *"Sani yadda al'amarin yake, duk wanda ya yi ma Allah kishiya, haƙiƙa, Allah ya haramta masa shiga Aljanna. Makomarsa ita ce Wuta. Azzalumai kuma ba su da mataimaka".*

## HUJJOJI A KAN HANA SHIRKA

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahab ya ce:*

*"Dalili kuma a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki:*

> *"Kuma wanda ya kira, waɗansu abubuwan bautawa na tare da Allah, alhalin ba shi da wani dalili game haka, to, hisabinsa yana wurin Ubangijinsa kawai. Lalle ne, kafirai ba su cin nasara".*

Ya kuma zo a cikin Hadisi cewa: *"Addu'a ita ce ɓargon ibada".*

Kuma Allah Maɗaukakin Sarkiya ce:

> *"Kuma Ubangijinku ya ce: Ku kira ni, zan karɓa muku. Haƙiƙa, lalle, waɗanda suke girman kai daga ibadata, za su shiga Jahannama suna ƙasƙantattu".*

*Kuma Allah Maɗaukakin Sarki:*

> *"Kada ku ji tsoronsu, kuma ku ji tsorona idan kun kasance muminai".*

*"Dalili kuma a kan",* cewa duk wanda ya karkatar da wani abu na ibada zuwa ga wanda ba Allah ba, yayi kafirci da shirka: *"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma wanda ya kira waɗansu ababen bauta tare da Allah,",* daga cikin rayayyu ko matattu, ko gumaka, ko duwatsu, ko waninsu: *"Alhalin ba shi da wani dalili a kan haka",* ma'ana, ba hujja ko madogara ta yin haka. An kawo wannan dabaibayi ne domin a bayyana irin yadda babu wata hujja ga duk wanda ya yi ma Allah kishiya a cikin bauta, illa ɓata da son zuciya, amma ba shiriya da wahayi ba. Duk wanda kuwa ya yi haka, to, haƙiƙa, Allah Maɗaukakin Sarki ya sha alwashin cewa: *"Ba zai tsira ba",* a duniya da Lahira. Kuma shi da ire-irensa, sun tabbata: *"Kafirai",* waɗanda suka bar Musulunci. Wannan aya babban dalili ce, da yake bayyana kafircin duk wanda ya kira Allah ya haɗashi da waninsa. Duk ɗaya ne, wanda aka kira ɗin

Mala'ika ne, ko Annabi ne, ko wani bawan Allah da ke kwance a cikin ƙabarinsa, ko ma dai wani abu na daban.

Bayan da mawallafin – Allah ya jiƙan sa - ya ambaci nau'ukan ibadoji a jumlace, sai kuma ya shiga bayyana hujjoji da dalilai a kan su. Amma, Musulunci, da imani, da *Ihsani*, zai kawo nasu dalilai da hujjoji a cikin shishshike na biyu. A maimakon hakan can, sai ya fara da 'addu'a' wadda ita ce asali kuma tushe ga kowace irin ibada, ya ce: ***" Ya kuma zo a cikin Hadisi cewa"***, addu'a tana daga cikin nau'ukan ibadoji. Ga yadda lafazin Hadisin yake daga Imam At-Tirmidhi.[127] *"Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ce:* ***"Addu'a",*** da roƙon Allah biyan buƙatu: ***"Ita ce ɓargon Ibada",*** wato tsintsarta, wadda Allah Maɗaukakin Sarki ya umarci halittunsa da ita. Wannan Hadisi yana matsayin fashin baƙi ne, ga wani Hadisin da yake cewa: *"Addu'a it ace Ibada".* Manzancin Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya zo ne domin luras da zukata tare da karkatar da su zuwa ga roƙon Allah *Subhanahu wa Ta'ala* shi kaɗai. Su kuma san cewa kira da roƙon wani wanda ba Allah ba, a cikin duk wani abin da ba mai iko a kan sa sai Allah, yana daga cikin nau'ukan Babbar Shirka irin wadda take rusa gaba ɗayan ayyuka. Ya zo a cikin *Ad-Durar As-Saniyyah* cewa: *"Kan gaba ɗayan malamai ya haɗu a kan cewa, duk ya wanda ya sanya wani tsani, tsakaninsa da Allah, wanda yake kira da roƙo da dogaro gare shi, to, haƙiƙa ya zama kafiri".* [128]

Irin wannan Shirka kuwa ta roƙo da kiran wani ba Allah ba, ta fi yawaita a tsakanin halittu, kamar yadda mai *Addurar As-Saniyyah* ya ƙara cewa: *"Daga cikin mafi girman nau'ukan Shirka, mafi kuma yawan faruwa a wannan zamani, akwai ce neman biyan buƙata daga wajen matattu, da neman agajinsu, da kuma mayar da su alƙibla. Wannan kuwa shi ne asalin Babbar Shirka".* [129] ***"Hujja kuma akan haka",*** cewa, kira da roƙo ibada ne, kuma karkatar da su zuwa ga wanin Allah Shirka ne: ***"Ita ce, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki***: ***"Kuma Ubangijinku Ya ce: Ku kira ni",*** ku kai kuka gare ni: ***"Zan karɓa***

[127] Hadisi na (3371) 5/456 daga Anas ɗan Malik *Radhiyallahu Anhu.*
[128] *Ad-Durar As-Saniyyah* 1/196.
[129] *Ad-Durar As-Saniyyah* 1/199.

***muku",*** in share muku hawaye. ***"Haƙiƙa, lalle, waɗanda suke girman kai",*** da kawar da shi: ***"Daga ibadata",*** da roƙona: ***"Za su shiga Wutar Jahannama suna ƙasƙantattu",*** walaƙantattu. Allah dai ya kiyashe mu. A wannan lokaci ne Allah Maɗaukakin Sarki zai saukar musu da kowane irin nau'i na azaba, da ƙasƙanci a matsayin sakamakon ƙin bauta masa shi kaɗai, kamar yadda ya wajabta a kan su.

Duk mai hankali ya san cewa, babu mai yaye baƙin ciki in ba Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ba, saboda shi kaɗai ne mai iko a kan haka, wanda:

> *"Haƙiƙa, al'amarinsa, idan ya so abu, sai kawai ya ce masa zamo, sai kuwa ya zamo".*

Duk kuwa wanda matsayinsa bai wuce na abokin halitta ba, ai, bai kamata, bai kuma dace da akira, a roƙa, a kuma nemi taimako da cetonsa ba, koma bayan Allah *Subhanahu wa Ta'ala.* Tabbas! Bai dace ba saboda shi bawa ne, kuma mai rauni; yana rashin lafiya yana kuma mutuwa. Babu wani abu da yake iya taɓuka ma kan sa na jawo amfani ko tunkuɗe cuta, balle ya iya hakan ga waninsa. Ya kuwa za a yi ya iya? Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"Waɗanda kuke kira koma bayansa, ba su mallakar ko kwatankwacin yanar gurtsin dabino".* Saboda haka, ɗan'uwa a dai dogara ga Allah shi kaɗai. Idan za ka nemi biyan wata buƙata, ka neme ta gare shi; ka roƙe shi zai karɓa. Ka kuma neme shi gafarar zunubanka, zai gafarta maka. Ka kuma kira shi da zuciya ɗaya a cikin *khushu'i*, sai ya saurare ka. Tabbas! Duk wanda ya fuskanci Allah da buƙatunsa, ya kuma dogara gare shi, zuciyarsa ta cika maƙil da son Ubangijinsa. A hannu ɗaya kuma ya kafirce ma duk wani abu da ake bauta, wanda ba Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ba, to, ya tabbata *muwahhidi.**

Wannan mataki na jin tsoron Allah Maɗaukakin Sarki shi kaɗai, yana daga cikin mafi girman ibadu waɗanda ake yi da zuciya. A matsayinsa kuma na wani gagarumin rukuni a layin bauta, tabbatar da shi ya zama wajibi a kan kowane musulmi, domin ba yadda za a yi addini ya zama tatacce saboda Allah, sai da shi. Ita kuwa wannan kalma ta tsoro, tana nufin jin raɗaɗi a cikin zuciya tare da girgizawarta sakamakon hasashe da hangen faruwar wani mugun abu

can gaba.[130] Amma, tsoro irin wanda shari'a take so, shi ne wanda ya hana mutum saɓa ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala.*

A larabce da kuma shar'ance, kalimomi huɗu na tsoro suna da bambanci. Waɗannan kalimomin su ne: *Wajalu da Khaufu* da *Khashyatu* da kuma *Rahbatu.* Shehun Malami Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Alwajalu da Al-khaufu da Al-khashyatu da Ar-rahbatu kalmomi ne makusanta, iri ɗaya ba".*[131] Bambancin da ke akwai tsakanin *'Khaufu'* da *'Wajalu,'* shi ne, ta farko tana nufin ƙonƙonar zuciya a kan wani abu da mutum yake fargaban faruwarsa a kan sa nan gaba. Kamar mutum ya samu tashin hankali da tsoron faɗawa cikin yunwa nan da wata ɗaya. A yayin da kalma ta biyu take nufin, raurawar zuciya da fargabanta a kan wani abu na tsoro da zai faɗa mata yanzu-yanzu. Wato, kamar mutum ya tsinkayi Zaki, sai hankalinsa ya tashi saboda ganin sa kawai da ya yi. To, irin wannan tashin hankali a daidai irin wannan lokaci, shi ake kira *'Al-wajal.'* A yayin da tashin hankalin rayuwa da faɗawarta a cikin fargaban abin da ka iya faɗa mata nan gaba, shi ake kira *'Khaufu.'* Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Al-wajalu' yana nufin girgizar zuciya da karayarta saboda tuna wani abu da yake dugunzuma ta ya azabtar da ita, koko a'a, ga abin garin da garin yana gani a gabanta".*[132]

***"Dalili",*** kuma: ***"A kan",*** cewa: ***"'Tsoro'"*** ibada ne daga cikin jumlar ibadu, wadda karkatar da ita zuwa ga wanin Allah ba ya halatta" ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kada ku ji tsoronsu",*** yana nufin mushrikai, ***"Kuma ku ji tsorona".*** Ni ne Ubangijinku wanda yake taimakon masoyansa, masu tsoro da fargaba zuwa gare shi: ***"Idan kun kasance muminai".***

Ko shakka babu, jin tsoron Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana daga cikin dalilan gyaruwar zuciya. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Ba a taɓa kiyaye iyakokin Allah da haramce-haramcensa ba, masu neman fada gare shi*

---

[130] *Madarij As-Salikin* 1/513, da *Bulgat As-Salik li Aƙrab Al-Masalik* na Sawi 4/438.
[131] *Madarij As-Salikin* 1/512
[132] *Madarij As-Salikin* 1/513.

*kuma, suka samu ba, ta hanyar wani abu, kamar yadda hakan ta tabbata ta hanyar jin tsoro da fatar samun alheri da ƙaunar Allah Subhanahu wa Ta'ala. Da zarar an nemi waɗannan abubuwa uku ga zuciya an rasa, to, ta gama ɓaci, ɓaci irin wanda ba a fatar gyaruwarta har abada. Duk kuma lokacin da ɗaya daga cikinsu ya raunana a cikinta, to, imaninsa ya raunana sakamakon haka".*[133]

*haka".*[133]

Saboda haka ne, Annabawa suka koyar da gaba ɗayan halitta tsoron Allah *Subhanahu wa Ta'ala*. Dubi abin da Annabi Nuhu *Alaihis Salam* yake cewa:

*"Lalle haƙiƙa, ni, ina ji muku tsoron azabar wuni mai girma".*

Annabi Shu'aibu *Alaihis Salam* kuma ya ce:

*"Kuma lalle haƙiƙa ni, ina ji muku tsoron azabar wuni mai kewayewa".*

Shi kuwa Annabinmu Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, ga abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya ce masa:

*"Ka ce: Lalle haƙiƙa ni, ina jin tsoron, idan na saɓa ma Ubangijina, azabar wuni mai girma".*

Saboda haka ne, ya tabbata cewa: *"Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam, idan yana sallah akan ji ƙirjinsa yana gurnani kamar tafasar tukunya, saboda kuka".*[134]

Sai dai tsoron Allah yana samuwa ne idan an san shi, sani na haƙiƙa. Kamar yadda tawaya a mizanin wannan masaniya take haifar da tawaya a mizanin tsoron Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ga bayinsa. Saboda haka ne babu rukunin mutanen da suka kai malamai jin tsoron Allah *Subhanahu wa Ta'ala.* A duk kuwa lokacin da ka ga tsoro da kunya da son Allah Maɗaukakin Sarki sun wadaci mutum, to, ka tabbata ya san Ubangijin nasa sani na haƙiƙa. Duk kuwa lokacin da wannan sani ya daɗa ƙaruwa, to, da kunyar, da tsoron, da son, su ma

---

[133] *Al-Fatawa* 15/21.

[134] *Sunan An-Nasa'i* Hadisi na (1214) 3/13 daga Abu Muɗrif *Radhiyallahu Anhu*

za su daɗa ƙaruwa, gwarwgadonsu. Wato, a taƙaice dai mataki da nauyin tsoro da fargaban Allah Maɗaukakin Sarki ba su taɓa kasa, mataki da nauyin ilimi da sanin da bawa yake da su ba. Tabbacin wannan kuwa shi ne faɗar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: *"Lalle haƙiƙa ni, na fi su sanin Allah da tsoronsa".* Buhari ne ya riwaito shi.[135] Haka kuma Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce: *"Inda kun san abin da na sani, da kun yi dariya kaɗan, kun yi kuka da yawa, da kuma ba ku ji daɗi da mata a kan shimfiɗa ba, da kuma kun fita kan hanya kuna hargowa da neman agaji daga Allah".*[136]

Irin wannan tsoro kuma da muke magana, na Allah *Subhanahu wa Ta'ala* shi ne hanyar zama cikin sahun masu yin ɗa'a zuwa gare shi. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *Tsoron Allah, hanya ce ta sanin ko waye shi. Saninsa kuma hanya ce ta zama cikin sahun masu tsoronsa. Shi kuwa tsoron nan nasa, da zarar ya samu, to, ba makawa ga yi masa ɗa'a da biyayya".* [137] Babu wata hanya da zuciya za ta samu nagarta sai idan tana tsoron Allah Maɗaukakin Sarki. A kan haka ne Abu Sulaiman Ad-Darani *Rahimahullah* yake cewa: *"Da zarar zuciya ta raba gari da tsoron Allah, to, ba abin da zai hana ta rushewa".* [138] Tsoron Allah shi ne abin da ke yi ma zuciya shamaki daga soye-soyenta. Ibrahim bn Sufyan *Rahimahullah* yana cewa: *"Da zarar tsoron Allah ya samu gindin zama a cikin zuciya, to, nan take zai ƙone gurabun soye-soyenta, ya kuma kori son duniya daga cikinta".* [139] Ashe kenan, da zuciya zuciya ta rasa jin tsoron Allah, ro, ta kama hanyar jeji. Malamin nan bamisire Dhun-Nuni *Rahimahullah* yana cewa: *"Mutane ba za su bar hanya ba matuƙar akwai tsoron Allah tare da su. Da zarar kuwa ya gushe, to, sun bi hanyar jeji kenan".*[140]

---

[135] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (20/16) daga A'isha *raliyallahu anha.*
[136] *Al-Musnad* Hadisi na (21555) 5/173, *Sunan At-Tirmidhi* Hadisi na (2312) 4/556 daga Abi Zarr *Radhiyallahu Anhu.*
[137] *Al-Fatawa* 7/24
[138] *Madarij As-Salikin* 1/513.
[139] *Madarij As-Salikin* 1/513.
[140] *Madarij As-Salikin* 1/513.

*Kazalika, Allah* Maɗaukakin Sarki yana wadata duk wanda yake jin tsoron sa, da hikima da sanin makamar ayoyi da alƙawurransa. Tabbacin wannan zance, shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Haƙiƙa a cikin wancan akwai aya ga wanda ya ji tsoron azabar Lahira".* A Lahira kuma, irin wannan mutum, za a buɗe masa ƙofofin gidan Aljanna: *"Kuma, ga wanda ya ji tsoron tsayuwa gaban Ubangijinsa, akwai gidajen Aljanna".* A wani wurin kuma *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"Kuma duk wanda ya ji tsoron tsayuwa gaban Ubangijinsa, ya kuma hana kan sa son zuciyarsa. To, lalle haƙiƙa, Aljanna ita ce makomarsa".* Duk kuma wanda girman Allah ya tabbata a cikin birnin zuciyarsa, to, Allah zai sanya girmansa ya tabbata a cikin zukatan mutane, ya kuma hana su tozarta shi.

Sa'annan kuma, 'tsoron Allah' yana daga cikin rukunan ibada. Sauran kuma sun haɗa da 'ƙauna' da 'soyayya' zuwa gare shi. Saboda haka, wajibi ne ga kowane bawa, ya tabbatar da samuwar waɗannan rukunai uku a tare da shi. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ya ce: *"Wasu daga cikin nagartattun bayi suna cewa: Duk wanda ya bauta ma Allah Ta'ala ta hanyar soyayya da ƙauna kawai, to, ya zama Zindiƙi. Wanda kuma ya bauta masa ta hanyar tsoro kawai, to, ya zama Baharije. Wanda kuma ya bauta masa ta hanyar ƙauna da fatar alherinsa kawai, shi kuma ya zama Bamurji'e. Wanda kuma ya bauta masa bisa tsoro da soyayya da ƙauna da fatar alheri gaba ɗaya, to, shi ne Mumini. Duk waɗannan matakai uku kuma, Allah Ta'ala ya tattara su a cikin faɗarsa: "Waɗancan, waɗanda suke kira suna neman tsani zuwa ga Ubangijinsu. Waɗanne ne suke mafifita a kusanta? Kuma suna fatar samun rahamarsa, suna kuma tsoron azabarsa".* Ka ga neman tsani ɗin nan, yana nufin nuna wa Allah Maɗaukakin Sarki soyayya, wadda take haifar da samun kusanci zuwa gare shi. Bayan haka kuma sai Buwayayyen Sarkin ya ambaci 'tsoro' da 'kwaɗayi da fatar alheri.' Hakan kuwa na nuna cewa, waɗannan abubuwa guda uku su ne tafarki tsakanin Allah *Subhanahu wa Ta'ala* da bayinsa makusanta.[141] Ita kuwa soyayya da ƙauna, suna haifarwa ne da samar da tsoron Allah. Malam Ibn Al-

[141] *Bada'i' Al-Fawaid* 3/43.

Kayyim *Rahimahullah* na cewa: *"Babu wani nau'i na soyayya face tare da shi akwai tsoro da fatar alheri. Kuma gwargwadon yadda ta kama zuciyar mutum gwargwadon yadda soyayyar da tsoron nasa za su kasance a cikin zuciyar".* *[142]

*142

Shi kuwa 'tsoro' a karan kansa, ya kasu kashi uku:

***Kashi na farko:*** Tsoro na ɓoye, wato a wayi gari mutum yana shayi da fargaban wani wanda ba Allah ba, kamar gunki, ko wani shugaba, kada ɗayansu ya cutar da shi. Wannan kuwa babbar Shirka ce. Wato, daidai take da jin tsoron wani matacce da yake kwance a cikin ƙabari, kada ya saukar da wata cuta ga mutum, ko wata azaba ta saukar masa idan bai dogara gare shi ba. Koko a'a, mamacin zai zama sanadiyyar faɗawar sa cikin wani mugun abu, idan ya faɗi wani aibi nasa. Misalin wannan shi ne labarin da Allah Maɗaukakin Sarki yake bayarwa game da mutanen Annabi Hudu da abin da suka gaya masa, cewa: *"Ba mu cewa kome, sai dai sashen abubuwan bautarmu ne ya same ka da cutar hauka…"* Ka ga suna ƙoƙari ne su kuɓutar da kan su kada waɗannan allola su saukar musu da musiba. Wato, kamar dai yadda Buwayayyen Sarkin yake cewa a wata ayar: *"Kuma suna tsoratar da kai da waɗanda suke koma bayansa".*

Irin wannan matsayi kuwa, hali ne na masu bautar ƙaburbura da gumaka da matara kama da su. Sai ka taras suna tsoron su, suna kuma ƙoƙarin sa ma'abuta Tauhidi su ji tsoron su. Musamman idan suka ƙi yarda ko amincewa da bautar da ake yi musu, suka tsaya kai da fata a kan cewa, sai an bauta ma Allah shi kaɗai da zuciya ɗaya. Irin wannan ɗabi'a kuwa, ba abin da take yi illa rusa soron Tauhidi. Kamar yadda idan mutum ya kira wanin Allah, ko ya kai kuka zuwa gare shi, hakan ta raba shi da imaninsa. To, da zarar ya yarda, ya ji tsoron wani wanda ba Allah ba, imaninsa ya warware. Shaikhul-Islam *Rahimahullah* yana cewa: *"Duk wanda ya daidaita kafaɗar Mahalicci da ta abin*

---

[142] *Madarij As-Salikin* 2/43.

*halitta, a cikin soyayyya da ƙauna, ko tsoro da fargaba, ko fatar wani alheri daga wurinsa, to, ya zama mushriki".* [143]

***Kashi na Biyu:*** Mutum ya ƙi aikata abin da ya wajaba a kan sa, yana ji yana gani, saboda tsoron wasu mutane. Mawallafin *Fath Al-Majid*, yana cewa: *"Irin wannan ɗabi'a haramun ce, wani nau'i ne kuma na yi ma Allah kishiya, wanda yake hana mizanin Tauhidi cika da kamala, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa:*

> *Haƙiƙa, wancananku, Shaiɗan ne, kawai, yake tsoratar da masoyansa. Saboda haka kada ku ji tsoronsa, kuma ku ji tsorona idan kun kasance muminai".* [144]

Shi kuma Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ga abin da yake cewa: " *Yana daga cikin makircin maƙiyan Allah, a wayi gari sun tsunduma muminai cikin kogon tsoro da fargaban rundunar waliyyansu, domin kada muminan su yi yunƙurin tarwatsa su. Saboda haka ne ba su horonsu da alheri, ba su kuma hanin su daga sharri. To, shi ne Allah Ta'ala ya bayar da labarin cewa, wannan wani makirci ne na Shaiɗan, da tsoratarwa daga gare shi. Ya kuma hane mu jin tsoron sa".* [145]

***Kashi na Uku:*** Tsoro irin na halitta, kamar mutum ya ji tsoron wani naman daji, ko Wuta, ko nutsewa a ruwa. Irin wannan, ba a zargin mutum a kan sa. Tabbacin wannan hukunci kuwa shi ne, labarin da Allah Ta'ala ya bayar na Annabi Musa *Alaihis Salam,* da cewa: *"Sai ya fita daga cikin ta yana mai jin tsoro yana sauna".*

Shi kuwa 'tsoro' da fargaban azabar Allah, wadda ya yi ma waɗanda suka saɓa masa alƙawari, wanda kuma yake bayar da labarinsa da cewa: *"Wancan, ga wanda ya ji tsoron haɗuwa da ni ne, ya kuma ji tsoron narkona",* da matara kama da wannan. Irin wannan tsoro shi ne matakin ƙoli-ƙoli na

---

[143] *Al-Fatawa* 27/339.
[144] *Fath Al-Majid Sharhin Kitab At-Tauhid* shafi na 396.
[145] *Igasat Al-Lahafani* 1/130.

imani. Miƙa wuya kuma ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala* tare da bar masa ikon kowane al'amari, yana daga cikin abubuwan da suke fitar da tsoro daga zuciyar ɗan Adam. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Sanadarin da yake kashe wutar jin tsoron wani wanda ba Allah ba, shi ne miƙa wuya gare shi gaba ɗaya. Tabbas! Duk wanda ya ajiye kayansa a wurin Allah, ya kuma sallama masa kai da ƙafa, ya kuma san babu yadda za a yi abin da ya ƙaddaro masa ya kuskure shi, ko wanda bai ƙaddaro masa ba ya same shi; ya san cewa babu abin da zai same shi, sai wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya ƙaddara masa. Duk wanda ya san haka, babu sauran gurbi a cikin zuciyarsa, wanda tsoron wani mahaluki zai shiga".* [146]

Duk wanda ya ji tsoron Ubangijinsa a nan gidan duniya, ranar Lahira ba zai haɗu da wani tsoro ko tashin hankali, lokacin da waɗanda suka miƙe ƙafa a nan duniya cikin aminci da rashin tsoron Allah, za su girgiza. Allah Maɗaukakin Sarki ba zai haɗa ma bayinsa zafi biyu ba. Ko dai tsoro duniya ko tsoro Lahira. Amma, dai tabbatacciyar magana ita ce, duk wanda ya ji tsoron Ubangijinsa, ba zai ji tsoron kowa ba. A maimakon haka zai rayu cikin natsuwa da kwanciyar hankali.

Bisa wannan mizani, za ka taras, duk wanda tsoron da yake tsakaninsa da Allah Maɗaukakin Sarki ya karɓa sunansa, to, kuwa ba zai kasa iya mayar da komai nasa gare shi ba. Kai ka san duk rayuwar da babu komai cikinta sai Allah, ta gama samun ni'ima. Sai dai ma'aunin da ake gane mai tsoron Allah da shi, shi ne nisantar zunubai. Saɓon Allah abu ne wanda jahilci yake haifarwa. Shi kuwa duk wanda ya san Allah, sani na haƙiƙa, to, ya ƙetare siraɗin jahilci.

Saboda haka, ya kai ɗan'uwana! Ba ka da wata mafita illa ka kiyayi Ubangjinka a cikin gaba ɗayan halayenka; ka guji saukar azabarsa. A haka sai ka wayi gari cikin jerin masu arzikin duniya da Lahira. Shi kuwa mutum abokin halitta irinka, idan ka ji tsoron sa ka yi aikin banza, domin hakan ba za

[146] *Madarij As-Salikin* 2/13.

ta ƙara maka komai ba illa zaman kura da akuya tsakanin kai da shi, wanda a ƙarshe za ka gudu ka bar shi. A yayin da shi kuwa Allah Maɗaukakin Sarki idan ka ji tsoron sa, abin da hakan za ta haifar a tsakaninka da shi, shi ne soyayya da ƙauna da son kusanci gare shi domin ɗebe kewa. Wannan shi ne bambanci.*

*"Raja'i"* ga Allah ibada ce ta zuciya. Ma'anarsa kuma ita ce, ƙauna da fatar samun wani alheri. Mataki ne kuma da ba a kai gare shi, sai tare da kamilar biyayya da kuma ƙanƙan da kai. Amma a lura, ba a son makahon tawakkali wanda ya tattara samnanci da kasala da rashin kataɓus. Wannan shi ake ce ma *"Tamanni"*.

*"Raja'i"* shi ne matuƙin zuciya da gaɓoɓi, kamar yadda Shehun Malami Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ya ce: *"Ba domin sanadarin "Raja'i" ba, da nau'ukan bauta waɗanda suka keɓanci zuciya da gaɓɓai, an neme su an rasa. Kuma da an yi ta rusa Ma'abidai da Coci-coci da Masallatai, waɗanda ake ambaton Allah a cikinsu babu kama hannun yaro".* [147] Sai dai kamar yadda Ibn Al-Kayyim ya ce: *"Raja'i" ba zai karɓa sunansa ba, sai idan an gwama shi da "Khaufi". A haka sai a wayi gari bawa yana aikata abin da aka umarce shi da shi sakamakon hasken imanin da yake da shi, da buƙatar lada. A hannu ɗaya kuma yana nisantar abin duk da aka hane shi, shi kuma sakamakon hasken imani da tsoro da fargaban azaba".* [148]

*"Raja'i"* ya kasu kashi uku:

Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* na cewa: *"Raja'i" kashi uku ne. Kashi biyu, Shari'a ta yarda da su. Kashi ɗaya kuma sai a hankali. Kashi na farkon, shi ne, guri da ƙaunar samun sakamako ga bawan da ya yi biyayya ga Allah kamar yadda Allah ya so. Na biyu kuma, bawan da ya saɓa ma Allah, sa'annan ya tuba, ya shiga kwaɗayi da fata da ƙaunar samun gafarar Allah Ta'ala, da yafewa, da jinƙayi, da karamci, da haƙurewarsa. Na uku kuma, shi*

[147] *Madarij As-Salikin* 2/42.
[148] *Madarij As-Salikin* 1/502.

*ne, mutumin da bai gushe ba yana saɓon Allah da wuce iyaka, amma kuma, tattare da haka, wai yana guri da fatar samun gafara da rahamar Allah ba tare da ya yi wani aiki na a zo a gani ba. Irin wannan matsayi ruɗi ne kawai da makauniyar fata".* [149]

Duk wanda kuwa fata da ƙaunar alherinsa daga wurin Allah suka kai matuƙa, to, za ka tarar ya ƙara ƙaimi da ƙwazo a fagen ayyukan alheri. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *Duk lokacin da kwaɗayin bawa ga Allah ya ƙarfafa, to, zai ƙara ƙwazo a cikin bauta. Kamar manomi ne, a duk lokacin da yake kyautata zaton alheri da samun sa daga ƙasa, sai hakan ta sa ya cika ta maƙil da iri. Haka kuma idan kwaɗayin nasa ya raunana, zai ƙwazonsa ga shuka ya ƙaranta".* [150]

*"Raja'i"* ɗin nan da ake magana, shi ne abin da yake inganta yunƙurin da bawa yake a kan sa na samun isa ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala* a wayi gari yana jin daɗi da ɗoki da annashuwa. A haka sai ya shiga zabura da jin garɗin tafiyar tare da fatar rashin yankewarta. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"In ba domin '"Raja'i" ba, da ba a samu wanda ya kama tafarkin isa fadar Allah ba, saboda 'tsoro' kawai ba ya motsa bawa. Babban abin da yake motsawa tare da harraka shi babu kamar sanadarin "Raja'i".*[151]

Saboda haka, babu yadda za a yi bawa ya iya karɓa sunan maibauta ga Allah, sai idan ya haɗa hancin waɗannan abubuwa guda uku, wato*, "Mahabba"* da *"Raja'i"* da *"Khaufi"* ko ka ce, soyayya da fata, tare da tsoro. Shaikhul-Islam yana cewa: *Ka sani abubuwan da kawai suke motsa zuciya ta zabura zuwa ga neman isa fadar Allah Maɗaukakin Sarki, uku ne: 'so' da 'fata' da 'ƙauna.'* Sai dai 'soyayya' ita ce mafi ƙarfi daga cikinsu. Dalili kuwa shi ne, ita ake girka sanwarta domin a sha romonta a nan duniya da kuma gobe Kiyama. Saɓanin tsoro, wanda shi zai gushe da zarar an wayi gari Lafira. Allah Ta'ala yan cewa a kan haka:*"Ku saurara! Lalle haƙiƙa, masoyan Allah, babu*

---

[149] *Madarij As-Salikin* 2/36.
[150] *Alfawa'id* shafi 129.
[151] *Madarij As-Salikin*2/50.

*tsoro gare su, babu kuma suna yin baƙin ciki".* Wani bambancin kuma da yake tsakanin 'tsoro' da 'soyayya,' shi ne, na farko ana yafa mayafinsa ne domin gargaɗin rai, da ja masa kunne kada ya saki hanya. Ta biyun kuwa, tana ɗora bawa ne a kan nagartaccen tafarkin saduwa da abin da yake so. Kuma gwargwadon ƙarfi ko rauninta, gwargwadon yadda wannan tafiya tasa za ta kasance. Shi kuwa *Khaufi*, kamar yadda aka ambata a baya kaɗan, yana hana rai ne kawai, karkacewa ko barin hanyar da zai sadu da abin da yake son, tata. *"Raja'i"* kuma shi ne yake yi masa jagora a kan tabbatuwar haka.

Wannan tushe, kuma shishshike da muke magana a kan sa, sanadari ne mai matuƙar girma da ɗaukaka, wanda kuma yake wajaba a kan kowane bawa na Allah, ya mayar da hankali gare shi da kyau. Ya sani ba yadda za a yi ya iya zama cikin sahun bayin Allah na gari, masu bauta masa da zuciya ɗaya, ba tare da shi ba. ga shi kuma ya riga ya zama wajibi a kan kowane mahaluki, ya yi ƙoƙarin zama bawa ga Allah Maɗaukakin Sarki kawai, koma bayan waninsa.

Idan kuma wani ya yi ƙarfin halin cewa, ai tana yiwuwa a samu wani bawan Allah, a waɗansu lokuta, tare da shi akwai sanadarin soyayya, wanda yake motsawa tare da tunkuɗa shi neman abin son sa. Idan aka ce soyayya ba ta wannan aiki, to, me nene sirrin wannan motsi nasa? A nan sai mu karɓa da cewa, abubuwa guda biyu ne kawai suke wannan gagarumin aiki:

Na farko: Shi ne yawan begen masoyi. Da zarar kuwa haka ta samu, to, za a wayi gari zuciya ta rataya da shi abin da ake son. Saboda haka ne Allah Maɗaukakin Sarki, ya yi umurni da yawan ambatonsa, da cewa: *"Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku ambaci Allah, Ambato mai yawa. Ku kuma tsarkake shi safiya da marece.*

Na biyu kuma: Shi ne yawan nazari da duba ni'imomin Allah *Subhanahu wa Ta'ala*. Wannan shi ne dalilin da ya sa, Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya yi umurni da cewa:

> *"To, ku tuna ni'imomin Allah, tsammaninku, ku samu babban rabo".*

A wata ayar kuma Maɗaukakin Sarkin yake cewa:

> *"Kuma duk ni'imar da take tare da ku, to, daga Allah ne".*

A wata ayar kuma *Subhanahu wa Ta'ala* ya ce:

> *"Ya kuma zubo ni'imominsa na bayyane da na ɓoye a kanku".*

Haka kuma a wata ayar yana cewa:

> *"Kuma da za ku lissafa ni'imomin Allah ba za ku iya ƙididdige su ba".*

To, da zarar bawa ya kalli irin ni'imomin da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi masa, waɗanda suka haɗa da hore masa sama da ƙasa da abin da yake cikinsu, wanda ya haɗa da itatuwa da dabbobi, da wasu ni'imomi na zahiri da baɗini, waɗanda suka yi masa zobe ta ko ina. Ga kuma ni'imar imani mai samar da cikakkiyar natsuwa. Da haka ake samun *"Raja'i"* kuma 'ya'yan halittar da suke da alhakin kula da wannana nahiya, sukan motsa ne a duk lokacin da mutum ya kalli karimci da haƙuri da afuwa irin na Allah Maɗaukakin Sarki". [152]

*"Raja'i"* yana ƙarfafa ne a duk lokacin da bawa ya san Allah sani na haƙiƙa. Ibn Al-Kayyim yana cewa: *"Karfin matakin "Raja'i"* yana tafiya ne kafaɗa da kafaɗa da ƙarfi da nauyin masaniyar da bawa yake da su da Ubangijinsa, da sunaye da siffofinsa". [153] Haka kuma *"Raja'i"* wani sanadari ne, wanda a sanadiyyarsa bawa yake samun biyan buƙatarsa daga wurin Ubangijinsa. Karfin ƙaunar samun lada tare da miƙa wuya ga Ubangiji, da zubewa a gabansa, da yarda da gurabun hukunce-hukuncensa. Duk waɗannan ba komai ba ne, illa wasu matakai daga cikin matakan ƙauna da fatar samun rahamar Ubangijin nasa, ya gafarta ya kuma yafe masa zunubansa. Ayyukan da ya yi kuma na alheri, tattare da sankara da miyakun da suke da su, yana fatar a

---

[152] *Al-Fatawa* 1/ 95.
[153] *Madarij As-Salikin* 2/42.

karɓa, a kuma yafe laifukansa. Ka ga ƙarfin wannan ƙauna da fata ne suka wajabta masa wannan irin sallamawa da miƙa wuya, da kuma sunkuyawa a bakin ƙofar. Ka kuwa ga babu yadda hankali zai yarda da yiwuwar faruwar duk haka, ba tare da sanadarin *"Raja'i"* ba, har abada. Saboda haka ne Allah Maɗaukakin Sarki, yake matuƙar son bayinsa su cika da guri, su kuma ɗaga ƙoƙunan baran falalarsa zuwa gare shi. Ba kuwa don komai ba, sai domin kasancewarsa Sarkin gaskiya, mai matsananciyar baiwa, fiye da duk wanda za a roƙa, mai kuma yalwatawa fiye da duk wanda zai bayar. Shi kuwa duk mai tsananin kyauta, ba abin da yake farin ciki da shi, kamar a roƙe shi, a kuma yi fata da gurin cin nasara. Saboda haka a duk lokacin da gurin bawa da kwaɗayinsa ga samun falalar Allah da rahama da sauwaƙewarsa a cikin al'amurra, suka ƙarfafa. Hakan ta saka shi cikin jerin bayin Allah masu gagarumar bauta zuwa ga Allah.*

*HUJJOJI A KAN ABINDA YA GABATA*

***Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:***

***"Dalilin "Raja'i" shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Duk wanda ya kasance yana ƙaunar haɗuwa da Ubangijinsa, to, ya aikata aiki na ƙwarai, Kuma kada ya haɗa Allah da wani a cikin bautarsa". Dalilin "Tawakkali" kuma shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma ga Allah, sai ku dogara idan kun kasance muminai". Da kuma faɗarsa mai girma da ɗaukaka: "Kuma duk wanda ya dogara ga Allah, shi ne mai kyautatawa". Dalilin "Kwaɗayi" da "Fargaba" da "Kanƙan da Kai" shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma lalle ne su, sun kasance suna gudun tsere zuwa ga ayyukan alheri. Kuma suna kiran mu a cikin kwaɗayi da fargaba. Kuma sun kasance masu sauna gare mu". Dalilin "Fargaba" kuma shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "To, kada ku ji tsoronsu, kuma ku ji tsorona".***

***"Dalilin",*** cewa: ***"Raja'i",*** wato ƙauna da kyautata ma Allah zato ibada ne, wadda ba ya halatta a karkatar zuwa ga wanin Allah: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Duk wanda ya kasance yana",*** fata da: ***"Kaunar haɗuwa da Ubangijinsa",*** haɗuwa mai kyau ta samun lada da alƙawarinsa: ***"To, ya aikata aiki na ƙwarai",*** wanda ya dace da koyarwar Shari'a: ***"Kuma kada ya haɗa Allah da wani a cikin bautarsa".*** A maimakon haka, kamata ya yi a taras da gaba ɗayan ayyukansa yana yin su ne da zuciya ɗaya; domin Allah. Duk wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi ma tagomashin sanya tsarkin niyya a cikin aikinsa, da yi domin Allah kawai, to, zai samu biyan buƙata. Duk wanda kuwa ya rasa wannan, to, ya tabbata hasararre. Ba shi ba samun kusanci ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, balle samun yardarsa.

A wasu wuraren Allah *Subhanahu wa Ta'ala* da kan sa, ya yi umurni da kaɗaita shi da *"Raja'i"* ya ce: *"Me ya same ku, ba ku fatar samun natsuwa daga Allah?"* Saboda haka ne duk musulmi, in dai ya karɓa sunansa, babu inda yake kai kuka y zube gurace-guracensa sai wurin Allah *Subhanahu wa Ta'ala.*

Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Idan kun kasance kuna jin raɗaɗi, to, haƙiƙa lalle su ma, suna jin raɗaɗi. Kuna kuna fata daga Allah abin da ba su fata. Kuma Allah ya kasance Masani mai Hikima".* Bisa wannan horo, za ka taras duk wanda kwaɗayi da gurinsa bai wuce Allah Maɗaukakin Sarki ba, yana ƙoƙarin koyi da Annabinsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Shi ne Maɗaukakin Sarkin yake cewa: *"Lalle abin koyi mai kyau ya kasance gare ku ga Manzon Allah, ga wanda ya kasance yana fatar rahamar Allah da samun rabon Lahira, kuma ya ambaci Allah da yawa".* Bisa wannan, duk wanda bai shiga sahun masu fatar samun rahamar Allah ba, to, haƙiƙa ya jefa kan sa cikin ƙangin alwashin azaba. Dubi abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: *"Lalle, waɗanda ba su fatar haɗuwa da rahamarmu, sun amince da rayuwar duniya, sun kuma natsu da ita, da kuma waɗanda suke rafkanannu ne daga ayoyinmu". Waɗannan, makomarsu ita ce Wuta sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa".*

Bisa wannan ma'auni, duk wanda ya guraci wani abu, irin wanda babu mai iko da shi sai Allah, daga wanin Allah, kamar gafarta zunubai, da warkar da maras lafiya, haƙiƙa ya karkatar da wannan ibada zuwa ga wanin Allah, ya kuma faɗa cikin masu babbar Shirka. Saboda yin haka kwaɗayi ne a cikin abin da babu mai iko da shi sai Allah. Fatar samunsa daga wanda ba shi ba kuwa, karkatar da ibadar *"Raja'i"* ne ga wanin Allah. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Bai kamata a jingina "Raja'i" ga wani wanda ba Allah ba; kada a rataya shi ga wata halitta, ko ƙarfin wani bawa, ko aikinsa. Haƙiƙa yin haka Shirka ne, duk da yake Allah yana sanya wasiɗa tsakanin buƙata da biyanta. Sai dai ita wasiɗa ba ta da wani tasiri na ƙashin kanta; dole ne sai ta samu wata gudunmawa. Saboda biyan buƙata da wanzuwarta ba su yiwuwa sai da yardar Allah Ta'ala.*[154]

Saboda haka duk wanda ya guraci wani abu daga wani abokin halitta, ko ya rataya kwaɗayinsa gare shi, to, zuciyarsa za ta fita daga da'irar bauta ga Allah Maɗaukakin Sarki. A haka kuma ya zama bawa ga wanin Allah. Kuma babu ranar da zai 'yantu daga wannan bauta matuƙar a cikin zuciyarsa akwai

[154] *Al-Fatawa* 10/256.

ɓurɓushin wannan kwaɗayi da dogaro, waɗanda suka sa har ya ƙasƙantar da kai ga wanda ba Allah ba, ya sunkuya masa. Shaikhul-Islam *Rahimahullah* yana cewa: *"Babu lokacin da kwaɗayin bawa da tawakkalinsa za su rataya ga wanda ba Allah ba, ko ya neni agajinsa face ya samu kansa cikin ƙasƙanci da taɓewa. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Ta'ala: "Kuma suka riƙi gumaka baicin Allah, domin su kasance mataimaka a gare su. A'aha! Za su kafirta da ibadarsu, kuma su kasance maƙiya a kan su".* Ashe kenan duk wanda ya rataya kwaɗayinsa ga ɗan Adam, to, babu abin da zai haɗu da shi sai ƙasƙanci. Wannan shi ne abin da Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa: *"Duk wanada ya ji tsoron wani abu ba Allah ba, to, za a rinjayar da abin a kan sa. Kamar haka ne, duk wanda ya so Allah tare da waninsa, to, za a azabtar da shi da wanin. Wanda kuma ya ƙaunaci wani abu daga wurin Allah da kuma waninsa, to, ba zai samu komai ba daga can.* [155]

*Saboda haka ya zama wajibi a kan kowane bawa na Allah, ya rataya gurinsa ga Allah koma bayan waninsa, saboda halitta gaba ɗayanta, an tsara ta bisa rauni, ta yadda babu ɗaya daga cikinta, da yake iya kawo ma kan sa wani amfani, ko tunkuɗe mata wata cuta. To, ina ta ga waninsa?* Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Ba lokacin da mutum zai rataya gurinsa ga wani abin halitta, ko ya dogara gare shi. face ya ɓakalce ya taɓe a cikin yin haka".*[156] Ba abin da zai ƙaru da shi sai ƙasƙanci da wulaƙanci. Shaihul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Idan mutum ya rataya da mahaluki ɗan'uwansa, ya kuma ƙaunaci wani alheri daga gare shi, ko tunkuɗe sharri. To, ko shakka babu buƙatarsa ba za ta biya ba ta fuskarsa. Tana ma yiwuwa har sai ya ƙara da zuba musa wani kuɗi, ko yi masa wata hidima, da matara kama da haka, wadda yake fatar a dalilinta ya biya masa wata buƙata idan lokacinta ya kama. Amma, sai a ƙarshe hakan ta kasa tabbata, ko dai sanadiyyar zamansa kasasshe, ko a wayi gari ya sake wasu kwastomomi. Amma, da zai fuskanci Allah da gasken gaske irin na mai buƙata zuwa gare shi, ya kuma nemi agajinsa da zuciya ɗaya, sai*

---

[155] *Miftah Dar As-Sa'adah* 2/256.
[156] *Al-Fatawa* 10/257.

*Allah ya karɓa roƙonsa, ya kawar da matsalarsa, bayan haka kuma ya buɗe masa ƙofofin rahama da jinƙayinsa".*[157]

Saboda haka ya kai ɗan'uwa! Kada ka rataya gurace-gurace da buƙatunka ga wanda ba Allah ba. Ka sani, babu abin da za ka samu, idan ka yi haka, baya ga hasara, da ƙasƙanci irin na mabukaci, da kuma ƙetare iyaka a cikin ibada mai girman daraja. Kai dai yi fata da gurin samun karimcin Allah da baiwa da alherinsa masu yawa. Idan buƙatu sun yi maka ƙawanya, al'amurra sun rikice maka, to, kada ka nemi agajin kowa sai nasa. Yin haka shi ne mafi ɗaukaka ga matsayinka, da daraja ga rayuwarka. Duk bayan haka kuma ga biyan buƙata, da ɗauke nauyin wata gagarumar ibada, wato, *"Raja'i".* *

Shi kuwa "Tawakkali" yana nufin mayar da kowane lamari ga Allah Maɗaukakin Sarki, da gasken gaske, tare da nuna kasawa da sallamawa zuwa gare shi. Shi ma kuma wani nau'i ne na ibada. Kai! yana ma ɗaya daga cikin jiga-jigan nau'o'inta. Shi ne kuma mafi girma daga cikin matakan Tauhidi. Malam Sulaimanu ɗan Abdulahi ɗan Muhammad bn Abdilwahhabi *Rahimahullah* yana cewa: *"Tawakkali farilla ne, wadda kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki a cikinta yake wajaba, saboda ɗaya ce daga cikin mafi girman ibadu, kuma mafi girma da ɗaukakar matakan Tauhidi. Hasali ma! Babu wanda ke iya tsare alfarmar wannan shishshike kamar yadda ya kamata sai zaɓaɓɓu kuma keɓantattun bayi, muminai, irin waɗanda aka ambata a cikin sifar mutanen nan dubu sittin waɗanda za su shiga Aljanna ba tare da hisabi ko azaba ba. Saboda haka ne Allah Subhanahu wa Ta'ala ya yi umurni da Tawakkali a cikin ayoyi da dama na Alƙur'ani, fiye da yadda ya yi umurni da alwala, da wankan Janaba. Kai! sai ga shi ma Allah Subhanahu wa Ta'ala ya sanya shi, a matsayin sharaɗin cikar Imani da Musulunci. A taƙaice ma'anar hakan ita ce, da zarar babu Tawakkali, to, babu imani babu kuma Musulunci".*[158] Shi kuma Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ga abin da yake cewa: *"Tawakkali shi ne rabin addini, ɗayan rabin kuma shi ne, "Inabah" wato komawa ga Allah. Da ma addinin sashe biyu yake da su kacal; Neman taimako*

---

[157] *Al-Fatawa* 10/650.
[158] *Taisir Al-Aziz Al-Hamid Sharh Kitab At-Tauhid,* shafi na 417.

*da kuma bauta. To, Tawakkali shi ne neman taimako, a yayin da "Inabah" take matsayin ibada. Sai dai matsayin da Tawakkali yake da shi, ya fi kowane matsayi faɗi da yalwa".* [159]

Kamar yadda aka ambata a baya kaɗan, matsayin Tawakkali yana gaba da na *Inabah.* Shehun Malami Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ya ce: *"Matsayin Tawakkali yana gaba da matsayin Inabah ne, saboda ana yin Tawakkali ne domin tabbatar da komawa ga Allah. Saboda Tawakkali shi ne hanya, a yayin da Inabah take matsayin masauki".*[160] Sa'annan kuma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya hukunta Tawakkali ya zama wata hanya ta samun so da ƙaunarsa in da yake cewa: *"Lalle haƙiƙa, Allah yana son masu tawakkali".* Karewa da ƙarau, Tawakkali, Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana cewa, shi ne, alamar samuwar imani: *"Kuma Musa (Alaihis Salam) ya ce: Ya ku mutanena! Idan kun kasance kun yi imani da Allah, to, ku dogara gare shi, idan kun kasance musulmi".*

Haƙiƙanin abin da 'Tawakkali' yake nufi kuma, shi ne, sanya Allah a cikin zuciya game da al'amari, da kuma biyar hanyoyin da buƙata za ta biya, amma ba tare da dogara a kan su ba. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Sirrin Tawakkali da haƙiƙaninsa, shi ne, dogarar zuciya da Allah shi kaɗai, ba tare da cuɗanya da hanyoyin biyan buƙata ta nakkasa dogaron ba. Lalle ne kuma a kakkaɓe zuciya daga dogara a kan waɗannan hanyoyi da karkata zuwa gare su. A kuma lura, buɗa baki mutum ya ce: 'Na dogara ga Allah' alhali kuma dogaro da karkata da wadatuwarsa ga wanin Allah yake. Hakan ba ya amfanar mutum da komai. Tawakkali da harshe wani abu ne, Tawakkali da zuciya kuma wani abu ne daban".* [161]

Tawakkali ba ya kamala sai idan an kama wani silali, amma ba tare da an dogara gare shi ba. Ba kuma zai karɓa sunansa ba, sai idan ga Allah aka jingina shi. Ga abin da Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa game da haka: *"Tawakkali na tafiya kafaɗa da kafaɗa ne, da hanyoyin neman biyan*

---

[159] *Madarij As-Salikin* 2/113.
[160] *Madarij As-Salikin* 1/134.
[161] *Alfawa'id* 164.

*buƙatun rayuwa. Ba kuma zai karɓa sunansa ba sai idan an nufi Allah Subhanahu wa Ta'ala da shi. Misalin wannan shi ne, manomi da zai tona ƙasa ya zuba iri. Ka ga a haka ya dogara ga Allah Subhanahu wa Ta'ala; shi zai tsiro masa da wannan shuka har ya ci amfaninta. Ka ga irin wannan, ya ba wa Tawakkali haƙƙinsa".* [162]

Sai dai Tawakkali ba ya nufin rungume hannaye ba tare da bin hanyoyin biyan buƙata ba; yin haka wajibi ne, amma ba tare da an dogara da hanyoyin ba. Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* na cewa: *"Duk wanda ya ƙi yin abin da ya kamata, da sunan Tawakkali, to, ba kuwa zai ci ribarsa ba. Sai dai rashin dogara ga abin da ya kamata ɗin idan an yi shi, tare da yanke alaƙa tsakaninsa da zuciya, shi ne abin da yake sa Tawakkali ya karɓa sunansa. A haka sai ya kasance, iskar ruhin da yake cikin zuciyar tasa, yana kaɗawa ne da sunan Allah ba na hanyar da ya bi ba. Amma, gangan jikinsa da shi take kirkiza".* [163]

Tawakkali ya kasu gida biyu: Akwai Tawakkali na Lalura. Irin wannan kuwa kamar yankan wuƙa yake; take ne buƙata ta biya a cikinsa. Akwai kuma Tawakkali na Ganin Dama. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Wani lokaci Tawakkali yana zama na Dole, wanda yake faruwa a lokacin da bawa ba shi da makarkara ko madafa sai ta hanyar komawa ga Allah da buƙata. Wato, kamar a wayi gari al'amurra sun ƙukƙulle, rayuwa ta yi ƙunci, har mutum ya yanke ƙauna daga kowace irin mafita sai ta wajen Allah. Irin wannan Tawakkali, nan take ne, ake samun mafita da sauƙi da sassafci a cikinsa. Wani lokaci kuma Tawakkali yana kasancewa na Zaɓi. Wato, kamar inda mutum yake da dalilin samun biyan buƙata. To, a irin nan, idan dalilin nan na halas ne, Shari'a ba za ta lamunta idan aka yi watsi da shi ba. Idan kuma mutum ya yi watsi da Tawakkalin, ya kama dalilin, nan ma Shari'a ba za ta lamunta ba. Amma, abin da yake wajaba a kan sa, kamar yadda kalmar malaman wannan al'umma ta haɗu, bisa koyarwar Alƙur'ani, shi ne, wajabcin haɗa hancin waɗannan abubuwa guda biyu. Idan kuwa dalilin, na haramiya ne, to, haramun ne a yi riƙo da shi. A nan, Tawakkali shi ne dalilinsa a matsayinsa*

162 *Zad Al-Ma'ad fi Hady Khair Ibad* 2/ 364.
163 *Madarij As-Salikin* 2/120.

*na wata ɗaya-ɗayan hanya, wadda buƙata take biya da ita. Abin da ake ƙyama kuma, a wayi gari babu shi. Kai! Idan ka ce ma shi ne mafi ƙarfin dalili kwata-kwata, ba ka yi ƙarya ba. To, idan aka yi sa'a ma, dalilin da mutum yake da shi, na halas ne, akwai buƙatar ya duba da kyau, kama shi, yana raunana ƙarfin Tawakkalinka ko, a'a? Idan ka ji ya raunana shi, ta hanyar jin hankalinka ya rabu biyu tsakaninsu, to, barinsa ya fi. Idan kuma ba haka ba, to, mafificin abu shi ne ka yi riƙo da shi, saboda hukuncin Sarkin masu hikima, ya ƙaddara haɗuwar Tawakkali da dalili, saboda haka kada ka ɓata wannan tsari".* [164]

Haka kuma, Tawakkali ya kasu zuwa wasu manyan gidaje biyu. Akwai Tawakkali a cikin al'amurran duniya. Akwai kuma Tawakkali cikin al'amurran Lahira. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Tawakkali ya kasu kashi biyu:"*

Kashi na Farko: Bar ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* iko a cikin biyan buƙatun bawa, da sauran lamurransa na duniya, ko kuranyewar wasu miyagun abubuwa, da sauran musibun ɗakin duniya.

Na biyu kuma shi ne, Tawakkali ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala* a cikin tabbatar da abin da yake, Allah na son sa kuma ya yarda da shi, kamar imani, ya yaƙini, da jihadi, da kira zuwa ga tafarkinsa.

A tsakanin waɗannan kalolin Tawakkali biyu, akwai bambanci da fifiko mai yawan gaske, wanda babu wanda ya san iyakarsa sai Allah Maɗaukakin Sarki. Sai dai tabbatacciyar magana ita ce, da zarar bawa ya bar ma Allah iko, bari na gaske a cikin nau'in Tawakkali na biyu, to, zai isar masa a cikin nau'i na farko iyakar isa. Amma, idan aka yi tawanƙala, ya sakar masa iko a cikin nau'i na farko, ya yi watsi da na biyu. Ba zai ƙi isar masa ba a cikinsa, sai dai ba zai samu irin ladar da wanda ya sakar masa har cikin na biyun ba yake samu. Saboda haka dai, mafi girman Tawakkali a wurin Allah *Subhanahu wa Ta'ala* shi ne, Tawakkali a cikin shiriya, da tabbatar da Tauhidinsa, da biyayya ga Manzonsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, da kuma ƙoƙarin shiryarwa da

[164] *Al-Fawa'id,* shafi na163.

ankarar da waɗanda ba su gane ba. Wannan shi ne irin nau'in Tawakkalin da Annabawa suka yi, da kuma zaɓaɓɓu daga cikin mabiyansu".[165]

To, da zarar kuma Tauhidin bawa ya ƙarfafa, Tawakkalinsa ma zai ƙarfafa. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Ba yadda za a yi Tawakkalin bawa ya karɓa sunansa, sai idan Tauhidinsa ingantacce ne. Hasali ma, ba komai ne Tawakkali ba, illa kaɗaita zuciya da fuskantar da ita wuri ɗaya. Da zarar a cikinta akwai ɓurɓushin Shirka, to, Tawakkalin mai ita ya zama gurgu, kuma baƙon haure. Kenan gwargwadon ingancin Tauhidin bawa, gwargwadon nauyi da ingancin Tawakkalinsa. Shi ya sa da zarar bawa ya waiwayi wani wanda ba Allah ba, sai hakan ta tafi da wani yanki na jinin zuciyarsa. Gwargwadon jinin nan ne kuma, wani abu na Tawakkalinsa zai salwanta. Daga wannan mataki ne, waɗansu suka zaci cewa, Tawakkali ba ya tabbata, sai idan an yi ko'oho da sabubba. Eh! To, wannan gaskiya ne ta wata fuska. Amma, ana nufin kakkaɓe su daga cikin zuciya ne kawai, ba gaɓoɓi ba. Tabbas! Da zarar bawa yana jin wata ƙima ga sabubba a cikin zuciyarsa, ko ga gaɓoɓinsa, to, Tawakkalinsa yana da saura. A'a, lalle ne ya yi katangar ƙarfe tsakaninsa da su".[166]*

A taƙaice dai, shi 'Tawakkali' ibada ce da ake yi da jinin zuciya. Da zarar kuwa bawa ya dogara ga wanda ba Allah ba, a cikin abin da babu mai iko da shi sai Allah, to, ya faɗa cikin kadarkon Babbar Shirka kenan. Kai! ko dogara ya yi ga waɗansu Sarakuna rayayyu da matara kama da su, a cikin abin da Allah ya ba su iko da shi, ya yi Shirka, sai dai ƙarama.*

***"Dalilin",*** kasancewar ***'Tawakkali'*** ibada, wadda karkatar da ita zuwa ga wanin Allah yake haramta: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki, da ya ce: "Kuma ga Allah",*** shi kaɗai: ***"Sai ku dogara;"*** ku bar masa gaba ɗayan al'amurranku: ***"Idan kun kasance muminai".*** Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Duk wanda ya dogara da wani sharaɗi, wanda buƙata ke biya ta hanyarsa, to, da zarar sharaɗin ya gushe shi ma zai gushe. Wannan shi ne abin da yake tabbatar da cewa, duk wanda ba ya dogara ga*

---

[165] *Duba littafin da ya gabata.*
[166] *Madarij As-Salikin* 2/120.

*Allah, to, ba shi da imani ko masoso. Ya kuwa za a yi wanda ya rasa wannan sanadari ya yi imani, tunda cewa Allah Maɗaukakin Sarki ya yi: "Kuma ga Allah sai ku dogara idan kun kasance muminai". A wata ayar kuma ya ce: "Kuma ga Allah sai muminai su dogara". A wata ayar kuma ya ƙara da cewa: "Lalle haƙiƙa, waɗanda kawai suka tabbata muminai, su ne waɗanda idan aka ambaci Allah, sai zukatansu su raurawa. Idan kuma aka karanta musu ayoyinsa, sai su ƙara musu imani, kuma ga Ubangijinsu kaɗai ne suke dogara".* Waɗannan ayoyi sun isa hujja a kan cewa, duk wanda yake dogara ga wani ba Allah ba, shi ba mumini ba ne.

Bisa wannan tsari, duk wanda ya bar kayansa ga Allah Maɗaukakin Sarki, to, zai kuwa isar masa. Tabbacin haka shi ne abin da Buwayayyen Sarki yake cewa: *"Duk wanda ya dogara ga Allah",* a cikin gaba ɗayan lamurransa: *"To, Allah zai tsaya masa".* Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* bai gaji ba; ya ƙara da cewa: *"Duk wanda kuwa Allah ya zama garkuwa da mashinsa, babu yadda za a yi abokin gabarsa ya samu nasara a kan sa. Kai! babu wani sharri da zai same shi, sai irin wanda ba ya da makawa ɗin nan. Wato, ina nufin kamar zafin rana ko sanyi, ko yunwa, ko ƙishi. Amma dai a ce, ga wani abu, wanda ba makawa sai ya bi ta hanyarsa, sannnan wata buƙata tasa za ta biya, kuma abin ya cutar da shi, a'a; har abada. Ai dai kowa ya san akwai bambanci tsakanin wahala irin wadda a zahiri matsala ce, da wannan wahala, wadda hanya ce ita ta samun waraka".* [167]

Amma dai, tabbatacciyar magana ita ce, duk wanda ya zaɓi Allah, ya kuma dogara gare shi, har Allah ya yarda da shi, to, zai tsaya masa a cikin gaba ɗayan al'amurransa, ta yadda ba zai buƙaci wani wanda ba shi ba. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* ya ce: *"Neman agajin Allah Maɗaukakin Sarki, da dogara gare shi, da laɓewa wurinsa, da roƙon sa, su ne abubuwan da suke ƙarfafa bawa, su kuma sauwaƙe masa al'amurransa. Saboda haka ne wasu magabata suka ce: Duk wanda yake farin cikin a wayi gari babu mai iya ja da shi, to, ya dogara ga Allah".*[168]

---

[167] *Bada'i' Al-Fawaid* 2/465.
[168] *Al-Fatawa* 10/ 32.

Saboda matsayin da ‘Tawakkali’ yake da shi ne, Allah *Subhanahu wa Ta’ala* bai ambaci wani sakamako ga wanda yake yin sa ba, illa cewa, zai jiɓinci al’amarinsa. Ina nufin, babu wata ibada daga cikin ibadu, wadda aka samu Allah *Subhanahu wa Ta’ala* ya ce wa mai ita: *“Shi ne Maga’isansa”,* sai ‘Tawakkali’ idan an tsayar da tutarsa, tsayi na haƙiƙa. Ka ga hakan na nuna irin girman da ibadar ‘Tawakkali’ take da shi. Kazalika, wannan sakamako yana nuna cewa ‘Tawakkali’ shi ne mafi girman ibadu, mafi kuma girman hanyar samun kowane irin amfani, da kuɓuce ma kowace irin cuta. Duk bayan wannan albishir kuma Maɗaukakin Sarki ya sake gaya mana cewa: *”Lalle, Allah mai isar da nufinsa ne”,* ma wanda ya dogara gare shi; babu wani abu da zai tunkara, ya gagare shi. Shaihul-Islami *Rahimahullah* ya ƙara da cewa: *“Ku sani, mafi ribar kasuwanci, babu kamar, dogara ga Allah, da amincewa da ya isa, da kuma kyautata masa zato. Ashe kenan, babu abin da ya kamaci duk wanda ya mayar da hankali ga neman wani arziki, illa ya dogara ga Allah, ya kuma matsa da roƙonsa”.*[169]

Kai! a taƙaice, ina tabbata maka, babu yadda za a yi wata rayuwa ta samu hutu, sai idan gangar jikin da take ɗauke da ita, ta mayar da gaba ɗayan al’amarinta ga Allah Mahaliccinta. Wannan shi zai sa ta ƙara shaƙuwa da Maƙagin nata, jin cewa yana sane da halin da take ciki, a shirye yake kuma ya yi mata jinƙayi kamar yadda ya saba. Mai iko ne kuma a kan yaye mata duk wata damuwa. Mai matuƙar karimci ne, da ya yi mata tanadin kyakkyawan sakamako a kan duk wata musiba da ta same ta, ta hanyar maye mata gurbinta da wani abu mafi zama alheri. Ai! Da zarar an yarda da Allah Maɗaukakin Sarki, kamar yadda ya kamata, to, abin da zai biyo baya shi ne, sauraren saukar buwayayyen ikonsa. A kan haka ne Malamin namu, Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa: *“Duk wanda ya dogara ga Allah, dogara ta haƙiƙa, a cikin wata buƙata, to, ta gama biya. Sai dai mizani shi ne, idan buƙatar tasa, aba ce, wadda Shari’a ta yarda da ita, to, zai yi kyakkyawan ƙarshe. Idan kuwa irin buƙatun nan ne masu motsa fushin Rabbu, to, abin da ya samu sanadin*

[169] *Al-Fatawa* 10/662

*Tawakkalin ba zai zame masa alheri ba. Idan abu ne na halas, amma, bai yi aiki da shi ta hanyar yin ɗa'a ga Allah ba, to, zai samu ladar Tawakkali, amma ba zai samu ta aikin ba".* [170]

Saboda haka, ya kai ɗan'uwana! Ina ba ka shawarar rataya zuciyarka ga Allah Maɗaukakin Sarki, da dogara gare shi a duk lokacin da kake neman kuɓuta daga wani sharri, ko tsere ma waɗansu fitinu, ko samun wani arziki, ko shiga Aljanna, da tsira daga Wuta. A cikin yin haka kuma, ka bi duk hanyar da za ta taimaka maka buƙatar ta biya, matuƙar ta halas ce. Kada ka kuskura ka dogara ga wani abokin halitta domin ba shi da wani iko ko waye shi, da zai iya yaye maka wani baƙin ciki, balle ya yi maka irin kyautar nan wadda ta fi gaban na gode. A sane nake cewa, akwai wani nau'i na iko, wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya damƙa hannun wasu bayi nasa. To, ko irin wannan, kada ka dogara ga bawan a cikinsa. Kai dai tsaya ga Allah shi kaɗai. Masu hikima suna cewa: Duk wanda ya dogara ga asalinsa, babu shakka zai ƙasƙanta. Wanda kuma ya dogara da hankalinsa, zai shiga jeji. Shi kuma wanda ya dogara da dukiyarsa, sai ya tsiyace. A yayin da shi kuma wanda ya dogara da mutane, za a wayi gari ya gaji sun gaji.

Ina ƙara nanata maka. Ka dogara ga Allah Shi kaɗai. Idan ka yi haka, zai tsaya maka a kan duk lamurranka. Sarki ne wanda ya isa ga yin hakan idan an bar masa iko da iyawa, an kuma kyautata masa zato. Kada ka manta kuma, ba a dogara gare Allah *Subhanahu wa Ta'ala* rabi da rabi. Idan ka saurari wannan gargaɗi da kyau, ka kuma yi aiki da shi, to, ka tsare alfarmar ɗaya daga cikin manya-manyan ibadu, maɗaukaka. Tabbatacciyar magana kuma ita ce, har adaba, babu yadda za a yi wanda ya aje kayansa a wurin Allah, ya ƙasƙanta, ko ya nakkasa. Ba batun tawaya ake yi ba.

Ita kuwa 'Fata' wato, *"Ragba"* a Larabce, tana nufin neman samun biyan wata buƙata da aka sa a gaba. Sai dai akwai bambanci tsakanin ta da kalmar *"Raja'i"* wadda muka fassara da 'kwaɗayi.' Misalin wannan shi ne, Aljanna. Wanda yake fatar shigar ta, kawai, a Larabce ana kiran wannan matsayi nasa *"Raja'i"* ne. Amma, idan ya yi ma wannan 'fátá' tasa rakiya da ayyuka na

---

[170] *Madarij As-Salikin* 2/114

ƙwarai, sai a ce ya hau matakin *"Ragba"* kenan, wato 'gúri' in ka so. Saboda haka, kenan cika da kamalar kowace *"ragba"* shi ne a haɗa ta da *"raja'i".* Ga abin da Malam Ibn Al-Kayyim yake cewa: *"Bambanci tsakanin "Ragba" da "Raja'i" shi ne, ta farko na nufin fátá, a yayin da ta biyu take nufin kwaɗayi. "Raja'i" kenan shi yake haifar da "Ragba". Shi ya sa da zarar son abu ya zauna cikin zuciyar mutum, sai ya shiga fafutukar neman sa. A wata Hausa, zumuncin da yake tsakaninsu, kamar wanda yake tsakanin kalmar 'gudu' ne, da 'tsoro".*[171]

Ita kuwa kalmar *"Rahba"* tana nufin fargaba da tashin hankali irin waɗanda suke haifar da gudu daga abin da ake tsoro. Wato, kalma ce da ta haɗa hancin motsawar rai da kaɗawar zuciya, a hannu ɗaya, da kuma motsawar gangan jiki a ɗayan hannun. Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Ita kuwa "Rahba" kaiwa matuƙa ce a cikin gudu daga abin da ake ƙi da ƙyama. A haka tana matsayin kishiya kenan ga "Ragba" wadda ita kuma take nufin waɗarin zuciya a cikin neman abin da ake so da kwaɗayi".* [172]

To, da *'"Ragba"* da *"Rahba",* kwaɗayi da fargaba, duk ba su karɓa sunansu, sai tare da haƙuri da godiya. *"Rahba"* ita ke sa bawa dole ya yi haƙuri, a yayin da ita kuwa *"Ragba"* take kai mai ita zuwa ga matakin godiya. Sa'annan kuma a matsayinsu na ibadoji, suna taƙaituwa ne ga bawa gwargwadon zunubansa. Suna kuma ci gaba da hauhawa gwargwadon imaninsa. Daman kuma gamon katari ga bawa, suna samuwa ne, da yardar Allah, gwargwadon nauyin waɗancan buƙatu. Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Idan Allah na son bawansa da alheri, sai ya yi masa muwafaƙar mayar da gaba ɗayan ƙoƙarinsa a cikin ibadar 'kwaɗayi' da 'fargaba.'* Babu wani sanadari na samun muwafaƙa da ya kama ƙafarsu; gwargwadon matsayin da suke da shi ne a cikin zuciyar bawa, yake samun dace da nasara". [173]

Shi kuwa *"Khushu'i"* yana nufin ƙanƙan da kai tare da sallamawa ga girman Allah Maɗaukakin Sarki, ibada ce kuma da take kasancewa ta hanyar

---

[171] *Madarij As-Salikin* 2/55.
[172] *Madarij As-Salikin* 1/512.

[173] Shifa'ul-Alil shafi na 226.

zuciya da gaɓoɓi. Suna da kusanci na sosai da *"Khudhu'i"* illa dai shi, bai kai cikin ɗakin zuciya ba, iyakarsa nan ga gaɓoɓin jiki. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Khushu'i, wato ƙanƙan da kai, yana nufin Khudhu'i, wato zubewar gaba ɗayan gangar jiki saboda girman Allah, tare da samun natsuwa a cikin zuciya da gangar jiki a cikin yin haka".* [174]

Bayan shi kuma, Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ya ƙara da cewa: *Kanƙan da kai, ana yinsa ne da zuciya, amma tsirinsa yana bayyana ne ga gaɓoɓi; su suke tabbatar da samuwarsa.*[175] Wani abin kuma shi ne, duk lokacin da zuciya ta sunkuya ma girman Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, hakan, zai haifar da cika da kamala ga matsayin mai ita, a duniyar bautar Allah. Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ya ƙara da cewa: *"Mafi cika da kamalar mizanin ibada a cikin halitta, gaba ɗaya, shi ne, wanda ya fi su cikar mizanin ƙasƙantar da kai ga Allah Maɗaukakin Sarki, da ɗa'a zuwa gare shi".* [176]

Wata baiwa kuma da falala na Allah *Subhanahu wa Ta'ala* zuwa ga bayinsa, ita ce, hukuntawa da ya yi, duk wanda ya yi kwaɗayin abin da yake hannunsa, ya kuma tashi haiƙan domin samun sa, to, zai ba shi lada. Wanda kuma ya ji tsoro da fargaban azabarsa, Maɗaukakin Sarkin zai shiga tsakanin sa da ita. Haka kuma wanda ya sunkuyar da zuciya da gaɓoɓinsa gare shi *Subhanahu wa Ta'ala*, to, zai rayu cikin girma da ɗaukaka; ba wani mahaluki da zai bautar da shi ko ya ƙasƙantar da shi.

---

174 *Al-Fatawa* 27/31.
175 *Madarij As-Salikin* 1/521.
176 *Miftah Dar As-Sa'adah* 2/300

*HUJJOJI A KAN ABINDA YA GABATA*

***Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:***

***"Dalilin 'Kwaɗayi' da 'Fargaba' da 'Kanƙan da Kai' kuma shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle ne su, sun kasance suna gudun tsere a cikin ayyukan alheri. Suna kuma kiran mu a cikin kwaɗayi da fargaba, sun kuma kasance masu sauna ne a gare mu". Dalilin ƙanƙan da kai kuma shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "To, kada ku ji tsoronsu, kuma ku ji tsorona".***

***"Dalilin",*** cewa: ***"'Kwaɗayi"*** a cikin abin da yake hannun Allah: ***"Da 'Fargaban"*** azabarsa: ***"Da 'Kanƙan da Kai'"*** zuwa gare shi, shi kaɗai, duka waɗannan nau'ukan ibada ne. Dalili a kan haka: ***"Shi ne",*** abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya ambata game da Annabawa da bayinsa salihai, inda ya yaba tare da jinjina musu da cewa: ***"Lalle ne su, sun kasance suna gudun tsere",*** a cikin sigar gasa: ***"A cikin ayyukan alheri",*** da ɗa'a ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala* da suran ayyukan neman fada da kusanci zuwa gare shi. ***"Suna kuma kiran mu",*** in ji Allah, mu kaɗai, suna roƙon mu biyan buƙatu. Suna kuma yin haka ne: ***"A cikin kwaɗayi",*** na abin da yake hannun muna alheri: ***"Da fargaba",*** a kan azabar da muka yi tanadi. ***"Sun kuma kasance masu sauna ne a gare mu".*** Saboda haka suke ƙanƙan da kai, suna taulahi da shi sakamakon cikakkiyar masaniya da suke da ita, da irin matsayin Ubangijinsu.

Kai tsaye, wannan aya ta nuna cewa, waɗannan abubuwa guda uku, da suka haɗa da, kwaɗayin abin da yake hannun Allah, da tsoro da fargabansa, da kuma ƙanƙan da kai zuwa gare shi, duk suna daga cikin ibadu mafi girma. Duk kuwa wanda ya karkatar da wani sashe nasu, zuwa ga wanin Allah Maɗaukakin Sarki, to, ya zama mushriki.

Kalmar *"Khashya"* ita kuma tana nufin *"Khaufi"* ne, wato tsoro a Larabce. Sai dai da'irar ta farko ƙuntatacciya ce, saboda tsoron duk da bai tare da masaniya da Allah Maɗaukakin Sarki, to, ba za a kira shi *"Khashya"* ba. Dalili a kan wannan fashin baƙi shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki:

*"Waɗanda kawai suke tsoron Allah daga cikin bayinsa su ne malamai".* Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* ya ce: *"Tsoron Allah Ta'ala yana tafiya ne kafaɗa da kafaɗa da sanin sa. Saboda haka gwargwadon nauyin saninsa ne, ake jin tsoronsa".* [177]

Shi kuma tsoron Allah ya ƙunshi kwaɗayi da fatar samun alheri daaga wurinsa. Shaikhul-Islam *Rahimahullah* yana cewa: *"Tsoron Allah har kodayaushe, yana tafiya ne tare da kwaɗayi. Idan kuwa abin ya kasa zama haka, to, ya zama yanke ƙauna kenan. Haka abin yake, kamar yadda "Raja'i" ba ya karɓa saunansa sai idan an gwama shi da "Khaufi" wanda shi ma idan hakan ta kasa tabbata, to, sunan wannan matsayi shi ne, 'aminci' ba tsoro ba. Saboda haka, ba kowa ne ke iya taka matsayin jin tsoron Allah Ta'ala ba, sai masana. Su ne kuma ya yaba da yin haka, Subhanahu wa Ta'ala".*[178]

Jin tsoron Allah Maɗaukakin Sarki ibada ne, wadda ba ya halatta a karkatar zuwa ga waninsa. ***"Dalilin",*** haka: ***"Shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "To, kada ku ji tsoron su. Kuma ku ji tsorona".*** Domin ba su cancanci a ji tsoron su ba. Ka ga a nan Allah Maɗauakakin Sarki ya umarci bayinsa da jin tsoronsa, saboda tsoron sa shi ne mabuɗin kowane irin alheri. Shi ya sa, ba yadda za a yi wanda ba ya tsoron Allah ya nisanci saɓonsa. Haka kuma ba zai tsaya a kan horace-horacensa ba. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Ba yadda za a yi mutum ya iya sadar da abin da Allah ya yi umurni da sadarwa, sai idan yana jin tsoron sa. Da zarar kuwa wannan sifa ta tsoro, aka neme ta a cikin ƙoƙon zuciya aka rasa, to, ba kuwa inda za a je".*

Duk kuwa wanda ya ji tsoron Ubangijinsa, Allah Maɗaukakin Sarki zai raya zuciyarsa, ta yadda idan an yi masa wa'azi da gargaɗi zai ji ya kuma ɗauka. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Da sannu wanda yake jin tsoron Allah zai wa'aztu".* A wata ayar kuma ya ce: *"Haƙiƙa, lalle, a cikin wannan akwai abin lura ga masu tsoron Allah".* Haka abin yake, duk wanda yake tsoron Allah Maɗaukakin Sarki, to da an gan shi za a ga alamar sanin girman Allah tare da shi. A kan haka ne Allah *Subhanahu wa*

[177] *At-Tibyan,* shafi na 88.
[178] *Al-Fatawa,* shafi na 21.

*Ta'ala* yake cewa: *"Fatun waɗanda ke tsoron Ubangijinsu suna takura saboda shi, sa'annan fatunsu da zukatansu su yi laushi zuwa ga ambaton Allah…"* Shiriya idan ta samu ga mutum, to, alamarta ita ce, a wayi gari yana tsoron Ubangijinsa. Idan kana son tabbatar da haka kalli faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Kuma in shiryar da kai zuwa ga Ubangijinka domin ka ji tsoron sa".* Bayan haka kuma, shiriya tana wajabtar da samun gafarar Allah Maɗaukakin Sarki da gagarumar falalarsa. A kan haka ne Buwayayyen Sarkin yake cewa: *"Lalle, haƙiƙa, waɗanda suke jin tsoron Ubangijinsu a ɓoye, suna da gafara da sakamako mai girma".* Haka kuma tana zama silali kuma sanadin shiga Aljanna, kamar yadda Maɗaukakin Sarki ya ce: *"Sakamakonsu a wurin Ubangijinsu, shi ne gidajen Aljannar zama, ƙoramu na gudana daga ƙarƙashinsu, suna madauwama a cikinsu har abada. Allah ya yarda da su, kuma su, sun yarda da shi. Wannan sakamako ne ga wanda ya ji tsoron Ubangijinsa".* Haka kuma ba za ka taras da mutum ya cika ya batse da tsoron Allah ba, face ya zama ɗaya daga cikin waɗanda suka san shi, sani na haƙiƙa. Duk kuwa wanda yake jin cewa ya san Ubangijinsa, amma, shi ba malami ba ne, to, yana yaudarar kansa ne kawai. Tabbacin haka kuwa shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Lalle, haƙiƙa, masu jin tsoron Allah daga cikin bayinsa su ne malamai".* Shaikhul-Islam *Rahimahullah* yana cewa: *"Duk wanda ya ji tsoron Allah, shi ne malami".*[179] Kai! tsoron Allah a karan kansa ilimi ne, ko shi kaɗai mutum ya mallaka ya fi ƙarfin a ce masa jahili. Ga abin da ɗan Mas'udu *radhiyallahu ahnu* yake cewa: *"Tsoron Allah ya isa zama ilimi, rashin sanin Allah kuwa, babu jahilcin da ya kai shi".* [180] Duk wanda ya ji tsoron Allah ya kuma yi masa ɗa'a da biyayya ta hanyar tsare alfarmar umarce-umarce da hane-hanensa *Subhanahu wa Ta'ala*, to, ya gama zama malami, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki da kan sa yake cewa: *"Shin, wanda yake mai tawali'u sa'o'in dare, yana mai sujada kuma yana mai tsayi ga sallah, yana tsoron Lahira, kuma yana fatar rahamar Ubangijinsa. Ka ce: Ashe waɗanda suka sani, suna daidaita da waɗanda ba su sani ba? Masu hankali ne kawai ke yin tunani".*

---

[179] *Al-Fatawa,* 7/17.

[180] *Al-Musannaf,* na Ibnu Abi Shaiba, Hadisi na (34532) 7/104.

Duk kuma wanda ya ji tsoron Ubangijinsa, babu shakka zai rayu rayuwa mangarciya, mutane suna ganin girma da mutuncinsa. Saboda haka, shawarata gare ka ya kai ɗan'uwana! Ita ce, kodayaushe ka sa Allah a gabanka. Kada ka kuskura ka miƙe ƙafa, ka gafala ka kusanci duk wani abu da zai zama sanadin haɗuwa da fushi, da saukar azabarsa. Idan kuma kana son shiga sahun masu jin tsoron Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, to, ka yawaita ayyuka na ƙwarai. Kar ka ji wata shakka, Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya fi kowa da komai cancantar a ji tsoron sa. Ga shi kuma ya bayar da umurnin kada a haɗa shi da kowa da komai a cikin wannan ibada, inda yake cewa: *"To, kada ku ji tsoronsu, kuma ku ji tsorona domin in cika ni'imata a kanku, tsammaninku kuna shiryuwa".*

Tsoro kuma duk, idan ya zama na wani abin halitta ne, to, ba ya tare da komai sai ƙasƙanci da wulaƙanci. Saboda haka kada ka ji tsoron kowa sai Ubangijinka. Karkatar da wannan ibada, a matsayinta na mafi girman ibadu, zuwa ga wanin Allah *Subhanahu wa Ta'ala* Shirka ne. Ita kuwa zuciya, a duk lokacin da aka damƙa ragwamarta a hannun Allah Maɗaukakin Sarki, ta hanyar komawar mai ita zuwa gare shi, tare da kyakkyawar niyya, hakan wata gagarumar ibada ce, wadda a sanadinta bawa yake samun lada irin ta a zo a gani.

Kalmar *"Inábah"* wadda muka fassara da harshen Hausa, da cewa, "komawa ga Allah", tana nufin mayar da al'amari gaba ɗaya a hannunsa. Hakan kuwa ba za ta taɓa samuwa ba, sai idan an wayi gari, soyayya ta ƙullu tsakanin zuciyar bawa da Mahaliccinsa, tana kuma shirye da yin cikakkiyar ɗa'a da biyayya zuwa gare shi, a matsayinsa na abin nema kuma abin gurinta. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Inábah tana nufin zaman zuciyar bawa, babu abin da yake cikinta sai Allah Maɗaukakin Sarki, kamar yadda idan mutum ya tare a cikin Masallaci yana ibada sai a ce yana li'itikafi, wato, ya tare a cikinsa. Manufa dai anan ita ce, ƙulluwar soyayya tsakanin zuciyar bawa da Ubangijinta, ta hanyar yawaita ambato da girmamawa da*

*ɗaukaka matsayinsa, bisa koyarwar Manzonsa Sallallahu Alaihi wa Sallam".* [181]

Wani lokacin kuma, ma'anar kalmar *"Inába"* takan tafi kafaɗa da kafaɗa da Kalmar Tuba. Dalili kuwa shi ne, tuba na nufin ƙulla azamar nisantar saɓa ma Allah Maɗaukakin Sarki, tare da yin da-na-sani a kan abin da ya gabata, da kuma ƙudurin ba za a sake ba har abada. To, idan bawa ya ci gaba da biyar godaben tuba, ya ci gaba da bauta ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, kuma bayan tubar, ya ƙara da waɗansu ayyukan ɗa'a, kamar karatun Alƙur'ani, da sadaka, to, sai akalle shi a matsayin wanda ya koma ga Allah baki ɗaya. a Larabce shi ake cewa ya yi *"Inábah"* ko kuma ya zama *"Munib".* Wani ƙarin misali shi ne, yau da wani ɓarawo zai tuba, ya bar sata. Bayan haka kuma, sai aka taras ya tsare waɗansu ayyukan ɗa'a, kamar *istigfári* da zikiri, da matara kama da su, sai a ce ya zama na-Allah sosai. A wannan mizani, kenan *"Inábah"* wani ma'auni ne da ake gane tubar mutum da shi, ake kuma fahimtar cewa bawa ya kama tafarkin bauta ma Allah Maɗaukakin Sarki.

Sai dai idan aka lura, za a ga cewa, mawallafin bai ambaci "tuba" a matsayinta na ɗaya daga cikin na'ukan ibada ba. A maimakon haka sai ya taƙaita a kan amabatom *"Inába"* kawai. To, ya yi haka ne, saboda irin yadda ake iya fahimtar kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki da bauta, a cikin *"Inába",* ba a fahimtar haka a cikin "tuba". Tabbas! Akwai fifiko tsakaninsu idan ana batun mayar da hankali ga Allah Maɗaukakin Sarki da bauta masa shi kaɗai. Bayan haka kuma, a tsabar ma'ana *"Inába"* tana gaba da tuba.

Kazalika, ana gane komawar bawa ga Allah ne, ta hanyar mayar da hankalinsa ga aikata abubuwan da Allah yake so yake kuma ƙauna, ta yadda komai nasa yana tafiya a kan hukuncin Allah. Da zarar kuma an ce ga wani abu, wanda yake sa a samu son Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, to, ba tare da wani ɓata lokaci ba zai shiga sahun masu aikatawa. A kan hake ne Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa: *"Mayar da hankali ga Allah Maɗaukakin Sarki tare da mayar da komai a hannunsa, irin wanda yake sa mutum ya shiga sahun masoyan Allah, ita ce, kaɗaita shi a matsayin Ubangiji, da bauta masa*

[181] *Alfawa'id,* shafi na 341.

*shi kaɗai, tare da nuna masa matsananciyar ƙauna. Irin wannan "Inába" kuwa, ta ƙunshi abubuwa guda huɗu ne, da suka haɗa da: Son Allah Subhanahu wa Ta'ala, da ƙanƙan da kai, da mayar da hankali zuwa gare shi, da juya ma duk abin da ba shi ba, baya. A haka sai ka taras, da zarar bawa ya shiga wannan sahu, na waɗanda suka sabunta matsayinsu a wajen Allah, sai a taras ba ya wasa da, duk wani abu da Allah yake so, a kowane lokaci. Da zarar kuma ya fahimci abinda ke sa zumunci tsakanin bawa da Ubangijinsa, sai ya yi fararat ya aikata shi, komai nasa na Allah ne".*[182] *

Komawa ga Allah Maɗaukakin Sarki, wato, *"Inába"* da muke magana a kan ta, ita ce aiki, wanda Annabawa da Manzanni amincn Allah ya tabata a gare su, ba su taɓa gajiya da shi ba. Saurari abinda Allah ya ce game da Annabinsa Dawud *Alaihis Salam*: *"Kuma Dawuda ya tabbata cewa, mun fitine shi ne, saboda haka, ya nemi Ubangijinsa gafara, kuma ya faɗi yana mai sujada, ya kuma mayar da al'amari ga Allah (ya yi "Inába").* A game da Sulaiman *Alaihis Salam,* ga abin da Allah yake cewa: *"Kuma lalle haƙiƙa, mun fitini Sulaimanu, muka kuma jefa wani jikin mutum a kan karagarsa. Sa'annan ya mayar da al'amari zuwa gare mu (ya yi "Inába").* Shi kuma Annabi Shu'aibu *Alaihis Salam,* cewa ya yi: *"Kuma muwafaƙata ba ta zama ba, face daga Allah. A gare shi na dogara, kuma zuwa gare shi na mayar da al'amarina (na yi "Inába")".* Annabinmu Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam* shi ma cewa ya yi: "*Wancan shi ne Allah Ubangijina, a gare shi na dogara, kuma zuwa gare shi nake mayar da al'amarina".* Haka kakansa kuma Annabi Ibrahim *Alaihis Salam,* badaɗayi kuma masoyin Allah wanda ya samu kyakkyawan yabo daga Allah Maɗaukakin Sarki, sakamakon irin yadda yake mayar da gaba ɗayan al'amurransa, a kowane lokaci, zuwa gare shi. Maɗaukakin Sarkin ya ce: *"Lalle Ibrahimu, haƙiƙa mai haƙuri ne, mai yawan addu'a, mai "Inába" (komawa ga Allah)".* Bayan haka kuma, Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wata bakandamiyar bushara ga masu haƙuri da mayar da al'amurransu zuwa gare shi, yana mai cewa: *"Kuma waɗanda suka nisanci shaiɗanu, ga bauta musu, suka kuma mayar da al'amari ga Allah (suka yi "Inába"), suna da bushara…"*

---

182 *Madarij As-Salikin,* 1/431.

Wani abin ban sha'awa ma, duk bai fi irin yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana cewa ba, babu mai iya fahimtar waɗannan ayoyi, balle aiki da abin da suka ƙunsa, sai bawan da yake *"Inába"* zuwa gare shi. Wannan tabbaci yana cikin faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Domin mayar da ido da tunatarwa ga dukkan bawa mai "Inába"*. Karin bayani a kan hake ne, Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yake cewa: *"Da zarar bawa ya mayar da al'amurransa ga Allah, sai ya zama mai ganewa tare da fahimtar ma'noni da darussan da suke ƙunshe a cikin ayoyin Allah Subhanahu wa Ta'ala".* [183] Haka kuma tawakkali da mayar da al'amurra ga Maɗaukakin Sarki Allah, na nisantar da bawa daga azabobinsa. Tabbacin wannan shi ne faɗar Buwayayyen Sarkin: *"Kuma ku mayar da al'amari zuwa ga Ubangijinku, ku kuma sallama masa. A gabanin azaba ta zo muku, bisa auke, kuma ku ba ku sani ba".* Haka kuma Aljanna, gida ce, wadda Maɗaukakin Sarki ya yi tanadi ba domin kowa ba, sai bayinsa masu zuciya mai sunkuyawa tare da mayar da al'amari zuwa gare shi. ga abin da Allah yake cewa a kan haka: *"Kuma a kusantar da Aljanna ga masu taƙawa, ba da nisa ba. Wannan shi ne abin da ake yi muku wa'adi da shi ga dukkan mai yawan komawa ga Allah, mai kiyaye umurninsa. Wanda ya ji tsoron mai rahama a fake, kuma ya zo da wata irin zuciya mai tawakkali".* A wata ayar kuma Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: *"Kuna masu mayar da al'amari zuwa gare shi, ku kuma bi shi da taƙawa, kuma ku tsayar da salla, kada kuma ku kasance daga cikin mushrikai".* Yana da matuƙar kyau kuma a lura da cewa, tawakkali yana gaba da *"Inába".* Saboda ana dogara ga Allah ne, domin a cim ma matakin mayar da al'amari zuwa gare shi.

Haka kuma mayar da lamari ga Allah, wani dalili ne da yake tabbatar ma bawa da samun arzikin duniya da Lahira. Tabbacin haka kuwa shi ne, faɗar Sheikhul Islam *Rahimahullah*: *"Shi bawa na Allah duk, babu abin da aka halicce shi domin sa, illa bauta ma Ubangijinsa. Saboda haka, ba shi da wani jin daɗi, da fari ciki, ko wata nagarta, da cika da kamala, sai idan ya tsare*

---

[183] *Madarij As-Salikin,* 1/244.

*alfarmar bautar nan ta Ubangijinsa, ya kuma mayar da gaba ɗayan al'amurransa zuwa gare shi".* [184]

Kai! saboda maɗaukakin matsayin da *Inába* take da shi ne a wurin Allah, Shaiɗan zai yi iyakar yinsa domin ya hana bawa aiwatar da ita. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Shaiɗan ba ya tashi yawaita kai hari ga bawa, sai lokacin da ya ɗaura aniyar mayar da al'amarinsa zuwa ga Ubangijinsa, ya kuma niƙi garin neman kusanci da saduwa da shi.*

Sai dai wannan ibada ta tawakkali da mayar da al'amari ga Allah wani al'amari ne, wanda matsayin bayin Allah a cikinsa yake bambanta. Wasu bayin sukan hau wannan mataki ne ta hanyar nisanta da ƙaurace ma ayyukan saɓo da yi ma Shari'a karan tsaye. A yayin da wasu kuwa sukan samu hakan ne ta hanyar shiga wasu nau'ukan ibada irin na fadanci da neman kusanci zuwa gare Allah *Subhanahu wa Ta'ala.* Wani kuma nasa matakin yakan tabbata ne ta hanyar ƙanƙan da kai ga Allah da yawaita du'a'i, da kuma nuna buƙata da kwaɗayi zuwa gare shi, ta hanyar yawaita roƙonsa biyan gaba ɗayan buƙatunsa". [185]

Kai! Hasali ma tsarin halittar ɗan Adam na azaliyya, abu ne da yake bayyana wajabcin tawakkali da bar ma Allah Maɗaukakin Sarki, al'amurra. Dubi abin da Shaihul-Islami *Rahimahullah* yake cewa: *"Tsarin halittar ɗan Adam na azaliyya yana tabbatar da wajabcin ƙudurta samuwar Allah da mayar da gaba ɗayan al'amurra zuwa gare shi".*

---

[184] *Al-Fatawa,* 14/32.

[185] *Ɗariƙ Al-Hijratain,* na Ibn Al-Kayyim, shafi na 292.

*HUJJOJIN TABBATAR DA ABINDA YA GABATA*

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:*

*"Dalili a kan Inába (tana cikin Ibada), shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ku kuma mayar da al'amari zuwa ga Ubangijinku, ku kuma sallama masa". Dalili a kan Neman taimako (na cikin Ibada) kuma, shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kai kaɗai muke bauta, kuma kai kaɗai muke neman taimako gare ka". A cikin Hadisi kuma: "Idan za ka nemi taimako, to, ka nemi taimakon Allah". Dalili a kan neman tsari (na cikin Ibada) kuma shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ka ce: Ina neman tsari da Ubangijin safiya". Da kuma faɗarsa: "Ina neman tsari da Ubangijin mutane". Dalili kuma a kan Neman agaji (na cikin Ibada), shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: A lokacin da kuke neman agajin Ubangijinku, sai ya karɓa muku". Dalili a kan Yanka (yana cikin Ibada) kuma shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ka ce: Lalle ne sallata, da baikona, da rayuwata, da mutuwata, na Allah ne Ubangijin talikai. Babu abokin tarayya a gare shi. kuma da wancan aka umarce ni, kuma ni ne farkon masu sallamawa". A cikin hadisi kuma an ce: Allah ya la'anci duk wanda ya yi yanka da sunan wanin Allah". Dalilia kan alwashi (na cikin Ibada) shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Suna cika alwashi kuma suna tsoron wani wuni wanda sharrinsa ya kasance mai tartsatsi ne".*

*"Dalili a kan",* cewa: *"Inába",* wata ƙasaitacciyar ibada ce, wadda Allah Maɗaukakin Sarki ya umarci bayinsa da ita: *"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ku kuma mayar da al'amari zuwa ga Ubangijinku, kuma ku sallama masa"* ta hanyar amfani da gaɓoɓinku. Wannan aya tana nunawa a fili cewa, mayar da lamari ga Allah, ibada ce, wadda Shari'a ke so. Saboda haka, karkatar da wannan ibada, ta hanyar mayar da lamari ga wanin Allah, Shirka ne.*

Ita kuwa *"Isti'anah"* tana nufin neman taimako. Ta kuma ƙunshi amincewa da Allah Maɗaukakin Sarki da kuma dogara gare shi, a cikin sigar cikakken ƙanƙan da kai. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Neman taimakon Allah Subhanahu wa Ta'ala ya haɗa abubuwa guda uku, waɗanda suka haɗa da cikakken ƙanƙan da kai ga Allah Maɗaukakin Sarki, da cikakkiyar amincewa da shi, da kuma dogara gare shi. Saboda haka duk wanda ya nemi taimakon wani wanda ba Allah ba, tare da jingina waɗannan abubuwa guda uku gare shi, to, ya yi ma Allah kishiya".* [186]

***"Dalili a kan",*** cewa: ***"Neman ceto",*** ibada ne: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kai kaɗai muke bauta, kuma gare ka ne kaɗai muke neman taimako"*** ba tare da wani daga cikin halittarka ba. Ambaton neman taimako bayan an ambaci ibada tattare da kasancewar tafiyarsu ɗaya ya faru ne sakamakon irin yadda bawa yake da buƙata da neman taimakon Allah Maɗaukakin Sarki a cikin kowace irin ibada. Saboda da zarar Allah bai sa masa hannu ba, ibadar kanta ba za ta samu yadda ake so ba. Ita dai bautar Allah Maɗaukakin Sarki, tana nufin nisantar gaba ɗayan ababen Shirka. A yayin da shi kuma neman taimakonsa yake tabbatar da yarda da rashin wani ƙarfi da wata dabara, sai nasa.

Daga nan zamu gane cewa, ginshiƙan addini guda biyu ne; bauta ma Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma neman agaji da taimakonsa shi kaɗai. Tsare alfarma da martabar bautar Allah, da rashin karkatar da ibadar neman agaji zuwa ga waninsa, su ne hanya ƙwara ɗaya tal, wadda ake bi a samu babban rabo na har abada, da kuma tsira daga kowane irin sharri. Haka maganar take, ko a so ko kar a so, tsira daga siratsin rayuwar duniya, da ɗimbin aikin da yake gaban ɗan Adam a Lahira, samunsu, sai an kiyaye martabar waɗannan ginshiƙai guda biyu. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Ba komai ake kira addini ba, illa bauta ma Allah Shi kaɗai, da kuma neman agaji da taimakonsa".* [187] Ba kuwa komai ne dalili ba, illa kasanceewar bauta tana wakiltar *Tauhidin Uluhiyyah* ne. A yayin da shi kuma kaɗaita Allah da neman

---

[186] *Madarij As-Salikin* 1/74.
[187] *Al-Fatawa* 11/524.

taimako, yake wakiltar *Tauhidin Rububiyyah.* Ga abin da Shaikhul-Islami *Rahimahullah* ya ce: *"Iyyaka Na'budu", ta ƙunshi tsantsar bauta ga Allah Maɗaukakin Sarki a matsayinsa na Ubangiji Makaɗaici. Haka kuma ta ƙunshi nuna masa ƙauna, da tsoron sa, da fatar samun alheri daga wurinsa, da kuma bin umurninsa, kazalika da nisantar abin da ya yi hani da shi. "Wa Iyyaka Nasta'inu", ita kuma tana nuni ne zuwa ga siffofin da suka taru, suka tabbatar da zaman Allah Maɗaukakin Sarki, Ubangiji, wato, Rububiyyah, waɗanda suka haɗa da tawakkali da mayar da al'amari, da kuma sallamawa gare shi".* [188]

Kuma *Isti'ána,* ɗin nan da ake magana, wato kaɗaita Allah da neman taimako da agaji, tana tabbata ne a cikin al'amurra da ba su riga sun kawo jiki ba. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* ya ce: *"Tawakkali da neman taimakon Allah, suna da alaƙa ne kawai, da al'amarin da aka sa gaba. Shi kuwa wanda ya riga ya faru, alaƙar da take tsakaninsa da bawa, ita ce, haƙuri da yarda da miƙa wuya".* [189]

Haka kuma neman taimakon Allah ibada ce mai girman daraja. Babu kuma abin da yake taimaka ma bawa wajen aiwatar da ita, sai faɗar *La-haula-wala-ƙuwata illa bil-lah.* Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Da zarar mutum ya furta La-haula-wala-ƙuwata illa bil-lah, to, ya nemi taimakon Allah. Saboda haka ne Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya Sunnanta faɗar ta a duk lokacin da ladan ya ce: Hayya alas salati. Mai karɓa masa ya ce: La-haula wala-ƙuwata illa bil-lah.[190]"[191]* A wani wurin kuma malamin yake cewa: *"Saɓanin yadda aka zata, tabbas, wannan kalma ta: La-haula wala-ƙuwata illa bil-lah, kalma ce da ake kira Istirjá'i don tana buɗe hanyar neman agajin Allah. Amma sai ga shi da yawa mutane sukan furta ta ne idan musibu sun kai musu ko'ina da nufin sakar ma Allah al'amari. Kuma a mafi yawan lokuta ba ta fitowa daga bakunansu, sai da amon fargaba da kasawa, ba haƙuri da juriya*

[188] *Al-Fatawa* 1/89.
[189] *Al-Fatawa* 13/321.
[190] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (588/) 1/222 daga Mu'awiyya *Radhiyallahu Anhu,* da *Sahih Muslim,* Hadisi na (385) 1/289 daga Umar ɗan Khaɗɗabi *Radhiyallahu Anhu.*
[191] *Al-Fatawa* 13322.

*ba".* [192] Ba kuwa wannan kalma kawai ba, ai mafi yawan addu'o'i, ana yin su ne saboda neman agaji a kan yi ma Allah cikakkiyar ɗa'a. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Shaikhul-Islami Rahimahullah yana cewa: Na yi nazari a kan wace addu'a ce ta fi kowace amfani? Sai na ga cewa, ita ce addu'ar da, a cikinta, bawa ya roƙi Allah taimako a kan aikata abin da Allah ya yarda da shi. Ko da na duba kuma, sai na taras, ayar da take cikin Suratul-Fatiha, wato, "Iyyaka na'abudu wa iyyaka nasta'inu" ta ƙunshi wannan ma'ana".* [193]

To, kuma yadda wannan lamari yake shi ne, da zarar musulmi ya tauna garɗin neman taimakon Allah Maɗaukakin Sarki, babu wani lokaci, da a cikinsa, zai sake neman taimako da agaji daga wani mahaluki. Da ma kuma babu wani lokaci da bawa zai samu sifar cika da kamala, sai lokacin da ya mayar da buƙatunsa gaba ɗaya a wurin Ubangijinsa. Shi kuwa duk wanda ya ƙi neman agaji da gudunmawar Allah, ya koma yana neman su ga waninsa, sai Allah ya bar shi da wancan bawan. Da zarar aka yi haka kuwa, to, babu abin da zai girba sai taɓewa da rashin arziki. Saboda haka ne, tarsashin Annabawa suka yi tsaye, tsayin daga a kan ganin sun umarci mutanensu da riƙa Allah Maɗaukakin Sarki wajen neman taimakonsu, shi kaɗai. Ga abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake cewa ta bakin Annabi Musa *Alaihis Salam: "Musa ya ce ma mutanensa, ku nemi taimakon Allah, ku kuma yi haƙuri".* ***"A cikin",*** wani: ***"Hadisi kuma",*** wanda Tirmidhi ya riwaito, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya umarci kowane musulmi da neman taimakon Allah Maɗaukakin Sarki shi kaɗai, da cewa: *"Idan za ka nemi taimako, to, ka nemi taimakon Allah"*[194] Malam Ibn Daƙiƙ Al-Id *Rahimahullah* ya ce: *"Gwargwadon duk yadda bawa ya dogara ga wanin Allah Maɗaukakin Sarki da wata buƙata, ko da bugawar numfashin zuciyarsa, ko wani guri, to, ya yi bankwana da Ubangijinsa, ya fuskanci wanda bai iya amfani ko cutar da shi da komai. Haka hukuncin yake a cikin jin tsoron wani wanda ba Allah ba".*

[192] *Al-Fatawa* 10/686.
[193] *Madarij As-Salikin* 1/78.
[194] *Sunan At-Tirmidhi* Hadisi na (2516) 2/385 daga Abdullahi ɗan Abbas *Radhiyallahu Anhu.*

Sai dai a kula, babu wata damuwa idan an nemi taimakon wani mahaluki, rayayye, a cikin wani abu da Allah ya ba shi iko a kan sa. Idan hulɗar ta kasance a kan wani lamari ne na alheri, to, ta zama kyautatawa kenan, wato, *Ihsani.* A kan haka ne Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake cewa: *"Kuma ku taimaki juna a kan ɗa'a da taƙawa".* Idan kuma hulɗa ce ta zunubi da wani aiki na ashsha, to, ta zama haramun kenan. A kan wannan kuma, Allah Maɗaukakin Sarki cewa ya yi: *"Kuma kada ku taimaki juna a kan zunubi da shishshigi".* Amma, neman taimako da agajin matattu, ko wasu rayayyu waɗanda ba su kusa, kai ko waɗanda suke kusa ɗin, a kan wani al'amari wanda Allah bai ba su iko a kai ba, yin haka Shirka ne.

Shi kuwa bawa, ko waye, mai cikakken rauni ne a karan kansa; babu yadda za a yi ya wadatu da kan sa, a wayi gari ba shi da buƙata da Ubangijinsa. Saboda haka duk wanda ya sa wata manufa a gabansa, to, babu abin da yake wajaba a kan sa, illa ya nemi taimako da gudunmawar Ubangijinsa, a cikin siga ta tawakkali da nuna fatara da buƙata zuwa gare shi don cin ma nasara. Tabbatacciyar magana ce kuwa, a matsayin wata falala, wadda Allah Maɗaukakin Sarki, ya tanadar ma bayinsa cewa, babu wani lokaci da wani bawa nasa zai dogara gare shi, face ya taimake shi. Ashe kenan *Istiána* ibada ce mai girman daraja, wadda in babu ta ba addini. Saboda haka ya zama wajibi a kan duk wani bawa na Allah, ya tsare alfarmarta, ya kuma nisanci yin wasa da lamarita. A wata Hausar kana iya cewa, *Istiána* na nufin neman mafaka, da madafa ne, da kuma makarkata. A tantagaryar magana kuma, ba komai take nufi ba illa, tsere ma wani abu da ake tsoro da fargaba, zuwa ga wanda yake da ikon bayar da kariya daga gare shi. Bisa wannan fassara, idan mutum ya nemi taimakon Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, to kamar ya fake a wurinsa kenan, a cikin siga ta neman agaji. Sa'annan kuma yana ji a ransa cewa, lalle Allah Maɗaukakin Sarki ya isa ya ba shi wannan kariya, cikakkiya daga kowane irin sharri.

*Istiána,* ibada ce daga cikin ibadojin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya umarci bayinsa da su. Kamar yadda yake cewa: *"Kuma idan wata fizga daga Shaiɗan ta fizge ka, sai ka nemi tsari ga Allah".* A wata ayar kuma *Subhanahu*

*wa Ta'ala* yake cewa: *"Sa'annan idan ka karanta Alƙur'ani, sai ka nemi tsari ga Allah daga Shaiɗan jefaffe".* Mawallafin littafin *Fathul-Majid* shi kuma, ga abin da yake cewa: *"Tabbas, kan malamai ya haɗu a kan cewa, ba ya halatta a nemi tsari da wanin Allah".* [195] Babu kuma wanda yake iya kare mutum, ko yaye masa baƙin ciki, ya kuma kuranye masa kowane irin haɗari, sai Allah Ubangijin talikai. Ita kuwa rayuwa a wannan gidan duniya cike take maƙil da matsaloli, da miyagun abubuwa irin waɗanda ɗan Adam yake ƙi, yake kuma ƙyama. Babu kuma wani mahaluki, wanda ba shi da maƙiya daga cikin aljannu da mutane, waɗanda babba daga cikinsu shi ne Ɗan-lisu, la'antaccen Allah. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* : *"Lalle, haƙiƙa, Shaiɗan, a gare ku, maƙiyi ne. Saboda haka ku riƙe shi a matsayinsa na maƙiya".* Ba sauran mutane fararen hula kawai ba, duk da Annabawa *Alaihimus Salam,* suna da maƙiya daga cikin aljannu da mutane. Ga abin da Allah yake cewa a kan haka: *"Kuma kamar wancan ne, muka sanya ma kowane Annabi maƙiyi; Shaiɗanun mutane da aljannu, sashensu yana yin ishara zuwa ga sashe da ƙawataccen zance bisa ga ruɗi".* Haka su ma mabiyan Annabawa da Manzanni, sukan haɗu da jarrabawowi iri-iri.

Ashe kenan, babu wani mahaluki da zai iya bugun gaba, ya ce, ba shi da buƙata da kariya da tsarin Allah Maɗaukakin Sarki, daga sharrin mutane da aljannu, da kuma sauran matsalolin rayuwa. Wanda kuma duk ya tsayar da buƙatarsa ta neman tsari ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, to, haƙiƙa ya tsare alfarma da mutuncin wata ibada mai maɗaukakiyar daraja, wadda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi umurni da ita a wurare da yawa a cikin littafinsa.

***"Dalili a kan",*** cewa: ***"Neman tsari kuma",*** wani nau'i ne na ibada: ***"Shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki",*** ya kai Manzo: ***"Ka ce",*** a cikin siga ta neman tsari, kai da gaba ɗayan al'ummarka: ***"Ina neman tsari",*** da mafaka da madogara: ***"Da Ubangijin safiya",*** kuma mahaliccinta. ***"Da kuma faɗarsa: Ka ce: "Ina neman tsari da Ubangijin mutane",*** kuma mahaliccinsu. An kuma samo cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana ce ma Uƙbatu ɗan Amir *Radhiyallahu Anhu: "Ko ka samu labarin wasu ayoyi da aka saukar a daren*

---

[195] *Fath Al-Majid Sharh Kitab At-Tauhid*, shafi na 188.

*yau, waɗanda ba a taɓa saukar da irinsu ba, wato, ƙula'uzu bi Rabbin Nasi* da *bi Rabbil Falaƙi".* Muslim ne ya riwaito.[196]

Saboda wannan matsayi da suke da shi, waɗannan Surori, yake wajaba ga kowane musulmi ya lizimci karanta su domin neman tsari kullum, safiya da marece. Idan ya yi haka, wani abu mummuna, ba zai same shi ba a cikin wannan wuni da darensa. An riwaito cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam,* ya yi ma Sahabi Uƙbatu ɗan Amiru wasicci da neman tsari ta hanyar karanta su, yana mai cewa masa: *"Ka nemi tsari ta hanyar karanta Kula'uzzai, domin babu wani mahaluki da ya nemi tsari da wani abu wanda ya kai su".* Abu Dawuda ne ya riwaito.[197] Kari a kan haka kuma Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullahu* yana cewa: *"Buƙatar da bawa yake da ita, ta neman tsari, ta hanyar karanta waɗannan Surori, ta fi ƙarfin buƙatar da yake da ita, ta rayuwa da abin ci, da na sha, da kuma tufafi".* [198]

Tabbatacciyar magana ce kuwa cewa, Allah Maɗaukakin Sarki mai cikakken ƙarfi da ɗaukaka ne. Saboda haka duk wanda ya nemi mafaka a wurin sa, babu mai iya watse masa kaya. Duk irin yadda dalilan saukar wani bala'i ko wata musiba, suka tattara a kan sa, sai su sami kansu cikin rikici. Ga abin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake cewa: *"Duk wanda ya sauka wani wuri, kuma ya ce: "A'uzu bi kalmatillahit-tammati min sharri ma khalaƙ", babu wani abu da zai cutar da shi, har lokacin da ya naɗe kayansa ya bar wurin".* Muslimu ne ya riwaito.[199] Imamul Kurɗabi *Rahimahullah* kuma ya ce: *"Wannan hadisi ne ingantacce, magana ce kuma wadda ba ta tashi. Bayan masaniyar da muke da ita, ta ingancinta ta fuskar karatu da ilimi, mun kuma jarraba mun gani. Ni da kaina, tun lokacin da na ji wannan Hadisi nake amfani da shi, tun daga wannan lokaci kuwa, babu wani abu da ya same ni. Haka na yi ta rayuwa, sai can wani ɗan lokaci, na daina karantawa, ai kuwa sai kunama ta*

---

[196] *Sahih Muslim,* Hadisi na (814) 1/558.
[197] *Sunan Abi Dawud,* Hadisi na (1463) 2/73.
[198] *Bada'i' Al-Fawa'id*, 2/199.
[199] Hadisi na (2704) 4/2081 daga Khaulatu 'yar Hakim *raliyallahu anha..*

*cije ni a wani wuri da ake kira Mahadiyyah*[200] *a cikin dare. Da na yi nazari sai na tuna cewa, lalle na manta ne in karanta waccan addu'a".* [201]

Mutum ko waye shi, tsattsage tsarin halittarsa yake da rauni. Saboda haka babu wata cuta da cutarwar da ba su iya samunsa. Idan ka ji ɗan Adam yana jin daɗin rayuwa, to, kada ma ka tambaya, yana cikin masu neman tsarin Allah Maɗaukakin Sarki. Bisa haka, ya zama wajibi bawa ya san cewa, cuta da amfani duk a hannun Allah suke. Duk irin yadda wani mahaluki ɗan'uwanka ya lashi takobin cutar da kai, ba yadda za a yi wannan buƙata tasa ta iya biya, matuƙar Allah bai so ba. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa: *"Kuma ka sani, in da gaba ɗayan al'umma za su taru domin su amfane ka da wani abu, ba za su iya amfanin ka da komai ba, sai da abin da Allah ya rubuta maka shit un can daɗai. In da kuma za su taru domin su cuta maka da wani abu, ba za su iya cutar da kai da komai ba, sai da abin da daman Allah ya riga ya rubuta maka shi tun daɗai. An riga an rubuta kuma bakin alƙalami ya riga ya bushe".* Tirmidhi ne ya riwaito shi.[202]

A cikin Alƙur'ani kuma, Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana cewa, akwai waɗansu abubuwa waɗanda a zahiri, tabbas sihiri ne, a ganin idon bawa. Amma kuma, tattare da haka, tasirinsu yana da shamaki da dabaibayi. Ga abin da Buwayayyen Sarkin yake cewa: *"Kuma ba su zamo masu cutar da wani da shi ba, face sai da izinin Allah".*

Saboda haka neman tsarin Allah Maɗaukakin Sarki, ibada ce, daga cikin manya-manyan ibadoji. Ah! Ba ka ganin har Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, ta tabbata, Allah ya umarce shi da neman tsari ta hanyar karanta Kula'uzzai, domin samun kariya daga sharrin gaba ɗayan abokan halitta, da sharrin mahassada, da masihirta, da 'yan dabo da ƙulunboto? Ma'ana, Sarkin da yake da ƙarfin ikon gusar da duhun dare, shi ne kaɗai yake da ƙarfin ikon kawar da duk wani abu da, wanda ya nemi tsarinsa, yake tsoro da fargaba.

---

[200] Mahadiyyah, wata alƙarya ce babba a ƙasar Andalusiya.

[201] *Fath Al-Majid*, shafi na 190.

[202] *As-Sunan,* na Tirmidhi, Hadisi na (2516) 2/385 daga Abdullahi ɗan Abbas *Radhiyallahu Anhuma.*

Sai dai kamar yadda muke ta faɗa, muna daɗa maimaitawa. Babu laifi a nemi taimako da agajin wani abokin halitta, rayayye, wanda kuma yake kusa a cikin abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya fuwace masa. Tabbacin wannan kuwa shi ne Hadisin Jabir ɗan Abdullahi *Radhiyallahu Anhu,* wanda yake cewa, an kama wata Bamakhzumiya, ta yi sata, aka kuma taso ƙeyarta sai gaban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* Ganin haka ita kuma sai ta nemi agaji wajen Ummu Salamata *Radhiiyallahu Anha,* matar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* Sai Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce mata: *"Ai ba ita ba, ko Faɗimatu 'yar Muhammadu - Sallallahu Alaihi wa Sallam - aka kama da laifin sata babu abin da zai hana Hauni ya sha hannunta".* Muslim ne ya riwaito shi.[203] Mawallafin littafin *Taisir Al-Aziz Al-Hamid* yana cewa a kan haka: *"Ya halatta a nemi taimakon wani abokin halitta a cikin abin da yake da iko da shi, a kuma nemi tsarinsa. Saɓanin abin da ba shi da iko a kai. Irin wannan kam, ba ya halatta a nemi agajin kowa a cikinsa, sai Allah".* [204]

Amma, neman tsari da matattu, ko waɗanda ba su kusa, rayayyu, ko kuma da rayayyu waɗanda suke kusa, a kan wani al'amari wanda ba huruminsu ba, wannan Shirka ne. tabbacin wannan kuwa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki da ya ce: *"Kuma tabbas, wasu mazaje daga cikin mutane, sun kasance suna neman tsari da wasu mazaje daga cikin aljannu, saboda haka suka ƙara musu girman kai".*

Saboda haka ɗan'uwa musulmi! Kada ka kuskura ka nemi taimako ko tsari ga wani, wanda ba Allah Maɗaukakin Sarki ba. Babu mai iya yi maka kariya daga duk wata halaka bayan shi. haka kuma babu mai iya samar maka da wani amfani in ba shi ba.*

Ga abin da ya gabata, ana iya fahimtar cewa, *Istigása,* tana nufin neman ceto da agaji da mafita daga wani mawuyacin hali da yanayi mai tsanani. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: "*Istigása* ba ta zuwa sai bayan an cika da tsoro da fargaba da tashin hankali". [205] Ɗan bambancin da

---

[203] *Sahih Muslim,* Hadisi na (1689)3/1316.
[204] *Taisir Al-Aziz Al-Hamid*, shafi na 211.
[205] *Bada'i' Al-Fawa'id,* 1/60.

yake akwai tsakanin addu'a irin waɗanda aka sani, da *Istigása,* shi ne, ita *Istigása* tana zuwa ne daga wanda baƙin ciki ya yi ma riga da wando. A yayin da ita kuwa addu'a, sha kundum ce. Ma'ana da wanda baƙin cikin ya yi wa zoba, da wanda ba shi ba, duk suna yin ta. Ashe kenan akwai bambanci, idan wanda ya samu kansa a cikin kogin baƙin ciki da damuwa, ya ɗaga hannu sama ya roƙi Ubagijinsa, sai a ce, ya nemi agaji da ceto, wato, *Istigása* kenan. Ita wani nau'i ne, na addu'a, na musamman wanda ake yi a lokacin matsuwa.

Haka kuma akwai bambanci tsakanin *Istigása* da *Istiáza.* Kamar yadda bayani ya gabata, *Istiáza* tana nufin neman tsari da kariya daga faruwar wani bala'i. A yayin da ita *Istigása*, neman agaji ne ga Allah Maɗaukaki Sarki, ya kuranye ma mutum wani bala'i da ya riga ya faɗa masa.

Bisa wannan fassara, kenan, *Istigása* ta ƙunshi cikakkiyar buƙata zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma ƙudurcewa a zuci cewa, ya isa ɗaukar wannan nauyi. A wannan matsayi nata, ana lissafa ta, ɗaya daga cikin manya-manyan ayyuka na ibada, masu cika da kamala. Hakan kuwa na ƙara fitowa fili, idan aka yi la'akari da yadda, *asalatan*, rayuwar ɗan Adam take cike maƙil da matsaloli na baƙin ciki iri-iri da sauran bala'o'i. To, duk wanda ya nemi agaji da ceton Ubangijinsa a cikin kuranyewar waɗannan matsaloli, haƙiƙa, ya tsare alfarmar wata gagarumar ibada, wadda Annabawa da Salihan mutane suka yi matuƙar kulawa da mayar da hankali ga reta, a duk lokacin da suka samu kansu a cikin tsanani. Nan take kuwa sai Allah ya kawo musu agaji ta hanyar fitar da su daga cikin kowane irin baƙin ciki.

***"Dalili a kan",*** cewa: ***"Neman Ceto",*** da agaji ibada ne: ***"Shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki:*** Ku tuna ni'imar Ubangijinku:***"A",*** daidai: ***"Lokacin da",*** kuka kusa haɗuwa da maƙiyanku, sai: ***"Kuke neman agajin Ubangijinku, Sai ya karɓa muku…"*** Wannan aya tana bayar da labarin abin da ya faru ne a ranar yaƙin Badar, lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya fahimci irin yadda mushrikai suke da yawa. Sai kawai ya fuskanci Ubangijinsa, yana roƙo yana fadanci zuwa gare shi, da neman agaji da ceto da gudunmawa. *Allahu Akbar! "Ko wane ne yake karɓa ma mai buƙata idan ya kira shi?!* Nan take kuwa sai Allah Maɗaukakin Sarki ya ba wa Annabinsa nasara da

cikakkiyar galaba a kan maƙiyansa, inda suka kashe na kashewa, suka kama na kamawa, tutar Musulunci ta filfila, har aka raɗa ma wannan rana suna, "Ranar Raba Gardama".

Waɗannan ayoyi da suka gabata, suna nuna cewa, *Istigása* na daga cikin manya-manyan ibadoji. Karkatar da ita kuma, zuwa ga wani, wanda ba Allah Maɗaukakin Sarki ba, Shirka ne. Wato, kamar a wayi gari mutum yana neman agaji daga wani gunki, ko wasu matattu, ko waɗanda ba su kusa, ko matara kama da su. Malam Ibn Al-Kayyim yana cewa: *"Neman biyan wata buƙata ga wasu matattu, da neman agajinsu, da mayar da hankali gare su, yana daga cikin nau'ukan Shirka. Hasali ma da irin haka ne Shirka ta soma a bayan ƙasa. Ai, in akwai hankali kamata ya yi a gane cewa, wanda duk ya mutu, komai nasa ya ƙare. Ba ya iya amfanar da kan sa da wani abu; tabbatar da alheri ko kuranye sharri, balle ya amfani waninsa, da ya roƙi wata buƙata ko wani ceto, tsakanin sa da Allah".* [206] Irin wannan neman ceto, babu abin da zai ƙara ma mai shi, sai da-na-sani da hasara. Tunda yana bibiyar ruwan faƙo ne, babu kuwa ranar da zai kai gare shi, ko ya yi shekarun Abarshi. Haka zai tabbata cikin hasara a nan duniya, Lahira kuma ya taras da baƙar azaba. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* ya cirato daga Abu Yazid *Rahimahullah* yana cewa: *"Neman ceto tsakanin abokin halitta da abokin halitta ɗan'uwansa, kamar neman ceto ne tsakanin wanda ruwa ya ci, ga wani ɗan uwansa shi ma wanda ya faɗa a cikin teku zai nutse".*

Saboda haka duk wanda yake kiran wani, ba Allah ba, daga cikin matattu, ko rayayyu waɗanda ba su kusa, da sunan neman biyan wata buƙata. To, har abada buƙatar tasa ba za ta biya ba komai tsawon shekarun da ya kwashe a kan haka. Ga abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa a kan haka: *"Ko da kun kira su, ba su jin kiranku. Ko da sun jiya kuma, ba za su karɓa muku ba".* Sai dai kamar yadda muka sha faɗa muna nanatawa a baya, neman biyan buƙata ga rayayyu, waɗanda suke kusa, suke kuma da iko a kan wani abu, ya halatta idan a kan abin ne ake da buƙatar. Ga abin da Allah Ta'ala yake cewa a cikin ƙissar Annabi Musa *Alaihis Salam: "Sai wanda yake daga cikin mutanensa ya nemi agajinsa a kan wanda yake cikin maƙiyansa".* Wannan

[206] *Madarij As-Salikin,* 1/346

kenan. Amma, saukarwa tare da neman biyan wata buƙata gare su, alhali ba su da iko a kan ta, ko neman ta ga waɗansu matattu, ko waɗanda ba su kusa, yin haka, Shirka ne a cikin bauta.

A maimakon haka, idan bala'i ya faɗa maka, ko baƙin ciki ya yi maka katutu. Kada ka nemi agaji da taimako daga kowa sai masanin gaibi, Allah *Subhanahu wa Ta'ala.* A hannunsa ne ikon sammai da ƙassai suke shi kaɗai. Maɗaukakin Sarkin yana cewa a kan haka: *"Umurninsa yana kasancewa ne kawai, idan ya yi nufin faruwar wani abu, sai ya ce masa: "kasance" sai abin ya kasance (yadda ya nufe shi)".*

Yanka da sunan Allah na daga cikin manya-manyan ayyukan ɗa'a, kuma mafi girman duk wata ibada da ake yi da dukiya. Haka kuma wata alama ce da take nuna nauyin imanin mutum da tsarkin zuciyarsa. Saboda ita dabbar da za a yanka ɗin, ai abu ce da bawa yake so yake kuma bukata. To, idan aka wayi gari ya sadaukar da ita domin Allah da neman kusanci gare shi. Haka ta sa ya kwantar da ita ya yanka, to, ai ba mamaki idan an ce, babu wata ibada ta dukiya da ta kama ƙafar wannan. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Irin yadda imani da Allah da ikhlasi suke bayyana a fuskokin masu yanka dabbobi saboda Allah, da ƙarfin yaƙini, da kyautata zato, al'amari ne mai ban sha'awa".* [207] Abin a fili yake kamar hasken rana.

***"Dalili a kan cewa Yanka",*** ibada ne mai girma a wurin Allah: ***"Shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ka ce: Haƙiƙa Sallata",*** ta yau da kullum: ***"Da yankana, da rayuwata da mutuwata duk na Allah ne, Ubangijin talikai",*** kuma abin bautarsu: ***"Babu abokin tarayya a gare shi",*** a cikin bauta, kamar yadda ba shi da abokin tarayya a cikin mallaka da sarrafa ɗakin duniya. ***"Kuma da wancan",*** hali ne, na tsarkakae waɗannan ayyuka na ibada domin Allah: ***"Aka umarce ni",*** umurni mai tsananin ƙarfi, wanda saɓa shi gare ni, ba shi yiwuwa: ***"Kuma ni ne farkon masu sallamawa",*** daga cikin wannan al'umma.[208]

---

[207] *Al-Fatawa* 16/532.

[208] Allah maɗaukakin Sarki ya keɓance waɗannan ibadoji ne, ya ambace su, su kaɗai, saboda girma da ɗaukakar da suke da su, da matsayin da suke da shi na alamar da ake gane mutum yana so yana kuma ƙaunar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* da ita, da kuma

Ka kuwa san dai, duk wanda lalacewa da rashin sanin girman kansa, suka ba shi dammar yin wata ibada ba domin Allah ba. Wato, kamar yanka domin wasu gumaka ko ƙaburbura, domin girmamawa zuwa gare su, ko tsoronsu, ko neman wata alfarma daga ma'abuta wuraren, ko don farin cikin karɓar baƙuncin wasu shigabanni, ko wani abu mai kama da wannan. To, tabbas ya faɗa cikin Shirka. Daɗa dabbar da ya yanka ɗin aƙumi ne ko nagge, tunkiya ko akuya, kaza ko wani tsuntsun ƙanƙani. Koma dai mene ne, alwashin narko ya riga ya tuzgo: ***"A cikin Hadisi kuma",*** inda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake cewa: ***"Allah ya la'anci wanda ya yi yanka da sunan wanin Allah".*** Wato a kori mai irin wannan aiki daga rahamarsa; ba shi ba ta, tunda ya zubar da jinni domin waninsa". Muslimu ne ya riwaito.[209]

Saboda haka duk wanda Shaiɗan ya yi wa kiɗa, ya kuma taka ta hanyar yanka wata dabba domin wanin Mahaliccinsa, haƙiƙa ya kafirce ma ni'imar Allah, ya kuma rusa wani ɓangare na *Rububiyyah,* ya kuma yi tasgaro ga *Uluhiyyah*, tunda ya ɗaukaka darajar wani mahaluki fiye da yadda ya kamata. Saboda haka kuma, ya tsunduma kan sa a cikin azabar Allah, kuma an la'ance shi, an kore shi sakamakon wannan aika-aika. Eh! aika-aika mana, tunda ya zubar da jini ta hanyar yanka domin wanin Allah.*

Shi kuwa "alwashi" yana nufin mutum mai hankali, ya ɗora ma kan sa wani nauyi, wanda Allah bai ɗora masa ba asalatan a shar'ance. To, shi ma wannan ibada ce, wadda karkatar da ita zuwa ga wanin Allah ba ya halatta.

---

bauta masa da zuciya ɗaya. Salla ibada ce maɗaukakiya, wadda ake gudanarwa da gangar jiki. Yanka kuwa ibada ce, shi ma mai girman daraja, wadda ake yi da dukiya. Duk kuwa wanda ya yi salla, ya kuma yi yanka, saboda Allah Maɗaukakin Sarki shi kaɗai, ba zai kasa yin sauran ibadoji na aiki da magana saboda shi ba. Duk kuwa wanda ya sadaukar da jiki da dukiyarsa ta hanyar yanka domin samun yarda da kusanci ga Allah Maɗaukakin Sarki, lalle ya cika musulmi. Dubi irin yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya umarci Manzonsa da yin waɗannan ibadoji guda biyu dominsa kawai saboda girman matsayin da suke da shi, ya ce masa: *"Sai ka yi salla domin Ubangijinka ka kuma soke dabba"* dominsa ba shi kaɗai. Kamar dai yadda sallah, ba ya halatta a yi ta ba domin Allah ba, *kazalika,* yanka ba ya halatta a yi shi ba dominsa ba.

[209] *Sahih Muslim,* Hadisi na (1978) 3/1567 daga Aliyu ɗan Abi Ɗalib *Radhiyallahu Anhu,* da wannan lafazi, wato: *"Allah ya la'anci wanda ya yi yanka domin wanin Allah. Ya kuma la'anci wanda ya ba wa ɗ an bidi'a mafaka, da wanda ya la'anci mahaifansa, da wanda ya canza wa mannara alƙibla."*

*"Dalilin"*, kasancewar: *"Alwashi"*, ibada ne wadda kaɗaita Allah Maɗaukakin da ita, yake wajaba: *"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki"*, yana yabon masu yin sa da cewa: *"Suna cika alwashi"*, irin wanda suka ɗora wa kan su. Tunda kuwa suke cika alwashin da suka ɗora ma kan su, irin waɗannan bayi na Allah, ashe ɗauke nauyin abin da aka ɗora musu na farillai na asali, shi ne mafi sauƙi da zama kusa. Irin wannan yabo kuwa da suka samu daga Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ba kasafai yake yin sa ba, sai ga waɗanda suka cika sharuɗɗan zama bayinsa na gaske.

Bayan haka kuma ya ci gaba da cewa, su waɗannan mutane: *"Suna kuma tsoron wani wuni"*, mai tsanani: *"Wanda sharrinsa"*, wato, tsanance-tsanance da tashin hankali irin waɗanda suke tattare a cikinsa, mizaninsu: *"Ya kasance mai tartsatsi ne"*, da galabaitarwa ga duk wanda rahamar Allah Maɗaukakin Sarki ba ta yi masa inuwa ba. Sai dai duk musulmi na ƙwarai, ya tsira daga wannan azaba, tunda ba yadda za a yi, ya karkatar da wani yanki na bauta ga wanin Allah. Ba zai yi haka ba ko alama, tunda zuciyarsa kodayaushe tana cike da so da ƙaunar Allah *Subhanahu wa Ta'ala.* A maimakon haka dukkan ibadojinsa yana gudanar da su ne zuwa ga Allah. Babu kuma wani alƙawari ko alwashi da zai sha ko ɗauka, a cikin wani da Shari'a ba ta wajabta masa ba, face a wajen Allah kawai. Yana kuma yin haka ne bisa aiki da faɗar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam: "Duk wanda ya sha alwashin aikata wani abu domin Allah, to, ya zartar da shi. Wanda kuwa ya sha alwashin saɓa ma Allah, to, kada ya aikata".* Buhari ne ya riwaito.[210]

Bisa wannan magana ta Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, duk wanda ya kuskura, ya sha wani alwashi don girman wani mahaluki koma bayan Allah, to, ya sani, ya tabbata ɗaya daga cikin waɗanda suka karkatar da wani nau'in ibada zuwa ga wanin Allah. Sakamakon haka kuma, ya zama mushriki, kuma laifinsa ya fi ƙarfin na duk wani mai saɓo. Shaikhul-Islami *Rahimahullahu* yana cewa: *"Duk wanda ya ɗauki alwashi ga wani wanda ba Allah ba, to, ya*

[210] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (6318) 6/ 2463.

*tabbata mushriki. Matsayinsa, matsayin wanda ya yi rantsuwa ne da wanin Allah; Shirk ace babba wadda babu irinta".* [211]

Duk wanda ya sha wani alwashi saboda girman wanin Allah, to, ba ruwan Allah da shi; alwashinsa ma bai karɓa sunan alwashi ba a idanun Shari'a. Saboda haka ba dole ba ne sai ya cika shi. Kai! yin haka ma haramun ne. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Shan alwashi saboda girma wasu ƙaburbura, ko wani da yake kwance a cikinsu. Kamar shan alwashi saboda girman Annabi Ibrahimu alaihissalam,* ko na wani Shaihin Malami, ko dai wani can daban, ko wasu ɗaiɗaiku daga cikin mutanen gidan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, ko waninsu, duk wannan ya saɓa ma Shari'a. Saboda haka ba lalle ne, sai ya cika shi ba, bisa haɗin kan shugabannin addini. Kai! cika shi ma haramun ne. Ai, ta riga ta tabbata a cikin ingantaccen littafi,[212] daga Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, cewa: *"Duk wanda ya sha alwashin biyayya ga Allah, to, ya aikata. Wanda kuma duk ya sha alwashin saɓa masa, to, ya sake shawara".* Bukhari ne ya riwaito.[213]

To, wai ya ma za a yi kana musulmi, ka karkatar da wata ibada zuwa ga wani mahaluki, wanda ba Allah ba, wanda ba shi da ikon amfanarwa ko cutar da kai. Kai ka san duk wanda ya yi haka, ya cika maras gaskiya. Hasali dai shi alwashi, ba a shan sa, sai domin girma da ɗaukakar Allah *Subhanahu wa Ta'ala.* Duk kuma wani alwashin da aka sha domin Maɗaukakin Sarki Allah, to, wajibi ne a cika shi. Sai dai *asalatan* shan alwashin ko domin Allah Maɗaukakin Sarki, makaruhi ne. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam,* ya bayyana cewa shan sa, ko alama: *"Ba ya sa komai, ba ya kuma hana komai. Kuma lalle, babu wani alheri da yake zuwa da shi, illa dai kawai, ana tantance marowaci ne ta hanyarsa".* Buhari da Muslimu ne suka riwaito shi.[214] Sai dai idan har mutum ya riga ya ƙulla alwashi, to, wajibi ne ya yi shi domin Allah, kawai, saboda alwashi ibada ne.*

---

[211] *Al-Fatawa,* 33/123.
[212] Yana nufin *Sahih Al-Bukhari*
[213] *Al-Fatawa* 27/147.
[214] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (6234) 6/2437, da *Sahih Muslim.* Hadisi na (1639) 3/1261 daga Ibnu Umar *Radhiyallahu Anhu.*

## SHISHSHIKE NA BIYU: MU SAN ADDININ ALLAH

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:*

*"Shishishike na biyu shi ne: Sanin addinin Musulunci ba sanin shanu ba; bisa hujjoji da dalilai. Shi ne miƙa wuya ga Allah Maɗaukakin Sarki ta hanyar kaɗaitawa, da jawuwa zuwa gare shi ta hanyar biyayya, da yi ma Shirka da mutanenta tawaye. Shi kuma mataki uku ne: Musulunci da Imani da Ihsani. Kowane mataki kuma yana da shika-shikai. Shika-shikan Musulunci biyar ne: Shaidar babu abin bauta sai Allah, da tsayar da Sallah, da bayar da Zakkah, da Azumin watan Ramadhan, da Ziyartar ɗakin Allah mai alfarma".*

Kamar yadda bayani ya gabata, wajibi ne a kan kowane musulmi, ya ƙwanƙwance tuwasu guda uku, waɗanda suka haɗa: Sanin ko waye Ubangijinsa, kamar yadda mawallafin littafin *Rahimahullah* na asali ya bayyana a baya kaɗan, cewa Ubangijinmu dai shi ne Allah. Shi ne kuma abin bautarmu, shi kaɗai. Mun kuma gane samuwarsa ne, da duk abin da ya shafe shi, ta hanyar ayoyi da halittunsa. Sa'annan kuma mawallafin ya ambaci wasu dangogin ibada, ya kuma bayyana cewa ba ya halatta a karkatar da su, zuwa ga wanin Allah Maɗaukakin Sarki. Yin haka kuwa, Shirka ce ba 'yar ƙarama ba.

Daga nan kuma sai mawallafin ya ci gaba, a nan, da cewa: *"Shisshike na biyu shi ne: Sanin addinin Musulunci",* wanda Allah Maɗaukakin ya halicce mu domin mu bauta masa da shi.

Sanin ƙabli da ba'adin wannan addini da tuwasun da aka ɗora harsashensa a kai, na ayoyi da hadisai, wajibi ne ga mutum. Domin hakan ce kawai za ta ba shi cikakkiyar damar bauta ma Allah ala basiratin. Matuƙar hakan ta faskara kuwa, to, ana ji wa musulmi tsoro a rayuwarsa ta duniya da ta Lahira. Bayan mutuwarsa, a cikin ƙabari, lokacin da Mala'iku za su tambaye shi, abu ne mai matuƙar sauƙi ya shiga ruɗani; ya bayar da mummunar amsa,

ta hanyar buɗe baki ya ce: *"ban sani ba!, ban sani ba!!, ban sani ba!!! Na dai ji mutane suna faɗa ne kawai, ni ma na faɗa".* [215] Saɓanin mutumin da ya san addini, yake kuma bauta ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* bisa hujjoji da dalilai na ayoyi da hadisai. A rayuwarsa ta duniya kuma, yana biye da gaskiya kamar yadda addini ya yi masa tanadi. Irin wannan mahaluki, da zarar ya samu kansa gaban waɗancan Mala'iku, suka kuma yi masa irin waɗancan tambayoyi, nan take zai karɓa masu da cewa: Ubangijina shi ne Allah. Addinina kuma shi ne Musulunci. Annabina kuma shi ne Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*[216] To, babu kuwa abin da yake taimakon mutum a kan amsa waɗannan

---

[215] Wannan shi ne abin da zai faru kamar yadda ya zo a cikin Hadisin Bara'u ɗan Azib *Radhiyallahu Anhu,* cewa: *"Sai a mayar wa mamaci rayuwarsa a cikin gangar jikinsa. Ana nan sai wasu Mala'iku biyu su zo masa. Bayan sun zauna sai su tambaye shi: Wa ye Ubangijinka? Sai ya buɗe baki ya ce: Ban sani ba. Sai kuma su sake ce masa: To, mene ne addininka? Sai ya buɗe baki ya ce: Ban sani ba. Sai su sake ce masa: To, mene ne matsayin mutumin da aka aika maku? Shi ma sai ya buɗe baki ya ce: Ban sani ba. Sai kawai a ji wani sauti daga sama yana cewa: Karya yake yi! Ku yi masa shimfiɗar wuta, ku kuma buɗe masa wata taga daga gidan wuta, ta yadda zafi da dafinta za su riƙa shigo masa. Daga nan sai a ƙuntata masa ƙabarinsa har sai haƙarƙarinsa na dama sun haɗu da na hagu. Sai kuma ya ga wani mutum mai mummunar fuska da munanan tufafi, mai ɗoyi, ya zo masa. Da zuwa sai ya ce masa: Ina farin cikin sheda maka yau za ka haɗu da abubuwan baƙin ciki a wannan rana da ta daɗe tana jiran ka, wadda aka yi maka alƙawari. Sai shi kuma ya tambaye shi: Waye kai? Ɗan baƙi mai baƙin labari? Sai ya karɓa masa da cewa: Ni ne mummunan aikinka. Da jin haka sai ya roƙi Ubangiji yana cewa: Ya Allah! Kada ka nuna mini ranar Alƙiyama."* Ahmad ne ya riwaito shi, Hadisi na (18557) 4/187.

[216] Tabbacin wannan shi ne, Hadisin Bara'u ɗan Azib *Radhiyallahu Anhu,* cewa: *"Da zarar bawa mumini ya kai marhalar barin duniya da fusakantar Lahira, sai waɗansu Mala'iku masu fararen fuskoki kamar hasken rana, suna ɗauke da likkafanin aljanna, da nau'ukan turare daga can, su sauko masa daga sama. Sai su zauna kusa da shi sosai, yana ganin su suna ganin sa. Daga nan sai Mala'ikan mutuwa ya sauko. Shi kuma sai ya zauna a daidai kansa, ya ce masa: Ya ke 'yar gatar numfashi! Ki fito zuwa ga rahama da yarda da amincin Ubangijinki. Sai kawai rayuwa ta fito cikin tsanaki kamar yadda ɗigon ruwa yake fitowa daga bakin tsuntsuwar da take shayar da 'ya'yanta. Sai ya sa hannu ya riƙo ta. Su kuwa waɗancan ba za su bari ko iska ta sha ba a hannunsa, sai su karɓa, su kuma saka ta cikin wancan ƙyalle da waɗancan turaruka. Nan take sai ta fito kamar Almiski ko tagullan zinari mafi daraja da ake da shi a bayan ƙasa. Ya ci gaba da cewa: Sai waɗannan Mala'iku su tashi sama da ita. A haka kuma babu wani gungu na Mala'iku, da za su haɗu da su a kan hanyarsu, face sun tambaya; wace irin rayuwa ce wannan mai tsananin ƙanshi? Sai su karɓa musu da cewa: Ai, wane ne jikan wane. Sai su ambaci mafi kyawon sunan da ake ambatarsa da shi a duniya. Haka za su yi ta tafiya har su isa sama ta farko. Da sun isa za su ƙwanƙwasa ƙofa a kuma buɗe musu. Sai Mala'ikun da suke nan su bi su baya suna rakiya. Haka za su ci gaba da tafiya, Mala'ikun kowace sama suna ƙara ma yawansu*

tambayoyi kamar yadda ya dace, illa karatu da neman sanin ingantaccen addini bisa koyarwar Alƙur'ani da Sunna. Sai kuma aiki da su.

Shi kuwa addinin da muke bauta ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* da shi: ***"Shi ne miƙa wuya ga Allah Maɗaukakin Sarki",*** ta hanyar nuna ƙanƙanci da sunkuyawa gare shi. Hakan kuma tana tabbata ne idan an kaɗaita shi da zama Ubangijin bayi, wanda ya halicce su, yake kuma tasarrufi da al'amarinsu, shi kaɗai: ***"Ta hanyar kaɗaita shi",*** da gaba ɗayan dangogin ibada.

A zahirin gaskiya ma, ai ba komai ne addinin Musulunci ba, illa komai mutum zai yi, ya yi shi domin Allah shi kaɗai. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Ba komai ne Musulunci ba, illa miƙa wuya ga Allah Maɗaukakin Sarki koma bayan waninsa. Wannan kuma ita ce ma'anar Lailaha illallah".* [217] Musulmi kuma an ambace shi musulmi ne saboda irin yadda gaɓoɓinsa suke biyayya ga Ubangijinsa. Shaikhul-Islam *Rahimahullah* yana cewa: *"Musulunci shi ne miƙa wuya, wanda ya ƙunshi ƙanƙan da kai ga Allah shi kaɗai, da kuma jawuwa zuwa gare shi, da bauta masa ba tare da abokin tarayya ba".* [218]

---

*abki, har a isa sama ta bakwai. Isarsu take da wuya, sai Allah Maɗaukakin Sarki ya umarci Mala'iku da rubuta sunansa a cikin littafin mafi girman makusanta a wurinsa. Ya kuma ce: "Ku mayar da shi a cikin ƙabarinsa. Da ma da ƙasa na halicce su, a cikinta kuma na hukunta zaman su bayan sun mutu, daga cikinta ne kuma zan sake tayar da su". Bayan an mayar da rayuwar tasa a cikin gangar jikinsa, sai Mala'iku biyu su zo masa, su zauna su ce masa: waye Ubangijinka? Nan take ba da wata-wata ba, sai ya karɓa da cewa: Ubangijina shi ne Allah. Sai su kuma ce masa: Mene ne addininka? Shi kuma ya ce: Addinina Musulunci. Sai su sake ce masa: To, mene ne matsayin mutumin nan da aka aika muku? Sai ya karɓa da cewa: Manzon Allah ne Sallallahu Alihi wa Sallam. Sai kuma su sake tambayarsa: To, wane aiki ka rayu a kan sa? Sai ya ce: Na karanta littafin Allah, na kuma yi imani da shi, na gaskata. Daga nan sai wani sauti daga sama ya shiga cewa: Bawana ya faɗi gaskiya. Ku shimfiɗa masa tabarmar aljanna, ku saka masa tufafin aljanna, kuma ku buɗe masa tagarta domin ƙanshi da iskanta su riƙa shigo masa. Daga nan sai a faɗaɗa ƙabarin nasa iyakar ganin idonsa. Ya ci gaba da cewa: Sai wani kyakkyawan mutum, mai kyakkyawan tufafi, yana kuma ƙanshi, ya zo masa, yana cewa: Yau za ka haɗu da abubuwan alheri waɗanda suka daɗe suna jiran ka. Sai shi kuma ya tambaye shi, waye kai? Ɗan fari mai farar fuska da farantacciyar magana? Sai ya karɓa masa da cewa: Ni ne kyakkyawan aikinka. Jin haka sai shi kuma ya roƙi Ubangijinsa da cewa: Ya Allah! Ko a yau ma ayi tashin ƙiyama domin in koma cikin iyalaina da dukiyata."* Ahmad ne ya riwaito shi, Hadisi na (18557) 4/287.

[217] *Al-Fatawa* 4/245.

[218] *Al-Fatawa* 7/247.

Duk wanda ya miƙa wuya ga Allah Maɗaukakin Sarki, ya kuma miƙa ga waninsa a lokaci ɗaya, ya zama mushriki. Wanda kuma ya ƙi miƙawa sam sam to, sunansa mutakabbiri. Wanda kuwa duk ya ƙi biyayya ga Allah, to, za a jarrabe shi da biyar Shaiɗan. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Duk wanda ya ƙi biyayya ga Allah Maɗaukakin Sarki, to, Allah zai jarrabe shi da biyayya ga Shaiɗan. Saboda haka zancen zaman mutakabbiri mushriki, kamar yadda Allah ya ambata, magana ce tabbatacciya; babu tambaba".* [219]

Shi kuwa Musulunci da kake gani, abu ne da yake da kai. Kansa shi ne kalmar shahada. Yana kuma da kishiyoyi guda biyu, wato, girman kai da Shirka. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Musulunci wanda yake shi ne addinin Allah da ya saukar da littattafansa, ya aiko Manzanninsa da shi, shi ne bawa ya miƙa wuyansa ga Allah Ubangijin talikai shi kaɗai ba tare da yi masa kishiya ba. Ya kuma ci gaba da tabbatar da ingancin wannan aƙida ta hanyar nisantar ɗaukar wani wanda ba shi ba abin bauta, kamar dai yadda mafificin halitta ya bayyana. Kalmar Shahada ita ce kan Musulunci, kishiyoinsa kuma su ne Shirka da girman kai. Saboda haka ne aka riwaito cewa Annabi Nuhu Alaihis Salam ya umarci 'ya'yansa da lizimtar La'ilaha Illallah da Subhanallah. Ya kuma yi musu kashedi da girman kai da Shirka a cikin wani Hadisi da nake jin na ambata a wani wurin daban. Wanda duk ya naɗa ma kan sa rawanin tsiya, ta hanyar yi ma bautar Allah Maɗaukakin Sarki ƙememe; ya ƙi yinta. Ba yadda za a yi a lissafa shi cikin masu miƙa wuya. Wanda kuma ya yarda yana bauta masa, yana kuma bauta ma waninsa, sunansa mushriki kai tsaye. Zancen lamuni tsakaninsa da Allah babu tunda ya yi masa abokin tarayya. Dama kuma lafazin Musulunci a karan kansa, yana nufin miƙa wuya ne kwata-kwata da kuma nisantar yamutsa hazo da gamin ganbiza. Wannan shi ake kira ikhlasi".*[220]

Tattare kuma: ***"Da"***, zubewar bawa gaban Ubangijinsa da ƙanƙan da kai gare shi, wajibi ne ya nuna: ***"Jawuwa"***, da saurarawa: ***"Zuwa gare Allah"***, mai girma da ɗaukaka: ***"Ta hanyar biyayya"***, wadda ta ƙunshi aikata abin duk da

---

[219] *Al-Fatawa* 7/632.
[220] *Al-Fatawa* 7/623.

aka umarce shi, da nisantar wanda aka hane shi saboda biyayya ga umurnin Allah *Subhanahu wa Ta'ala.* Wannan shi ne abin da Allah yake cewa a cikin wata aya: *"Ka ce: Ku yi ɗa'a ga Allah, kuma ku yi ɗa'a ga Manzo".* Da kuma faɗar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam: "Duk abin da na hane ku da shi, ku nisance shi, wanda kuma na umarce ku da shi, ku aikata shi gwargwadon ikonku. Ku sani ba komai ya halakar da waɗanda suka zo gabaninku ba, illa yawan tambayoyinsu da saɓawarsu ga Annabawansu".* [221]

Mataki na ƙarshe kuma idan ana zancen cika da kamala a fagen aƙidar Musulunci, shi ne, sallamawa ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, kai da fata. Duk wanda hakan ta kasa samuwa daga gare shi zuwa ga wannan addini, to, babu shakka Allah zai ƙasƙanta shi. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Duk wanda ya ƙanƙan da kai ga Allah, zai ɗaukaka shi. Haka kuma duk wanda ya yi mutakabbiranci; ya ƙi miƙa wuya ga mahaliccinsa, to, zai ƙasƙanta, ya tozarta, ya kuma wulaƙanta shi".*[222]

Tabbatacciyar magana ce, cewa, girman kai shi ne babban abin da yake hana wasu bayi miƙa wuya kacokam ga karantarwar addini. Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* da yake lissafa dalilan da suke hana jawuwar bawa zuwa ga hukuncin Allah cewa ya yi: *"Dalili na uku shi ne samun wani shamaki, wanda yake iya zama hassada ko girman kai. waɗannan su ne abubuwan da suka hana Ɗan-lisu miƙa wuya ga umurnin Allah. Su ne kuma ciwarwatan mutanen farko da na ƙarshe, sai fa wanda Allah ya kare shi. Su ne kuma suka hana Yahudawan da suka rayu tare da Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam, suka kuma san yanayin mu'amalarsa, da sauran waɗanda suka biyo godabe irin nasu, yin imani da shi".*[223]

Haka kuma yana daga cikin abubuwan da, sani da imani da aiki da su, suke wajaba a kan kowane musulmi, cewa, Musulunci yana nufin kaɗaita Allah da bauta, da kuma miƙa wuya gare shi ta hanyar biyayya: ***"Da",*** kuma: ***"Yi ma Shirka da masu yin ta tawaye",*** ta hanyar nisantar duk wani aiki ko zance,

---

[221] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (6858) 6/2658, da *Sahih Muslim,* Hadisi na (1337) 2/975 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*
[222] *MadarijAs-Salikin,* 2/333.
[223] *Miftah Dar As-Sa'adah* 1/99

da suke da alaƙa da su, da yin imani da zamanta ɓata. Kai! Wajibi ne ya nisanci duk wata ɗabi'a irin tasu, ko wata dangantaka da su. A taƙaice dai ana so ne ya raba gari da su; maganarsa daban, tasu daban, aikinsu daban nasa daban; kama a tsakaninsu babu ya sam, ko masoso.

A dunƙule dai, shi addinin Musulunci yana da waɗansu gunshiƙai guda uku, waɗanda haɗuwar hancinsu a lokaci ɗaya kafin ya karɓa sunansa, take wajaba. Ga su kamar haka:

1. Miƙa wuya ga Allah ta hanyar kaɗaita shi.
2. Miƙa wuya ga Allah ta hanyar yi masa biyayya.
3. Yi ma Shirka da Mushrikai tawaye.

Ita *'Bará'a'* ko ka ce tawaye a Hausance, ga Shirka da ma'abutanta, ɗayan rukunan addini ne guda biyu, waɗanda a kan su ne aka gina shi. Babu kuma yadda za a yi Tauhidi ya tabbata sai da su, kamar yadda bawa ba zai iya zama cikin sahun waɗanda suka kaɗaita Mahalicci ba, sai idan ya haɗa hancinsu a cikin ƙoƙon zuciyarsa, wato "korewa" da "tabbatarwa". Duk kuwa wanda ya rasa ɗaya daga cikinsu, to, ya rasa Tauhidi. Na farko shi ne kore samuwar wani abin bauta koma bayan Allah, da kuma tabbatar da ita ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala* shi kaɗai. Ga abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake faɗa game da Annabi Ibrahimu *Alaihis Salam,* da nufin a taru a yi koyi da shi: *"Kuma a lokacin da Ibrahimu ya ce ma mutanensa: Haƙiƙa fa ni, na yi tawaye ma abin da kuke bauta wa".* Rukuni na farko kenan; yi ma Shirka da ma'abotanta tawaye. Sai kuma abinda ya biyo baya, wato, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki a harshen Annabin nasa: *"Sai fa wanda ya halicce ni".* Ya tabbatar da rukuni na biyu. Hakan kuma ta yi daidai da faɗar Allah Maɗaukakin Sarki a wata ayar cewa: *"Babu tilastawa a cikin addini. Haƙiƙa gaskiya ta bayyana – tana mai bambance kanta - daga ɓata. To, duk wanda ya kafirce ma Ɗagutu…".* Wannan shi ake ce ma tawaye, wato kore samuwar wani abin bauta koma bayan Allah *Subhanahu wa Ta'ala.* Sai kuma ya ce: *"…Ya kuma yi imani da Allah".* Wannan kuma shi ne tabbatarwar.

Kenan, ma'anar kalmar Shahada ita ce, *"Babu abin bauta akan cancanta sai Allah".* Yau da mutum zai tsayar da Sallah da Azumi, ya yi Hajji da Sadaƙa. Amma, a gefe ɗaya ba ya ganin illa da laifi a cikin Shirka; yana ganin ingancin abin da mushrikai suka yi imani da shi, to, wannan ba musulmi ba ne, saboda bai yi ma Shirka da ma'abutanta tawaye ba. Ashe kenan wajibi ne bayan tabbatar da imani da Allah, ta hanyar kaɗaita shi da bauta, a kuma tabbatar da yin tawaye ga Mushrikai. Bisa wannan ƙa'ida, idan mutum yana tsare Sallah, amma bai bar ɗabi'u irin na Mushrikai ba, Sallarsa ba za ta amfane shi da komai ba. dalili kuwa shi ne rashin nisantar Shirka da ya yi.

Wani abun kuma shi ne, ya zama wajibi har yau, a kan bawa bayan ya san ciki da wajen wannan addini, ya kuma nuna masa kishi da soyayya. Shaikhul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"An riga an halicci zukata a kan sani da tabbatar da samuwar Allah Maɗukakin Sarki, da kuma gaskata shi, da bauta masa. Sai dai tattare da haka, sai ka taras waɗansu abubuwa na ɓarna suna bijiro masu, waɗanda ka iya ɓata su. Ita kuwa gaskiya, alamar an san ta, ita ce a wayi gari ana so ana kuma ƙaunar ta. Kamar yadda ɓarna, ba za a iya fahimtar an san ta ba, sai idan an wayi gari ana ƙi ana kuma ƙyamarta. Da,an a tsarin halittar ɗan Adam na azaliyya, an shirya shi ne a kan son gaskiya da ƙin ɓata. Sai dai abu ne mai sauƙin gaske wani abu ya iya gurɓata yanayinta, kamar sha'awa, wadda takan iya hana ta yarda da wata gaskiya, ko ta hana ta biyar ta".*

Saboda haka wajibi ne a kan kowane musulmi ya riƙa alfahari da addininsa. Ya yi imani da cewa, addinin nan nasa shi ne kawai gaskiya, wanda ba shi ba kuma ɓata ne. Dalili shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki da ya ce: *"Haƙiƙa, Addini a wurin Allah shi ne Musulunci zalla".* Ta kuma tabbata cewa, Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya umarci Manzonsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da shelanta ma duniya haka, a cewarsa: *"Ka ce: lalle ni, Ubangijina ya shiryar da ni zuwa ga tafarki madaidaici, addini tsayayye, aƙidar Annabi Ibrahimu, mai karkata zuwa ga gaskiya, bai kuma kasance daga cikin masu Shirka ba".* Tabbas! Duk wanda Allah ya shirya zuwa ga wannan addini, ya cancanci ya yi farin ciki, saboda wannan ni'ima, ya kuma riƙe shi da kyau.

Bawa ba ya da wani girma ko wani ƙarfi matuƙar ba addininsa ya riƙa da kyau ba. Bayan haka kuma ya kira mutane zuwa gare shi saboda kasancewarsa tafarkin samun ni'ima ga bayin Allah. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"To, ka yi riƙo da abin da aka yi maka wahayi, lalle haƙiƙa kai, kana a kan tafarki madaidaici".** 

***"Shi kuma",*** Addinin Musulunci: ***"Mataki uku ne: Musulunci, da Imani da Ihsani".*** Da wuya ne musulmi ya kasa ɗaukar ɗaya daga cikin waɗannan matakai. Tana kuma iya yiwuwa ya cirata daga wani mataki zuwa wani na sama, ko na ƙasa gare shi gwargwadon biyayyarsa ga Allah Maɗaukakin Sarki ko kuma saɓonsa. Mataki na farko daga cikin waɗancan matakai, shi ne, Matakin Musulunci. Na tsakiya kuma shi ne, Matakin Imani. Matakin Ishani kuma shi ne mafi ɗaukaka. Bisa wannan lissafi duk wanda ya hau mataki na ƙarshe, to, ya riga ya taka na farko da wanda yake bi masa. A wata hausa, duk wanda za a kira shi da sunan *Muhsini,* to, sai da ya fara zama *Mumini* kuma *Musulmi.* Sai dai ba lalle ne Musulmi ya zama Mumini ba. Malam Abu Sulaimana Al-Khaɗɗabi *Rahimahullah* yana cewa: *"Da yawa mutane suke kuskure a cikin wannan lissafi".* [224]

Matakin Musulunci shi ne mafi faɗi da yalwa, tattare da kasancewarsa makimanci. Wannan mataki shi ne ƙofar da kafiri yake shiga Musulunci da ita, da zarar ya buɗa baki ya furta Kalmar Shahada, ya kuma bi dokokinsa kai da fata. Ga abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake cwa a kan haka: *"Kauyawa suka ce: Mun yi imani. Ka ce: Ba ku yi imani ba, amma dai ku ce: Mun musulunta, imani bai gama shiga a cikin zukatanku ba".* Sa'annan, shi wannan mataki na Musulunci, babu abin da yake fitar da mutum daga cikinsa, sai kafirci, da Shirka irin wadda take fitar da mutum daga cikin dangi.

Mataki na biyu shi ne, matakin Imani, wanda shi yake take sawun na Musulunci a matsayi da daraja. Saboda haka faɗinsa bai kai na Musulunci ba. Ibnu Abi Shaibata *Rahimahullah* ya ce: *"Musulunci ba ya tabbata sai da Imani. Haka kuma Imani ba ya tabbata sai da Musulunci".* [225] Inda kawai ake iya

---

[224] *Sharhin Imam An-Nawawi a kan Sahih Muslim,* 1/144.
[225] *Ta'azim Kadr As-Salah,*na Al-Maruzi Hadisi na (583) 2/527.

rarrabewa tsakaninsu shi ne, ayyukan duk da suka kasance na baɗini ne, to, sun fi rinjaye a ɓangaren Imani. Su kuwa ibadoji waɗanda ake yi da gaɓɓai; ga su sarai, ƙarara a fili, kowa na ganin lokacin da ake gabatar da su, kamar furta Kalmar Shahada, da Sallah, da sauran matara kama da su, sun fi rinjaya ga ɓangaren Musulunci. Kenan farfajiyar Musulunci ta fi ta Imani faɗi, kamar yadda ta Imani ta fi ta *Ihsani*.

Mataki na uku kuwa shi ne, matakin *Ihsani*. Tabbas! Wannan mataki yana sama ga na Imani, amma bai kai faɗi da yalwar sauran matakan biyu ba. Shi ya sa waɗanda suka taka wannan matsayi a cikin al'umma suke taƙaitattu idan aka kwatanta da sauran matakan. *Ihsani*, mataki ne mai matuƙar girma da ɗaukaka, wanda babu mai iya taka shi sai bayin Allah zaɓaɓɓu kuma nagartattu.

Wannan kashe-kashe na matakan addini, abu ne da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya bayar da labarinsa a cikin sanannen Hadisin nan na Jibrilu *Alaihis Salam*.[226] Haka kuma Alƙur'ani mai girma ya zo da shi, inda ya karkasa gaba ɗayan wannan al'umma a kan waɗannan matakai guda uku. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Sa'annan, muka gadar da Littafi, ga waɗanda muka zaɓa daga cikin bayinmu, kuma daga cikinsu akwai mai zalunci ga kan sa, kuma daga cikinsu akwai mai tsakaitawa, kuma daga cikinsu akwai mai tserewa da ayyukan alheri da izinin Allah. Waccan ita ce falala mai girma"*. Bisa karantarwar wannan aya, duk musulmin da bai tsare alfarmar tanade-tanaden imani ba, shi ne wanda ya zalunci kansa. Mai tsakaitawa kuma shi ne mumini farar hula, wanda ya kiyaye alfarmar wajibai, ya kuma nisanci abubuwan da aka haramta. Wanda kuma yake tserewa da ayyukan alheri, shi ne mai *Ihsani*, wanda ya bauta ma Allah kamar yana ganinsa. Ko ya bauta ma Ubagijin nasa kamar, Ubangijin yana ganinsa.

Saboda haka, kenan matsayin mutane a farfajiyar Tauhidi ya bambanta, bambanci mai yawa mai girma. Darajojinsu a cikinsa, na wasu sun ɗara na wasu. Saboda haka wasu daga cikinsu, za su shiga Aljanna ba tare da hisabi ba, ba kuma tare da wata azaba ba. Wasu daga cikinsu kuma za su shiga Wuta,

[226] Wannan Hadisi zai zo a nan gaba kaɗan in Allah ya so.

sakamakon saɓa ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* da suka yi, bai kuma yi nufin gafarta musu ba. Saboda haka sai ya bi su da halinsu. Amma, zaman da za su yi a cikinta ba zai wuce gwargwadon zunubinsu ba. Sa'annan, sai a fitar da su sakamakon Tauhidi da imanin da suke da shi a cikin zukatansu.*

***"Kowane mataki",*** daga cikin waɗannan matakai guda uku: ***"Yana da shika-shikai",*** waɗannan in babu su, babu shi. A haka kuma sai a wayi gari gaba ɗayan matakan sun yi ko sama ko ƙasa. ***"Shika-shikan Musulunci biyar ne",*** babu kuma yadda za a yi ya iya tabbata sai tare da su. Waɗannan shika-shikai suna ƙunshe a cikin faɗar annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: *"An gina Musulunci a kan abubuwa biyar: Shaida babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, kuma Muhammad manzonsa ne, da tsayar da Sallah, da bayar da Zakka, da ziyarar Ɗakin Allah, da Azumin watan Ramadhan".* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[227] Malam Ibnu Rajab *Rahimahullah* ya ce: *"Abin da wannan Hadisi yake nufi shi ne, waɗannan abubuwa guda biyar su ne harsashen da aka gina Musulunci a kai. Matsayinsu matsayin fandisho ne da filoli da sauran muƙarraban gini. Ana kuma nufin ne a kamanta Musulunci da gini, wanda ginshiƙansa su ne waɗannan abubuwa guda biyar, kuma da zarar babu su, to, babu shi. Sauran tanade-tanaden Musulunci kuma daidai suke da sauran kayan gini da tarkacensa. Da zarar kuwa wani sashe nasu ya samu tasgaro, to, ginin ya samu naƙasu kenan. Amma da zarar ya kafu da ƙafafunsa, to, babu wani abu da zai tauye shi, saɓanin idan waɗannan ginshiƙai na Musulunci sun samu wata tawaya. Nan take ne za a neme shi a rasa. Haka kuma da zarar Kalmar Shahada ta warware, shi ma ya warware".* [228]

A bisa wannan tafarki, mawallafin ya ɗauki tsarin gabatar da abu mafi muhimmanci sannan mai bi masa, daga cikin rukunan Musulunci. Saboda haka sai ya fara da manya-manya gazun-gazun, wato: Kalmar Shahada wadda take nufin cikakken imani da Allah da Manzonsa. Lafazin "shaida" an yi amfani da shi ne, saboda a bayyana cewa, wajibi ne wannan imani da ake nema ya zama

---

[227] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (8) 1/11-12, da Hadisi na (4243) 1641, da *Sahih Muslim*, Hadisi na (16) 1/45 daga ɗan Umar.
[228] Jami'il Ulumi wal Hikam 1/43.

yankakke, cikakke kuma tabbatacce, ta yadda abin da ake imani da shi ɗin, zai zama kamar ga shi ana gani ƙarara. Wato, zuciya ta ƙudurce cewa Allah Maɗaukakin Sarki, shi ne kawai abin bauta. Muhammadu kuma Manzonsa, wanda ya aiko zuwa ga mutane gaba ɗaya domin bushara da gargaɗi.

Sanin wannan shisshike kuwa ga kowane musulmi, abu ne mai matuƙar girma da ɗaukaka. Saboda kasancewarsa ginshiƙi, wanda yake bambancewa tsakanin masu imani da marasa shi, wato, imani da kaɗaituwar Allah, da kuma Manzancin Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* Ko a wata Hausa ka ce: Shaida babu abin wanda bauta da gaskiya sai Allah, Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* kuma, Manzon Allah ne. Malam Ibn Al-Ƙayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Harsashen Tauhidi da sanadarin girkinsa, shi ne shaida babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam kuma Manzon Allah ne.*[229] *Wannan kalma kuma ita ce mabuɗin Aljanna. Saboda Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam yana cewa: Mabuɗin Aljanna shi ne: Shaida babu wanda ya cancanci bauta sai Allah".* [230] A wani wurin kuma malamin *Rahimahullah* yana cewa: *"Kalmar Shahada ita ce ruwan ɗan maduɗin Aljanna. Sallah kuma da sauran Rukunai su ne haurunsa, waɗanda ba yadda za a yi a iya buɗe ta sai da su, saboda sharaɗin shigarta shi ne mallakar irin wannan makulli mai ruwa da haurunsa".* [231] Wata rana an tambayi Wahbu ɗan Munabbah *Rahimahullah* cewa: *"Ashe Kalmar Shahada ba ita ce mabuɗin Aljanna ba?"* sai ya karɓa da cewa: *"Tabbas haka ne, sai dai babu mabuɗin da ba shi da hauru. Idan ka zo da mabuɗi mai hauru za a buɗe maka. Idan kuwa ba haka ba, to, ba za a buɗe maka ba".* [232]

Sai dai yana da kyau a lura, Kalmar Shahada da ɓangarorinta guba biyu, an ɗauke su ne a matsayin rukuni ɗaya. Shaidar babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, da takwararta; shaidar Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* Manzo ne, ba rukunai ne mabambanta ba. Ko alama. Babu wani aiki na ibada

---

[229] Shifa'ul-Alil shafi na 288.
[230] Bazzar ne ya riwaito shi daga Mu'azu ɗan Jabalu *Radhiyallahu Anhu* Hadisi na (2660) 7/103.
[231] Assalatu Wa Hukmu Tarikiha shafi na 66.
[232] Buhari ya riwaito shi, rataye, 1/417.

da zai samu karɓuwa a wurin Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, balle ya zama ingantacce, sai idan an yi shi bisa asasin waɗannan rukunai biyu, a haɗe. Don haka, kafin aiki ya zama karɓaɓɓe a idon Shari'a, sai sharaɗi biyu sun tabbata:

1. Tsarkake niyya.
2. Biyar Sunnar Manzo *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*

To, idan an samu tsarkin niyya, shaidar babu abin bauta sai Allah ta tabbata kenan. Idan kuma aka samu biyayya ga Sunnar Manzo, to, shaidar *Muhammadur Rasulullahi*, ita ma ta tabbata. Tabbatar da samuwar wannan shaida ta biyu wajibi ne. Saboda Manzo *Sallallahu Alaihi wa Sallam* shi ne wanda ya zo da saƙon addini daga wurin Allah. Ashe imani da zamansa Manzo kuma bawan Allah na daga cikin abin da Kalmar Shahada ba ta cika sai da shi. Kenan ɓangaren wannan kalmar ta biyu, yana cika ne tare da kammala cangare na farko. Shaihul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: "*Addinin Musulunci an gina shi ne a kan wasu tuwasu guda biyu, da suka haɗa da: Tabbatar da babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam kuma, Manzonsa ne".* [233]

Rukuni na biyu kuma daga cikin rukunan Musulunci shi ne: ***"Tsayar da Sallah",*** wato, yin ta a cikin lokacinta, cikakkiya, bisa sharuɗɗa da rukunai da wajibbanta.

Rukuni na uku kuma: ***"Bayar da Zakka",*** gwargwadon abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya wajabta ma bawa.

Rukuni na uku huɗu shi ne: ***"Azumin watan Ramadhan",*** ta hanyar kamewa daga duk wani abu da yake ɓata Azumi, tun daga ketowar alfijir zuwa faɗuwar rana, ga wanda Azumi ya wajaba a kan sa.

Rukuni na biyar shi ne: ***"Ziyartar ɗakin Allah mai alfarma",*** domin sauke nauyin ibadar Aikin Hajji.*

---

[233] *Al-Fatawa* 1/310.

## DALILAI A KAN ABIN DA YA GABATA

***Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:***

***"Dalili a kan Kalmar Shahada shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Allah ya shaida cewa, haƙiƙa, babu abin bauta bisa cancanta face shi, kuma Mala'iku da ma'abuta ilimi sun sheda da haka. Yana tsaye da adalci, babu abin bauta bisa cancanta face shi, Mabuwayi, mai hikima". Ma'anar wannan kalma ita ce, babu wanda ya cancanci bauta sai Allah. "La'ilaha" korewa ce ga samuwar wani abin bauta da ya cancance ta koma bayan Allah. "Illallah" kuwa tabbatar da bauta ne ga Allah shi kaɗai, wanda ba shi da abokin tarayya a cikin ibada ko a sarautarsa".***

Bayan da mawallafin *Rahimahullah* ya lissafo rukunan Musulunci guda biyar, sai kuma ya shiga bayyana dalilan kowane ɗaya daga cikinsu, yana mai cewa: ***"Dalili a kan Kalmar Shahada, shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Allah ya shaida..".*** Magana kuwa ta girma tun da Allah da kan sa yake shaida. Wannan ita ce shaida mafi girma da daraja da aka taɓa yi a faɗin duniya. Kamar yadda Maɗaukakin Sarki ya ce a wani wurin: *"Ka ce: Wane abu ne ya fi girman shaida? Ka ce: Allah".* Wannan shaida kuma da ya bayar *Subhanahu wa Ta'ala,* ya bayar da ita ne a kan abu mafi girma da ya sifanta da shi: ***"Cewa, lalle ne babu abin bautawa",*** bisa cancanta: ***"Face shi",*** Allah *Subhanahu wa Ta'ala.*

Haka: ***"Kuma Mala'iku",*** su ma sun shaida cewa babu Ubangiji sai shi, kamar dai yadda Buwayayyen Sarkin ya shaida ma zatinsa mai tsarki. ***"Da kuma ma'abuta ilimi",*** su ma sun yi shaida a kan haka. A haka Allah Maɗaukakin Sarki ya kafa wannan shaida ta Mala'iku da ma'abuta ilimi, a matsayin wata babbar hujja a kan zamansa Makaɗaici. Saboda haka kuma karɓar wannan shaida ya zama wajibi a kan kowane mukallafi, wadda aka bayar bisa gaskiya da adalci. A kaikaice kuma wani ƙaimi ne ake yi ma musulmi a kan tashi tsaye don neman ilimi. Cewa, shi da Mala'iku da ma'abuta ilimi, duk sun bayar da wannan shaida, ɗaukaka ce ba 'yar ƙarama ba ga

malamai, kasancewar Ubangijin talikai ya shigar da su a cikin wannan sha'ani. Ka kuwa san babu wani yabo da gaskatawa, da za a yi musu waɗanda suka kama ƙafar wannan. Sanya su matsayin hujja a kan duk wanda yake musun kaɗaituwar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* da bauta, wata 'yar manuniya ce da take ishara a kan maɗaukakin matsayin da suke da shi.

Sai dai ilimin da ake magana a nan shi ne ilimin Shari'a, saboda matsayin da yake da shi, na haskaka zukata. Duk ilimin da ba shi ba kuwa, raɓa-darni ne, mai taƙaiyataccen hurumi. Za ka taras yana magana ne kawai a kan abin da ya shafi rayuwar duniya a jumlace, ko bugun ƙasa, wato hisabi, ko kuma ƙere-ƙere, ko wani abu mai kama da haka. To, gaba ɗayan ma'abuta irin waɗannan ilimoma, ba su daga cikin tsarin malaman da Allah Maɗaukakin Sarki yake nufin sun yi waccan shaida. Masu ilimin Shari'a ne kawai suka caancanci dangantawa da hakan sakamakon kalar ilimin nasu.

Shi Allah Maɗaukakin Sarki: ***"Yana tsaye da adalci",*** a cikin gaba ɗayan sha'aninsa. Wannan shi ne halinsa daɗai Maɗaukaki Sarki. ***"Babu abin bautawa face shi, Mabuwayi",*** ta kowace fuska ***"Mai hikima",*** a cikin gaba ɗayan lamurransa da tsarin Shari'arsa da kuma mulkinsa. ***"Ma'anar wannan kalma",*** ta Tauhidi, ***"Ita ce, babu abin bauta",*** bisa cancanta; ***"Da gaskiya…"*** Eh! "da gaskiya". Amfani da wannan kalma ya zama wajibi, domin bambancewa tsakanin abubuwa masu yawan gaske da ake bauta koma bayan Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, tattare da zamansu banza a banza. Ina nufin kamar al'adar nan ta masu bautar ƙaburbura, da duwatsu, da gumaka. Dalilina kuma a kan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Wancananka! Saboda Allah shi ne gaskiya. Kuma, lalle, abin da suke bauta koma bayansa, banza ne;"* babu ɗaya daga cikinsu da ya cancanci bauta. Duk wanda ya bauta musu kuwa ya kama daji. Haka ne. Babu abin da ya cancanci bauta da gaskiya: ***"Sai Allah",*** shi kaɗai.

Wani abin bauta bisa cancanta, babu shi, bayan Allah maɗaukakin Sarki. Duk wanda ba shi ba kuwa, ko duniya ta taru ta naɗa masa rawanin ubangizantaka, ta yi a banzar bazara. Wannan, a taƙaice, shi ne ma'anar *la'ilaha illallah,* wato, kore ubangizantaka daga duk wani abu mahaluki, wanda

ba Allah ba, tare da tabbatar masa da ita *Subhanahu wa Ta'ala*, shi kaɗai. A kula, Kalmar Shahada ba tana nufin babu mai halitta ko azurtawa sai Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ba. Wannan *Tauhidin Rububiyyah* ne. Kuma ƙarfinsa ba zai iya tabbatar da kaɗaituwar Allah da gaba ɗayan dangogin bauta, waɗanda aka aiko Manzanni da su ba, aka kuma saukar da littattafai domin tabbatarwa da ƙara ƙwaƙwancewa da yanyanawa.

Shi *Tauhidin Rububiyyah,* mushrikaai ma, irin su Abu Jahali, da takwarorinsa, sun tabbatar da shi, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki yake gaya mana: *"Ka ce: Wane ne yake azurta ku daga sama da ƙasa? Ko wane ne yake mallakar ji da gani? Kuma wane ne yake fitar da rayayye daga matacce? Yake kuma fitar da matacce daga rayayye? Wane ne kuma yake sarrafa al'amari? Za su ce: Allah ne".* Sun san shi ne yake gaba ɗayan waɗannan ayyuka. Babu wata jayayya da tarihi ya tabbatar sun yi a cikin wannan nau'i na Tauhidi, balle su buga kai ga ƙasa su ce ba za su furta ba. Hasali ma, abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi, shi ne kafa musu hujja da amincewar da suka yi da wannan *Tauhidin Rububiyyah* suka bar na *Uluhiyyah,* ya ce: *"To, ka ce musu: Me zai hana ku yi taƙawa?"* Ku nisanci yi masa kishiya a cikin bauta?!

Wannan ya nuna cewa, da gangan mushrikai suke wannan mugun aiki; sun sani sarai, abin da wannan aya ta ƙunsa, da ƙoƙarin da take yi na tabbatar da wajabcin kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki da bauta. Hasali ma wannan dalilin ne ya sa suka ƙi yarda da zaman sa abin bauta ƙwaya ɗaya. Wannan shi ne abin da bugawar zuciyarsu yake gaya musu cewa, lalle Allah shi ne abin so da ƙauna da nufi da biyan buƙata, da tsoro da fatar samun alherinsa. Wannan shi ne Tauhidin da Manzanni gaba ɗayansu, suka zo da shi; bauta ma Allah shi kaɗai, wanda ya ƙunshi cikakkiyar biyayya da ƙanƙan da kai da jawuwa zuwa ga hukunce-hukuncen Shari'a, tare da cikakkiyar ƙauna da dogara gare shi *Subhanahu wa Ta'ala. Kazalika,* da zuba iyakar ƙoƙari a cikin ɗa'a da biyayya a cikin neman yardarsa. Abubuwa da suke tabbata ta hanyar fifita abin da yake so, da manufarsa a cikin saukar da wannan addini. Ya fifita waɗannan abubuwa a kan abin da shi yake so na ƙashin kansa. Wannan shi ne harsashen da gaba ɗayan Annabawa *alaihimussalamu,* suka ɗora wa'azi da kiransu a kai. Wannan

kuma shi ne nau'in Tauhidi, wanda Allah Maɗaukakin Sarki ba ya karɓar wani addini, wanda bai ƙunshe shi ba. Daɗa kuwa daga mutanen farko ne ko na ƙarshe. Shi ne kuma abin da Allah ya umarci Manzanni da shi, ya saukar da littattafai a kan sa, ya kira bayinsa zuwa ga tabbatar da shi da aikata shi. Albarkacinsa ne kuma Buwayayyen Sarkin ya halicci aljanna da Wuta a matsayin sakamaon lada ko na azaba. Shari'o'i ma, Allah ya shimfiɗa su ne a matsayin abokan tafiyar wannan Tahidi; masu taimakawa a cikin cika da kammalarsa. Malam Ibnu Rajab *Rahimahullah* yana cewa: *"Ubangiji shi ne wanda ake yi ma ɗa'a, ba tare da an saɓa masa ba, saboda kwarjini, da girma, da so, da tsoron da ake yi masa. Gare shi kuma ake dogara tare da fatar samun alherinsa. Bayan haka wani mahaluki duk, ba za a roƙe shi wani abu ba, ko a yi wata addu'a domin sa, sai shi kaɗai Subhanahu wa Ta'ala. To, gaba ɗayan waɗannan abubuwa, ɗayansu duk, ba ya halatta a jingina shi ga wani wanda ba Allah Maɗaukakin Sarki ba. Duk kuwa wanda ya tara wani abin halitta a cikin ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa, waɗanda suke mallakar Ubangiji ne shi kaɗai. Ya tara Allah da wani a cikinsu, to, hakan zai sa a yi shakku a cikin ingancin imani da Tauhidinsa. Daga wannan rana kuma, ya samu wani kaso na bautar wani abin halitta koma bayan Allah gwargwadon yadda ya shiga ciki. Wannan kuma, gaba ɗayansa, wani nau'i ne na Shirka".* [234]

Ita wannan kalmar Tauhidi, ta ƙunshi abubuwa ne guda biyu a matsayin Rukunai, wato, korewa da tabbatarwa. ***"Cewa "la'ilaha",*** ma'anarta: ***"Korewa ce ga samuwar",*** duk: ***"Wani abu da ake bauta koma bayan Allah",*** wanda ya haɗa da ƙaburbura, da itace, da duwatsu, da wasunsu. Wanda yake son shiga sahun masu kaɗaita Allah, yana ƙudurcewa ne tare da furta cewa: Ni ba zan bauta ma duk wani abin bauta ba sai Allah shi kaɗai.

***"Cewa kuma: Illallah"*** na nufin: ***"Tabbatar da bauta ne ga Allah shi kaɗai".*** Wato, kamar *muwahhidi* yana cewa ne: Ba zan bauta ma duk wani wanda ba Allah ba. Kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki yake Makaɗaici a cikin mallakar wannan gida na duniya, to, wajibi ne a kaɗaita shi a cikin bauta. Ɗaukar wani abin halitta, wanda ba ya da wani haƙƙi a cikin waccan mallaka ta

[234] *Kalimatul-Ikhlas,* shafi na 23.

halitta. A ɗauke shi a matsayin abokin tarayya da Allah Maɗaukakin Sarki a cikin ibada. Yin haka babban zalunci ne, kuma Allah ya fi ƙarfin wannan matsayi. Saboda haka ne Buwayayyen Sarkin yake kafa hujja ga, wanda ya ƙi yarda da zamansa Ubangiji *"Ilahu"*, da abin da suka yi imani da shi, na zamansa abin mahalicci; *"Rabbu"*.

Shi mushriki, idan har ya yi imani da Allah Maɗaukakin Sarki a ɓangaren *Rububiyyah,* to, ya zama wajibi a kan sa ya yi imani da shi a ɓangaren *Uluhiyyah.* Ah! Ai rashin hujja ne, ya yarda da zaman Allah makaɗaici a cikin mallakar ɗakin duniya, amma ya kasa yarda da zamansa Makaɗaici, wanda ya cancanci bauta daga mazaunanta. Tabbas babu wata hujja ko wani dalili, saboda *Rububiyyah,* na tafiya ne kafaɗa da kafaɗa da *Uluhiyyah.* Kai! shi ne ma yake yi masa zagi. Bisa wannan dalili ne malamin ya ce: ***"Kamar yadda Allah ba shi da abokin tarayya a cikin mulkinsa…"***.

Da wannan za mu fahimci cewa, *La'ilaha Illallahu* tana da ɓangarora biyu ne muhimmai, waɗada suke riƙe da gadon bayanta, wato, korewa; *"la'ilaha"* da kuma tabbatarwa, wato, *"illallah"*. Amma, korewa idan ta zama ta gaba ɗaya, wadda ba ta da wani dabaibayi ko ganɗo, wato a kore samuwar wani abin bauta, ba tare da an tabatar da Allah Maɗaukakin Sarki ba a bagiren, wannan ba Tauhidi ba ne. Wajibi ne a haɗa hancinsu.

Mai karatu kunnenka nawa? Na sani biyu ne. To, ƙara na uku ka sha labari. Kalmar Tauhidi tana da sharuɗɗa guda takwas, waɗanda halartowa da su da furta su ya zama wajibi, kafin ta karɓa sunanta. Duk kuwa wanda ya kasa tabbatar da alfarma da alkadarin ɗaya daga cikinsu, to, addininsa ya samu matsala. Ga sharuɗɗan nata kamar haka:

1. Sanin ma'anar kalmar da manufarta ciki da waje, ɓangaren korewa da tabbatarwa. Yin haka ne kawai zai kore jahilcin da ake da shi da ma'ana da manufofin kalmar. Dalili a kan wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"<u>Ka sani</u> cewa, yadda al'amari yake, babu abin bauta sai Allah"*. A wata ayar kuma ya ce: *"….Sai waɗanda suka yi shaidar gaskiya alhali <u>suna sane</u>"*. Shaidar gaskiya ita ce *la'ilaha illallah.* Ma'ana sai waɗanda suka faɗe ta alhalin suna sane da abin

da suke faɗi, zukatansu kuma sun sakankance. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* kuma ya ce: *"Duk wanda ya mutu yana sanin babu wanda ya cancanci bauta sai Allah zai shiga Aljanna".* Muslim ne ya riwaito shi.[235]

2. Sakankancewa da rashin kokwanto ga abin da kalmar take karantarwa. Wato, wanda ya furta ta, ya kasance har a cikin birnin zuciyarsa, ba ya jin wani motsi ko kaɗan game da abin da kalmar ta ƙunsa, ta yadda babu wani abu da zai girgiza shi. Samun haka wajibi ne, saboda al'amari irin wannan na imani, wata masaniya wadda ba yankakka ba, irin wannan, ba ya amfanar mata komai. Kame-kame da na-ji-na-ji, ba yi ba ne, balle zato da kirdado. Balle daɗa a ce kokwanto game da ita ya shige shi. Ga abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake cewa a kan haka: *"Muminan gaskiya, kawai, su ne waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, sa'annan ba su yi shakka ba…".* Ka ga a nan Allah Maɗaukakin Sarki ya sharɗanta rashin kokwanto kafin imanin da suka yi da shi, da Manzonsa, muminai, ya zama ingantacce. A wani Hadisi kuma Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake cewa: *"Babu wanda zai haɗu da Allah yana shaida cewa, babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, kuma ni Manzonsa ne, ba yana mai kokwanto ba, face ya shiga Aljanna".* Musuli ne ya riwaito shi.[236] A wani Hadisin kuma yake cewa: *"Duk wanda ka haɗu da shi bayan wannan shinge yana shaidar babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, ba tare da wani kokwanto ko shakka ba, to, ka yi masa bushara da shiga Aljanna".* Muslim ne ya riwaito shi.[237]
3. Karɓar abin da kalmar ta ƙunsa a zuci da baki, ba tare da yingirman kai ko bada wani hanzari ba. Tabbacin wannan shi ne, irin yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana mana irin tanadin da ya yi ma

---

[235] *Sahih Muslim,* Hadisi na (26) 1/55 daga Usman ɗan Affan *Radhiyallahu Anhu.*
[236] *Sahih Muslim,* Hadisi na (26) 1/55 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*
[237] *Sahih Muslim,* Hadisi na (13) 1/ 59-60 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

waɗanda ya ce: *"Kuma kamar haka ba mu aika wani mai gargaɗi ba a gabaninka, a cikin wata alƙarya, face mani'imtanta sun ce: Lalle mu, mun samu ubanninmu a kan wani addini, kuma lalle mu masu koyi ne a kan gurabunsu".* A wata ayar kuma *Subhanahu wa Ta'ala* ya ce: *"Lalle haƙiƙa su, sun kasance idan aka ce musu babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, <u>sai su shiga girman kai</u>".* Bisa wannan dalili ne kuma Allah Maɗaukakin Sarki zai azabtar da su, saboda girman kan da ya hana su karɓar wannan kalma ta gaskiya.

4. Miƙa wuya ga abin da kalmar take karantarwa na umurni da hani, wanda yake tabbabar da rashin ingancin ƙin biyar abin da ta ƙunsa. Hujja a kan haka ita ce, faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Wa ya kai kyawon addinin wanda ya miƙa wuya ga Allah <u>yana mai kyautatawa</u>!".* A wata ayar kuma ya ce: *"Duk wanda ya miƙa wuya ga Allah <u>yana mai kyautatawa</u>",* wato, yana mai kaɗaita shi: *"Haƙiƙa ya yi riƙo da igiya mai ƙwari".* Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* kuma ya ce: *"Ɗayanku ba zai zama mai cikakken imani ba, face zuciyarsa ta zama <u>mai biya</u> ga abin da na zo da shi".* Ibnu Abi Asim ne ya riwaito shi a cikin littafinsa *As-Sunan.*[238]
5. Tsarkake niyya dangane da imani da abin da wannan kalma take karantarwa, wanda yake hannun riga da Shirka. Ma'ana, wanda ya furta wannan kalma kada ya kuskura ya cakuɗa ta Shirka. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Ku saurara! Addini <u>tsarkakakke</u> shi ne na Allah".* Ma'ana, addinin da aka yi shi tatacce babu surki. A wata ayar kuma ya ce: *"Ka ce: Allah nake bauta ina mai <u>tsarkake</u> addini zuwa gare shi".* A wata aya kuma *Subhanahu wa Ta'ala* yake cewa game da munafukai: *"Lalle ne, munafukai suna a magangara mafi ƙasƙanci daga wuta. Kuma ba za ka sama masu mataimaki ba. Sai waɗanda suka tuba, kuma suka gyara, kuma suka nemi fakuwa ga Allah, suka kuma <u>tsarkake addininsu</u> domin Allah…"* Shi kuma

[238] *As-Sunan,* na Ibnu Abi Asim, Hadisi na 1/12 daga Abdullahi ɗan Amru ɗan Asi *Radhiyallahu Anhuma.*

Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sai yake cewa: *"Mafi dacewar mutane da samun cetona ranar Alƙiyama su ne waɗanda suka furta la'ilaha illallahu* <u>*da zuciya ɗaya*</u>*".* Buhari ne ya riwaito shi.[239] A cikin wani Hadisin kuma ya ce: *"Lalle haƙiƙa, Allah ya haramta wuta ga wanda ya furta la'ilaha illallah,* <u>*yana neman yardar*</u> *Allah da yin hakan".* Buhari da Muslimu ne suka riwaito shi.[240]

6. Kudurce kalmar da gaskiya a zuci, wanda hakan yake hana ƙaryata sauran abubuwan da ta ƙunsa waɗanda aka yi imani da su, wato, irin ɗabi'ar nan ta munafukai, waɗanda suke aikata saɓanin abin da yake cikin zukatansu. Ga abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa game da haka: *"Kuma lalle haƙiƙa, mun fitini waɗanda ke a gabaninsu, domin lalle Allah ya san waɗanda suka yi gaskiya kuma lalle ne ya san maƙaryata".* A wata ayar kuma Maɗaukakin Sarkin yake cewa, game da wanda bai cika wannan sharaɗi ba: *"Kuma daga cikin mutane akwai wanda ya ce cewa: Mun yi imani da Allah, da kuma Wunin Lahira, alhali kuwa su ba muminai ne ba".* Shi kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce: *Babu wani mahaluki da zai shaida babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, Muhammadu kuma bawansa ne, kuma Manzonsa, da zuciya ɗaya, face Allah ya haramta wa wuta shi".* Buhari da Muslimu ne suka riwaito shi.[241] Ka ga sharaɗin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya gindaya kafin wanda ya furta Kalmar Shahada ya samu tsira daga Wuta, shi ne, faɗin ta da zuciya ɗaya. Ashe idan harshe ne kawai ya faɗa ba tare da zuciya ta yarda ba, babu wani amfani daa za a samu.
7. Nuna wa kalmar, da duk abin da ta ƙunsa, da sauran musulmin da ke riƙe da ita, suna kuma aikin da karantarwarta bisa sharuɗɗa da dokokinta, matuƙar so da ƙauna. A haannun ɗaya kuma, waɗanda suka ƙi yin aimani da ita, da duk abin da take sakin saƙa da shi, a

[239] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (99) 1/49.
[240] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (415)1/164.
[241] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (128) 1/59.

nuna musu ƙiyayya da ƙyama. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Kuma akwai daga cikin mutane, wanda yake riƙon kinaye, baicin Allah, suna son su, kamar son Allah…"* Shi kuwa bawa matuƙar yana son Ubangijinsa, to, alamar da take tabbatar da haka, a taras yana fifitawa tare da gabatar da abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake so, ko da hakan ya saɓa ma shi, son zuciya da muradinsa. A hannu ɗaya kuma, ya ƙi abin da Allah yake ƙi, duk kuwa irin yadda zuciyarsa take son sa. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa: *"Ɗayanku duk, ba zai zama mai cikakken imani ba, sai zuciyarsa ta zama* <u>*mai biya*</u> *ga abin da na zo da shi".* Ibnu Abi Asim ne ya riwaito shi a cikin *As-Sunan.*[242]

8. Kafirce ma duk wani abu da ake bauta ba Allah Maɗaukakin Sarki ba, da yin tawaye ga Shirka da ma'abotanta. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"Duk wanda ya kafirce ma Ɗagutu, ya kuma yi imani da Allah, to, haƙiƙa ya yi riƙo da igiya mai ƙwari, wadda ba ta tsinkewa".* A ƙarshe, an samu wani malami da ya haɗa hancin waɗannan sharuɗɗa a cikin baitin waƙa biyu kamar haka:

*"Ilimi, yaƙini da ikhlasi da yin su da kyau,*
*Da so, da bi, kana karɓawa gareta duka.*
*"Sannan ka ƙara da kafirce ma dukka abin,*
*Da wansu ke bi a saɓanin Ubangijinmu du ka".* [243]

Sai dai a kula, ba wajibi ba ne sai mutum ya hardace waɗannan sharuɗɗa ba, ɗaya bayan ɗaya. Abin da kawai ake buƙata shi ne kiyayewa tare da tsare alfarmar abin da suka ƙunsa tare kuma da tabbatar da shi a aikace. Ga abin da Hafiz Al-Hakami *Rahimahullah* yake cewa a kan haka: *"Abin da ake nufi da wajabcin cika waɗannan sharuɗɗa shi ne, tattarar su a cikin jiki da jinin*

---

[242] *As-Sunan,* na Ibn Abi Asim, Hadisi na (15) 1/12 daga Abdullahi ɗan Amru ɗan Asi *Radhiyallahu Anhu.*
[243] *Ad-Durus Al-Muhimmah,* na Ibn Baz *rahimahillahu* shafi na 1.

*bawa tare da lizimtar ma'anarsu da karantarwarsu, ba tare da ya yi sanadin ɗaya daga cikinsu ya samu cikas ba. Ba lalle ne sai ya hardace lafuzzansu ba. Ai, akwai da yawa daga cikin fararen hula musulmi, wanda da ka gan shi, ka san babu ɗaya daga cikin waɗannan sharuɗɗa, da bai samu gindin zama a cikin jinin imaninsa ba. Amma, da za a tambaye shi su, ba zai iya kawo ko ɗaya ba. Akwai kuma da yawa, wanda ya san su ɗaya bayan ɗaya, amma, da yawa daga cikin ayyukansa, sun yi ban hannun makaho da su. Tabbas, dace a hannun Allah yake".* [244]

Saboda haka duk wanda ya furta Kalmar Shahada, ya kuma san ma'anarta, amma ya aikata wani abu daga cikin abubuwan da suke warware Musulunci, kamar Shirka, ko jiɓintar mushrikai, ko sihiri, ko wani abu mai kama da waɗannan, to, ya fita Musulunci, duk kuwa irin yadda yake maimaita wannan kalma. Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab *Rahimahullah* yana cewa: *"Ibada ba ta karɓa sunanta, sai idan ta samu shimfiɗar Tauhidi, kamar yadda sallah ba ta karɓa sunanta sai idan an yi tsarki. To, da zarar idaba ta haɗu da Shirka, ta tashi daga sunan ibada, kamar dai yadda ka san najasa idan ta shiga cikin ruwa mai tsarki".* [245]

---

[244] *Ma'arij Al-Kabul,* 1/377.
[245] *Alƙawa'id Al-Arba'a*, shafi na 1.

## FASSARAR KALMAR SHAHADA

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:*

*"Tafsirin Kalmar Shahada kuma, wanda yake fitowa da ita fili, shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma lokacin da Ibrahimu ya ce wa babansa da mutanensa: Lalle ni, mai barranta ne daga abin da kuke bautawa. Face wannan da ya ƙaga halittata, to, lalle shi zai shiryar da ni. Kuma ya sanya ta kalma mai wanzuwa a cikin zuriyarsa tsammanin su komo daga ɓata". Da kuma faɗarsa: "Ka ce: Ya ku Mutanen Littafi! Ku taho zuwa ga kalma mai daidaitawa a tsakanin mu da ku; kada mu bauta ma kowa face Allah. Kuma kada mu haɗa kome da shi, kuma kada sashenmu ya riƙi sashe abin bauta, baicin Allah. To, idan sun juya baya sai ku ce: Ku yi shaida cewa, lalle ne mu masu sallamawa ne". Dalilin kuma shaida cewa, lalle Muhammadu Manzon Allah ne, shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle ne, haƙiƙa, Manzo daga cikinku ya je muku. Abin da duk ke wahalar da ku mai nauyi ne a kansa. Mai kwaɗayi ne saboda ku. Mai tausayi ne mai jinƙayi ga muminai".*

*Ma'anar kuma shaidar cewa, lalle, Muhammadu Manzon Allah ne, ita ce, yi masa biyayya a cikin abin da ya yi umurni da shi, da kuma gaskata shi a cikin abin da ya bayar da labarinsa, da kuma nisantar abin da ya hana, ya kuma tsoratar, da kuma ƙin bauta ma Allah sai da abin da ya shar'anta".*

***"Tafsirn Kalmar Shahada kuma",*** wato cewa, *la'ilaha illallah:* ***"Wanda",*** shi ne: ***"Yake fitowa da ita fili",*** a cikin bayani mai gamsarwa: ***"Shi ne",*** abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya ambata a cikin littafinsa, wato, ***"Faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma",*** ka tuna: ***"Lokacin da",*** limamin masu kaɗaita Allah: ***"Ibrahimu",*** *Alaihis Salam:* ***"Ya ce wa babansa",*** Azara: ***"Da mutanensa",*** waɗanda suka riƙi wasu allola baicin Allah, suna bauta musu, suna kuma fadanci ta hanyarsu. Annabi Ibrahimu ya ce musu: ***"Lalle ni mai***

***barranta ne”,*** da fushi da nuna ƙyama gare ku ya ku ma’abuta Shirka, mai kuma raba gari ne, da yin nesa-nesa: ***“Daga abin da kuke bautawa”,*** koma bayan Allah a matsayin allola. Wannan magana ta Annabi Ibrahimu *Alaihis Salam* ita take ƙunshe da ma’anar *“la’ilaha”.*

Ita kuwa faɗarsa: ***“Face wannan da ya ƙaga halittata”,*** bayan a da can babu ni, ita take ɗauke da ma’anar *“illallah”.* Wato, daga cikin abubuwan da ake bauta ma ɗin nan, sai ya ware Ubangijinsa. Ya kuma ci gaba da cewa: ***“To, lalle shi zai shiryar da ni”,*** zuwa ga addini ƙwaƙƙwara da tafarki madaidaici, ta hanyar sa in kama tafarkin shiriya, da ilimi da kuma aiki da gaskiya, kamar yadda ya ƙaga halittata, ya kuma jiɓinci kyautata lamurrana na duniya da Lahira. Annabi Ibrahimu kenan *Alaihis Salam.* Ka kuwa san ta tabbata a cikin Alƙur’ani cewa, Allah Maɗaukakin Sarki ya umurce mu da koyi da shi. Inda yake cewa: *“Haƙiƙa, kyakkawan abin koyi da Ibrahimu da waɗanda suke tare da shi, ya kasance a gare ku, a lokacin da suka ce wa mutanensu, lalle haƙiƙa, mu masu barranta ne daga gare ku, da abin da kuke bauta baicin Allah”.*

***“Kuma”,*** Annabin Allah Ibrahimu *Alaihis Salam:* ***“Ya sanya ta”,*** ita wannan: ***“Kalma”,*** ta Tauhidi, wato, *la’ilaha illallah”,* da abin da take ƙunshe da shi, na bauta ma Allah Maɗaukakin Sarki shi kaɗai, da zuciya ɗaya, da kuma kafirce ma duk wani abu da ake bauta koma bayansa. Ya sanya wannan kalma ta zama: ***“Mai wanzuwa a cikin zuriyarsa”,*** ‘ya’ya da jikoki da tattaɓa kunne da taka kushewa: ***“Tsammanin su komo daga ɓata”,*** zuwa gare ta***”.*** Wato, a wayi gari bayansu, tana koyi da waɗanda Allah *Subhanahu wa Ta’ala* ya shiryar daga cikin zuri’ar. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullahu* yana cewa: *“Allah Ta’ala ya umurce mu da mu yi koyi da shugaban sahun Tauhidi a cikin korewa da tabbatarwa”.* [246]

A taƙaice, wannan bayani da ya gabata yana nuna mana cewa, Kalmar Shahada dai, tana nufin tawaye ga duk wani abu da ake bauta koma bayan Allah *Subhanahu wa Ta’ala.* A hannu ɗaya kuma a tsarkake gaba ɗayan nau’ukan bauta; a yi su saboda Allah. Shaikhul-Islami *Rahimahullahu* yana cewa: *“Lalle Allah ya umurci gaba ɗayan bayinsa, da bauta masa shi kaɗai, da*

[246] *Madarij As-Salikin* 3/484.

*zuciya ɗaya. Yin haka kuwa shi ne Addinin Musulunci, wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko Annabawan farko da na ƙarshe da shi. Saboda haka duk wanda ya yi wani addini baicin wannan, to, ba shi da wani sakamako a wurin Allah. Ga abin da Buwayayyen Sarkin yake cewa: Kuma wanda duk ya riƙi wani addini baicin Musulunci, ba za a karɓar masa ba, kuma a ranar Lahira yana daga cikin masu hasara".* [247]

Kamar kuma yadda bayani ya gabata, Kalmar *La'ilaha Illallahu,* ta ƙunshi korewa ne da tabbatarwa. To, duk wanda ya ƙudurta cewa. Lalle, zai shiga Aljanna saboda kawai ya furta wannan kalma; ba zai shiga Wuta ba, to, haƙiƙa ya yi kuskure. Saboda wannan kalma, tana da abubuwan da suke warware ta, su fitar da mutum daga cikin Musulunci, ko da kuma yana cikin masu furta ta, ya kuma san ma'anarta. Ai Allah Maɗaukakin Sarki ya riga ya bayyana a cikin ayoyi daban-daban, cewa: *"Kuma Ubangijinka ya hukunta, kada ku bauta ma kowa sai shi".* A wata ayar kuma yake cewa: *"Kuma ku bauta ma Allah, kada ku haɗa shi da komai a wurin bauta".*

Wasu ayoyin sun haɗa: ***"Da kuma faɗarsa",*** Maɗaukakin Sarki: ***"Ka ce",*** ya kai Manzo! ***"Ya ku Mutanen Littafi!"*** daga cikin Yahudawa da Nasara, da sauran waɗanda suka rufa musu baya daga cikin *Mushrikai*: ***"Ku taho",*** ku matso, ku gurguso: ***"Zuwa ga kalma",*** ɗaya tal: ***"Mai daidaitawa a tsakanin mu da ku",*** ta haɗa mu a kan gaskiya da adalci, wadda babu wani Annabi ko Manzo, da ba zai yarda da ita ba. Wadda kuma mu da ku, babu wanda Allah *Subhanahu wa Ta'ala* bai wajabta ma ita ba, kuma zuwa gare ta ne Manzanni suke kiran mutanensu. Wannan kalma kuwa ita ce: ***"Kada mu bauta ma kowa face Allah",*** Maɗaukakin Sarki shi kaɗai: ***"Kuma kada mu haɗa kome da shi".*** A maimakon haka, mu dai kaɗaita Allah shi kaɗai, wanda ba shi da abokin tarayya. Wannan shi ne abin da gargaɗi da wa'azin gaba ɗayan Manzanni ya ƙunsa. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"Kuma ba mu aika wani Manzo ba a gabaninka, face mun yi wahayi zuwa gare shi, cewa, lalle haƙiƙa, babu wanda ya cancanci bauta face ni. Saboda haka ku bauta mini".*

---

[247] *Al-Fatawa* 1/188.

Cewar kuma da Allah Buwayayyen Sarki ya yi: ***"Kuma kada sashenmu ya riƙi sashe Ubangiji, baicin Allah",*** yana nufi ne, kada sashenmu ya yi biyayya ga sashe a cikin wani aiki na saɓa ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* kamar yadda Yahudawa da Nasara suke yi.

Ya kuma ci gaba da cewa: ***"To, idan sun juya baya",*** suka ɗauke kai, suka ƙi karɓa kiran da ake yi musu na kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki da bauta: ***"Sai ku ce",*** musu, ku al'ummar Annabi Muhammadu: ***"Ku yi shaida cewa, lalle ne mu masu sallamawa ne",*** masu kaɗaita Allah shi ɗaya, da zuciya ɗaya. Babu kuma wata rana, wadda a cikinta za mu tsame hannunmu mu bar wannan addini, wanda Allah ya shar'anta mana, duk kuwa irin yadda kuka ƙi yarda da mu. Hakan ba za ta taɓa faruwa ba. Ku iya tabbata musu cewa, yadda suka zaɓi zama kafirai, ku kuma kun zaɓi zama musulmi. Yadda kuma suka yi muku tawaye, ku ma kun yi musu tawaye. Ka ga ashe kenan, wannan aya tana nuna mana wajabcin bayyana wa kafirai wannan matsayi ƙarara, ba tare da wani kekeke ba, har a wayi gari sun gane, sun fahimci cewa addinin da suke a kansa ba addini ba ne. Kamar yadda addinin nasu ya sha bamban da na Musulunci, haka shi ma Musulunci, wanda kuke a kansa, ya sha bamban da nasu.

Wannan aya mai girman daraja, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* yakan rubuta ta a matsayin wasiƙa, ya aika da ita zuwa ga Sarakunan *Ahlul-Kitabi*. Wasu lokuta kuma yakan karanta ta a cikin raka'a ta biyu idan yana nafilar gabanin alfijir. Ba kuwa domin komai yake yin haka ba, Ma'aiki *Sallallahu Alaihi Wasallam*, sai don abin da yake tattare a cikinta na kira zuwa ga addini ɗaya, wanda Annabawa gaba ɗaya, da Manzanni *alaihimussalam*, suka haɗu a kansa. Bayan haka kuma ga bayanin *Tauhidin Uluhiyyah*, wanda yake nufin bauta ma Allah Maɗaukakin Sarki shi ɗaya, ta ƙunsa. Wajibi ne a yi imani da cewa, babu wani mahaluki da sauran gaba ɗayan halitta, wanda ya cancanci wata sifa daga cikin siffofin Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya keɓanta da su. Idan *Ahlul-Kitabi* da sauran matara kama da su, sun miƙa wuya ga wannan tanadi, to, sun zama cikin shiryayyu. Idan kuwa haka ta faskara, to, ba su gushe ba suna cikin ɗemuwa da ɓata.*

*"Dalilin kuma shaida cewa, lalle Muhammadu Manzon Allah ne",* daga cikin Alƙur'ani: *"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle ne, haƙiƙa, Manzo daga cikinku",* wanda kuka san nasaba da asali da kuma irin gaskiyarsa: *"Ya je muku".* Mutum ne shi ba Mala'ika ba, ba kuma aljani ba, ko alama. Halitta dai ce irin wadda kuke iya zama da ita, ku ci abinci tare, har ma ku yi yauci tare da shi. Kafin haka kuma, ku da kanku kun riga kun shaide shi, yana da siffofi kyawawa, waɗanda suka haɗa da gaskiya da karimci, da riƙon amana. Zaɓar mai irin wannan shaida don a aiko shi a cikin ku, babu shakka ba ƙaramar ni'ima ce ba a gare ku.

*" Abin",* kuma duk: *"Da yake wahalar da ku mai nauyi ne a kansa".* Wato, babu wani abu da yake ci wa al'ummarsa tuwo a ƙwarya, ya zame mata takunkumi da mari da dabaibayi, face yana cikin abubuwan da suka sha masa kai. *"Mai",* kuma: *"Kwaɗayi ne saboda ku;"* yana guri da fatar ya ga kun shiriya, kun kama tafarki madaidaici, wanda zai nisantar da ku daga shiga wuta. *"Mai tausayi ne mai jinƙayi ga muminai",* mai kuma so musu kowane irin alheri.

Daga cikin dalilan kuma da suke tabbatar da kasancewar Annabi Muhammadu, Manzon Allah, akwai shaidar da Allah Maɗaukakin Sarki da kansa ya bayar cewa, tabbas shi Manzo ne daga cikin bayinsa. Ga abin da Buwayayyen Sarkin yake cewa: *"Kuma waɗanda suka kafirce suna cewa, kai ba Manzo ba ne. Ka ce musu: Allah ya isa shaida tsakanina da ku, da kuma waɗanda a wurinsu akwai ilimin littafi".* Bayan haka kuma, sai Allah Maɗaukakin Sarki ya agaza wa Manzonsa da ayoyi bayyanannu, waɗanda suke nuna wa tare da tabbatar da gaskiyar Manzancinsa. Mafi girma daga cikin waɗannan ayoyi shi ne Alƙur'ani mai girma, littafin da ya gajiyar da mutanen da suke a bayan ƙasa baki ɗaya, ta hanyar fasaha da balagar da yake ƙunshe da su.

Daga cikin hujjojin da suke tabbatar da gaskiyar wannan Manzo, akwai nasarar da Allah Maɗaukakin Sarki ya ba wa waɗanda suka mara masa baya, tattare da kasancewar su a cikin halin rauni. A hannu ɗaya kuma ya wulaƙantar

tare da tozartar da maƙiyansu, ya kuma saka su a cikin matsananciyar azaba a nan duniya, ba tare da la'akari da zaman su mafiya ƙarfi daga cikin mutane ba.

Sai dai haka ita ma, shaidar kasancewar Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* Manzon Allah, ba tana nufin kawai a furta da fatar baki ba, ko alama. Kamar takwararta, ana so ne bayan furtawa, a kuma tabbatar da an yi aiki da abin da ta ƙunsa, take kuma karantarwa. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullahu* yana cewa: *"Bayar da gaskiya da zaman Manzon Allah Annabi, kawai, ba ya shigar da mutum Musulunci, matuƙar bai yi masa ɗa'a da biyayya ba. Ai ka ga imanin da Baffansa Abu Ɗalib ya yi da zamansa Manzo na gaskiya, da kuma cewa addinin da ya zo da shi, yana daga cikin mafi ingancin addinan da ɗan Adam ya sani. Duk wannan shaida da ya yi, ba ta shigar da shi Musulunci ba. Ba shi kawai ba duk wanda ya san tarihi da tabbatattun labaran irin yadda wasu ahlul-Kitabi da mushrikai da yawa, suka yarda da annabcin Muhammadu Sallallahu Alaihi Wasallam, da cewa mai gaskiya ne, amma duk wannan bai shigar da su Musulunci ba. Zai san cewa lalle addinin Musulunci, inda duk ake zatonsa ya wuce nan. Sani kawai da furtawa ko tabbatarwa, ba su isa. Amma, idan aka samu sani, aka kuma furta, aka tabbatar, sannan aka miƙa wuya tare da ƙanƙame yi masa ɗa'a da biyayya a zahiri da baɗini, to, abu ya yi".* [248]

***"Ma'anar shaidar cewa, Muhammadu Manzon Allah ne, ita ce, yi masa biyayya a cikin abin da ya yi umurni da shi",*** na wajibai da mustahabbai, saboda Allah Maɗaukakin Sarki ya gwama ingancin yi masa ɗa'a da yi wa wannan Manzo ita, *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* Kamar in da Maɗaukakin Sarkin yake cewa: *"Duk wanda ya yi wa Manzo ɗa'a, to, haƙiƙa, ya yi wa Allah ɗa'a".* Kazalika: ***"Da kuma gaskata shi a cikin abin da ya bayar da labarinsa",*** wanda ya shafi al'ummomin da suka gabata, ko al'amurran da ake fuskanta. Duk labarin da ya fito daga bakinsa gaskiya ne; babu ƙarya a ciki ko alama. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullahu* yana cewa: *"Duk imanin da bai ginu a kan waɗansu abubuwa guda biyu ba, to, bai cancanci a kira shi imani ba,*

[248] *Za'd Al-Ma'ad* 3/638.

*wato, ɗa'a ga Manzo Sallallahu Alaihi Wasallam a cikin abin da ya yi umurni da shi, da kuma gaskata shi a cikin abin da ya bayar da labarinsa".* [249]

Bayan haka: ***"Da kuma nisantar abin da ya hana, ya kuma tsoratar".*** Wato, yin nesa-nesa da duk abin da Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya yi kashedi da shi. Ga abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa game da haka: *"Kuma abin da Manzo ya zo muku da shi, to, ku riƙe shi, abin kuma da ya hane ku da shi, to, ku nisance shi".* Shi kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ga abin da yake cewa: *"Idan na hane ku wani abu, to, ku nisance shi. Idan kuma na umurce ku da wani, to, ku aikata shi gwargwadon ikonku".* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[250] Bisa wannan, ya zama wajibi a girmama umurnin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* a kuma ƙimanta shi, ba tare da an gabatar da zancen wani a kansa ba. Domin gwargwadon duk yadda mutum yake nisantar miyagun ayyuka, yake kuma aikata ayyuka na ƙwarai, shi ne gwargwadon yadda kalmar Shahadarsa take ƙara inganci. Shaihul-Islami *Rahimahullahu* yana cewa: "*A duk lokacin da mutum yake ƙara ƙaimi a cikin biyayya da ɗa'a ga Annabi Sallallahu Alaihi Wasallam lokacin ne Tauhidinsa da Allah yake ƙara nauyi, addininsa kuma yake zama ingantacce. Gwargwadon kuma duk yadda yake nisanta da ƙaurace wa biyayya gare shi, kamar haka ne addininsa yake samun tawaya da tasgaro. Da zarar kuma irin wannan nisanta ta bayyana a zahiri, to, sai alamun Shirka da bidi'a su fara bayyana gare shi, gwargwadon yadda ba su bayyana ga wanda ya fi shi kusa ga biyar Manzo Sallallahu Alaihi wa Sallam ba".* [251]

***"Da kuma ƙin bauta ma Allah sai da abin da",*** Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: ***"Ya shar'anta",*** a cikin littafinsa, Manzo kuma *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya zo da shi. Kada mu bauta ma Allah ta hanyar son zuciya ko Bidi'a. Imamuz-Zuhuri *Rahimahullahu* yana cewa: *"Saƙon Musulunci daga*

---

249 *Ahkam Ahl Az-Zimma* 2/451.

250 *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (6856) 6/2658, *Sahih Muslim* Hadisi na (1337) 2/975 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

251 *Al-Fatawa* 17/498.

*wurin Allah yake, isarwa kuma aikin Manzo ce, mu kuwa namu shi ne miƙa wuya da sallamawa".* [252]

Saboda haka, farkon abin da yake wajaba a kan mutum shi ne sanin ma'anar Kalmar Shahada, tare da furta ta da bakinsa, ya kuma yi aiki da abin da take karantarwa. Duk wanda ya cika waɗannan sharuɗɗa, to, ya cika musulmi na ƙwarai mai cikakken arziki. Ga abin da Shaukhul-Islami yake cewa a kan haka: *"Mafi arzikin mutane, da girman ni'ima da ɗaukaka da daraja, su ne waɗanda suka fi yin gamon katar da bin Manzon Allah a cikin ayyukansu da karatunsu".* [253]

Kenan dai ba komai ne addinin Musulunci ba, illa bauta ma Allah shi kaɗai, kamar yadda Shari'a ta tanada; ba tare da yi masa kishiya ba, a cikin abin da ya shafi wajibbai da mustahabbai da kuma sunnoni. Saboda haka duk wanda ya bi wata hanya, wadda ba ta fiyayyen halitta; Almusɗafa *Sallallahu Alaihi Wasallam* ba, ba za a buɗe masa ƙofar Aljanna ba, balle ya shiga. Malam Janaidu *Rahimahullahu* yana cewa: *"Babu wata ƙofa da aka buɗe wa halitta (ta zuwa aljanna), sai bin sawun Manzo Allah Sallallahu Alaihi Wasallam, da riƙe Sunnarsa, da rungumar tafarkinsa. Duk wanda ya kasance haka, babu wata ƙofa ta alheri, da ba za a buɗe masa ba".* [254] *

[252] *Sahih Al-Buhari,* ba da isnadi cikakke ba. Hadisi na (46) 6/ 2738.
[253] *Al-Fatawa* 4/26.
[254] *Madarij As-Salikin* 3/121.

HUJJOJI A KAN ABIN DA YA GABATA

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:*

*"Dalilin kuma Sallah da Zakka da fashin baƙin Tauhidi shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma ba a umurce su da komai ba, face su bauta ma Allah da zuciya ɗaya, suna masu karkata zuwa ga addinin gaskiya, su kuma tsayar da Sallah, kuma su bayar da Zakka. Wannan kuma shi ne addinin waɗanda suke a kan hanyar ƙwarai". Dalilin Azumi kuma shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ya ku waɗanda suka yi imani, an wajabta Azumi a kanku kamar yadda aka wajabta shi a kan waɗanda suke daga gabaninku tsammanin ku za ku yi taƙawa". Dalili a kan Hajji kuma shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma akwai Hajjin Ɗakin domin Allah a kan mutane, ga wanda ya samu ikon zuwa gare shi, wanda kuma ya kafirta, to, lalle Allah Mawadaci ne daga talikai".*

*"Dalilin",* cewa: *"Kuma Sallah",* ta farillah: *"Da Zakka",* suna daga cikin Rukunan Musulunci: *"Da",* wancan: *"Fashin baƙin",* da muka yi wa: *"Tauhidi",* wanda shi ne harsashin da Musulunci ba ya tsayuwa sai a kansa. Wannan dalili: *"Shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: Kuma ba a umurce su",* wato kafirai na kowane zamani: *"Da komai ba, face bauta ma Allah",* shi kaɗai: *"Da zuciya ɗaya",* suna masu manufa ɗaya a cikin wannan ibada, wadda ba ta wuce neman yardar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ba, da neman kusanci zuwa gare shi: *"Suna",* kuma: *"Masu karkata",* daga gaba ɗayan addinai: *"Zuwa ga addinin gaskiya",* wato Musulunci. *"Su kuma tsayar da Sallah",* ta hanyar cika rukunai da wajibbai da kuma yin ta a cikin lokacinta, a matsayinta na mafi girman ibada wadda ake gudanarwa da gangar jiki. *"Kuma su bayar da Zakka",* wadda aka wajabta musu, wadda ta ƙunshi kyautata ma mabuƙata da sauran talakawa. Allah Maɗaukaki ya keɓance Sallah da Zakka ne a nan, ba tare da ya ambaci sauran ibadu ba, tattare da zaman su ƙunshe a cikin faɗarsa:

*"Face bauta ma Allah da zuciya ɗaya".* Ya yi haka ne Maɗaukakin Sarki saboda girma da matsayin da suke da shi.

Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya ci gaba da cewa: *"Wannan kuma",* yana nufin Tauhidi da Ikhlasi a cikin addini, da tsayar da Sallah, ba dayar da Zakka: *"Shi ne addinin waɗanda suke a kan hanyar ƙwarai",* addini tsayayye kuma madaidaici, da Shari'a ta adalci tantagarya, wadda aka tsago daga madaidaicin addini. Ta hanyar biyarsa kuma ake samun shiga gidan Aljanna. Duk abin da kuma ba shi ba, to, hanya ce da babu inda take tuƙewa sai gidan Wuta.

*"Dalilin",* cewa: *"Azumi",* na watan Ramadhan mai albarka yana ɗaya daga cikin Rukunan Musulunci guda biyar, waɗanda Musulunci ba ya tsayuwa sai da su: *"Shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: Ya ku waɗanda suka yi imani, an wajabta Azumi a kanku",* a cikin shekara ta uku bayan hijira, ya ku al'ummar Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallam*: *"Kamar yadda aka wajabta shi a kan",* al'ummomi: *"Waɗanda suka shuɗe gabanin ku".*

Daga cikin hikimomin da suke ƙunshe a cikin wajabta wannan ibada ta Azumi a kan gaba ɗayan al'ummomi, ita ce buƙatar da ke akwai ga taƙawa da tsoron Allah su samu gindin zama a cikin zukata. Wannan shi ne abin da ƙarshen ayar yake tabbatarwa da cewa: *"Tsammanin ku za ku yi taƙawa".* Ba kuwa domin komai ba, sai domin ku amfana da sanadarin da yake kimshe a cikinsa, wanda yake wankewa tare da gusar da dauɗar da take a cikin zukata, wadda ta yi wa ɗabi'u da halayenku dabaibayi. Wannan mataki kuwa wani ƙaimi ne, wanda yake zaburar da gaba ɗayan ɗaiɗaukun wannan al'umma tare da saka masu karsashi, cewa, yana kamata a kanmu, mu yi gwagwarmaya da sauran takwarorinmu a fagen ganin duk aikin da za mu yi ya cika mizani, yana kuma a kan nagartaccen tafarki.

*"Dalili a kan",* cewa: *"Hajji",* shi ma rukuni ne, kuma na biyar daga cikin rukunan Musulunci: *"Shi ne, faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma akwai Hajjin Ɗakin domin Allah, a kan mutane",* wato, ɗauke nauyin wannan ibada wajibi ne a kan su, kamar yadda ɗauke nauyin kowace irin ibada yake wajibi a kan su. Ziyarar Ɗakin Allah mai alfarma wanda yake a birnin Makka: *"Ga wanda ya samu ikon zuwa gare shi",* daga cikin mukallafai. Wato, a wayi

gari mutum yana iya zuwa da kansa. Ya kuma mallaki guzuri da abin hawa, wanda zai kai shi ya kuma dawo da shi, da kuma samun amintaccen ɗan rakiya; *mahrami* ga mace. ***"Wanda kuma",*** duk: ***"Ya kafirta;"*** ya ƙi bauta ma Ubangijinsa ƙiri da muzu, ya juya baya. ***"To, lalle Allah Mawadaci ne daga",*** gaba ɗayan: ***"Talikai".*** Hasali ma dai su ne masu buƙata zuwa gare shi. Shi kuwa Maɗaukakin Sarki mawadaci ne ga barin su. Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Idan kun kafirta, to, lalle Allah wadatacce ne daga barinku, kuma ba shi yarda da kafirci ga bayinsa. Kuma idan kun gode zai yarda da haka…"*

# MATAKIN IMANI

*Malam Muhammadu ɗan Abudlwahabi ya ci gaba da cewa:*

*"Mataki na biyu: Imani, shi kuwa matakai saba'in da 'yan kai ne. Mafi ɗaukakarta ita ce faɗar La'ilaha Illallah. Mafi ƙaranci kuma kawar da ƙazanta daga hanya. Kunya tana daga cikin imani. Rukunan imani kuwa shida ne: Ka yi imani da Allah, da Mala'ikunsa, da littattafansa, da Manzanninsa, da ranar Karshe. Ka kuma yi imani da ƙaddara ta alheri da ta sharri. "Dalili kuma a kan waɗannan rukunai guda shida, shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Bai zama addini ba domin kawai kun juyar da fuskokinku wajen gabas da yamma, kuma amma addini shi ne ga wanda ya yi imani da Allah da Ranar Lahira da Mala'ikunsa da littattafansa da Annabawa…" Dalilin wajabcin yarda da ƙaddara kuma shi ne faɗar Allah Mabuwayin Sarki: "Lalle haƙiƙa mu, mun halicci komai da ƙaddara".*

*"Mataki na biyu",* kuma daga cikin waɗancan matakai na addini, shi ne: *"Imani".* Shi kuwa imani ya ƙunshi faɗa ne da fatar baki, da ƙudurcewa a zuci, da kuma aikatawa da gaɓoɓin jiki. Waɗannan ma'aunai guda uku, kowane daga cikinsu yana haɓaka da bunƙasa, ko tawaya da ragewa gwargwadon yadda mutum yake ɗa'a ko yake keta hurumi da saɓa ma Allah Maɗaukakin Sarki. Saboda haka babu wani horo, ko wani hani, wanda ba daga cikin kayan cikinsa ba, waɗanda suka ƙunshi wajibbai da mustahabbai. Kai! babu wata ɗabi'a, wadda ake iya kira da sunan ɗa'a ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, face tana cikin ayarin imani. Kazalika, nisantar haramiya babba da ƙarama, duk sai da imani suke tabbata.

*"Shi kuwa",* imani: *"Matakai saba'in da 'yan kai ne".* Wannan shi ne lafazin Hadisin da Muslim ya riwaito.[255] Buhari kuma ya riwaito shi da wani lafazin na daban, cewa: *"Matakai sittin da 'yan kai ne".* [256] Ko a wurin

---

[255] *Sahih Muslim,* Hadisi na (35)1/63 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

[256] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (9) 1/12 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

Muslim[257] ɗin ma, Hadisin ya tuzgo da wata riwaya mai baki biyu, wato, cewa: *"Matakai sittin da 'yan kai ne, ko kuma saba'in da 'yan kai".* Malam Ibn Hajar *Rahimahullahu* ya ce: *"Riwayar dai da aka saba da ita, wadda aka tantance aka kuma haƙiƙance, tattare da zamanta ba mai yawa ba, ita ce, cewa, matakai sittin da ɗoriya ne".* [258] Ita kuwa kalmar *"bidh'u"* ta Larabci, wadda muka fassara da "ɗoriya" ko kuma "'yan kai" tana nufin lissafi daga uku zuwa tara. A yayin da ita kuma kalmar *"Shu'batu"* ta Larabci ita ma, wadda muka fassara da "mataki" take nufin wani rukuni na wani abu, gaɓarsa ko kuma yankinsa.

To, idan ana zancen imani, akwai halaye da ɗabi'u da siffofi da dama, waɗanda suke ƙarƙashin inuwarsa. Duk wata ɗabi'a, wadda ka sani, ta ƙwarai, tana daga cikin matakan imani. Sai dai: ***"Mafi ɗaukakarsu",*** da daraja da girma, da zama asasi: ***"Ita ce faɗar La'ilaha Illallah",*** wato, kalmar ikhlasi, kuma kalmar Musulunci. Ita ce kuma kalmar da ake yi ma laƙabi da, *"al'urwatul-Wusƙa",* da *"Kalimatut-Taƙawa",* da *"Asasul-Millah",* da *"Miftahul-Janna".* Ita ce "igiya mai tsauri", ko "Kalmar tsoron Allah" ko "Harsashen Musulunci" ko "Mabuɗin Aljanna". ***"Mafi ƙaranci kuma",*** daga cikin waɗannan darajoji da matakai na imani, ita ce: ***"Kawar da ƙazanta daga hanya",*** wadda ta shafi kamar ƙaya, ko dutse, ko matara kama da hakan, daga cikin abubwan da suke cutar da mai wucewa.

***"Kunya"*** ma: ***"Tana daga cikin",*** matakan: ***"Imani.*** A fassara kuwa, kunya wasu 'ya'yan halitta ne na azaliyya, da suke zaburar da mutum zuwa ga aikata abu mai kyau irin na madalla. A hannu ɗaya kuma tana yi masa dabaibayi da hana shi aikata kishiyarsa, wato mugun aiki irin na ashsha. Ta kuma tabbata cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya bayyana cewa, Allah ba zai taɓa kunyata mai kunya ba". Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[259]

---

[257] *Sahih Muslim,* Hadisi na (35) 1/63 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

[258] *Fath Al-Bari* 1/52.

[259] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (5766) 5/1167, da *Sahih Muslim* Hadisi na (37)1/64 daga Umran ɗan Husain *Radhiyallahu Anhu.*

Abin da ya sa aka lissafa kunya daga cikin matakan imani, shi ne, kasancewar tana yin dabaibayi ga mai ita, ta hana shi saɓa ma Mahalicci. Shi kuwa imani, da ma kashi biyu ne; aikata abin da aka yi umurni da shi, da nisantar abin da aka hana. To, da zarar kuwa aka nisanci abin ƙi, sakamakon kunya, ai ta zama wani rukuni na imani kenan. Ta ma tabbata, babu wani hali, ko wata ɗabi'a, da ta kai girma da daraja da ɗaukakar kunya. Kai! Hasali ma duk mutumin da ba shi da kunya, to, masu hankali ba su lissafawa da shi a cikin jerin mutane. Ga shi kuma ya zo a cikin Hadisi cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya ce: *"Babu wanda yake aikata abin da ya ga dama sai wanda ba shi da kunya".* Buhari ne ya riwaito shi.[260]

Wannan daraja ko ka ce mataki na Imani, ya fi matakin Musulunci tsauri da nauyi, idan aka kalle ta a ware aka kuma a kalli ma'abutanta a ware. Bisa wannan fashin baƙi ne, muminai suka hau matakin zama mutane na musamman daga cikin musulmi. Saboda haka ne Musulmi suka fi muminai yawa; ba muminai suka fi su ba. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki, da ya ce: *"Kauyawa sun ce: Mun yi imani. Ka ce: Ba ku yi imani ba, amma dai ku ce: Mun miƙa wuya".* Kenan duk wanda nassosa suka yanke hukuncin zamansa mumini, to, ya gama zama musulmi, ta kowace fuska. Wannan shaida kuma da ya samu ta zama mumini, ita ce mafi girma da ɗaukaka bisa waccan ta zamansa musulmi. Dalili, shi Imani abu ne da aka samo sunansa daga kalmar "aminci". Shi kuwa aminci abu ne da ya jiɓinci baɗinin mutum, wanda ake samun kwanciyar hankali sanadinsa. Saboda haka abu ne shi na ɓoye. A yayin da shi kuwa Musulunci al'amari ne da ake gani da ƙwayar ido a zahiri. Malamai suka ce, an tsago sunan ne daga kalmar "miƙa wuya" ko "zama lafiya".

Saboda haka duk nassin da ka ji ya ambaci Imani, to, ka tabbata cewa, Musulunci yana nan ƙunshe a cikinsa. Amma, idan ka ji an ambaci Musulunci, to, sai ka shiga neman inda Imani yake. Duk wanda kuma aka tabbatar da zamansa mumini a cikin wani nassi. To, ka sani hakan ta gama tabbatar masa da zama musulmi. Sai dai wajibi a kan kowane musulmi ya zama ya yi imani

[260] Hadisi na (5769) 2267 daga Abu Mas'ud *Radhiyallahu Anhu.*

da rukunan Imani guda shida, kafin Musuluncinsa ya inganta. Idan kuwa ba haka ba, to, sunansa munafuki. To, idan kuma musulmi ya yi imani da waɗannan rukunai guda shida, amma ya yi wa wasu wajibbai na Imani ɗin, riƙon sakainar kashi. To, bai cancanci a yabe shi yabo maras dabaibayi ba, saboda imaninsa yana da matsala. Ya zo a cikin littafin *Ad-Durar As-Saniyyah*, cewa: *"Duk wanda ya yi wa nassosa nazarin ƙwaƙwaf, to, zai fahimci cewa darajojin mutane suna bambanta a cikin Tauhidi da Imani bambanci mai girma. Hakan kuma tana faruwa ne gwargwadon sani, da imanin da yake a cikin zukatansu, da Allah, da kuma ikhlasi da yaƙini".* [261]

***"Rukunan imani kuwa",*** da ginshiƙansa, waɗanda aka ɗora harsashen gininsa a kai, waɗanda kuma da zarar babu su, babu shi, guda: ***"Shida ne".*** Da zarar an rasa ɗaya daga cikinsu, kuma ga mutum, to, ya zama kafiri, kafirci irin wanda yake hana mutum zama cikin da'irar Musulunci. Sauran rukunan kuwa, ba su taka irin wannan rawa. Amma, daga cikinsu akwai wanda idan ya kau, to, imani irin na wajibi, ya samu tasgaro da naƙasu. Daga cikinsu kuma akwai wanda shi ko, Imani irin na mustahabbi ne, rashinsa yake shafa wa laɓo. To, rukuni na farko daga cikin waɗannan rukunan kuma tubalai, na Imani, shi ne: ***"Imani da Allah".*** Wannan shi ne rukuni mafi girma da muhimmanci. Duk sauran rukunai suna ƙarƙashinsa ne. Shi ne asali, shi ne kuma harsashe. Yana kuma nufin bayar da gaskiya da Allah Maɗaukakin Sarki a ɓangaren *Rububiyyah,* da *Uluhiyyah,* da Sunaye da kuma Siffofinsa *Subhanahu wa Ta'ala.*

Imani da *Rububiyyar* Allah *Subhanahu wa Ta'ala* kuwa na nufin rashin jingina ma wani mahaluki, ɗaya daga cikin ayyukan da babu wanda yake da iko da su, sai shi. Wato, kamar halittawa, da azurtawa, da gudanarwa, da rayawa, da kashewa, da sauran matara kama da waɗannan, daga cikin ayyukan da shi kaɗai ne mai su, *Jallah.* Bisa wannan wajibi ne a kan mu, mu yi imani da cewa, babu mai rayawa da kashewa, ko halittawa da azurtawa, sai shi Maɗaukakin Sarki. Wannan shi ake ce ma Tauhidin *Rububiyya.*

---

[261] *Ad-Durar As-Saniyya* 1/207.

Imani da *Uluhiyyar Allah Subhanahu wa Ta'ala* kuwa, na nufin kaɗaita shi da ayyukan ibada. Wato, kada bawa ya karkatar da akalar wata ibada zuwa ga wani wanda ba Allah Maɗaukakin Sarki ba; ya bauta masa. Kamar ɗawafi, da addu'a, da matara kama da su, daga cikin dangogin ibada. Sa'annan kuma mu yi imani da cewa, bautar duk wani abu ba Allah ba shirme ne kawai.

Shi kuwa imani da Allah ta hanyar kaɗaita shi a ɓangaren sunaye da siffofinsa, yana nufin tabbatar ma Allah da sunayen girma da siffofin kamala da ya tabbatar ma kansa. Bayan haka kuma, Manzo *Sallallahu Alaihi wa Sallam,* ya tabbatar masa su, ba tare da wani kankajeli ko waskiya ba. A dai bar su yadda Allah mafi sani ya bar abinsa. Wato, mu yi imani da babu wani abu da ya yi kama da Allah, tare da haka, shi mai ji ne mai kuma gani. Ba irin ji, ko ganin sauran halittu ba.

Rukuni na biyu, daga cikin waɗannan rukunai shida, shi ne, imani: ***"Da Mala'ikunsa",*** Ma'anar wannan shi ne mutum ya sakankance tare da ƙudurcewa, cewa, akwai Mala'iku, kuma gaba ɗayansu bayin Allah ne masu girma da ɗaukaka. Ba kuma yadda za a yi su yi wa Allah katsalanda, sai dai su aikata abin da ya umurce su. Lalle ne musulmi ya yi imani da su a dunƙule da ɗaiɗaice da kuma tantance, kamar dai yadda suka zo a cikin Alƙur'ani da Sunna. Wato, kamar Jibrilu, da Mika'ilu, da Israfilu, da Maliku, da Mala'ikan mutuwa. Duk waɗannan Mala'iku, babu ɗaya daga cikinsu, wanda yake da wata sifa ta Ubangizantaka, ko ƙyas. Su, wata halitta ce kawai ta ɓoye, wadda Allah Maɗaukakin Sarki ya samar daga haske. Ta fuskar adadi kuma, babu wanda ya san yawansu sai Allah.

Rukuni na uku shi ne imani: ***"Da littattafan Allah",*** Waɗanda ya saukar. Ma'ana, yin imani da gaba ɗayan littattafan da aka saukar wa Annabawa daga sama, a dunƙule da kuma a ɗaiɗaice, waɗanda suke sanannu daga cikinsu, su ne, Alƙur'ani, da Zabura, da Attaura, da Linjila, da littattafan Annabi Ibrahimu da na Musa. Mu kuma yi imani da cewa, gaba ɗayan littattafan da suka gabaci Alƙur'ani mai girma, Alƙur'anin ya shafe su. Waɗanda ke akwai a yanzu masu ɗauke da sunansu, ba komai ba ne illa tarkace, wanda ya haɗa gaskiya da ƙarya ya gauraya. Don haka, ba ya halatta a yi aiki ko hukunci da wani abu daga

cikinsu. Aiki ko hukunci, suna wajaba ne kawai idan suka tabbata a cikin Alƙur’ani mai girma ko a cikin Sunnar Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallam*. Allah *Subhanahu wa Ta’ala* yana cewa: *“Idan kuka yi jayayya a cikin wani abu, to, ku mayar da shi ga Allah da Manzo idan kun kasance kun yi imani da Allah da ranar ƙarshe”.*

Rukuni na huɗu daga cikin rukunan imani, shi ne imani: ***“Imani da Manzannin Allah”.*** Abin da hakan ke nufi shi ne, bayar da gaskiya da gaba ɗayan Manzanni a dunƙule kamar yadda aka dunƙule su, da kuma a ɗaiɗaice a inda aka fayyace su. Ma’ana, wajibi ne mu bayar da gaskiya ga gaba ɗayan manzannin da aka ambata garin da garin a cikin Alƙur’ani da Sunna. Mafi girma kuma daga cikinsu, wanda miƙidarin wajabcin imani da shi ya fi nauyi, shi ne Annabinmu Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallam*. Sauran Manzanni takwarorinsa kuma, a wannan ɓangare suna rufa masa baya a muhimmanci. Akwai manya-manya daga cikin Manzanni, wato *ulul-azmi,* waɗanda suka haɗa da Annabi Nuhu, da Ibrahimu, da Musa, da Isah, da kuma ɗungurungum, Muhammadu, yardar Allah da amincewarsa su ƙara tabbata a gare su gaba ɗaya. Bayan su kuma, sai imani da sauran Manzanni, waɗanda sunayensu suka zo a cikin Alƙur’ani, ko kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya ambata mana su. Haka kuma sauran waɗanda babu inda aka ambace sunayensu a cikin nassi, su ma imani da su ya wajaba, hakanan, ba sai an san sunayensu ba. A taƙaice dai, ba za mu nuna bambanci a tsakanin su ba, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗa a cikin littafinsa mai tsarki: *“Ba za mu nuna bambanci ba tsakanin ɗaya daga cikin Manzanninsa ba”.*

Eh! ko shaka babu, imani da Manzanni farilla ne. Abin da yake nufi kuma shi ne, bayar da gaskiya cewa dukansu Manzanni ne, waɗanda Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko su domin su isar da saƙonni zuwa ga bayinsa. Duk abin da suka faɗa kuwa gaskiya ce zalla daga wurin Allah. Miƙidarin abin kuma duk da suka isar, shi ne kammalallen saƙon da aka aiko su da shi; ba su rage komai ba. Sun kuma isar da shi ga rukunin da aka aiko su zuwa gare shi, wato mukallafai, mutanen da suka isa ɗaukar nauyin Shari’a. Annabawa ba su

mallaki komai ba daga cikin siffofin Ubangiji da suka keɓance shi. Imani da waɗannan sharuɗɗa duk wajibi ne.

Rukuni na biyar kuwa, shi ne: ***"Imani da ranar Karshe".*** Abin da wannan yake nufi shi ne, ƙudurcewa a zuci cewa, lalle akwai wata rana tana zuwa, wadda a cikinta duniya za ta ƙare, waɗansu abubuwa kuma su biyo baya, bayan an mutu, an kuma ƙare rayuwar cikin ƙabari, wanda ya haɗa da ni'ima ko azaba na har abada a cikin aljanna ko Wuta. Hakan kuma za ta faru ne bayan hisabi da awon ayyukan bayi. Aljanna da Wuta kuma, wajibi ne su ma a yi imani da kasancewar su waɗansu gidaje guda biyu, na isar da sakamako ga waɗanda suka kyautata ko suka munana a yayin rayuwarsu ta duniya. Mafi girma a cikin wannan lamari na tashin Alƙiyama, shi ne, imani da cewa a wannan rana, za a tayar da mutane a cikin waɗancan gangunan jiki, waɗanda suka rayu da su a duniya, ƙashi da tsoka ɓargo da jijiya. An kuma yi haka ne da zimmar a riskar da gaba ɗayan wancan sakamako a kan gangar jikin da ruhinta baki ɗaya bisa ga abin da suka aikata na ɗa'a da biyayya, ko kangara da fanɗarewa ga Allah Maɗaukakin Sarki. Kenan, ya zama wajibi a kan mahaluki, ya yi imani da cewa Sarkin da ya samar da waɗannan gangunan jiki, ya halicce su, shi kaɗai ba tare da sa hannun waninsa ba, yana nan raye, zai kuma tayar da su kamar yadda suke.*

Rukuni na shida daga cikin rukunan imani shi ne: ***"Imani da ƙaddara",*** wadda take ɗauke da abin da Allah ya rubuta: ***"Ta alheri",*** da farin ciki: ***"Da kuma ta sharri",*** da baƙin ciki. Imani da ƙaddara ya ƙunshi imani da ƙudurcewa da bayar da gaskiya da waɗansu matakai ne guda huɗu:

Mataki na ɗaya shi ne, bayar da gaskiya da cewa Allah Maɗaukakin Sarki ya san duk abin da zai faru, da sadda zai faru, da kuma yadda zai faru, kafin ya faru ɗin, ta hanyar daɗaɗɗen iliminsa da ba shi da farko. Tabbacin wannan shi ne faɗarsa *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Ashe ba ka sani ba cewa, lalle Allah ya san abin da yake cikin sammai da ƙasa?!"*

Mataki na biyu kuma shi ne, bayar da gaskiya da cewa, babu wani abu da zai faru ga bawa, face Maɗaukakin Sarki ya daɗe da rubuta shi a cikin *Lauhul-mahfuzi.* Ga abin da Buwayayyen Sarkin yake cewa: *"Ashe ba ka sani*

*ba cewa, Allah ya san abin da yake cikin sammai da ƙasa? Lalle haƙiƙa wancan yana cikin littafi, lalle wancan mai sauƙi wurin Allah".* Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* kuma ya ce: *"Allah ya gama rubuta duk abin da zai samu gaba ɗayan halitta tun kafin ya halicci sammai da ƙasa, da shekara dubu hamsin, al'arshinsa kuma yana a kan ruwa".* Muslim ne ya riwaito shi.[262]

Mataki na uku shi ne, bayar da gaskiya cewa, abin da duk Allah ya so, ba makawa zai kasance. Abin kuma duk da bai so ba, ko an yi tsafi da baƙar jaɓa, ba zai kasance ba. Duk abin da yake mallakarsa ce *Subhanahu wa Ta'ala*, to, babu wani abu da zai iya kasancewa a cikin wannan farfajiya sai wanda ya so. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Kuma Ubangijinka yana halittar abin da ya so, ya kuma zaɓa".* Mai buwayayyen Karfin kuma yana cewa a wata ayar: *"Yana kuma aikata abin da ya so".*

Mataki na huɗu kuma shi ne, bayar da gaskiya cewa, Allah Maɗaukakin Sarki ne ya samar da gaba ɗayan halitta; duk abin da yake cikin wannan duniya ya samu ne ƙarƙashin iko da buwaya da kuma iyawarsa *Subhanahu wa Ta'ala.* Ga abin da yake cewa: *"Allah ne ya halicci dukan komai".* A wata ayar kuma yake cewa: *"Ya kuma halitta dukan komai, ya kuma ƙaddara shi ƙaddarawa".*

Bisa wannan tsari, babu wanda za a lissafa daga cikin waɗanda suka yi imani da ƙaddara irin ta Allah, sai idan ya yi imani da waɗannan abubuwa guda huɗu, kamar yadda wani mai hikima ya waƙe su:

*"Ilimi, rubutunsa Maulana, nufarsa, tsaya,*
*Da yin halitta da samarwa, ka ƙirga duka.*

Saboda haka ya zama wajibi a kan bawa ya yi imani da cewa, dukan abin da ya same shi, ba yadda za a yi ya kuskure shi. Abin kuma duk da ya kuskure shi, ba yadda za a yi ya same shi. Tabbacin wannan fashin baƙi shi ne faɗar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam*: *"Kuma ka sani dukan abin da ya*

[262] *Sahih Muslim,* Hadisi na (2653) 2044 daga Abdullahi ɗan Amru ɗan Asi *Radhiyallahu Anhu.*

*same ka, bai zama mai kuskure ka ba. Abin kuma duk da ya kuskure ka, bai zama mai samun ka".* Abu Dawuda ne ya riwaito shi.[263]*

***"Dalili kuma akan waɗannan rukunai",*** na imani: ***"Guda shida",*** waɗanda imanin mutum ba ya tabbata sai da samuwar gaba ɗayansu; duk lokacin da ɗayansu ya samu tasgaro, imanin mutum ya tawaya: ***"Shi ne faɗar Allah  Maɗaukakin Sarki: "Bai zama addini ba domin kawai kun juyar da fuskokinku wajen gabas da yamma, kuma amma addini shi ne ga wanda ya yi imani da Allah da Ranar Lahira da Mala'iku da Littafi da Annabawa…"***

Wannan aya ta sauka ne a daidai lokacin da Allah Maɗaukakin Sarki ya umurci muminai da fuskantar *Baitul-maƙadisi,* bayan haka nan kuma ya umurce su da barin sa su fuskanci Ka'abah. To, sai biyar wannan umurni nan take, ya yi nauyi ga waɗansu daga cikin musulmi da kuma *Ahlul-kitabi.* Sai Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar da cikakken bayanin hikimar da take cikin yin haka. Ba kuma komai ne ya kawo haka ba, illa domin ya jarraba nauyin ɗa'arsu da biyayyarsu a gare shi *Subhanahu wa Ta'ala* ta hanyar mayar da gaba duk inda ya yi umurni, da biyar shari'arsa sau da ƙafa. Yin haka shi ne cikakkiyar ɗa'a, shi ne taƙawa, shi ne kuma cikakken imani, ba wai ci gaba da fuskantar wata nahiya; gabas ko yamma ko kudu ko arewa ba, matuƙar ba Allah Maɗaukakin  Sarki ne da shari'arsa suka yi umurni da hakan ba. Saboda haka ne, ya ce:  ***"Bai zama addini ba",*** da cikakkiyar ɗa'ar da ake nema ga bayi: ***"domin kawai kun juyar da fuskokinku wajen gabas da yamma, kuma amma addini shi ne ga wanda ya",*** bi umurnin Allah ta hanyar kama tafarkin Shari'arsa. To, kuma mafi girman abin da wannan aya, ko waɗannan nau'uka na biyayya, suka ƙunsa shi ne, farawa da ambaton imani, da cewa, wanda ya: ***"Yi imani da Allah".*** Wato, abin nufi a nan, addini shi ne yin imani da Allah, da ƙudurce cewa, Allah shi kaɗai yake a cikin siffarsa ta *Rububiyyah* da*Uluhiyyah,* da sunayensa kyawawa da siffofinsa maɗaukaka, shi ne kuma mafarin komai. ***"Da",*** kuma imani da: ***"Ranar Lahira",*** ta hanyar duk abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗa a cikin littafinsa, Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallam* kuma ya ƙarfafa tare da tabbatarwa, game da abubuwan da za su faru

[263] *Sunan Abi Dawud,* Hadisi na (2999) 4/2295 daga Suhaibu *Radhiyallahu Anhu.*

bayan mutuwa, waɗanda suka ƙunshi tayar da halitta a cikin tsofaffin gangunan jikinsu kamar yadda suke a da can, da kuma mayar da rayuka a cikinsu, da tattara halittar farko da ta ƙarshe, domin a saka ma kowa da abin da ya aikata.

***"Da",*** kuma imani da: ***"Mala'iku",*** waɗanda Allah ya ambata a cikin littafinsa, Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallam* kuma ya ƙarfafa a cikin Sunnarsa. ***"Da",*** kuma imani da: ***"Littafi".*** Cewa littafi alami ne, da ya haɗa gaba ɗayan littattafan da Allah ya saukar daga sama, ga Annabawa, wanda a ƙarshe aka shafe gaɓa da mafi girman daraja daga cikinsu, wato Alƙur'ani, wanda yake shi ne alƙali a tsakanin gaba ɗayan littattafan da suka gabace shi, ya kuma yi musu *naskhi.* ***"Da",*** kuma imani da: ***"Annabawa",*** gaba ɗayansu, musamman kuma cikamakin tsarinsu, Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*

***"Dalilin",*** cewa: ***"Kaddara kuma",*** rukuni ce daga cikin rukunan imani, waɗanda imani ba ya karɓa sunansa sai da su: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle haƙiƙa mu, mun halicci komai da ƙaddara".*** Yana nufin gaba ɗayan halitta ta cikin sammai da cikin ƙasa. Allah ya halicce su ba wani ba, ba kuma da sa hannun kowa ba. Cewa kuma "da ƙaddara" yana nufin duk abin da Allah ya halitta *Subhanahu wa Ta'ala*, ƙaddare yake, kuma rubuce a cikin *Lauhul-mahfuz* bisa ƙadimin iliminsa, wanda kuma yawun alƙalaminsa ya riga ya shimfiɗa, cewa zai faru bisa wani gwargwadon lokaci da miƙdari tantantacce, da kuma gaba ɗayan siffofin da suka shafi abin.

Sai dai tattare da haka kana ganin waɗansu mutane, ba su gamsuwa da irin arzikin da Allah Maɗaukakin Sarki ya yanko musu na alheri. Idan kuma wata 'yar tangarɗa ta same su a rayuwa sai ka taras sun fi komai raki da ganin la'ayarin Mahalicci. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullahu* yana cewa: *"Mafi yawan halitta, ko in ce gaba ɗayansu, sai fa wanda Allah ya tsare, suna munana wa Allah zato. A haka sai ka taras da mafi yawan 'ya'yan Adamu suna jin an tauye musu arziki a ɗakin duniya; sun cancanci fiye da abin da Allah ya yanka musu. Idan za ka leƙa birnin zuciyarsu sai ka ji ɗayansu yana cewa, Ubangijina ya zalunce ni, ya ƙi ba ni abin da na cancanta. Bugawar numfashinsa shi ne shaida a kan wannan fashin baƙi. Duk kuwa irin yadda ya yi musun haka da fatar bakinsa, duk wanda ya binciki birnin zuciyarsa ya kuma zurfafa a cikin*

*sassa da lungunanta zai ga waɗannan kalmomi saƙe a cikinta kamar yadda ɓurɓushin wuta yake saƙe a cikin tokar wutar karan gero. Duk wanda ka ƙwanƙwashi makamashi ɗaya daga cikin makamasan wutar da ke ci a cikin zuciyarsa za ka taras da wannan magana da muke faɗa; za ka taras yana zargin ƙaddara yana kuma fushi da ita, yana jin ya cancanci fiye da abin da aka riga aka ba shi. Yana batun zuci yana cewa, ai kaza ko kaza ya cancanta, haka ya kamata abin ya kasance; ya fi haka yawa. To, sai ka yaƙi birnin zuciyarka ka gani shin ka tsira daga irin wannan mugun hali, ko ƙaƙa?!!"*[264]

---

[264] *Zad Al-Ma'ad* (3/235)

## MATAKIN IHSANI

***Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:***

***"Mataki na uku kuma shi ne Ihsani. Rukuni ne mai zaman kansa, "idan ba ka ganinsa, to, shi yana ganinka". Dalili kuma a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: " Lalle Allah yana tare da waɗanda suka yi taƙawa, da kuma waɗanda su ne masu kyautatawa". Da kuma Allah Mabuwayi: "Kuma ka dogara ga mabuwayi mai jinƙayi. Wanda yake ganin ka a lokacin da kake tashi tsaye. Da jujjuyawarka a cikin masu yin sujada. Lalle shi, shi ne mai ji Masani". Da kuma faɗarsa: "Kuma ba ka kasancewa a cikin wani sha'ani, kuma ba ka karanta wani abin karatu daga gare shi ba, kuma ba ka aikata wani aiki, face mun kasance halarce a lokacin da kuke kutsawa a cikinsa".***

***"Mataki na uku kuma",*** daga cikin matakan addini: ***"Shi ne",*** matakin: ***"Ihsani".*** *Ihsani* kuwa shi ne zango na ƙarshe a cikin zangunan *Ikhlasi.* Shi kuwa *Ikhlasi*, yana nufin bauta ma Allah *Subhanahu wa Ta'ala* a cikin cikakkiyar siga zahiri da baɗini. Wannan shi ake ce wa *Ihsani.* Saboda haka ne ma wasu malamai suke fassara *Ihsani* da *Ikhlasi.* Ita wannan kalma kuma ta *Ihsani* an tsago ta ne daga kalmar *Husnu.* Abin da yake nufi kuma shi ne kaiwa matuƙa a cikin kyautata niyya a zuci. A zahiri kuma kaiwa matuƙa a cikin biyar Sunna sau da ƙafa.

Malaman da suka fassara *Ihsani* da *Ikhlasi,* sun yi haka ne ta hanyar la'akari da ƙarshen abin da yake samarwa da haifarwa. Wato, duk wanda sifar *Ihsani* ta tabbata gare shi, to, mawuyacin abu ne a rasa samun sa a cikin sahun masu kyautata ibada da yin ta a cikin kamala ta zahiri da baɗini. Shaihul-Islami *Rahimahullahu* yana cewa: *"Abin da Ihsani yake nufi shi ne, aikata abin da aka yi umurni da shi, daɗa kyautata wa mutane ne ko kai. Amma, mafi girman Ihsani ga alkadari shi ne, imani da Tauhidi da komawa ga Allah Ta'ala, da fuskantar sa da kuma dogara gare shi. Sa'annan kuma mutum ya bauta masa kamar yana ganin sa saboda girmamawa da kunya da so da ƙauna da kuma*

*fargaba. Wannan shi ne matakin Ihsani".* [265] Malam Ibn Daƙiƙil-Idi *Rahimahullahu* yana cewa: *"Karshen abin da Ihsani yake nufi, shi ne kyautata ibada, da kiyaye haƙƙoƙan Allah Ta'ala da kiyaye lamarinsa, da kuma halartowa da girma da ɗaukakarsa a lokacin da ake bauta masa".*

*Ihsanin* nan da ake zance kuma shi ne mafi girman gaba ɗayan matakan da bayaninsu ya gabata, shi ne kuma mafi faɗi da gamewa a ƙashin kan kowannensu. Ta ɓangaren waɗanda suka sifaitu da su kuma, shi ne mafi lada. Duk wanda ya taka matakin *Ihsani,* to, ya gama taka matakin Imani da Musulunci. Amma, ba duk wanda ya taka matakin Musulunci ba ne ya gama taka na Imani da *Ihsani.* Wato, idan za a yi gwarigwari, sai a ce, idan aka ambaci *Ihsani*, to, a ƙarƙashinsa akwai Imani da Musulunci. Kasancewar Imani da Musulunci da *Ihsani*, ba su rabuwa da juna, wato, matakai ne, da wani yana take sawun wani. Sai dai mafi faɗi daga cikinsu shi ne matakin Musulunci. Sa'annan matakin Imani yana bi masa. Shi kuma matakin *Ihsani* yana rufa masa baya, shi ne kuma mafi zama taƙaitacce. Wato, kamar dai a ce, kowane mataki daga cikinsu, yana sarƙe ne da ɗaya daga cikin biyun, haka-haka. Sanannen abu ne kuma, duk wanda ya taka matakin *Ihsani,* to, ya gama shiga cikin sahun musulmi masu kuma imani. Idan kuma ya yi ƙasa kaɗan, wato, ya taka mataki na biyu, to, ya hau matakin imani kenan. Idan kuma likkafarsa ta gaza ya ɗan yi ƙasa, ya bar wannan mataki, ya sauka a na uku, to, zai samu kansa a matakin Musulunci kenan. Duk kuwa wanda ya kasa samun kansa a cikin ɗaya daga cikin waɗannan matakai, to, ya shiga shiga cikin farfajiyar fushi da azabar Allah Maɗaukakin Sarki; ya faɗa hannun Shaiɗan kenan. Allah ya kiyaye mu.

Da wannan misali kuma da aka buga ta hanyar amfani fa kalmar "mataki" ana iya tabbatar da ingancin zancen waɗanda suke cewa, dukan *muhsini*, *mumini* ne kuma musulmi, amma ba duk musulmi ne, *mumini* kuma *muhsini* ba. A wata Hausa ana nufin, ba lalle ba ne wanda ya shiga cikin Musulunci ba, ya zama *mumini* kuma *muhsini.* Ba kuma ana nufin a ce, duk wanda bai zama mumini kuma muhsini ba, kafiri ne, ko alama. A'a, yana nan

[265] *Al-Fatawa* 15/10

dai musulmin sa, a tare da shi kuma akwai wani miƙidari na *Ihsani,* gwargwadon abin da zai inganta Musuluncinsa. Sai dai ba za a lisafta shi cikin muminai masu cikakken imani ba, irin wanda zai sa su cancanci gagarumin yabo, cikakke. Amma, ɗan ƙwarya-ƙwaryan yabo, na ba ka rasa ba, zai same shi gwargwadon nauyin imaninsa. Abin nufi a nan shi ne, inda ace ya samu taka wancan mataki na cikar imani, ba za a same shi yana aikata wasu 'yan ƙananan laifuka ba, da faɗawa cikin taƙaitacciyar haramiya. Ta tabbata wata rana an ce wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam*: *"Ya za ka ba su wane, ka manta da wane, alhali mumini ne?!"* Sai ya ce: *"Mumini ko dai musulmi?"* Ahmad ne ya riwaito shi.[266] A wani wurin kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya ce: *"Mazinaci ba zai yi zina ba, a lokacin da yake yin ta yana mumini. Ɓarawo kuma ba zai yi sata ba a lokacin da yake yin ta yana mumini".* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[267] A wani wurin kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya ce: *"Wallahi ba shi da imani! Wallahi ba shi da imani!! Wallahi ba shi da imani!!! Sahabbai suka ce: Waye ya Manzon Allah? Ya karɓa musu da cewa: Wanda maƙwabcinsa bai tsere wa sharrinsa ba".* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[268] Ka ga babu wani nassi daga cikin waɗannan nassosa da ya kore zaman musulmi, musulmi saboda aikata laifi. Hasali ma, sai dai suka tabbatar masa da tanade-tanaden da Musulunci ya yi masa, na kuɓutar jini da matara kama da shi.

Mutanen da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya yi wa arzikin taka matakin *Ihsani,* su ne halitta mafi tsada daga cikin tarayyar masu imani. Su kuwa waɗanda suka taka matakin Imani, su ne mafiya tsada a da'irar Musulmi. Su ma'abuta *Ihsani* ɗin nan, ba su sami taka wannan matsayi ba, sai da suka ratsa da'irar bauta ga Allah, suka yi ta a cikin cikakkiyar sifa har suka kai zangon *muraƙaba*, jin kamar ga su ga Allah. Su ne kuma zaɓaɓɓu, na musamman daga cikin bayinsa muminai.

---

266 *Al-Musnad,* Hadisi na (1579) 1/182 daga Sa'ad ɗan Malik.

267 *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (6882) 4/ 245, da *Sahih Muslim,* Hadisi na (57) 1/76-77 daga Abu Hurairata da ɗan Abbas *Radhiyallahu Anhuma.*

268 *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (5670)5/2240, da *Sahih Muslim,* Hadisi na (46) 1/67 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

Daga cikin kuma abubuwan da suke taimakawa ga isa matakin *Ihsani*, akwai yawaita ambaton Allah Maɗaukakin Sarki. Ibn Al-Ƙayyim *Rahimahullahu* yana cewa: *"Zikiri yana sa mutum ya riƙa jin kamar ga shi ga Allah. A haka har ya samu kansa a cikin da'irar Ihsani, ya riƙa bauta ma Allah kamar yana ganinsa. Babu kuwa yadda za a yi gafalalle ya iya kai ga wannan mataki na Ihsani, kamar yadda ba yadda za a yi wanda ya share wuri ya zauna a tsakiyar hanya ya samu isa gida".* [269]

Ita kuwa *"muraƙaba",* wato, jin kamar ga ka ga Allah, ita ce tushen ingancin duk wata ibada, wadda mahallinta shi ne zuciya. Ga abin da Ibn Al-Ƙayyim yake cewa game da haka: *"Muraƙaba ita ce tushen gaba ɗayan ayyukan zuciya, ginshiƙin kuma da suka dogara a kai".* [270]

Shi kuma *Ihsani* ɗin nan, wani: ***"Rukuni ne mai zaman kansa".*** Abin da yake nufi kuma shi ne: ***"Ka bauta ma Allah",*** kowace irin bauta: ***"Kamar kana ganin sa",*** a matsayinsa na Ubangijinka wanda kake tsaye a gabansa kana bauta masa. ***"Idan kai ba ka ganinsa",*** ba ka taka matakin *muraƙaba* ba: ***"To, shi yana ganin ka",*** yana kuma ganin duk abin da yake a cikin birnin zuciyarka. To, su waɗannan matakai guda biyu, ɗaya daga cikinsu ta ɗara ɗaya cika da kamala. Abin da ake so shi ne, idan ka kasa bauta ma Allah *Ta'ala* kamar kana ganin sa. To, ka ƙudurce cewa, shi yana ganin ka, yana kuma ganin duk abin da kake aikatawa.

***"Dalili kuma a kan haka;"*** zaman matakin *Ihsani,* matakin Musulunci, daga cikin Alƙur'ani: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle Allah yana tare da waɗanda suka yi taƙawa;"*** suka ji tsoron Ubangijinsu ta hanyar aikata ayyukan ɗa'a, da nisantar haramiya. ***"Da kuma waɗanda su ne masu kyautatawa",*** a cikin ibadojinsu zuwa ga Ubangijinsu, da kuma kyautatawarsu zuwa ga takwarorinsu abokan halitta. Tabbas Allah yana tare da bayinsa masu taƙawa, masu kuma kyautatawa a cikin ayyukansu. Allah zai kiyaye ya kuma ƙarfafa ya kuma ɗauki nauyin rayuwarsu. Wannan ita ce tarayyar da take tsakaninsa *Subhanahu wa Ta'ala* da su, ta musamman.

[269] *Alwabil As-Sayyib,* shafi na 52.
[270] *I'ilam Al-Muwaƙƙi'in* (4/204).

Dalili na biyu kuma a kan matakin *Ihsani,* shi ne: ***"Faɗarsa",*** *Subhanahu wa Ta'ala*: ***"Kuma ka dogara",*** a cikin gaba ɗayan al'amurranka: ***"Ga Mabuwayi, mai jinƙayi".*** Tabbas zai ƙarfafe ka ya kuma kiyaye ka. Bayan haka kuma sai ya faɗakar a kan neman agaji da taimako, ta hanyar halartowa da kusanci da Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, da ƙoƙarin hawa matakin *Ihsani*, ya ce: ***"Wanda yake ganin ka",*** a cikin wannan babbar ibada ta Sallah: ***"Lokacin da kake tashi tsaye",*** domin yin ta.

***"Da jujjuyawarka a cikin masu yin sujada;"*** duk yana ganin ka a yayin da kake sujada da ruku'i da zama a cikin ta. Allah Maɗaukakin Sarki ya ambaci Sallah ita kaɗai ne, saboda falala da girman darajarta. Da kuma kasancewar duk wanda ya halarto da kusanci da Ubangijinsa, ya kuma ƙasƙantar da kai, ya kuma kammala ta iyakar kammalawa. To, da zarar haka ta samu, Sallah ta kammala, za ta zama ƙaimi da taimako ga cika da kamalar sauran ayyuka. ***"Lalle shi, shi ne mai ji Masani",*** yana ji ya kuma san gaba ɗayan motsin mutum.

Dalili na uku: ***"kuma",*** a kan matakin *Ihsani,* shi ne: ***faɗarsa: "Kuma ba ka kasancewa",*** ya kai Annabi: ***"A cikin wani sha'ani",*** daga cikin ayyukanka gaba ɗaya. ***"Kuma ba ka karanta wani abin karatu daga gare shi",*** wata aya daga cikin ayoyin alƙur'ani. ***"Kuma ba ka aikata wani aiki",*** babba ko ƙarami, kai da al'ummarka: ***"Face mun kasance halarce",*** muna ganin duk abin da yake faruwa, wanda ya shafi yanayi da halayen bayi a cikin motsinsu da zamansu: ***"A lokacin da kuke kutsawa a cikinsa".*** Lokacin da musulmi suke shiga cikin ibadar Sallah, da ci gaba da gudanar da ita, har zuwa lokacin da za su ƙare ta. Duk waɗannan al'amurra suna faruwa a kan idonsa Maɗaukakin Sarki.

## HADISIN JIBRIL ALAIHIS SALAM

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:*

*"Dalili kuma daga cikin Sunna, shi ne shahararren Hadisin nan na Mala'ika Jibrilu Alaihis Salam. Daga Sayyidi Umar ɗan Khaɗɗabi Radhiyallahu Anhu, inda ya ce: Wata rana muna zaune a wurin Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam sai wani mutum ya hudo mana. Mai tsananin farin tufafi, mai tsananin baƙin gashi, ba a ganin alamun tafiya a gare shi. Babu kuma ɗaya daga cikinmu wanda ya san shi. Har ya zauna wurin Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam, ya jingina guwawunsa a jikin guwawunsa, ya kuma ɗora tafukansa a kan cinyoyinsa, ya kuma ce: Ya kai Muhammadu! Ba ni labari game da Musulunci. Sai ya ce: Shi ne ka shaida babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, kuma Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma ka tsayar da Sallah, ka bayar da Zakka, ka yi Azumin watan Ramadhan, ka ziyarci ɗakin Allah idan ka samu iko. Ya ce: Ka yi gaskiya. Sai muka yi mamakin sa. Yana tambayarsa yana kuma gaskata shi! Ya ce: To, ba ni labari game da Imani. Sai ya ce: Ka yi imani da Allah, da Mala'ikunsa, da littattafansa, da Manzanninsa, da Ranar Karshe, ka kuma yi imani da ƙaddara ta alhairi da ta sharri. Ya ce: Ka yi gaskiya. Ya ce: To, ba ni labari game da Ihsani. Sai ya ce: Shi ne ka bauta ma Allah kamar kana ganin sa. Domin idan kai ba ka ganin sa, to, shi yana ganin ka. Ya ce: Ba ni labari game da Alƙiyama. Sai ya ce: Wanda aka tambaya bai fi wanda ya yi tambaya sani ba. Ya ce: To, ba ni labari game da alamominta. Sai ya ce: Bauya za ta haifi uwar gijiyarta. Za ka kuma ga talakawa marasa takalma, huntaye, masu kiwon awaki suna gasa gina dogayen benaye. Ya ce: Sai kawai ya tafiyar sa. Sai muka ci gaba da zama ɗan ƙanƙanin lokaci. Sai Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ce: Ya Umar! Shin ko ka san wannan mai tambayar? Sai na ce: Sanin a wurin Allah da Manzonsa. Sai ya ce: Wannan Jibrilu ne ya zo domin ya sanar da ku addininku."*

***"Dalili kuma,"*** a kan waɗancan matakai na addini guda uku, wato, Musulunci, da Imani, da Ihsani: ***"Daga cikin Sunna,"*** ta Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Shi ne shahararren Hadisin nan na Mala'ika Jibrilu Alaihis Salam,"*** wanda malam Kurɗabi *Rahimahullah* ya ce game da shi: *"Da za a raɗa ma wannan Hadisi suna Garken Sunna saboda irin yadda ya tattara gaba ɗayan abin da Sunna take karantarwa, ba a yi laifi ba; ya cancanci haka."*[271] Sa'annan kuma Imamun-Nawawi *Rahimahullah* ya ce game da shi: *"Ka sani, haƙiƙa wannan Hadisi ya tara dangogin sannai da ilimuka da ladubba da matakai masu tarin yawa. Kai! Hasali ma shi ne ginshiƙin Musulunci."*[272]

Imamu Muslim ya fitar da wannan hadisi mai girman daraja, a cikin ingantaccen littafinsa: ***"Daga Sayyidi Umar ɗan Khaɗɗabi Radhiyallahu Anhu,"*** Halifa na biyu daga cikin Halifofin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Inda ya ce,"*** a ƙoƙarinsa na kawo irin yadda ya faru tsakanin mafi girma da darajar Manzanni, Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da mafi girma da darajar Mala'iku, Jibrilu *Alaihis Salam*:

***"Wata rana muna zaune a wurin Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam."*** A wata riwaya kuma a cikin ingantattun littattafan Buhari da Muslim, ya ƙara da cewa: *"A ranar Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya saki jiki a cikin mutane."* ***"Sai wani mutum ya hudo mana,"*** a cikin surar mutum. Amma, a haƙiƙa Mala'ika ne. ***"Mai tsananin farin tufafi;"*** babu wani ɗosanon datti a kan su. Wannan kuwa hujja ce da take tabbatar da bukatar saka tufafi masu kyau da kyautata yanayi a duk lokacin da mutum zai kai ziyara ga wani babban mutum ko Malami ko Sarki. ***"Mai,"*** kuma: ***"Tsananin baƙin gashi,"*** ba ƙura ko kaɗan a kansa. Ka kuwa san alama ce wadda ake gane matafiyi da ita, a ga gashinsa ya yi ƙutut-ƙutut. Amma, tattare da haka: ***"Ba a ganin alamun tafiya tare da shi,"*** waɗanda suka haɗa da gajiya da ƙosawa da gurabun galabaita da canjawar yanayi sakamakon hawa da gangara. ***"Babu kuma ɗaya daga cikin mu wanda ya san shi."*** Eh! babu wasu alamun matafiyi tare da shi. Babu kuma

271 *Fath Al-Bari* 1/125.

272 Sharhin Imam Nawawi a kan *Sahih Muslim,* 1/160.

wani sahabi daga cikinmu, wanda zai ce ya san ko waye shi. Ya kuwa za a yi wani ya san shi, tunda ba mazauni garin Madina ne ba! Waɗannan dalilai sai suka saka tarayyar sahabbai a cikin mamaki da al'ajabi.

***"Har ya zauna wurin Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam;"*** kusa da shi. ***"Ya jingina guwawunsa,"*** shi baƙon: ***"A jikin guwawunsa,"*** wato guwawun Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya kuma ɗora tafukansa,"*** shi baƙon: ***"A kan cinyoyinsa,"*** wato, cinyoyin Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Ya kuma zauna a cikin siga irin ta mai neman sani. A cikin wata riwaya kuma ta Daraƙuɗni[273], cewa ya yi: *"Sai ya ɗora hannayensa a kan guwawun Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam."* Shi kuma Sulaimanu At-Tamimi *Rahimahullahu* a tasa riwayar cewa ya yi: *"Sai ya ƙetara kafaɗun sahabbai har ya kai ga durƙusawa a gaban Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam kamar yadda ɗayanmu yake zaman sallah. Sa'annan ya ɗora hannayensa a kan guwawun Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam.*[274] Ka ga wannan mataki da wannan baƙo ya ɗauka, alama ce da take nuna irin yadda yake shirye da sauraren mai masaukinsa. Yanayin kuma ɗauke yake da ishara a kan irin yadda ya kamata mai tambaya ya yi tawali'u, ya kuma kawar da kai daga duk abin da zai haɗu da shi.

To, sai Mala'ika Jibrilu: ***"Ya kuma ce: Ya Muhammadu! Ba ni labari,"*** yana nufin Annabi ya karantar da shi: ***"Game da,"*** rukunnan: ***"Musulunci;"*** da abin da ya ƙunsa. ***"Sai,"*** Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya ce: Shi ne ka shaida,"*** ka kuma sakankance: ***"Babu wanda ya cancanci bauta sai Allah,"*** shi kaɗai: ***"Kuma Muhammadu,"*** *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Manzon Allah ne. "Kuma ka tsayar da Sallah,"*** ta farilla, kamar yadda aka ce ka yi ta, da sharuɗɗa, da rukunai, da kuma wajibanta. ***"Ka bayar da Zakka,"*** ta farilla, ga waɗanda suka cancance ta. ***"Ka,"*** kuma: ***"Yi Azumin watan Ramadhan,"*** mai albarka. Kuma: ***"Ka ziyarci ɗakin Allah,"*** mai alfarma; ka yi Hajji: ***"Idan ka samu iko,"*** a kan haka, wanda ya haɗa da guzuri da abin hawa, da samun amintaccen abokin rakiya *mahrami* ga 'ya mace, bisa dalilin faɗar Annabi

---

[273] *Sunan Ad-Dar-Kuɗni,* Hadisi na (207).
[274] *Fath Al-Bari,* na Ɗan Hajar (1/116).

*Sallallahu Alaihi wa Sallam*: *"Kada mace ta yi tafiya sai tare da mahrami. Sai wani sahabi ya ce: Ya Manzon Allah! Ni matata ta kama hanyar zuwa Hajji, ga shi kuma kuma an rubuta sunana a cikin waɗanda za su halarci yaƙi kaza da kaza. Sai Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ce: je ka, ka bi ta, kai ma ka yi hajjin."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[275] Shi aikin Hajji ibada ce da Allah Maɗaukakin Sarki ya wajabta wa musulmi sau ɗaya a cikin rayuwarsa. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya bayyana irin falalar da yake da ita a cikin faɗarsa: *"Duk wanda ya ziyarci wannan ɗaki, bai yi alfasha ba, bai kuma yi fasiƙanci ba, to, zai koma gida kamar ranar da uwarsa ta haife shi."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[276]

Waɗannan rukunai guda biyar su ne Musulunci. Tabbacin wannan ma shi ne riwayar Ahmad, wadda a cikinta yake cewa, sai mai tambayar ya ce: *"Yanzu idan na aikata waɗannan na zama musulmi kenan? Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya karɓa masa da cewa: Da zarar ka tsare alfarmarsu, tabbas, ka zama musulmi."* Wannan shi ne dalilin mataki na farko. Wasu malamai kuma sun ambaci waɗannan abubuwa da suna: *"Ayyukan gaɓɓai na zahiri."* Shakka babu, Musulunci shi ne addini. Dalili a kan haka kuwa shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* in da ya ce: *Haƙiƙa, addini a wurin Allah shi ne Musulunci."* Shi ne kuma tafarki madaidaici wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi umurni da kamawa.

Sai Mala'ika Jibrilu: ***"Ya ce: Ka yi gaskiya,"*** ya Muhammad! ***"Sai muka yi mamakin sa,"*** bisa wannan ƙarfin hali, ah! ***"Yana tambayarsa yana kuma gaskata shi!"*** Dalilin wannan mamaki na sahabbai kuwa shi ne, masaniyar da suke da ita cewa, wanda yake tambaya ya jahilci abin da yake tambaya a kan sa. Amma, sai ga shi yau baƙon nasu yana tambayar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana kuma ce masa: *"ka yi gaskiya."* Kamar dai da ma ya riga ya san abin da yake tambaya a kan sa. Amsar kuma da Annabi *Sallallahu Alaihi*

---

275 *Sahih Al-Buhari* lamba (1763) 2/658, *Sahih Muslim,* Hadisi na (1334) 2/978 daga Hadisin Ibn Abbas *Radhiyallahu Anhu.*

276 *Sahih Al-Buhari* lamba (1449) 2/553, *Sahih Muslim,* Hadisi na (1350) 2/983-984 daga Hadisin Ibn Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

*wa Sallam* ya ba shi, kamar ba a taɓa sanin ta a sararin *subhana* ba, sai daga bakinsa shi da yake tambayar. Irin wannan matambayi kuwa, ba su saba ganin irinsa ya baƙunci Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ba; baƙo ne a gare su. Ga shi kuma ya yi tambaya irin ta wanda ya riga ya san abu, ya tantance, ya kuma ƙwanƙwance shi. Wannan shi ne abin da ya ba su mamaki.

Sai Jibrilu *Alaihis Salam*: ***"Ya ce, To, ba ni labari,"*** ya Muhammad! ***"Game da Imani,"*** mene ne shi? ***"Sai,"*** Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya,"*** karɓa masa da: ***"Ce***wa," imani shi ne: ***"Ka yi imani da Allah,"*** da duk abin da ya shafi *Rububiyyah* da *Uluhiyyah* da sifofi da kuma sunayensa. Imani da Allah, shi ne asali kuma jadanin sauran rukunan imani; duk sauran rukunan da ba shi ba, suna ƙarƙashin inuwarsa ne.

Ka kuma yi imani: ***"Da Mala'ikunsa,"*** a dunƙule inda suke a dunƙule, da fayyace inda labarinsu ya zo a fayyace, da gaba ɗayan sunayensu da ayyukansu, da sauran hidimomin da aka jiɓinta musu. Ka kuma yarda da cewa, bayi ne su na Allah masu girma, waɗanda ba su saɓa wa umurnin da Allah ya ba su; ba abin da suke aikatawa sai wanda ya umurce su. Ka kuma yi imani: ***"Da littattafansa;"*** gaba ɗaya, waɗanda ya saukar ga Manzanninsa, kamar Attaura, da Linjila, da Zabura, da littattafan Ibrahimu da Musa. Kuma gaba ɗayansu, Alƙur'ani ya shafe su. Sauran waɗancan littattafan kuma, babu ɗaya daga cikinsu, wanda lahani da ɓarna ba su shige shi ba. Ka kuma yi imani: ***"Da Manzanninsa."*** Cewa Allah ya zaɓi wasu mutane ya aiko su a matsayin Manzanni, domin shiryar da mutane zuwa ga tafarkin gaskiya. Ka yi imani da su a jumlace a inda suke jumlace. Da kuma a fayyace inda suka zo a haka, waɗanda ka san sunayensu, da waɗanda ba ka sani ba, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: *"Da wasu Manzanni, haƙiƙa, mun ba da labarinsu a gare ka daga gabani, da wasu Manzanni waɗanda ba mu ba ka labarinsu ba."*

Ka kuma yi imani: ***"Da Ranar Karshe,"*** ka gaskata duk abin da ya zo a cikin Alƙur'ani da Sunna, game da abin da zai wakana bayan mutuwa. ***"Ka kuma yi imani da ƙaddara,"*** samuwarta da abin da Allah ya tara a cikinta: ***"Ta alhairi,"*** wadda ta ƙunshi farin ciki da murna: ***"Da,"*** kuma: ***"Ta sharri,"*** da abin da ta ƙunsa mai ɗaci da baƙin ciki, ba tare da raki da fushi a kai ba. A

taƙaice dai dole ne Musulmi ya bad a gaskiya a kan cewa, babu wani abu da ya faru ko zai faru nan gaba, face sai cikin yarda, da hukunci, da nufi, da ƙaddarawar Allah. A kuma lura, maimaita kalmar *"ka kuma yi imani,"* da aka yi a wajen magana a kan ƙaddara. Hakan ta kasance ne sakamakon muhimmancin lamarin. A cikin riwayar Ahmad ma cewa aka yi: *"Ka kuma yi imani da Aljanna, da Wuta, da hisabi, da ma'aunin lahira. Ka kuma yi imani da ƙaddara gaba ɗayanta; ta alhairi da ta sharri. Sai mai tambayar ya ce: Idan na aikata haka, na yi imani kenan? Annabi ya ce: Da zarar ka tsare alfarmar waɗannan abubuwa, to, ka yi imani."* [277] Sai Jibrilu ya ce: ***"Ya ce: Ka yi gaskiya."***

Waɗannan su ne dalilan mataki na biyu, wato, imani. Mawallafin kuma ya bayyana cewa, waɗannan matakai, su ne ayyukan baɗini. Hadisin kuma ya nuna cewa, idan aka haɗa hancin Musulunci da na Imani a wuri ɗaya, to, Musulunci ya zama ɗaya daga cikin ayyukan zahiri kenan. A yayin da shi kuwa Imani, zai ɗauki matsayin ayyuka irin na baɗini.

Sai Jibrilu *Alaihis Salam*: ***"Ya ce,"*** ya Muhammad! ***"To, ba ni labari game da Ihsani;"*** mene ne shi? ***"Sai,"*** Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya ce: Shi ne ka bauta wa Allah kamar kana ganin sa."*** Wato, ka rinjayar da zato a cikin zuciyarka, cewa kamar ga ka ga *Rabbul-Iz*zati, kamar dai kana ganin sa da ƙwayar idanunka. Duk wanda ya tsare alfarmar wannan ƙa'ida, to, zai bauta wa Allah bisa cika da kamala. ***"Domin idan kai ba ka ganinsa,"*** wato, ba ka iya ƙaddara kana ganin Allah Maɗaukakin Sarki ba. To, sai ka cirata zuwa mataki na biyu daga cikin matakan *ihsáni*. Wato, ka ji cewa: ***"To, shi,"*** fa Allah Ta'ala: ***"Yana ganinka,"*** yana kuma sane, gane, da duk abin da kake aikatawa; babu wani abu naka da yake iya shige masa duhu.

Wannan yanki na Hadisi wani shisshike ne, kuma tushe daga cikin tuwasu, kuma asullan addini. Wata ƙa'ida ce kuma daga cikin ƙa'idojin ilimi. Yana kuma daga cikin dunƙulallun kalmomi irin waɗanda Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya fuwace wa Annabinsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Ai ba komai ne

[277] *Al-Musnad,* Hadisi na (2926) 1/319.

kyautata ibada ba, illa yin ta da zuciya ɗaya tare da ƙanƙan da kai, da kakkaɓe zuciya daga komai a daidai lokacin gudanar da ita, da kuma tsoron Allah.

Bayan haka kuma amsar da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya bayar dangane da wannan tambaya, ta ƙunshi falle biyu ne. Mafi girma daga cikin su, ita ce: Rinjayar da zaton ganin Allah, har mutum ya ji kamar ga shi, ga shi, yana ganin shi da ƙwayar idonsa. Mataki na biyu kuma, ƙaddara cewa, Allah Maɗaukakin Sarki yana ganin sa, sane kuma yake da duk abin da yake aikatawa. Su kuwa waɗannan yanaye-yanaye guda biyu, sakamakonsu shi ne, gane Allah Maɗaukakin Sarki da kuma jin tsoron sa. Wannan shi ne abin da ya zo a cikin wata riwaya, cewa: *"Ka ji tsoron Allah kamar kana ganinsa."* Muslim ne ya riwaito shi.[278] ka ga a harshen Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, tsoron Allah shi ne *ihsáni.* Wannan kuma shi ne dalilin mataki na uku.

Wannan hadisi ya isa zama dalili a kan wannan martaba ta uku. Rukunanta kuma su ne waɗanda mawallafin *Rahimahullahu* ya lissafa.*

Sai Jibrilu: ***"Ya ce,"*** to: ***"Ba ni labari game da Alƙiyama,"*** ya Muhammad, yaushe ne za ta tsaya? ***"Sai,"*** Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya ce," "Wanda aka tambaya,"*** yana nufin shi kansa: ***"Bai fi wanda ya yi tambaya sani ba,"*** yana nufin Jibrilu. Wato, a taƙaice yana gaya masa ne cewa, ai, shi da shi ba wani bambanci a cikin wannan mas'ala; duk sun yi tarayyar rashin sani sa'ar da za a yi tashin ƙiyama. Sanin wannan lamari sai Allah Maɗaukakin Sarki shi kaɗai. Tabbacin wannan kuwa shi ne faɗar Buwayayyen Sarki Allah da yake cewa: *"Ka ce, abin sani kawai, sanin ta na a wurin Allah. Babu mai bayyana ta ga lokacinta face shi."*

Jibrilu *Alaihis Salam* ya ci gaba: ***"Ya ce,"*** idan baka da masaniya da lokacin da za a yi Tashin Kiyama, ya kai Muhammad! ***"To, ba ni labari game da alamominta,"*** waɗanda su ke share mata fage. ***"Sai,"*** Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya ce,"*** daga cikin alamominta akwai: ***"Baiwa,"*** ko kuyanga: ***"Za ta haifi uwar gijiyarta."*** Ma'ana, za a wayi gari sakamakon yawaitar bayi a tsakanin Larabawa har sai baiwa ta haifi uwargijiyarta; ɗiya ta sawo uwarta daga kasuwa a matsayin baiwarta ba tare da ta sani ba. Wasu

---

[278] Hadisi na (10)1/40.

malamai kuma suka bayar da wata fassarar daban. A taƙaice dai, wannan magana tana nuni ne zuwa ga irin yadda al'amurra za su juya a daidai lokacin da Alƙiyama ta kusanto; maƙasƙanta su ɗaukaka, maɗaukaka su ƙasƙanta.

Daga cikin alamominta: ***"Za ka ga talakawa, marasa talkama, huntaye, masu kiwon awaki suna gasar gina dogayen benaye,"*** suna kuma yi wa juna alfahari da su, bayan a da can kowa ya san matalauta ne. Ma'anar wannan shi ne, za a wayi gari ƙauyawa matalauta, duniya ta buɗe masu ƙofa, suna ta faɗi da liwasa. Malam Ibnu Daƙiƙi Al-Id *Rahimahullah* ya ce: *"Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ambaci wannan rukuni ne kawai saboda ko a ƙauye su ne mafiya rauni."*[279] Abin nufi kuma a nan shi ne za a wayi gari ƙananan mutane sun zama shugabanni, sun samu dukiya mai yawa har suna zuba ta wa ƙasa suna gine-ginen ƙasaita da alfahari. A cikin wani Hadisi Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa: *"Da zarar an wayi gari an jingina al'amari ga waɗanda ba masu shi ba, to, ku saurari tashin ƙiyama."* Buhari ne ya riwaito shi.[280] Ba kuwa don komai ba, sai don irin yadda hakan take yamutsa hazo a tsarin addini da na duniya. Irin waɗannan abubuwa kuwa suna daga cikin yanaye-yanaye na canjawar al'amurra a ƙarshen zamani.

Sai Umar ɗan Khaɗɗabi *Radhiiyallahu Anhu*: ***"Ya ce: Sai kawai,"*** mai tambayar ya: ***"Ya tafiyar sa. Sai muka ci gaba da zama,"*** tare da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ɗan ƙanƙanin lokaci. Sai, ya ce,"*** bayan baƙon nasa ya shuɗe: ***"Ya Umar!, shin ka san wannan mai tambaya kuwa?"*** wanda muka dinga musayar tambayoyi da amsoshin nan tare da shi kuna saurare. Ko ka san ko waye shi? ***"Sai na ce: Sani na wurin Allah da Manzonsa."*** Saboda mutumin baƙo ne a gare mu; babu wanda ya san shi daga cikin mu. Ba mu taɓa sa shi a ido ba kafin wannan rana. Irin wannan amsa da Umar *Radhiiyallahu Anhu ya bayar,* ta ƙunshi tsabar ladabi. Idan aka tambaye ka abin da baka sani ba, ka mayar da sani a wurin ma'abucinsa. Kada ka yi ƙarfin halin kutsa kai cikin abin da baka sani ba. Abin kuma da ka sani, kada ka ji shayin bayar da amsa a kan sa. Idan kuma baka sani ba, baka kuma san wani wanda ya sani ba,

---

[279] Sharhin Arba'unan na Nawawi na Ibnu DaƙiƙAl-Id shafi na 44.

[280] Hadisi na (59) 1/ daga Hadisin Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

to, sai ka ce: Allah shi ne masani. Idan kuma a lokacin rayuwar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ne, to, ya halasta ka ce: Allah da Manzonsa ke da sani. Saboda wahayin da yake sauka gare shi *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* Amma bayan fakuwar sa, idan aka tambayi mutum a kan abin da bai sani ba. To, kada ya wuce cewa: Allah ne mafi sani. Daga nan: ***"Sai,"*** Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya ce,"*** mai: ***"Wannan,"*** tambaya, Mala'ika: ***"Jibrilu ne,"*** mafi girma daga cikin Mala'iku: ***"Ya zo,"*** a cikin sifar mutane: ***"Domin ya sanar da ku,"*** al'amurran: ***"Addininku;"*** manya da ƙanana ta hanyar tambaya da amsa.

Ka ga a haka Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya bayyana wa duniya cewa, abin da wannan Hadisi ya ƙunsa, shi ne ginshiƙin addini. Saboda ya yi magana a kan asalin addini da aƙidunsa. Kai! gaba ɗayan ilimin Shari'ah ma an tattara shi a cikin wannan Hadisi; babu ɗaya daga ciki, da ba nan ne tushensa ba. Haka aƙidar *ahlus-Sunna wal Jama'ah*, nan ne tushe da makomarta. Girma kuma da ɗaukakar wannan Hadisi abu ne da kan gaba ɗayan malaman wannan al'umma ya haɗu a kai. Malam Ibnu Daƙiƙ Al-Id *Rahimahullah* yana cewa: *"Abin da malamai magabata da majinkirta suka tafi a kai, shi ne, duk wanda ya yi imani da abubuwan da wannan Hadisi ya ƙunsa, imani na gaskiya, irin wanda babu kokwanto ko wata gada-gada a cikinsa, to, ya gama zama mumini. Daɗa kuwa yana iya kare hakan da hujjoji da dalilai ko ba ya iyawa.*[281]

Alƙali Iyadh kuma *Rahimahullah* yana cewa game da Hadisin: *"Wannan Hadisi ya ƙunshi gaba ɗayan ayyukan ibada na zahiri da na baɗini; farko da tsakiya da kuma ƙarshe. Ya kuma haɗa da ayyukan gaɓɓai, da tsarkin zuciya da na ruhi, da kuma kaffa-kaffa game da miyagun ayyuka. Kai! a haka dai har gaba ɗayan ilimukkan shari'a, duk wannan Hadisi ne mafari da kuma makomarsu."*[282]

[281] Sharhin Al-arba'una Hadis na Ibn Daƙiƙ Al-Id, shafi na 42.
[282] *Fath Al-Bari* 1/125.

## SHISHSHIKE NA UKU: MU SAN MANZONALLAH
*Sallallahu Alaihi wa Sallam*

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:*

*"Shishshike na uku kuma shi ne: Mu san Annabinmu Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam. Shi ne Muhammadu ɗan Abdullahi, ɗan Abdulmuɗɗalabi, ɗan Hashimu. Shi kuwa Hashimu daga Kuraishu yake, kakan Larabawa. Larabawa kuma daga tsatson Annabi Isma'ila ɗan Ibrahimu Badaɗayin Allah suka fito, alaihima wa ala nabiyyina afdalussalati was salam. Shekarunsa a duniya sittin da uku ne. Daga cikinsu ya yi arba'in kafin annabta, ashirin da uku kuma bayan samun annabta da manzanci da ya yi. An ba shi annabta ne a ranar da aka saukar masa da "Iƙra'a,". Manzanci kuma a ranar da aka saukar masa Suratul muddassir." Garinsu shi ne Makka, daga can kuma ya yi hijira zuwa Madina. Allah ya aiko shi da gargaɗi a bar Shirka, ya kuma yi kira zuwa ga Tauhidi".*

*"Shishshike na uku kuma,"* daga cikin shika-shikan addini guda uku, waɗanda saninsu yake wajaba a kan kowane musulmi: *"Shi ne: Mu san Annabinmu Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam."* Wannan shishshike ne mai matuƙar girma da ɗaukaka, wanda sanin sa yake wajaba. Malam Ibn Al-Kayyin *Rahimahullah* na cewa: *"Bayin Allah ba su da wata lalura wadda ta kai masu neman sanin labarin Annabinsu Muhammadu, da abin da ya zo da shi, da gaskata shi a cikin duk labaran da ya bayar, da kuma yi masa ɗa'a a cikin duk umurnin da ya bayar."*[283] Wannan kuwa saboda matsayin da yake da shi na jekada tsakanin mu da Allah Maɗaukakin Sarki. Babu kuma wata hanya, wadda za mu san abin da zai tserar da mu daga fushin Allah da azabarsa, ya kuma kusantar da mu zuwa ga yarda da amincewa da kuma lada irin nasa, sai ta

[283] *Zad Al-Ma'ad* 1/69.

hanyar abin da Annabin nan Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya zo mana da shi.

Shaihkul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Bukatar da zukata suke da ita zuwa ga sanin abin da Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam da mabiyansa suka zo da shi, ta fi bukatar da suke da ita zuwa ga abin ci da abin sha. Domin waɗannan abubuwa babu abin da rashin su zai haifai baya ga rasa rayuwa a nan duniya. Wancan kuwa rashinsa yana haifar da azaba ne da ranar jin daɗi a gobe ƙiyama."*[284]

Malam Junaidu *Rahimahullah* shi kuma yana cewa: *"Babu wani mahaluki da yake da wata hanya wadda ba a rufe ba, face wanda ya yi koyi da gurabun Manzo Sallallahu Alaihi wa Sallam."*[285] Hasali ma dai babu yadda za a yi wannan duniya ta yi daɗin zama matuƙar babu sanadarin annabta a cikin sararinta.

Shaihul-Islami *Rahimahullah* yana cewa: *"Manzanci lalura ce, wadda ba yadda za a yi rayuwar bayi ta inganta sai da shi. Bukatar da suke da ita zuwa gare shi, ta fi wadda suke da ita zuwa ga komai. Manzanci shi ne rayuwar halittu, shi ne kuma hasken rayuwa."*[286] Saboda haka Manzanni da Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko, ya aiko su ne domin su zama rahama ga mutane. Tabbacin wannan shi ne faɗarsa *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Kuma ba mu aika ka ba face domin rahama ga mutane."* Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullah* yana cewa: *"Rahamar Allah ce, Mabuwayi mai jinƙayi, da ya aiko Manzanni domin su bayyana wa duniya ko waye shi. Su kuma yi kira zuwa ga addininsa. Su zama masu bushara ga wanda ya karɓa kiransu. Masu gargaɗi ga wanda ya saɓa musu. Ya kuma sanya mabuɗin wannan da'awah tasu, da haƙiƙanin manzancinsu, shi ne saninsa Subhanahu wa Ta'ala a matsayin abin bauta, ta hanyar sunaye da sifofi da ayyukansa, saboda a kan waɗannan fannona ne aka ɗora harsashen gaba ɗayan manufofin da Manzanci yake ƙunshe da su."*[287]

---

[284] *Al-Fatawa*1/5.
[285] *Al-Faƙih wa Al-Mutafaƙƙih,* na Khaɗibul- Bagadadi 1/389.
[286] *Al-Fatawa, (*19/93).
[287] *As-Sawa'iƙ Al-Mursalah,* (1/150).

Tunda kuwa haka al'amarin yake, kenan mun fahimci ta inda sanin ko waye Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya zama ɗaya daga cikin shikashikan addini, waɗanda sanin su a kanmu yake wajaba. Ko banza ba yadda za a yi mu iya sanin ko waye Ubangijinmu idan aka bar mu da tunaninmu. Ba kuma za mu iya sanin abin da asali na biyu ya ƙunsa ba, wato Musulunci, sai ta hanyar wani jakada, tsakanin mu da Allah Maɗaukakin Sarki.

Malam Ibn Al-Kayyim yana cewa: *"Tunda dai har ta tabbata babu yadda za a yi bawa ya samu tsira a duniya da Lahira, sai ta hanyar karantarwar Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam. To, ashe kenan ya zama wajibi a kan duk wanda yake son kansa da alhairi, da tsira da tagomashi, ya yi ƙoƙarin sanin wani abu daga cikin tarihin rayuwar wannan Manzo, gwargwadon abin da zai fitar da shi daga cikin sahun waɗanda ba su san komai ba game da shi. Da haka sai a wayi gari ya samu kansa a cikin jerin mabiya, masoya kuma dakarunsa. Mutane a wannan fage kuwa kashi uku ne. Wasu sun yi nisa a tafiyar, wasu kuma kadaran kadahan, a yayin da wasu ko bisimilla ba su yi ba. Amma dai ita falala a hannun Allah take yana kuma bayar da ita ne ga wanda ya so. Tabbas, Allah mai buwayayyar falala ne.'*[288]

Shi kuwa sanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ƙunshi abubuwa masu yawa. Daga cikin su akwai sanin suna, da nasaba, da shekaru, da kuma daidai lokacin da aka aiko shi. Da sanin abin da annabta da manzancin nasa suka ƙunsa. Da garinsa, da hijirarsa, da lokacin cikawar sa. To, abu mafi girma daga cikin gaba ɗayan waɗannan abubuwa shi ne sanin takamaiman abin da Allah ya aiko shi da shi. Da dai sauran abubuwan da wannan mawallafi da waninsa suka ambata.

**Sunan Manzon Allah:**

Shi dai Annabinmu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, sunansa: ***"Muhammadu."*** Ma'anar wannan suna ita ce, mutum abin gode ma, da yabawa, fiye da waninsa. Yana kuma da wasu sunaye da dama, amma, wannan shi ne mafi shahara da girma da ɗaukaka daga cikin su. Shi ya sa Alƙur'ani mai girma ya zo ɗauke da shi a cikin faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Kuma*

[288] *Zad Al-Ma'ad fi Hady Khair Al-Ibad,* 1/69.

*Muhammadu bai zamo uban ɗaya daga cikin mazajenku ba."* da kuma faɗarsa: *"Kuma Muhammadu bai zama ba face Manzo."* Da kuma wata faɗar tasa Maɗaukakin Sarki in da yake cewa: *"Muhammadu Manzon Allah ne."* Alkunyarsa kuma ita ce, Baban Kasim.

Sunan mahaifinsa kuwa shi ne: ***"Abdullahi."*** Manzon Allah bai same shi a raye ba; ya rasu a zamanin jahiliyya. An samo Hadisi daga Anas *Radhiyallahu Anhu,* cewa: *"Wani mutum ya ce wa Manzon Allah: Ina mahaifina yake? Sai ya karɓa masa da cewa yana wuta. Bayan da ya juya sai ya kira shi, ya ce masa: Haƙiƙa mahaifina da naka suna Wuta."* Muslim ne ya riwaito shi.[289] Kakansa kuma shi ne: ***"Abdulmuɗɗalabi".*** Amma cikakken sunansa shi ne Shaibatu, ana kuma ce masa Shaibatul-Hamdi saboda karimcinsa, da irin yadda Kuraishawa suka amince da zaman sa shugaba a gare su. Amma, laƙabin Abdulmuɗɗalabi, ana yi masa shi ne sakamakon tahowar da baffansa Muɗɗalabi ya yi da shi a garin Makka, wanda sakamakon nauyin tafiya launin fatar jikinsa ta canja. Sai mutanen Makka a wannan lokaci suka zaci ko bawansa ne ya taka masa baya. Sai suka riƙa cewa wannan bawan Muɗɗalab ne. Sai kuwa wannan suna ya bi shi. Mahaifin Abdulmuɗɗalab, shi ne: ***"Hashimu."*** Amma, cikakken sunansa shi ne, Amru. Ana ce masa Hashim ne saboda irin yadda yake taimaka wa mutanensa da gurasa da nama a duk lokacin da aka yi wata yunwa. ***"Shi kuwa Hashimu,"*** ɗin nan: ***"Daga,"*** ƙabilar ***"Kuraishu yake,"*** ƙabila mafi girma da ɗaukaka da shahara daga cikin ƙabilun Larabawa. ***"Kuraishawa dangin Larabawa ne."*** Su kuma: ***"Daga,"*** cikin: ***"Zuri'ar Annabi Isma'ila ɗan Ibrahimu Badaɗayin Allah,"*** kakan Annabawa: ***"Suke, alaihima wa ala nabiyyina,"*** Muhammad: ***"Afdalussalati was salam.***

Yadda al'amarin ya kasance kuwa shi ne, Annabi Ibrahimu *Alaihis Salam*, bayan da tsufa ya kama shi, sai Allah ya azurta shi da samun ɗa, wanda ya raɗa ma suna Isma'ilu, wanda aka fi sani da laƙabin *azzabihu,* wanda kuma ya rayu a hannun Larabawa. Bayansa kuma sai Allah ya ba shi Ishaƙa. To, daga

[289] *Sahih Muslim,* Hadisi na (521) 1/132. Mawallafin ya kawo hadisin a haka ba tare da ya yi nuni ga matsayin malamai da zantukansu a kan sa ba. Don neman ƙarin haske sai a tuntuɓi sharhohan malamai, musamman kuma Sharhin Imam Nawawi ga *Sahihu Muslim.* Daga Masu Fassara.

tsatson Isma'ila ne aka samu Annabinmu Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Shi kuwa Ishaƙa daga tsatsonsa ne sauran Annabawa suka fito. Allah *Ta'ala* yana cewa: *"Kuma mun sanya, annabta da littafi a cikin zuri'arsa."* Bisa wannan dalili ne aka ambaci Annabi Ibrahimu *Alaihis Salam* kakan Annabawa. Domin gaba ɗayan Annabawan da aka yi a bayansa jikokinsa ne, ko dai daga gidan Isma'ila, wato, Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, ko na Ishaƙa, wato, gaba ɗayan sauran Annabawa. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa: *"Haƙiƙa Allah ya zaɓi Kinanata daga cikin 'ya'yan Isma'ila. Ya kuma zaɓi Kuraishu daga cikin dangin Kinanata. Daga cikin Kuraishu kuma ya zaɓi Banu Hashim. Daga cikin Banu Hashim ne ya zaɓe ni."* Muslim ne ya riwaito shi.[290]

Ka ga kenan, Annabinmu shi ne mafi girman gaba ɗayan mutane ta fuskar asuli da daraja, saboda Bahashime ne kuma Baƙuraishe. Haka Allah Maɗaukakin Sarki ya saba. Yana tayar da Annabawa ne daga cikin mafi girman mutanensu daraja da tsarkin asuli.*

A daidai kuma tsakiyar watannin da mahaifiyar Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* take ɗauke da cikinsa, sai mahaifinsa ya rasu. Shi kuma aka haife shi a cikin shekarar giwaye, ranar Litinin. A kuma cikin irin wannan rana ce ta Litinin, wahayi ya fara sauka gare shi *Sallallahu Alaihi wa Sallam. Kazalika,* a cikin irinta ne aka yi Isra'i da Mi'iraji da shi zuwa sama. A cikin ta ne kuma ya yi hijira zuwa birnin Madina. Haka kuma a cikin ta ne ya yi wafati; ya koma ga mahaliccinsa. Shi da kansa *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa: *"Wannan ita ce ranar da aka haife ni a ciki, aka kuma saukar mani da wahayi a ciki."* Muslim ne ya riwaito.[291] Sai dai yana da kau a sani, ba ya halasta a girka taron Mauludi saboda bukin tunawa da haifuwarsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, saboda bai yi haka ba a lokacin rayuwarsa. Wani kuma daga

---

[290] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (2276) 4/1782 daga Hadisin Wasilatu ɗan Asƙa'u *Radhiyallahu Anhu.*
[291] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (1162) 2/819.

cikin sahabbansa, tattare da kasancewar sa mafi soyuwar mutane a wurinsu, bai yi haka ba.[292]

Sakamakon haifuwar sa maraya da aka yi, *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, sai kakansa Abdulmuɗɗalabi ya ɗauki nauyin renonsa. Bayan cikawarsa, Annabi ya bar gidansa, ya koma hannun baffansa Abu Ɗalib. Sa'annan kuma ya auri Sayyida Khadija yana ɗan shekaru ashirin da biyar. Ita ce mahaifiyar kusan gaba ɗayan 'ya'yansa *Sallallahu Alaihi wa Sallam* idan ka cire Ibrahimu, wanda kuyangarsa Mariya, 'yar asalin ƙasar Masar ta Haifa masa. Kafin a aiko shi a matsayin Manzo, *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, ya shahara da sunan *Al'amin* saboda tsabar gaskiyar sa da amincewar da mutane suka yi masa.

***"Shekarunsa kuma,"*** na rayuwa a gidan duniya: ***"Sittin da uku ne,"*** idan aka haɗa hancin gaba ɗayan shekarunsa daga haihuwa zuwa mutuwa. ***"Daga cikinsu,"*** ya kwashe shekaru: ***"Arba'in kafin annabta;"*** domin ba a fara yi masa wahayi ba, sai da shekarunsa suka kai arba'in. Wannan adadi na shekaru kuwa shi ne lokacin da mutum yake kai wa ma'isar waɗa, ya samu

292 Tarihi ya nuna cewa, Sarkunan Shi'a Baɗiniyya da aka yi a ƙasar Masar a cikin ƙarni na huɗu su ne suka fara bikin Maulidi. Mauludi shida suke yi a lokacinsu a kowace shekara. Na farko, Mauludin Annabi, sai Mauludin Sayyidi Ali, sai na Hasan da Husaini da Fatima, sannan na Sarki mai ci a wannan zamani. Su ne sarakunan da suka hana musulmi sallar Tarawihi, suka wajabta zagin Sayyidi Abubakar da Umar da uwar Muminai Sayyida A'isha da rubuta shi a cikin Masallatai. Su ne kuma suka je Makka suka yi ma alhazai kisan kiyashi suka zuba gawawwakinsu a cikin rijiyar Zamzam, suka cire *Hajrul Aswad* suka gudu da shi. Malaman Musulunci sun haɗu a kan kafircin waɗannan sarakuna da masu bin aƙidarsu kamar yadda Imam Dhahabi ya hikaito. Sauran duniyar Musulmi ba ta fara koyi da su a cikin bikin Mauludi ba sai bayan sama da shekaru ɗari biyu; a ƙarshen ƙarni na shida zuwa farkon ƙarni na Bakwai in da wasu sarakuna da suka haɗa da na Arbil da Sabta suka bi sawunsu. Daga bisani sarakunan Makka su ma suka fara yi, har ma suna buɗe Ka'aba a ranar Maulidi kuma suna ba da hutu kamar yadda 'yan Shi'ar suke yi. Daga baya an yi wasu sarakuna da suka hana, wasu kuma su zo su sake sabuntawa. Sha'anin Mauludi ya ƙara girma bayan da Sufaye suka fara yi ma waliyyansu. Adadin mahalarta bikin Mauludin wasu waliyyai a yanzu a wasu ƙasashe ya zarce yawan adadin masu zuwa aikin Hajji. Duba *Al-Khuɗaɗ Al-Maƙriziyya,* na Maƙrizi, da *HusnAl-Maƙsid fi Amal Al-Maulid,* na Jalaluddin As-Suyuɗi, da *Ahsan Al-Kalam fi ma Yata'allaƙ bi Al-Bid'at min Al-Ahkam,* na Sheikh Muhammad Bakhit Al-Muɗi'i, da *Subh Al-A'sha,* na Kalƙashandi da *Tarikh Al-Ihtifal bi Al-Maulid An-Nabawi,* na Hasan As-Sandubi. Daga Masu Fassara.

cikakken hankali. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Har idan ya kai ma'isar waɗa, ya kai shekaru arba'in."* Sauran shekaru: ***"Ashirin da uku kuma,"*** ya yi su ne: ***"Yana Annabi,"*** ana yi masa wahayi: ***"Kuma Manzo,"*** wanda ake ba wa umurni domin ya isar wa mutane.

A tsawon shekaru ashirin da uku, da ya kwashe yana Manzo, *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi goma sha uku a garin Makka. A birnin Madina kuma cibiyar annabta, ya yi goma. Waɗannan shekaru nasa, Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya musu albarka matuƙa. A cikinsu ne Musulunci ya ga sarari, Shari'arsa kuma ta shafe gaɓa; mutane suka yi ta shiga addini giye-giye. A tsawon wannan lokaci Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya haɗu da matsaloli, da suka haɗa da yunwa da fargaba da sauran jarabawoyi iri-iri na rayuwa. Maƙiya sun saka shi a gaba, suka bi shi har Madina domin su yaƙe shi. Amma, ya yi haƙuri, ya ci gaba da ƙoƙari, har Allah ya gwada masa ya isar da saƙon Ubangijinsa.

Tarihi ya tabbatar da cewa: ***"An ba shi annabta,"*** ne *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ta hanyar,"*** saukar masa da wahayi a ranar Litinin a cikin watan Ramadhan a kogon "Hira", da farkon Surar: ***"Iƙra'a,"*** in da aka karanta masa cewar Allah: *"Ka yi karatu da sunan Ubangijinka. Wanda ya halicci mutum daga ɗigon maniyyi. Ka yi karatu da sunan Ubangijinka mafi girma. Wanda ya sanar ta hanyar alƙalami. Ya sanar da mutum abin da bai sani ba."* Daga nan ya dawo gida hankalinsa a tashe, jikinsa yana ɓari, yana jin tsoron ko iskoka ne suka shafe shi. Sai matarsa; uwarmu Khadija ta shiga lallashinsa tana cewa masa: *"Ina! Wallahi Ubangijinka ba zai taɓa tozartar da kai ba, har abada."* Tana mai tunatar da shi irin halaye da ɗabi'un kirkinsa. Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[293]

***"Manzanci kuma,"*** ya sadu da shi ne *Sallallahu Alaihi wa Sallam* daga wurin Allah *Subhanahu wa Ta'ala*, bayan wani ɗan lokaci, da saukar wahayi: ***"Ta hanyar Suratul Muddassir."*** Yadda abin ya faru kuwa shi ne, a lokacin da Mala'ika ya kai masa ziyarar ba zata, sai hakan ta tayar masa da hankali *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Da ya koma gida ya dinga faɗin *"dassirúní;"* ku

[293] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (4670) 4/1894.

lulluɓe ni. A nan sai Allah ya saukar masa da wannan Sura yana cewa a farkonta: *"Ya kai wanda ya lulluɓa da mayafi."* Wannan sura ita ce farkon abin da aka saukar masa bayan an fara saukar masa da wahayi. Daga nan kuma sai wahayi ya ci gaba da sauka babu ƙyaƙƙyaftawa. Shi kuma a nasa ɓangare, sai ya saka wandon ƙarfe ya shiga kira zuwa ga addinin Allah.

***"Garinsu kuma shi ne Makka,"*** mafi girman wurare a duniya baki ɗaya, a wurin Allah. A nan ne aka haife shi, ya kuma girma. Sai fa ɗan zaman da ya yi a hannun Halimatus-Sa'adiyya uwar renonsa a ƙauye. Bayan hakanan kuma aka dawo da shi Makka a ƙarƙashin kulawar kakansa, sa'annan kawunsa ya karɓa. A wannan gari ne kuma na Makka aka fara saukar masa da wahayi. Ya kuma ci gaba da kasancewa a cikin ta ko bayan haka, har tsawon shekaru goma sha uku.

Bayan haka ne: ***"Ya yi hijira zuwa Madina,"*** sakamakon kashe shi da aka yi azama, inda ya ɓuya a cikin kogon "Hira". Daga nan suka wuce shi da Sayyidi Abubakar zuwa Madina. Daman dai mutanen Madina sun yi masa bai'a a kan taimako da ba shi goyon baya. Daga wannan hijirar ce ta Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, wannan al'umma take fara lissafin tarihinta.*

Mawallafin wannan littafi *Rahimallahu* ya ambaci duk abin ya kamata a sani dangane da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Mafi girma daga cikinsu da ɗaukaka shi ne, sanin abin da aka aiko shi da shi. Yadda abin yake kuwa shi ne: ***"Allah,"*** Maɗaukakin Sarki: ***"Ya aiko shi da gargaɗi a bar Shirka,"*** ta hanyar tsoratarwa daga mummunan sakamakon da yake tattare da ita a duniya da lahira. Aikin duk wanda yake Shirka, ba ya da wata albarka. Karshe kuma yana dauwama a gidan Wuta. Allah ya kuma aiko shi domin: ***"Ya yi kira zuwa ga Tauhidi,"*** ta hanyar kaɗaita Allah da bauta.

Mawallafin ya gabatar da gargaɗi game da Shirka da kira zuwa ga Tauhidi, saboda kawar da Shirka shi ne share fagen Tauhidi da gyara masa wurin zama. Sai kuma batun ayoyin da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa Manzonsa a cikin su: *"Ka tashi ka yi gargaɗi. Ka kuma girmama Ubangijinka."* Ita dai ibada daman ba ta inganta matuƙar akwai abin da yake ban hannun makaho da ita. Tabbacin haka shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Duk*

*wanda ya kafirce ma ɗagutu ya kuma yi imani da Allah. Tabbas haƙiƙa, ya yi riƙo da igiya mai ƙwari wadda ba ta tsinkewa."* Da kuma faɗar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da yake cewa: *"Duk wanda ya ce: La'ilaha illallah, ya kuma kafirce ma duk abin da ake bauta wa, wanda ba shi ba. To, jini da dukiyarsa sun haramta. Hisabinsa kuma yana wurin Allah Maɗaukakin Sarki."* Muslim ne ya riwaito shi.[294] Bayan haka sai mawallafin ya ambaci Tauhidi a mataki na biyu, saboda babu wani wajibi da ya kai ƙarfinsa. Wani aiki kuma duk, ba zai samu karɓuwa a wurin Allah Maɗaukakin Sarki ba, sai idan an buga masa hatimin Tauhidi. Ita kuwa Shirka, duk aikin da ta yi ma ƙawanya, nan take za ta ƙazanta shi, ta lalata shi. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"Kuma tabbas, an yi wahayi zuwa gare ka, da kuma zuwa ga waɗanda suke a gabaninka. Lalle ne idan ka yi wa Allah kishiya, haƙiƙa aikinka zai ɓaci, kuma lalle ne za ka kasance daga cikin masu hasara."*

[294] *Sahih Muslim*, Hadisi na (23) 1/53 daga Hadisin Abu Malik daga mahaifinsa *Radhiyallahu Anhu.*

MANUFAR KIRAN MANZON ALLAH

*Sallallahu Alaihi Wa Sallam*

***Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:***

***"Dalili kuma akan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ya wanda ya lulluɓe da mayafi! Ka tashi domin ka yi gargaɗi. Kuma Ubangijinka, sai ka girmama shi. Kuma tufafinka, sai ka tsarkake su. Kuma gumaka, sai ka ƙaurace musu. Kada ka yi kyauta kana neman ƙari. Kuma saboda Ubangijinka, sai ka yi haƙuri.***

***Ma'anar kuma: "Ka tashi ka yi gargaɗi," ita ce Manzo ya tsawaci mutane daga yi wa Allah kishiya, ya kuma kira su zuwa ga Tauhidi. "Kuma Ubangijinka sai ka girmama shi," ta hanyar kaɗaitawa. "Kuma tufafinka, sai ka tsarkake su." Yana nufin ayyukan Manzo, ya tsaarkake su daga Shirka. "Kuma gumaka, sai ka ƙaurace musu," ta hanyar ƙauracewa da yi musu tawaye, su da ma'abuta su.***

***"Dalili kuma a kan haka;"*** cewa Allah ya aiko Annabinsa Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* domin ya yi gargaɗi a kan Shirka, ya kuma yi kira zuwa ga Tauhidi: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ya wanda ya lulluɓe da mayafi!"*** domin ya tsira daga fargaban da ya same shi sakamakon haɗuwa da Mala'ika bai san shi ne ba, a lokacin saukar wahayi zuwa gare shi. ***"Ka tashi;"*** ka watsar da wannan lulluɓi: ***"Domin ka yi gargaɗi,"*** ga mutane su bar yi wa Allah kishiya. Ka kira su zuwa ga Tauhidi. Wannan ita ce aya ta farko da aka aiko Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da ita. Ita ce kuma umurni na farko da ya keta fatun kunnuwansa bayan an tabbatar masa da zama Manzo. Yadda abin ya faru kuwa shi ne a daidai lokacin da ya yi kiciɓis da Jibirilu, sa'adda ya saukar masa da *"Iƙra'a"* sai tsoro ya kama shi. Daga nan sai ya garzaya zuwa gida inda ya taras da iyalinsa yana cewa, *"dassirúní"* "ku lulluɓe ni." Sai Allah ya saukar masa da cewa: *"Ya wanda ya lulluɓe da mayafi."* A nan kuma sai lasisin zamansa Manzo ya ƙara bunƙasa da bubuta bayan ya kafu da saukar masa da *"Iƙra'a"* da aka yi.

Cewar kuma da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya yi: ***"Kuma Ubangijinka, sai ka girmama shi,"*** yana nufin Manzo ya tsarkake shi daga abin da *Mushrikai*, masu bautar gumaka suke jinginawa gare shi. ***"Kuma tufafinka, sai ka tsarkake su,"*** yana nufin zuciyar Manzo, ya tsarkake ta daga zunubai. Ya yi mata kinaya ne da tufafi, *Subhanahu wa Ta'ala*, saboda ita ma sutura ce ga lamirin mutum. ***"Kuma gumaka, sai ka ƙaurace musu,"*** ko kusantar su kada ka yi! Kalimar *"rujza"* wadda muka fassara da gumaka, tana nufin ƙazanta ne. Da ita da kalimar *"rijsu"* ma'anarsu ɗaya. Kamar inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: *"Sai ku kuma nisanci ƙazanta daga gumaka."*

Ya ci gaba da cewa: ***"Kada ka yi kyauta kana neman ƙari."*** Wato, kada ka bayar da dukiyarka cikin siga ta dabara kana neman a mayar maka da fiye da ita. Ko kuma, a'a, kada ka yi wa Allah gori a kan aikin alhairin da kake yi. Ko kuma, kada wani aiki naka ya riƙa cika maka fuska. Ko kuma kada ka yi ƙasa a guiwa daga aikata alheri. Duk ayar tana ɗaukar waɗannan ma'anoni. ***"Kuma saboda Ubangijinka, sai ka yi haƙuri"*** a kan yin biyayya ga umurninsa, ko a kan cutarwar da aka yi maka saboda shi.*

***"Ma'anar,"*** cewa: ***"Kuma: "Ka tashi,"*** yana nufin ne tashi ka zabura cikin kuzari da karsashi: ***"Ka yi gargaɗi,"*** ka kuma yi: ***"Tsawaci,"*** ga: ***"Mutane daga yi wa Allah kishiya,"*** ta hanyar amfani da kalmomi da ayyuka irin waɗanda za su taimaka ga biyan wannan bukata. Yin haka wajibi ne saboda Shirka ita ce mafi girman zunubi, wanda aka saɓa wa Allah Maɗaukakin Sarki ta hanyar sa. An tambayi Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cewa, wane kalar zunubi ne mafi girma? Sai ya karɓa da cewa, shi ne: *"Ka yi wa Allah kishiya alhali shi ya halicce ka."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[295] Ba kuma wani aiki da zai samu karɓuwa a wurin Allah *Subhanahu wa Ta'ala* matuƙar ana tare da Shirka. Ga abin da Buwayayyen Sarki yake cewa game da haka: *"Kuma lalle haƙiƙa an yi wahayi zuwa gare ka, da kuma zuwa ga waɗanda suke a gabaninka. Lalle idan ka yi Shirka, wallahi aikinka zai ɓaci, kuma wallahi za ka zama daga cikin masu hasara."* Ma'abuci Shirka kuma zai tabbata

[295] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (4207) 4/1626., da *Sahih Muslim,* Hadisi na (86) 1/90 daga Hadisin Ibn Mas'ud *Radhiyallahu Anhu.*

ne a cikin Wuta. Allah Ta'ala yana cewa: *"Yadda al'amarin yake, duk wanda ya yi wa Allah kishiya, haƙiƙa Allah ya haramta masa Aljanna, makomarsa ita ce Wuta."*

Bayan kuma wannan gargaɗi daga Shirka, an umurce shi da ***"Ya kira su zuwa ga Tauhidi,"*** saboda Tauhidi shi ne wajibi mafi ƙarfi daga cikin wajibai. Shi ne kuma abin da gaba ɗayan Manzanni suka rayu a kai tun daga farkon wa'azinsu har ƙarshensa. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Kuma tabbas, mun aika Manzo a cikin kowace al'umma, yana mai cewa, ku bauta wa Allah, ku kuma nisanci Ɗagutu."* Saboda haka sai Manzo *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya zare damtse ya shiga yaƙin fahimtar da mutane. Sakamakon haka, shi da mabiyansa suka haɗu da tsananin cutarwa.

***"Kuma Ubangijinka sai ka girmama shi."*** Ma'anar wannan umurni shi ne ka girmama Allah: ***"Ta hanyar kaɗaita shi,"*** a matsayinsa na Ubangijin gaskiya, wanda ya cancanci bauta shi kaɗai, ba tare da abokin tarayya ba. Saboda haka ka ɗaukaka alkadarinsa tare da kiyaye wannan matsayi nasa na Makaɗaici. Manufarka kuma ya kai Manzo a cikin wannan kira naka, ta zamo, sa mutane su girmama Ubangijinsu ta hanyar tsare alfarmar ibadarsa. Saboda babu wani abu da za a yi a girmama shi, a matsayinsa na Ubangiji, wanda ya kai ga Tauhidi. Abu na biyu kuma shi ne tsarkake shi daga abin da masu bautar gumaka suke jinginawa gare shi.

***"Kuma tufafinka, sai ka tsarkake su."*** ***Yana nufin ayyukanka, ka tsarkake su daga Shirka."*** Ka kuma sadaukar da su domin neman yardar Allah. A harshen Alƙur'ani, ayyuka, akan saya su a kira su tufafi. Kamar yadda yake a faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Kuma tufafin taƙawa, wancan shi ne alheri."* Yana nufin ayyukan tsoron Allah. Tsarkake tufafi kamar yadda aka saba a al'ada, ba shi ne haƙiƙanin abin da ake nufi a cikin wannan aya ba, saboda a wannan lokaci ba a riga ma an wajabta sallah ba. Abin dai da ake nufi a nan shi ne ayyuka. A kaikaice ana umurnin Manzo ne da ya tsarkake zuciyarsa daga ayyukan zunubi, waɗanda mafi girma daga cikinsu shi ne Shirka. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimallahu* yana cewa: *"Wannan fashin baƙi da aka yi ma wannan aya, a kansa zaƙaƙuran malamai daga cikin baraden fashin baƙin*

*alƙur'ani, suke. Kuma wannan fassara ita ce mafi ingancin zantuka."* [296] Wasu malamai kuma suka ce, ma'anar ita ce: *"Ka gyara aikinka kada wani ɓurɓushin Shirka ya cuɗanya da shi."*

***"Kuma gumaka, sai ka ƙaurace musu."*** Kalimar *"rijzu"* tana nufin: ***"Gumaka,"*** da sauran abubuwan da ake bauta koma bayan Allah.

Abin kuma da ake nufi da: ***"Kaurace wa,"*** gumaka da nisantarsu, shi ne: ***"Yi musu tawaye, su da ma'abuta su."*** Allah Maɗaukakin Sarki ya umarci Manzo ne *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da ƙaurace wa gumaka tare da nisantar su, da kuma yi musu tawaye, su da duk wanda yake da wata alaƙa da su. Wannan kuwa shi ne tafarkin gaba ɗayan Annabawa da Manzanni. Allah Ta'ala yana cewa ta harshen Annabi Ibrahimu *Alaihis Salam*: *"Ina kuma ƙaurace muku da abin da kuke bauta koma bayan Allah."* A wata ayar kuma ya ce: *"Haƙiƙa kuna da abin koyi daga Ibrahimu da waɗanda suke tare da shi, a lokacin da suka ce wa mutanensu: Haƙiƙa mu masu tawaye ne gare ku da abin da kuke bauta wa koma bayan Allah."* Wannan al'umma kuwa an umurce ta da koyi da Annabi Ibrahimu *Alaihis Salam* da waɗanda suka rufa masa baya a cikin yi wa *Mushrikai* tawaye.*

[296] *Madarij As-Salikin* 2/20.

## TAUHIDI YANA GABA DA SALLA

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:*

*"Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ɗauki tsawon shekaru goma a kan wannan aiki; kiran mutane zuwa ga Tauhidi. Bayan haka ne aka gayyace shi zuwa sama, inda ya ziyarci fadar Ubangiji kuma aka farlanta masa salloli biyar, shi da al'ummarsa. Ya kuma kwashe shekaru uku bayan haka yana salla a Makka. Sannan aka umurce shi da yin hijira zuwa Madina. Ita Hijira tana nufin ne tashi daga garin Shirka zuwa garin Musulunci. Hijira farilla ce a kan wannan al'umma daga garin Shirka zuwa garin Musulunci. Wajabcin hijira ba ya gushewa har Alƙiyama ta tsaya. Dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle ne, waɗanda Mala'iku suka karɓi rayukansu, suna masu zaluntar kansu, sun ce: a cikin me kuka kasance? Suka ce: Mun kasance waɗanda aka raunana a cikin ƙasa. Suka ce: Ashe ƙasar Allah ba ta kasance mayalwaciya ba, domin ku yi hijira a cikinta? To, waɗannan makomarsu Jahannama ce. Kuma ta munana ta zama makoma. Face waɗanda aka raunana daga cikin maza da mata da yara waɗanda ba su iya yin wata dabara, kuma ba su shiryuwa ga wata hanya.To, waɗannan akwai tsammanin Allah ya yafe laifi daga gare su, kuma Allah ya kasance mai yafewa ne, mai mai gafara." Da kuma faɗarsa: "Ya bayina, waɗanda suka yi imani! Lalle fa ƙasata mai yalwa ce, saboda haka ku bauta mini ni kaɗai."*

Ta kuma tabbata cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ***"Ya ɗauki tsawon shekaru goma a kan wannan aiki,"*** na bayanin matsayin Shirka da haɗarinta; gargaɗi da tsoratarwa a kan ta, da kuma bayanin Tauhidi da kira zuwa gare shi. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai gushe ba yana: ***"Kiran mutane zuwa ga Tauhidi,"*** da ja musu kunne game da Shirka tun ba a farlanta

sallah ba, wadda ita ce ginshiƙin addini. Haka kuma sauran shari'o'i duk ba a farlanta su ba.

Da wannan kuma mai karatu zai fahimci cewa, tantagaryar abin da aka aiko Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da shi, gaba ɗayan Manzanni kuma suka yi kira zuwa gare shi, shi ne gargaɗi da tsoratarwa game da Shirka, a hannu ɗaya kuma da kira zuwa ga Tauhidi da bayani dalla-dalla a kansa. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Kuma babu wani Manzo da muka aika a gabaninka, face mun yi wahayi zuwa gare shi, cewa, lalle, babu wanda ya cancanci bauta sai ni. Sai ku bauta mini."* A wata ayar Allah *Ta'ala* ya ce: *"Kuma haƙiƙa mun aika Manzo a cikin kowace al'umma, cewa: Ku bauta ma Allah ku kuma nisanci ɗagutu."* A waɗansu ayoyin kuma Buwayayyen Sarki ya bayar da labarin irin yadda Annabawa: Nuhu da Hudu da Salihu da Shuaibi *Alaihimussalam,* farkon abin da kowane ɗaya daga cikinsu yake ce wa mutanensa, shi ne: *"Ya ku mutanena! Ku bauta wa Allah. Ba ku da wani Ubangiji bayan shi."* Haka shi ma shugaban Annabawa, Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, farkon abin da ya gaya wa nasa mutane shi ne: *"Ku ce la'ilaha illalh, sai ku sami babban rabo."* Ahmad ne ya riwaito shi.[297]

Tabbas, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, babu abin da aka aiko shi da shi baya ga Tauhidi da tabbatar da ganin dashensa ya kama ƙasa. Hakan kuma ta kasance ne saboda matsayin da yake da shi na zama tushen wannan addini, wanda aka gina shi a kai. Ashe kenan da zarar an rasa Tauhidi, to, duk wani abu aikin banza ne. Eh! Ko shakka babu Tauhidi shi ne asali, sauran kuma Shari'o'in addini rassa ne gare shi. Da zarar kuwa aka nemi asali aka rasa, ai maganar reshe ta ƙare. Kuma shekaru goma da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kwashe yana kira zuwa ga Tauhidi tare da gargaɗi a kan Shirka, kafin daga bisani a wajabta masa sauran farilloli. Hakan ta nuna cewa, babu wani wajibi da ya kai girman Tauhidi. Koƙarin sanin sa kuma shi ne mafi girman farillai.

Sa'annan: *"**Bayan,**"* waɗannan shekaru: *"**Goma,**"* da farawar annabta da manzanci, duk Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana zaune a garin

[297] *Al-Musnad,* (16066) 3/492 daga Hadisin Rabi'ata ɗan Ubada Ad-Dailami.

Makka, sai: *"Aka gayyace shi zuwa sama,"* ta bakwai. Daga masallacin Baitul-Harami ne aka cirata da shi gaba ɗaya; ruhinsa da gangar jikinsa a kan wani abin hawa da ake kira Buraƙa.[298] Ba a zame da shi ko'ina ba sai Masallacin Baitul-Muƙaddas. An kuma yi wannan tafiya da shi ne yana farke; ba a mafarki ba. Wannan shi ne abin da ya tabbata a cikin Alƙur'ani mai girma. Allah Ta'ala yana cewa: *"Tsarki ya tabbata ga wanda ya yi tafiyar dare da bawansa zuwa Masallaci mafi nisa, wanda muka yi albarka a gefensa."* Bayan haka sai Jibrilu *Alaihis Salam* ya tashi tare da shi. Wannan tafiya ta biyu bayan sun ya da zango, ita ake kira *"mi'iraji."* Daga nan babu samar da za su kai face Mala'ikun da suke cikinta sun tarbe su irin tarbo na ban girma. Haka dai har suka isa wurin da ake ce ma *sidratul-muntaha.* A nan ne Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ji amon alƙaluma, masu rubuta ƙaddarorin Ubangiji. Daga nan kuma ya ci gaba da yi sama-sama irin yadda Allah ne kawai ya san miƙidarin hakan. A ƙarshen tafiya ne suka yi zance da Allah ba tare da wani shamaki ba; ya yi masa wahayin abin da ya ga dama.

Wannan sarari na samaniya, shi ne: *"Inda aka farlanta masa salloli biyar."* Amma, a farkon al'amari salloli hamsin ne aka wajabta. Daga nan Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya shiga safa da marwa tsakanin Ubangiji da Annabi Musa *Alaihis Salam* har aka samu Allah ya mayar da su sallah biyar. Amma kuma ya bayar da tabbaci yana mai cewa: *"Tabbas an mayar da su biyar a adadi, amma, a lada suna nan hamsin, wato, kowace ɗaya tana da ladar goma."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[299] Bayan haka sai aka saukar da shi a Baitul-Muƙaddas, aka kuma saukar da sauran Annabawa tare da shi, inda ya limance su salla a cikin wannan masallaci. Sa'annan ya sake hawan wannan Buraƙa ta mayar da shi birnin Makka duk a cikin dare guda. A nan ne ya

[298] Buraƙa wata dabba ce da girmanta bai kai na alfadari ba, ta kuma ɗara jaki. Wannan suna nata kuma an tsago shi ne daga kalmar *albarƙu* ta Larabci, wadda take nufin walƙiya. An kuma raɗa mata wannan suna ne saboda la'akari da tsananin hasken launinta. Wasu malamai kuma suka ce, a'a, saboda dai tsananin sauri da kazar-kazar ɗin da take da si ne. *Lisan Al-Arab,* na Ibn Manzhur 10/15.

[299] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (342) 1/136, daga Hadisin Abi Zarrin *Radhiyallahu Anhu,* da *Sahih Muslim,* Hadisi na (162) 1/145-147, daga Hadisin Anas ɗan Maliku *Radhiyallahu Anhu.*

labarta wa mutane abin da ya gani a cikin wannan tafiya. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya kuma kwashe shekaru uku yana salla a Makka"*** bayan dawowar sa.

***"Bayan haka ne,"*** wato, shekaru goma sha uku bayan tabbatar masa da zama Manzo: ***"Aka umurce shi da yin hijira,"*** daga garin Makka: ***"Zuwa Madina."*** Domin hakan ta ba shi damar ƙaurace wa *Mushrikai* da wuraren zamansu, ta yadda zai samu sararin tallata addini da kira zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki. Yin haka ya zama wajibi kuma farilla, saboda mutanen Makka sun kafa masa ƙahon zuƙa; ba za su bari ya yaɗa addini ba. Sai ga shi a birnin Madina, Ansaru sun yi masa gagarumar tariya; suka karɓe shi hannu bi-biyu, suka taimake shi, har ya samu damar yaɗa addinin Ubangijinsa; ya yaɗu ya game sasannin duniya.*

***"Ita,"*** kuwa: ***"Hijira tana nufin tashi daga garin Shirka zuwa garin Musulunci."*** Bisa wannan fashin baƙi duk wanda ya tashi daga garinsu ya koma wani da wannan manufa, to, ana lissafa shi cikin sahun masu hijira. Hijira a asalinta tana nufin tankiya da jan layi, da raba gari da wani. Dagan an ne Muhajiruna suka samu nasu suna, saboda tashi da barin garinsu da suka yi, saboda Allah. Suka koma wani garin, wanda ba su da kowa, ba su da wata dukiya a ciki a daidai lokacin.

Hijira ibada ce, wadda aka Shar'anta saboda addinin mutum ya samu kariya daga gushewa da nakkasa. Haka kuma tana taimakawa ga tsere wa fitina. Idan kuma an yi haka tsoron da ake da shi na rashin bayyanar Musulunci sai ya kau. Shaihul-Islami *Rahimallahu* yana cewa: *"Ba yadda za a yi mutum ya tsira daga sharrin Mushrikai sai idan ya raba jaha da su."*[300]

Tabbataccen abu ne kuma, cewa, babu yadda za a yi mutum ya kasa tasirantuwa da al'ummar da yake rayuwa a cikin ta, ta fuskar zama na gari, tsoron Allah, ko kuma nisantar Ubangijinsa da yin saɓo. Saboda haka ne: ***"Hijira,"*** ta zama: ***"Farilla a kan wannan al'umma,"*** ta Annabi Muhammadu: ***"Daga garin Shirka,"*** da kafirci: ***"Zuwa garin Musulunci."*** Kan malamai ya haɗu a kan cewa Hijira farilla ce. Musamman, la'akari da irin yadda Allah

---

[300] *Al-Fatawa,* 1/94.

Maɗaukakin Sarki ya shar'anta ta ga Manzonsa Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, da Sahabbansa tun kafin ya wajabta musu Azumi da Hajji. Duk kuwa wanda ya ƙi yin Hijira bayan ta wajaba, kuma yana da iko a kan haka, to, Allah ya yi ƙyacin narko a gare shi ranar alƙiyama. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa: *"Ba ruwana da duk wani musulmi da yake zaune a cikin Mushrikai"* Abu Dawuda da Tirmidhi suka riwaito shi.[301]

Cuɗanya da *Mushrikai* da yin hulɗa da su lalura ce a cikin addini. Amma, idan musulmi yana zaune a cikin garin da ba ya iya bayyana addininsa da kira zuwa gare shi. To, ya zama wajibi gare shi ya ƙaurace ma wannan gari domin ya samu inda zai iya bayyana addininsa, ya kuma kare martabar aƙidarsa. Ko shakka babu maƙwabtaka da su da zamantakewa da cuɗanya da su na cutar da addini. Shaikhul-Islami *Rahimallahu* yana cewa: *"Mun ga da yawa daga cikin musulmi waɗanda suka yawaita hulɗa da Yahudawa da Nasara su ne mafiya ƙarancin imani bisa ga wasun su."*[302]

Hijira kuma tana da amfani ga wanda ya yi ta, ta fusakar duniyarsa da lahirarsa. Malam Abdur-Rahman ɗan Hassan, jikan mawallafin wannan littafi *Rahimallahu* yana cewa: *"A mafi yawan lokuta hijira takan haifar wa waɗanda suka yi ta tsira da girma da kwanciyar hankali ne, kamar yadda hakan ta faru ga Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam, da mabiyansa tun can asali. Kai! Irin amfanin da hijira take tattare da shi na duniya fa ba ya misaltuwa."* Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Kuma waɗanda suka yi hijira a cikin sha'anin Allah bayan an zalunce su, haƙiƙa muna zaunar da su a cikin duniya cikin jin daɗi."*[303]

Haka kuma duk wanda ya ƙi yin hijira bayan ta wajaba alhali yana da iko a kan haka, to, zai haɗu da matsaloli a duniyarsa da lahirarsa. Malam Abdur-Rahman ɗan Husaini *Rahimallahu* yana cewa: *"Babu wata matsala wadda ƙin tsayar da Sunnar jihadi ke haifarwa, face ƙin raya Sunnar hijira yana haifar da makamanciyarta, ko ma fiye da ita. Duk masu hankali da basira sun*

---

301 *Sunan Abu-Dawud,* Hadisi na (2645) 4/155 daga Hadisin Jariru ɗan Abdullahi *Radhiyallahu Anhu.*

302 *Iƙtidha' Siraɗ Al-Mustaƙim,* shafi na 220.

303 *Ad-Durar As-Saniyyah* 8/240.

*fahimci haka. Hasali ma jihadi na ɗaya daga cikin abubuwan da hijira take lamuncewa. Ka tuna irin mugun halin da waɗanda suka yi ko oho da Sunnar hijira suka shiga a addini da duniyarsu."*[304] *

Kenan wanda yake da iko a kan yin hijira, da ƙaurace wa ƙasar Shirka, bai kuma yi ta ba. To, haƙiƙa ya zalunci kansa, ya kuma faɗa cikin zunubi.

***" Wajabcin hijira ba ya gushewa har alƙiyama ta tsaya."*** Babu wani lokaci, da a cikinsa za a ce ba wajibi ba ne a tsare alfarmar addini ta hanyar yin hijira. Ko alama. Wannan hukunci yana nan daram har ranar da Allah Maɗaukakin Sarki zai naɗe ƙasa da waɗanda ke cikin ta. A taƙaice, duk wanda yake zaune a ƙasar *Mushrikai*, yana kuma da ikon barin ta. To, hijira zuwa ƙasar musulmi ta wajaba a kansa har abada.

Shaikhul-Islami *Rahimallahu* yana cewa: "*Yanayi da halin garuruwa haka yake kamar yanayi da halin mutane. Mutum na iya zama musulmi, ko kafiri, ko mumini, ko munafuki. Wani lokaci kuma a same shi mai ɗa'a da biyayya ga Allah da kuma jin tsoron sa. Wani lokacin kuma ya zama fasiƙi, ko fajiri, ko shaƙiyyi. To, haka abin yake ko a garuruwa; gwargwadon duk yadda mazaunan wuri suke, haka shi ma yake. Saboda haka yin hijira ga mutum daga ƙasar kafirci da saɓo, zuwa ƙasar imani da bin Allah, daidai yake da tubar da zai yi daga aikin kafirci da saɓo zuwa ga na imani da biyayya. Wannan hukunci kuwa haka zai ci gaba da kasancewa har ranar da Allah zai naɗe ƙasa da halittunta."*[305]

***"Dalili kuma a kan haka;"*** cewa hijira wajibi ce bisa wannan tsari, daga cikin Alƙur'ani: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle ne, waɗanda Mala'iku suka karɓi rayukansu, suna masu zaluntar kansu."*** Tarihi ya tabbatar da cewa wannan aya ta sauka ne a kan wasu mutane daga cikin mazauna garin Makka, waɗanda suka shiga sahun Musulunci, amma suka ƙi yin hijira. To, shi ne Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya ce game da su: ***"Lalle ne, waɗanda Mala'iku suka karɓi rayukansu,"*** yana nufin Mala'ikan mutuwa da mataimakansa. To,

[304] *Ad-Durar As-Saniyyah,* 8/244.
[305] *Al-Fatawa,* 18/284.

matsayin waɗanda aka karɓi rayukan nasu suna cikin halin ƙin yin hijira shi ne, hakan ta faru: ***"Suna masu zaluntar kansu."*** Waɗannan Mala'iku: ***"Sukan ce,"*** musu: ***"A cikin me kuka kasance?"*** A cikin wane rukuni suke kenan, tunda ga shi sun ƙi su yi hijira, sun ci gaba da zama inda suke in da ba su iya aiwatar da addini yadda Allah ya umurta? Wannan tambaya ce irin ta wofintarwa da tabbatar da laifi a kaikaice. Sai waɗanda suka ƙi yin hijirar: ***"Su ce: Mun kasance waɗanda aka raunana a cikin ƙasa."*** Saboda haka ba za mu iya aiwatar da addini ba. Sai Mala'ikun: ***"Su,"*** karɓa musu, da cewa: ***"Ashe ƙasar Allah ba ta kasance mayalwaciya ba, domin ku yi hijira a cikinta?"*** Wannan tambaya ma irin waccan ce da ta gabata. A kaikaice suna gaya musu ne cewa, ai babu wanda bai san irin yadda wannan ƙasa da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya shimfiɗa take mai tsananin yalwa ba. To, me ya hana su yin hijira zuwa birnin Musulunci, su bar ƙasar Shirka? A taƙaice dai wannan hanzari nasu ba zai samu karɓuwa ba.

A duk lokacin da mutum ya samu kansa a wani wuri da ba ya iya bayyana addininsa a cikinsa. To, yana da cikakkar dama ta matsawa a wanin wurin inda zai iya bauta wa Allah ba tare da wata tsangwama ba, tunda ƙasar Allah yawa gare ta. Su kam waɗannan mutane da suka ƙi yin hijira, Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana rashin uzurinsu, da cewa: ***"To, waɗannan makomarsu Jahannama ce. Kuma ta munana ta zama makoma."*** Wannan aya tana nuna cewa, duk wanda hijira ta kama, yana kuma da ikon yin ta, amma ya ƙi. To, tabbas ya aikata babban laifi: ***"Face waɗanda aka raunana,"*** wato masu rauni, waɗanda ba su iya yin hijirar: ***"Daga cikin maza da mata, da yara,"*** waɗanda ba su balaga ba: ***"Waɗanda,"*** kuma: ***"Ba su iya yin wata dabara;"*** ta rabuwa da Mushrikai saboda ba su iya ciyar da kansu, balle ƙarfin halin fita: ***"Kuma ba su shiryuwa ga hanya."*** Wato, ko da sun yi ƙundunbalar yin hijira, ba su san hanyar da za su bi su bar garin Makka zuwa birnin Madina ba, wadda ita ce ƙasar Musulunci. A wannan lokaci kuma babu wani gari na Musulunci ita.

***"To, waɗannan akwai tsammanin Allah ya yafe laifi daga gare su,"*** saboda kasancewarsu masu rauni da uzuri, da suke sa a kasa yin hijira. ***"Kuma***

*Allah ya kasance mai yafewa ne,"* da gafarta laifuka. Kuma: *"Mai gafara,"* da kawar da kai daga masu laifuka a kan uzuri. Malam Ibn Kasir *Rahimallahu* yana cewa: *"Wannan aya mai girman daraja ta sauka ne a kan duk wanda yake zaune a cikin Mushrikai, alhali yana da ikon yin hijira. Yana ji yana kuma gani, amma ya kasa iya tsayar da addininsa da kyau. To, irin wannan mutum, tabbas ya zalunci kansa, tunda ya aikata abin da gaba ɗayan malamai suka yanke masa hukuncin zama haram, kamar yadda wannan aya ta tabbatar."*[306]*

Tunda kuwa har Shari'a ta yi umurni da yin hijira daga garuruwan *Mushrikai*, kenan tafiya ƙasashensu haram ne. Sai kuwa idan akwai wata lalura, wadda take tilasta haka, kamar neman magani da makamantansa. To, ko akwai irin wannan lalura, tafiyar ba ta halasta sai da waɗannan dalilai: Mutum ya zama:

1. Mai cikakken ilimi irin wanda zai hana shi faɗawa a cikin tarkon duk wata shubuha game da addininsa wadda za ta iya taron gabansa.
2. Mai nagartaccen addini, shi ma, da zai kare shi daga afka wa kowane irin rikici da ruɗani ta wannan hauji.
3. Mai iya gudanar da addininsa, da bautar Ubangijinsa kamar yadda Shari'a ta umurta. Ya kuma yi matuƙar kaffa-kaffa daga damƙa gaba ɗayan al'amarinsa a hannun Mushrikan.

Idan kuwa wani dalili ya hana mutum yin hijira. To, lalle ne ya tsare alfarmar ayyuka da alamomin addininsa, waɗanda suka haɗa da kamar Sallah, da makamantanta, gwargwadon iyawarsa. Ya kuma zama wajibi a kansa ya shiga kira da gayyatar waɗanda ba musulmi ba, zuwa ga shiga Musulunci. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Kuma wane ne mafi kyau ga magana daga wanda ya yi kira zuwa ga Allah, kuma ya aikata aiki na ƙwarai, kuma ya ce: Lalle ni, ina daga cikin masu miƙa wuya."*

Wani dalilin kuma daga cikin Alƙur'ani, a kan wajabcin yin hijira ga mai iko a kanta shi ne: *"Fadarsa,"* Maɗaukakin Sarki: *"Ya bayina, waɗanda,"* suka kaɗaita ni: *"Suka,"* kuma: *"Yi imani!"* da ni, da Manzannina, amma kuma suna zaune a ƙasar kafirai; ba su yi hijira ba, alhali kuwa suna da iko a

[306] *Tafsir Al-Kur'an Al'Azim,* na Ibn Kasir, (2/343).

kan haka. To, ku gaggauta yin hijira, domin: *"Lalle fa ƙasata mai yalwa ce,"* ba za ta kasa isar ku ba, balle ku yi zaune a inda ba ya halasta ku zauna. Idan kuma aiki ne mutum yake yi a wuri irin wanda aka yawaita saɓon Allah a cikin sa, ba kuma zai iya hanawa ba, to wajibinsa shi ne ya gaggauta barin wurin zuwa inda yake da sarari da 'yanci ga kowane mahaluki.

Wato, idan mutum ya samu kansa a ƙasar da bai iya bayyana addininsa a cikin ta. To, kada ya manta akwai wani wurin a bayan ƙasar Allah, inda yake iya bauta masa, ya kuma kaɗaita shi kamar yadda ya umurta. Haka duk wanda zama ya kama shi a tsakanin arna waɗanda ba su da aiki sai saɓon Allah. Ba shi kuma da yadda zai iya hana su. To, wajibi ne a kan sa ya yi hijira.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ci gaba da cewa: *"Saboda haka ku bauta mini."* Yana nufin ku bayyana addini ta hanyar bauta mini a cikin waccan ƙasa mai yalwa da kuka yi hijira zuwa gare ta. Na halitta ta ne, da gaba ɗayan abin da yake kanta domin amfaninku. Ku kuma ba domin komai na halicce ku a kan ta ba, sai domin ku bauta mini.

ADDINI YA KAMMALA

*Malam Muhammadu ɗan Abdulwahab ya ci gaba da cewa:*

*"Malam Bagawi Rahimallahu yana cewa: "Wannan aya ta sauka ne a kan musulmin da suke Makka ba su yi hijira ba. Sai Allah ya kira su da sunan imani."*

*Dalili a kan hijira kuma daga cikin Sunna, shi ne faɗar Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam: "Hijira ba za ta yanke ba har sai idan tuba ta yanke. Tuba kuma ba za ta yanke ba har sai rana ta fito daga yamma."*

*A lokacin kuma da Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya zauna sosai a Madina, sai aka umurce shi da sauran Shari'o'in Musulunci, kamar Zakka, da Azumi, da Hajji, kiran sallah, da Jihadi, da horo da alhairi, da hani da abin ƙi, da sauran Shari'o'in Musulunci waɗanda ba waɗannan ba. Ya ɗauki shekaru goma a kan wannan aiki. Bayan su ne Allah ya karɓi rayuwarsa Salatullahi wa Salamuhu Alaihi. Amma, addininsa yana nan. Wannan kuma shi ne addinin nasa. Babu wani alhairi face ya karantar da al'ummarsa shi, babu kuma wani sharri face ya tsoratar da su daga gare shi. Alhairin kuwa da ya karantar da wannan al'umma tasa, shi ne Tauhidi, da duk abin da Allah yake so, ya kuma yarda da shi. Sharrin kuma da ya tsoratar da su daga gare shi, shi ne Shirka, da kuma gaba ɗayan abin da Allah yake ƙi da ƙyama.*

***"Malam Bagawi,"*** Sunansa Muhammadu ɗan Husaini ɗan Mas'ud[307] ***yana cewa,"*** a cikin Tafsirinsa,[308] wanda Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimallahu* yake cewa game da shi: *"Gaba ɗayan wannan al'umma ta amince da Tafsirinsa da kuma karanta shi wa jama'a ba tare da wata gardama ba."* [309] Cewa Malamin ya yi: ***"Wannan aya ta sauka ne,"*** kamar yadda Malam Muƙatil ya

---

[307] Malamin ya rasu a shekara ta 516H.

[308] Sunan Tafsirin nasa shi ne: *Ma'alim At-Tanzil*

[309] *Ijtima' Al-juyush al-Islamiyya,* shafi na 239.

ce: ***"A kan musulmi,"*** masu rauni waɗanda: ***"suke,"*** zaune a: ***"Makka ba su yi hijira ba,"*** zuwa Madina: ***"Sai Allah ya kira su da sunan,"*** masu: ***"Imani."***[310] Hakan kuwa tana nuna cewa, wanda ya ƙi yin hijira, bayan ta wajaba a kansa, bai kafirta ba. Sai dai ya aikata abin da Allah ba ya so; mumini ne shi, amma mai raunin imani. Mai kuma laifi ne, amma bai fita da'irar masu Tauhidi kuma muminai ba.

***"Dalili a kan,"*** cewa: ***"Hijira"*** farilla ce a kan wannan al'umma, babu kuma ranar da wannan wajabci zai yanke har Alƙiyama ta tsaya. Dalili a kan haka: ***"Daga cikin Sunna, shi ne faɗar Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam,"*** a cikin Hadisin da Abu Dawuda ya riwaito daga Sayyidi Mu'awiyya *Radhiyallahu Anhu,* cewa, lalle Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce: *"Hijira ba za ta yanke ba har sai tuba ta yanke. Tuba kuma ba za ta yanke ba har sai rana ta fito daga yamma."*[311]

Cewa: ***"Hijira ba za ta yanke ba,"*** kuma, yana nufin wajabcinta ba zai faɗi ba, daga ƙasar Shirka zuwa ƙasar Musulunci: ***"Har sai idan tuba ta yanke,"*** an wayi gari an rufe ƙofarta. Kenan Hadisin yana cewa ne, lalle, matuƙar ba a rufe ƙofar tuba ba, aka bar karɓarta, to, hijira ma a wannan tsakani wajibi ce. Ita kuwa cewar da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi a wani wurin: *"Babu hijira bayan an ci Makka. Sai dai jihadi da niyya. Idan kuma aka nemi ku fito, to, ku fito."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[312] Abin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake nufi shi ne, babu sauran yin hijira daga Makka zuwa Madina bayan an ci Makka ɗin da yaƙi, tunda daga wannan rana

---

310 Malam Bagawi ya ce a cikin Tafsirinsa 3/472 a wurin faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Ya ku bayina waɗanda suka yi imani! Lalle ƙasata mayalwaciya ce. to, ku bauta mani ni kaɗai."* Ya ce, Malam Muƙatil da Kalabi sun ce: *"Wannan aya ta sauka ne a kan masu rauni daga cikin musulmi mazauna garin Makka. A taƙaice kuma abin da take cewa shi ne: "Idan zama garin Makka ya zamar muku lalura, ta yadda ba ku iya bayyana imaninku. To, sai ku bar ta zuwa birnin Madina. Lalle ƙasata, yana nufin Madina, mayalwaciya ce, kuma amintatta."*

311 *Sunan Abi Dawud* Hadisi na (2479) 3/3.

312 *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (2631) 3/1025. Daga Hadisin ɗan Abbas *Radhiyallahu Anhu.*

ita ma Makkar ta zama ƙasar Musulunci. Waccan hijira da aka yi, an yi umurni da ita ne sakamakon kasancewar garin na kafirci. Tunda kuwa yau an wayi gari ta canza zane, to, komai ya yi; zancen hijira, *wala.*

***"Tuba kuma ba za ta yanke ba har sai rana ta fito daga yamma."*** Da zarar an wayi gari wata rana, rana ta fito daga inda take faɗuwa, to, babu sauran karɓar tuba; an rufe ƙofarta. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: *"Ranar da wani sashe na ayoyin Ubangijinka suke zuwa, imanin wata rayuwa ba zai amfane ta ba, wadda ba ta riga ta yi imani, ko ta aikata alhairi a cikin imaninta ba."* Ka ga wannan aya tana nuna cewa, ana karɓar tubar bayi matuƙar rana ba ta fito daga yamma ba. To, matuƙar kuwa ba a rufe wannan ƙofa ba, to, wajabcin hijira shi ma yana nan.

Saboda haka, ya zama wajibi a kan kowane musulmi ya yi ƙoƙarin gyara kansa, ta hanyar samun abokan zama na ƙwarai. Duk abin kuma da zai karanta, ya tabbata wanda zai amfane shi ne a cikin sha'anin addininsa. Ya kuma nisanci duk abin da zai gurɓata rayuwarsa, ko zama a cikin jama'ar da yanayinta ba ya taimakawa ga aikata alhairi. Duk wata kafa komai ƙanƙantarta, matuƙar za ta ƙawata masa son zuciya da ɓarnace-ɓarnace ne, ko ingiza shi ya aikata saɓo da miyagun laifuka, to, lalle ya guje mata.*

Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya rayu a garin Makka tsawon shekaru goma, yana kira zuwa ga Tauhidi da bayani a kan sa. A hannu ɗaya kuma yana gargaɗi tare da hani game da kishiyarsa wato, Shirka. Kafin daga bisani ya yi hijira zuwa Madina. Hakan kuwa ta kasance ne sakamakon muhimmancin da Tauhidi yake da shi. ***"A lokacin kuma da ya zauna sosai a Madina,"*** bishiyar Tauhidi ta kama ƙasa sosai, mabiyansa kuma suka yawaita matuƙa. Suka kuma ci gaba da gudanar da sallah, ibada wadda aka farlanta masa, tare da jama'arsa shekaru uku kafin hijira. ***"Sai aka umurce shi da sauran Shari'o'in Musulunci,"*** waɗanda Allah ya wajabta wa bayinsa bauta masa ta hanyar su. Mafi yawan shari'o'i ba a wajabta su ba sai a Madina: ***"Kamar Zakka,"*** ta farilla da cikakken bayaninta: ***"Da Azumi,"*** wanda aka wajabta a cikin watan Ramadhan: ***"Da Hajji,"*** zuwa ɗakin Allah mai alfarma, da: ***"Kiran***

***sallah,"*** domin salloli biyar na wajibi: ***"Da Jihadi,"*** saboda Allah: ***"Da horo da alhairi,"*** bisa karantarwar Shari'a da hankali: ***"Da hani ga abin ƙi,"*** bisa karantarwar Shari'a da hankali: ***"Da sauran,"*** hukunce-hukunce da: ***"Shari'o'in Musulunci,"*** kamar Sallar Idi, da ta kisfewar rana, da ta roƙon ruwa.

Ta kuma tabbata, sai da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya ɗauki shekaru goma a kan wannan aiki,"*** na bayani da karantarwa, da kira zuwa ga sauran Shari'o'i. Ana yi kuma ana saukar masa da wasu bayan wasu. Da haka sai Shari'ar Allah ta kammala, adalci da gaskiya suka cika ƙasa. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"A yau na kammala maku addininku, na kuma cika ni'imata a kan ku. Na kuma yarda Musulunci ya zama addini a gare ku."*

***"Bayan su,"*** waɗannan shekaru, da cikar addinin Allah ma'isar ƙarfi ta hannunsa sai: ***"Allah ya karɓi rayuwarsa"*** a cikin shekara ta goma sha uku. A daidai wannan lokaci, babu wani abu, da ya ƙunshi arzikin duniya da lahira, wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai bayyana wa al'umma ba, bayani na ƙin ƙarawa. Abu Zarri *Radhiiyallahu Anhu* yana cewa: *"Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam bai bar ko da tsuntsu, wanda yake shawagi a sama ba, face ya karantar da mu wani ilimi game da shi."* Ahmad ne ya riwaito shi.[313] Sai wani mutum daga cikin *Mushrikai* ya ce wa salmanul-Farisi *Radhiyallahu Anhu: "Kana nufin babu abin da Annabinku bai sanar da ku ba, har da yadda ake bahaya?"*[314] Salmanu ya karɓa masa da cewa: *"Eh! Tabbas ya ya hana mu fuskantar alƙibla idan za mu yi bauli da bahaya, ko mu yi tsarki da hannun dama, ko da ƙasa, da abin da bai kai dutse uku ba, ko najasa, ko ƙashi."* Buhari ne ya riwaito shi.[315]

Manzon Allah kam lalle ya cika, ***"Amma, addininsa yana nan,"*** Allah ya kiyaye shi, yana nan ƙunshe a cikin Alƙur'ani da Sunna, taskace, kiyaye, har

---

[313] *Al-Musnad,* Hadisi na (21399) 5/163.

[314] Duba littafin *An-Nihaya,* na Ibn Al-Asir 2/17. Da *Lisan Al-Arab,* na Ibn Manzhur, 1/64.

[315] Hadisi na (262) 1/223.

ranar Alƙiyama. Duk kuma wanda ya yi riƙo da shi, to, ya wadace shi. Mai tsira da amincin Allah yana cewa: *"Na bar muku waɗansu abubuwa guda biyu, da ba za ku ɓace ba a bayana idan kun yi riƙo da su; Littafin Allah da Sunnata."* Hakim ya riwaito shi a cikin Almustadrak.[316]

***"Wannan kuwa shi ne addinin nasa,"*** wanda ya bar al'ummarsa a kai; Allah ya ɗauki nauyin kiyaye shi. Musulmi kuma da malamai ma'abuta ilimi, sun tsare hidimar addinin, suka gadar da shi ga ɗiya da jikoki. Wani malami daga cikin magabata yana cewa: *"Wannan shi ne abin da muka gada daga Annabinmu Sallallahu Alaihi wa Sallam, mu kuma mun gadar muku. Wannan kuma ita ce wasiyyar Ubangijinmu a gare mu. Ita ce kuma wasiyyarsa gare ku."*[317] Malamai da almajirai majinkirta na wannan al'umma, ba su gushe ba suna biyar sawun magabata da gurabunsu. Ba kuma za su bar wannan tafarki ba har Allah ya naɗe ƙasa. Wannan addini na Musulunci, addini ne mai girman daraja, wanda ya shamakance gaba ɗayan addinai, wanda ya ƙunshi ayyuka masu sauƙi, amma ladarsu sai wanda ya gani.

***"Babu wani alhairi face,"*** Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya karantar da alummarsa shi,"*** ya kuma ɗora su a kan hanyar samun sa. A kan haka ne Allah Maɗaukakin Sarki ya jinjina tare da yaba masa, yana mai cewa: *"Abin da duk yake wahalar ku mai nauyi ne a kan sa. Mai kwaɗayi ne saboda ku."* Kullum ƙoƙarinsa shi ne ya ga kun kama tafarkin gaskiya wanda ya ƙunshi ayyuka da maganganu da kuma ɗabi'un ƙwarai. ***"Babu kuma wani sharri,"*** na magana ko aiki: ***"Face ya tsoratar da su daga gare shi."*** Ya kuma yi haka ne *Sallallahu Alaihi wa Sallam* saboda irin yadda yake tsoratar wa wannan al'umma tasa faɗawa a cikin halaka. Da wannan kuma babu abin da bai isar ba na addini, ta hanyar bayyana shi tsaf, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya umurce shi, a cikin faɗarsa: *"Ya kai Manzo ka isar da abin da aka saukar zuwa gare ka daga Ubangijinka. Idan kuma ba ka aikata ba to, ba ka isar da saƙonsa ba."* A cikin wani Hadisi Manzo *Sallallahu Alaihi wa*

[316] *Al-Mustadrak,* na Hakim, Hadisi na (262) 172.
[317] *I'lam Al-Muwaƙƙi'in,* na Ibn Al-Kayyim 1/6.

*Sallam* da kansa yana faɗa cewa: *"Babu wani Annabi da aka yi a gabanina face ya zama wajibi a kansa ya sanar da al'ummarsa duk abin alhairin da ya sani, ya kuma yi musu gargaɗi a kan duk wani sharri da ya sani."* Buhari ne ya riwaito shi.[318]

***"Alhairin kuwa da,"*** Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: ***"Ya karantar da wannan al'umma tasa, shi ne Tauhidi,"*** a matsayinsa na tushen kowane irin alhairi, wato, kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki da bauta, wanda shi ne mafi girman wajibai, kuma babu wani aiki da zai sami karɓuwa a wurin Allah *Subhanahu wa Ta'ala* sai da shi. Saboda haka ne, babu wani Manzo wanda ba saƙon Tauhidi aka aiko shi isarwa ba. babu kuma wani littafi na addini da aka saukar, wanda ba wannan saƙo ne yake ƙunshe da shi ba.

Haka kuma Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya karantar: ***"Da,"*** mu: ***"Dukan abin da Allah yake so, ya kuma yarda da shi,"*** na zance da aiki, na baɗini da na zahiri. Babu kuma irin cutarwar da bai haɗu da ita ba, kafin ya isar da wannan saƙo zuwa gare mu, amma ya yi haƙuri har haƙarsa ta cim ma ruwa. Ya kuma yi haka ne saboda cika umurnin Allah Maɗaukakin Sarki da kuma jinƙayi da tausayawa a gare mu. ***"Sharrin kuma da ya tsoratar da su daga gare shi, shi ne Shirka."*** Shirka kuwa babu wani sharri da ya kama ƙafarta, saboda ita ce mafi girman zunubai a wurin Allah. Da zarar ta shiga cikin aiki, to, ta rusa shi kenan. Mai shi kuma zai tabbata ne a gidan Wuta. Saboda haka ne babu wani Annabi ko Manzo, da bai yi wa al'ummarsa hannunka mai sanda game da Shirka ba. A hannu ɗaya kuma ya ba su goron gayyata zuwa ga Tauhidi da kaɗaita Allah *Subhanahu wa Ta'ala*. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Kuma lalle ne, haƙiƙa, mun aika wani Manzo a cikin kowace al'umma, da cewa, ku bauta ma Allah, ku nisanci ɗagutu."* Haka: ***"Kuma,"*** Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya faɗakar da mu: ***"Gaba ɗayan abin da Allah yake ƙi da ƙyama,"*** na aiki da magana.*

[318] *Sahih Muslim,* Hadisi na (1844) 3/1427.

## KIRAN MANZON ALLAH GAMAMME NE

***Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:***

***"Allah ya aiki Annabi Muhamadu ne zuwa ga mutane baki ɗaya, ya kuma wajabta yi masa ɗa'a a kan manya-manyan halittu guda biyu; mutane da aljannu. Dalili a kan haka kuma shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ka ce: Ya ku mutane! Lalle ne, ni Manzon Allah ne zuwa gare ku baki ɗaya." Haka kuma Allah ya rufe ƙofar addini da shi. Dalili a kan haka kuma shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "A yau na cika addininku gare ku, na kuma cika ni'imata a kanku, na kuma yarda Musulunci ya zama addini gare ku." Dalili kuma a kan mutuwarsa Sallallahu Alaihi wa Sallam shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle kai mai mutuwa ne, kuma su ma lalle masu mutuwa ne. Sa'annan lalle ku, a Ranar alƙiyama, a wurin Ubangijinku za ku yi ta yin husuma."***

Akan aiko Annabawa ne, a tarihin Musulunci, zuwa ga mutanensu kawai. Amma: ***"Allah,"*** Maɗaukakin Sarki: ***"Ya aiki Annabi Muhamadu ne zuwa ga mutane baki ɗaya;"*** Larabawa da Bobayi, maza da mata, 'ya'ya da bayinsu. Sa'annan: ***"Ya kuma wajabta yi masa ɗa'a, a kan manya-manyan halittu guda biyu,"*** da suka haɗa da: ***"Mutane da aljannu."*** Tabbacin haka shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Kuma ba mu aika ka ba face zuwa ga mutane baki ɗaya, kana mai yin bushara mai kuma gargaɗi.."* Ta ɓangaren Aljannu kuma ga abin da suke cewa: *"Ya ku mutanenmu! Ku karɓa wa mai kira na Allah, ku kuma yi imani da shi, sai ya gafarta muku zunubanku, ya kuma tserar da ku daga azaba mai raɗaɗi."* Wannan yana tabbatar da cewa, Mazancin Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yah aɗe mutane da aljannu.

***"Dalili a kan haka kuma;"*** cewa, Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, an aiko shi ne ga mutane baki ɗaya: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Ka ce: Ya ku mutane!"*** Larabawa da Bobayi, Ahlul-

Kitabi da waɗanda ba su ba: *"Lalle ne, ni Manzon Allah ne zuwa gare ku baki ɗaya."* Saboda haka ya zama wajibi a kan ku ku yi mani ɗa'a. Karin ƙarfin wannan magana shi ne faɗar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: *"Annabawa, a kan aiko su ne zuwa ga mutanensu kawai. Amma ni, an aiko ni ne zuwa ga mutane baki ɗaya."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[319] Kasancewar Annabi Muhammadu, cikamakin tsarin Annabawa, saƙonsa kuma zuwa ga gaba ɗayan mutane yake, hakan na nuna girma da ɗaukakar darajarsa.

Saboda haka ya zama wajibi a kan mabiya gaba ɗayan sauran addinai, Yahudawa da Nasara da Majusawa, da waɗanda ba su ba, biyar addinin Annabinmu Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Wannan wani hukunci da, duniyar Musulunci ta sani bisa lalura. Shi ne kuma manufar aiko shi da aka yi ga gaba ɗayan mutane. Duk kuwa wanda ya ƙi bin wannan addini nasa, to, ya yanke wa kansa hukuncin zama cikin marasa arziki; zama cikin Wuta. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"Wanda kuma ya kafirta da shi daga cikin ƙungiyoyi, to, Wuta ce makomarsa."* Shi kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce: *"Ina rantsuwa da wanda rayuwar Muhammadu take hannunsa, babu wanda zai ji labarina daga cikin wannan al'umma, Bayahude, ko Banasare, sa'annan ya mutu ba tare da ya yi imani da abin da aka aiko ni da shi ba, face ya kasance daga cikin 'yan Wuta."* Muslim ne ya riwaito shi.[320] Bisa wannan dalili, duk wanda ya yi ɗa'a ga umurnin Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, to, lalle Allah zai yi masa rahama, ya kuma saka shi cikin waɗanda zai yi wa ni'ima. Tabbacin hakan kuma shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Kuma ku yi ɗa'a ga Allah da kuma Manzo, tsammanin za ku sami rahama."* Duk kuma wanda ya yi ɗa'a ga wani addini wanda ba nashi ba, to, ya yi ta bakin banza. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Duk kuma wanda ya bi wanin addinin Musulunci, to, ba za a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi, a ranar Lahira, yana daga cikin masu hasara."**

---

319 *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (328) 1/128, da *Sahih Muslim* Hadisi na (521) 1/370, daga Hadisin Jabiru ɗan Abdullahi *Radhiyallahu Anhu.*

320 *Sahih Muslim* Hadisi na (153)1/134, daga Hadisin Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

*"Haka kuma Allah ya rufe ƙofar addini da shi"* Babu wani Annabi da za a sake aikowa da wasu hukunce-hukunce da shari'o'i. A cikin yardar Allah Maɗaukakin Sarki da iyawarsa, wannan addinin na Musulunci, ya zama addini kammalalle. Babu wata tawaya a cikinsa ta kowace fuska. Saboda haka duk nahiyar da ka duba a cikinsa, za ka ga naso da gurabun cika da kamala da kowane irin alhairi. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai bar duniya ba sai da ya zazzage gaba ɗayan saƙon da Allah ya aiko shi da shi.

*"Dalili a kan haka kuma,"* wato, kasancewar shari'o'i da hukunce-hukuncen wannan addini kammalallu: *"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "A yau,"* yana nufin ranar Arafa, daidai lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake tsaye yana huɗuba a Hajjinsa na bankwana, kwana tamanin da ɗaya kafin ya kwanta dama:[321] *"Na cika addininku gare ku."* Ko shakka babu kuwa wannan babbar ni'ima ce, wadda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi ga wannan al'umma; aka wayi gari ba su da bukata da wani addini, ko wani Annabi, Annabi Muhammadu da Musulunci. Tabbacin wannan kuwa shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala* a wata ayar: *"Kuma kalimar Ubangijinka ta cika, tana mai gaskiya da adalci."* Babu wani labari da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya bayar, wanda ba gaskiya ba. *Kazalika,* babu wani horo ko wani hani, da zai tuzgo daga wurinsa, wanda ba cike yake da adalci ba. *"Wani mai iya canza kalmominsa kuma, babu shi."* Duk wanda ya ce, addinin Musulunci yana da bukata da wata gyaran fuska, to, ƙaryarsa ta sha ƙarya. A haka kuma ya

---

[321] Wannan lissafi yana daidai da na malaman da suke cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kwanta dama ne ranar biyu ga watan *Rabi' Al-Auwal.* Waɗannan malamai kuwa su ne Sulaimanu At-Taimi, da Al-Kalbi, da Khalifa ɗan Khayyaɗ, da wasunsu. Malam Suhaili kuma ya rinjayar da wannan magana tasu. Sai dai Ibnu Hajar ya faɗa a cikin littafinsa *Fath Al-Bari,* (8/130) cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya cika ne a ranar ɗaya ga watan *Rabi' Al-Auwal.* Wannan zance kuwa ba na kowa ba ne, illa Laith, da Ibnu Shihab, da Al-Fadhlu ɗan Dukain, da wasunsu. Wannan magana kuma ita ce abar dogara. A wani zancen kuma, cewa aka yi, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya cika ne a ranar sha biyu ga watan na *Rabi' Al-Auwal.* Wannan zance kuwa, na ɗan Ishaƙa ne, da Waƙidi, da Abubakar ɗan Hazam, da wasunsu. Malam Ibn Kasir kuma, a cikin littafinsa, *Al-Bidaya wa An-Nihaya* ya ƙara da cewa: *"Wannan shahararrar magana ce."*.

ƙaryata wannan aya, ya kuma ƙaryata faɗar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cewa: *"Ina yi muku kashedi da fararrun al'amurra. Saboda babu wani abu da aka ƙirƙira a cikin addini, wanda ba sunansa bidi'a ba. Ita kuwa bidi'a, kowace iri ce, sunanta ɓata."* Abu Dawuda ya riwaito shi.[322] Ka kuwa san duk abin da ya samu shedar cika da kamala, to, babu yadda za a yi wani abu, ya samu shiga cikin sa, ko ya fita. Balle daɗa zancen canzawa. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimallahu* yana cewa: *"Tabbas Allah Maɗaukakin Sarki ya cika kwarin addininsa, da aiko Annabi Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam. Saboda shi, ko al'ummarsa, a bayan rayuwarsa, ba wanda yake da bukata da wani hankali ko wani naƙali, ko ra'ayi, ko mafarki, ko kashfi. Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ishe mu."*[323]

Bayan kuma da Allah Maɗaukakin Sarki ya bayar da labarin cewa, ya kammala ma wannan al'umma addininta. Ni'ima wadda babu irinta. Sai kuma ya nanata tare da bayyana cewa: ***"Na kuma cika ni'imata a kan ku;"*** ta zahiri da ta baɗini. Shi kuwa ko ba a faɗi ba, duk wanda aka cika wa mizanin ni'ima, to, ya samu babban rabo. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimallahu* yana cewa: *"Ka kalli irin yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana zaɓaɓɓen addininsa na Musulunci da cewa, gulbi ne wanda ba shi da gefe a fagen cika da kamala. Ka kalli wannan magana da idon basira, da irin cikakkar ni'imar da Allah Subhanahu wa Ta'ala ya zuba wa bayinsa. Za ka fahimci cewa, wannan magana, ishara ce, da take tabbatar da irin yadda babu tawaya ko wani aibi a cikin wannan addini. Hasali ma dai, idan ana zancen cika da kamala da kyawo da nagarta da ɗaukaka, to, babu kamar sa. Sifaita wannan ni'ima kuma da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi da zama cikakka, ita ma ishara ce, zuwa ga dauwama da kuma ci gabanta ba tare da yankewa ba. Cewa kuma, babu wanda ya isa ya raba su da ita bayan Buwayayyen Sarkin ya tabbatar musu da*

---

[322] *Sunan Abi Dawud,* Hadisi na (4607) 4/200 daga Irbadu ɗan Sariya *Radhiyallahu Anhu.*

[323] *As-Sawa'iƙ Al-Mursalah* 3/826

*samuwar ta. A maimakon haka ma, za su ƙare rayuwarsu gaba ɗaya a cikin wannan gida na duniya, cikin ta. Su tashi kuma ranar ƙiyama a haka."*[324]

Cewa kuma da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* ya yi: ***"Na kuma yarda Musulunci ya zama addini gare ku."*** Yana kira ne ga sauran ɗaiɗaikun wannan a'umma, su ma su yarda da wannan addinin ya zama addini a wurin su. Ba kuwa don komai ba, sai domin irin yadda shi kansa Maɗaukakin Sarki yake ƙaunar wannan addinin, ya kuma yarda da shi. Ya kuma aiko mafi girma da ɗaukaka daga cikin Manzanninsa da shi. Littafin da yake ƙunshe da shi kuma, ya zama mafi daraja daga cikin littattafansa. Ka'abu *Rahimallahu* yana cewa: *"In da wata al'umma aka saukar wa wannan aya, ba ta Muhammadu ba, da sun ɗauki ranar saukarta a matsayin ranar buki."*[325] Sayyidi Umar *Radhiiyallahu Anhu* yana cewa: *"Ai wannan aya ta sauka ne ranar juma'a, kuma ranar Arfa."* Buhari ne ya riwaito shi.[326]

Saboda cika da kamalar wannan addini ne, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya bayar da labarin cewa: Duk wanda ya aikata abin da ba a umurce shi da shi ba, wato, ya ƙara wani abu a cikin addinin Allah, wanda Shari'a ba ta zo da shi ba an mayar masa da abinsa; wannan addini ba shi da bukata da shi. Wannan ma'ana tana ƙunshe ne a cikin faɗarsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: *"Duk wanda ya ƙirƙira wani abu a cikin wannan al'amari namu, wanda ba ya a cikinsa, to, an bar shi da abin sa."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[327]

Saboda haka babu abin da ya kamata musulmi ya yi, illa farin ciki da samuwar wannan addini, ya kuma riƙe shi hannu bi-biyu. Addini ne wanda ba shi da gefe, gaba ɗayan ma'abota waɗansu addinai, za su yi guri, a daidai

---

[324] *Miftah Dar As-Sa'adah* 1/315.

[325] Mu kam ba za mu yi haka ba, saboda haramun ne a ƙirƙiri wata rana ta buki a cikin Musulunci saɓanin ranar idin Azumi da na layya. Wannan shi ne dalilin da ya hana al'ummar Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ɗaukar wannan rana, ranar buki a addinance.

[326] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (6840) 6/2653.

[327] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (2550) 959, da *Sahih Muslim* Hadisi na (1718) 3/1343 daga Hadisin Aisha *raliyallahu anha.*

lokacin mutuwarsu, da bayan sun ga abubuwan tashin hankali irin na ranar Lahira, su zama ɗaya daga cikin mabiyan shi. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"Da yawa waɗanda suka kafirta suke gurin da dai sun kasance musulmi."* Sai dai Allah Maɗaukakin Sarki bai nufe su da shiriya ba, saboda wata hikima tasa *Subhanahu wa Ta'ala*. Don haka ya ce: *Sai Allah ya ɓatar da wanda ya so. Ya kuma shiryar da wanda ya so. Shi mabuwayi ne, mai hikima."**

Bayan haka kuma, Allah Maɗaukakin Sarki, ya sifaita da rayuwa ta har abada. Tabbacin wannan shi ne faɗarsa Maɗaukakin Sarki: *"Allah, babu abin bauta wa bisa cancanta sai shi; rayayyen Sarki, matabbaci."* Shi kuwa Annabinmu Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* mutum ne daga cikin mutane. Ɗaya ne kuma daga cikin ababen halitta. Saboda haka, babu wani abu da yake samun ababen halitta, wanda ba ya samun sa. Yakan ji yunwa, ko ya samu damuwa, da rashin lafiya, bale mutuwa. A wannan matsayi nasa kuwa, *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, mu *ahlussunna*, muke barin sa. Babu kuma wani lokaci da za mu tauye masa wannan haƙƙi na 'yan adamtaka. Amma dai, mun yi imani da cewa, mutum ne, wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya fifita shi ta hanyar aiko shi a matsayin Manzo. Amma kuma, tattare da haka, ba ya iya riskar da amfani ko akasinsa ga kansa, ko wani mahaluki wanda ba shi ba, a lokacin rayuwarsa ko bayan cikawarsa. Tarihi kuma ya tabbatar da cewa, Allah Maɗaukakin Sarki, ya karɓi rayuwarsa yana ɗan shekaru sittin da uku, bayan tsawon shekarun da ya ɗauka yana gwagwarmaya da kira zuwa ga tafarkin Allah, da kuma bauta masa. Kari a kan haka kuma ga matsananciyar sadaukarwa da haƙuri. Amma fa ajalinsa bai riske shi ba, sai bayan da ya kammala ginin soron addinin Allah a cikin cikakkiyar sifa da siga da kuma kama. A haka, har shi da kansa *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake cewa: *"Haƙiƙa na bar ku a kan wata kyakkyawar Shari'a, wadda babu bambanci tsakanin darenta da safiya."* Abud-Darda'i ya ce: *"Tabbas, Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam ya yi gaskiya. Wallahi ya bar mu a kan*

*kyakkyawar Shari'a, wadda babu bambanci tsakanin darenta da safiya."* Ibn Majah ne ya riwaito shi.[328]

***"Dalili kuma a kan mutuwarsa Sallallahu Alaihi wa Sallam,"*** daga cikin Alƙur'ani: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle kai,"*** ya kai Manzo! ***"Mai mutuwa ne."*** Ta kuma tabbata Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya rasu. Bayan haka aka yi masa wanka, aka saka masa likkafani, aka yi masa sallah, aka kuma rufe shi a garin Madina, a shekara ta 11H.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ci gaba da cewa: ***"Kuma su ma;"*** gaba ɗayan halitta ***"Lalle masu mutuwa ne,"*** kamar yadda zaka mutu. Kai! babu wata rayuwa da ba za ta ɗanɗani ɗacin mutuwa ba. ***"Sa'annan lalle ku, a Ranar Kiyama,"*** a filin hisabi: ***"A wurin Ubangijinku za ku yi ta yin husuma,"*** a kan abin da kuke jayayya a cikinsa. Shi kuma Buwayayyen Sarkin, sai ya shiga tsakani ta hanyar zartar da hukuncinsa na adalci tare da saka ma kowa da gwargwadon abin da ya aikata. To, ka dai gani. Ita mutuwa yadda za ta ɗauke gaba ɗayan Annabawa, haka za ta ɗauki kowane talaka. Tabbacin hakan kuwa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Kowace rayuwa mai ɗanɗana mutuwa ce."* A wata ayar kuma ya ce: *"Duk abin da ke a kan ta (ƙasa) mai ƙarewa ne. Sai fuskar Ubangiji ta yi saura."**

[328] *Sunan Ibn Majah,* Hadisi na (5) 1/ 4 daga Hadisin Abud-Darda'a *Radhiyallahu Anhu.*

## IMANI DA ALKIYAMA

*Malam Muhammad ɗan Abdulwahabi ya ci gaba da cewa:*

*"Su kuwa mutane, idan sun mutu za a tayar da su. Dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Daga gare ta ne muka halitta ku, kuma a cikin ta muke mayar da ku, kuma daga gare ta muke fitar da ku a wani lokaci na daban." Bayan tayarwar kuma za a yi musu hisabi da sakayya da ayyukansu. Dalili a kan haka kuwa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Domin Allah ya saka ma waɗanda suka munana da abin da suka aikata, ya kuma saka ma waɗanda suka kyautata da kyakkyawa."*

*Duk kuwa wanda ya ƙaryata tashin Alƙiyama, ya kafirta. Dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Waɗanda suka kafirta sun riya cewa ba za a tayar da su ba. Ka ce: Ni ina rantsuwa da Ubangijina. Lalle za a tayar da ku haƙiƙatan, sa'annan kuma lalle za a ba ku labari game da abin da kuka aikata. Kuma wannan mai sauƙi ne ga Allah."*

*"Su kuwa mutane, idan sun mutu za a tayar da su,"* domin a saka ma kowa gwargwadon aikinsa. Sashensu kuma, har da dabbobi, ya nemi haƙƙinsa daga sashe. Imani da cewa za a tayar da matattu, a kuma fito da su daga cikin ƙaburburansu na daga cikin jimillar turakun imani da Ranar Lahira. Tabbatacciyar magana ce cewa, imani da wannan rana ta Lahira ba ya cika, sai idan an ƙudurce cewa, za a tayar da matattu a cikinta. Kai! hasali ma dai, imani da tayar da matattu ɗin nan, shi ne mafi girman rukuni idan ana zancen ranar Lahira. Shi ne kuma abin da mutanen Jahiliyyar Larabawa suke *inkari.*

*"Dalili a kan haka,"* cewa za a tayar da mutane bayan sun mutu: *"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Daga gare ta ne,"* wato ƙasa: *"Muka halitta*

***ku;"*** Ita ce mafarinku, saboda da ita ne aka halicci kakanku Adamu. ***"Kuma a cikinta ne muke mayar da ku,"*** idan kun mutu; a cikinta ne za a rufe ku. ***"Kuma daga gare cikin ta ne muke fitar da ku,"*** ranar da za a tayar da ku, a yi muku hisabi: ***"A wani lokaci na daban."*** Ranar tashin ƙiyama kenan. Wannan aya ta yi daidai da wata irin ta, in da Maɗaukakin Sarki Allah yake cewa: *"… a cikinta ne kuke rayuwa, kuma a cikinta ne kuke mutuwa, daga gareta ne kuma ake fitar da ku."*

Wani: ***"Dalili,"*** kuma a kan cewa Allah Maɗaukakin Sarki zai tayar da mutane bayan mutuwarsu, shi ne: ***"Faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma Allah ya tsirar da ku daga ƙasa, tsirarwa."*** Abin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake nufi da haka shi ne, farkon halitta, wato Annabi Adamu *Alaihis Salam* da gaba ɗayan zuri'arsa, duk daga ƙasa aka halicce su. ***"Sa'annan,"*** kuma Allah Maɗaukakin Sarki: ***"Ya mayar da ku a cikinta,"*** bayan kun kwanta dama. ***"Kuma ya fitar da ku fitarwa,"*** daga cikin ƙaburburanku bayan ya mayar muku da rayukanku a wannan rana ta Alƙiyama, kamar yadda ya ƙagi halittarku tun da farko.

***"Bayan tayarwar kuma,"*** da za ayi wa halitta, ta hanyar fitowa da su daga cikin ƙaburburansu: ***"Za a yi musu hisabi,"*** a kan gaba ɗayan ayyukansu, komai girma komai kuma ƙanƙantarsu. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki a wata ayar: *"Ana labarta wa mutum, a wannan ranar, da abin da ya gabatar, da kuma wanda ya jinkirtar."* Babu wani aiki na ɗan Adamu, wanda ba a rubuce yake ba a cikin littafi. Wannan littafi ne za a hannunta ma kowa nasa a wannan rana. Ga abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa a kan haka: *"Kuma (idan) aka aza littafin ayyuka, sai ka ga masu laifi suna masu jin tsoro daga abin da ke cikinsa, kuma suna cewa: Kaitonmu! Mene ne ga wannan littafi, ba ya barin ƙarami, kuma ba ya barin babba, face ya ƙididdige su. Kuma suka samu abin da suka aikata a halarce. Kuma Ubangijinka ba ya zaluntar kowa."* Ma'aunin kuma da za a auna ayyukan bayi a wannan rana ta Alƙiyama, ma'auni ne lafiyayye, wanda ba ya tauye alƙalumma, ko wani zurmuguɗɗu, balle zalunci. Ga shaidar da Buwayayyen

Sarki ya bayar a kan haka: *"Kuma muna aza ma'aunan adalci a Ranar Kiyama, saboda haka ba a zaluntar rayuwa da komai."*

Bayan kuma wannan hisabi, za a biyo ma gaba ɗayan halitta: ***"Da sakayya da ayyukansu."*** Idan na alhairi ne, su ga alhairi. Idan kuma na sharri ne su ga sharri. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Duk wanda ya aikata alhairi kwantankwacin ƙwayar zarra, zai gan shi. Duk kuma wanda ya aikata sharri kwatankwacin ƙwayar zarra zai gan shi."* A wata ayar kuma Buwayayyen Sarkin ya ce: *"Domin a saka ma kowane mai rai da abin da ya aikata."*

***"Dalili a kan haka kuwa;"*** cewa za a tayar da mutane bayan mutuwarsu, a kuma yi musu hisabi a kan ayyukansu, ***shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Domin Allah ya saka ma waɗanda suka munana,"*** ayyuka; suka yi wa Allah kishiya, da sauran miyagun ayyukan da nauyinsu bai kama ƙafarta ba. Zai saka musu: ***"Da abin da suka aikata."*** Daidai zunubi daidai azaba. ***"Ya kuma saka ma waɗanda suka kyautata,"*** a cikin ibadar Ubangijinsu; ba su haɗa shi da wani a cikinta ba. Suka kuma riƙa takwarorinsu, halitta, da kyau; suna kyautata musu. Babu kuma wani motsi da za su yi babba ko ƙarami, face sun saka Allah Maɗaukakin Sarki gaba, a cikin sa. Irin waɗannan bayi, da sannu Allah zai yi musu tukuici: ***"Da kyakkyawa."*** Ita ce gidan Aljanna. Kai! hasali ma, zai yi musu toliya a kai, ya lamunce masu yin ido huɗu da shi *Subhanahu wa Ta'ala.* A wata ayar Maɗaukakin Sarkin yana cewa: *"Akwai kyakkyawa ga waɗanda suka kyautata, har da ƙari."* Wannan ƙari kuwa, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya fassara shi da shi ne: *"Samun damar yin ido huɗu da Zatin Allah mai girman daraja da ɗaukaka."* Muslim ne ya riwaito shi.[329]

Wata babbar hikima kuma, da take ƙunshe da tayar da mutane bayan sun mutu, da yi musu hisabi, ita ce tabbatar da adalci. In da 'yan' Adam sun san babu wata rana, wadda a cikinta za a saka wa bayi da ayyukansu, lalle, da sashensu sun yawaita zaluntar sashe. Hakan kuma za ta kasance ne ta hanyar

---

[329] *Sahih Muslim,* Hadisi na (181)1/489 daga Hadisin Suhaibu *Radhiyallahu Anhu.*

cinye dukiyoyi. A haka sai a wayi gari rashin tsari da nagarta sun yi yawa a bayan ƙasa. Ai ba komai ne yake hana mutane cin zarafin juna da danne haƙƙoƙansu ba, tare da ɗaure wa ayyukan saɓo gindi, illa tunawa da wannan rana ta hisabi da sakamakon lada ko azaba. Wannan kuma shi ne dalilin da ya sa kafirai, suna kasa ɗaga ƙafa daga kafircinsu, da zalunci. Shi ne kuma abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake ba mu labari cewa: *"Lalle haƙiƙa su, sun kasance ba su ƙaunar hisabi."* *

Matsayin da lamarin tashin Kiyama yake da shi a wurin Allah Maɗaukakin Sarki yana da matuƙar yawa. Ko ba komai ɗaya ne shi daga cikin rukunnan imani. ***"Duk kuma wanda ya ƙaryata tashin Alƙiyama, ya kafirta."*** Tun da ya ƙaryata Allah da Manzonsa da haɗuwar kan Musulmi. ***"Dalili kuma a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Waɗanda suka kafirta,"*** suka kama tafarkin ɓata da gangan: ***"Sun riya,"*** a cikin sigar zato: ***"Cewa ba za a tayar da su ba,"*** balle a yi musu wani hisabi ko sakamako. Saboda haka ne Allah Maɗaukakin Sarki ya yanke musu hukuncin zama kafirai. Ba su kawai ba, duk wanda ya ƙaryata wannan rana, ya bi sahunsu. Hasali ma, wannan mugun aiki shi ne mafi girman laifin da mutanen Jahiliyya suka yi wa Allah Maɗaukakin Sarki. Saboda haka ne, Buwayayyen Sarki ya gaya ma Annabinsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cewa: *"Ya kai Manzo!* ***"Ka ce,"*** ma masu musun tashin Alƙiyama: ***"Lalle ne za a tayar da ku haƙiƙatan."*** Kai! kada ma ka tsaya a gaya musu haka kawai. Ka ma sha musu *billahillazi*, ya kai Muhammadu! Ta hanyar yin amfani da kalmomi kamar haka: ***"Ina rantsuwa da Ubangijina,"*** kuma mahaliccina. *"Babu abin da zai hana a tayar da ku,"* a wannan rana ta Alƙiyama domin yi muku hisabi. ***"Sa'annan kuma lalle za a ba ku labari game da abin da kuka aikata,"*** sa'annan daga bisani a yi muku sakayya.

***"Kuma wannan,"*** aiki na tayar da matattu: ***"Mai sauƙi ne ga Allah;"*** hakan ba za ta gajiyar da shi, ko ta buwaye shi ba. Shi Allah Maɗaukakin Sarki mai iko ne a kan dukkan komai. Tabbacin haka shi ne faɗarsa *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Kuma idan ya hukunta wani al'amari, sai kawai ya ce masa: Kasance. Sai ya yi ta kasancewa.."* Ai, ko ba a gaya maka ba, kai ka san duk wanda ya

ƙaga halitta a farkon farawa, babu abin da zai hana ya iya sake sabunta mata rayuwa a duk lokacin da ya so. A wata ayar, Maɗaukakin Sarkin yana cewa: *"Kuma shi ne wanda ya ƙaga halitta, sa'annan ya sake ta, kuma ta fi sauƙi gare shi."*

Ai, tunda dai a can farkon farawa, babu ɗan Adamu a bayan ƙasa. Allah Maɗaukakin Sarki ya samar da shi ta hanyar halitta Adamu *Alaihis Salam* daga yunɓu. Ya kuma samar da zuri'arsa daga ruwan maniyyi, ƙasƙantacce. Sa'annan ya ƙaddara irin wannan yaɗuwa daga tsatson. To, irin wannan gagara-gasan Mahalicci, sake busa wa irin wannan halitta rayuwa, abu ne da ba zai taɓa buwayar sa ba. Ya kuwa za a yi haka ta kasance, tunda shi ne wanda ya samar da ita a farkon farawa. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce: *"Allah Maɗaukakain Sarki ya ce: Ɗan Adamu ya ƙaryata ni, bai kuwa kamata ya yi haka ba. Ya kuma zage ni, bai kuma kamata ya yi haka ba. Karyata ni da ya yi shi ne cewar da ya yi: Ba zan sabunta halittarsa ba kamar yadda na halicce shi a farkon farawa. Sake tayar da halittar nan kuwa, nauyinsa bai kai kamar samar da ita tun farko a wurina ba. Zagina kuwa da ya yi, shi ne, cewar da ya yi: Ina da ɗa, alhali kuwa ni kaɗai nake; abin nufi da bukata. Ban haifu ba, ba a kuma haife ni ba. Babu kuma wani tamka a gare ni."* Buhari ne ya riwaiato shi.[330]*

[330] Hadisi na (4690) 4/1903 daga Hadisin Abu HUrairata *raliyallahu.*

IMANI DA MANZANNI

***Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:***

***"Kuma Allah ya aiko gaba ɗayan Manzanni domin bushara da gargaɗi. Dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Manzanni ne masu bushara da gargaɗi domin kada mutane su samu wata hujja a kan Allah bayan zuwan Manzannin."***

***Na farkonsu shi ne, Nuhu Alaihis Salam. Na ƙarshensu kuwa shi ne Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam. Dalili a kan kasancewar Nuhu Alaihis Salam farkon Manzanni shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Tabbas fa, mu, mun yi wahayi a gare ka kamar yadda muka yi wahayi ga Nuhu da Manzanni da suka zo bayansa." Babu kuwa wata al'umma, da Allah bai aika ma ta Manzo ba tsakanin Nuhu zuwa Muhammadu, domin ya umurce su da bautar Allah shi kaɗai, ya kuma hana su bautar Ɗagutu. Dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma haƙiƙa mun aika Manzo a cikin kowace al'umma, suna cewa: "ku bauta ma Allah, ku nisanci Ɗagutu."***

***"Kuma Allah ya aiko gaba ɗayan Manzanni,"*** tun daga na farkonsu har zuwa na ƙarshe, domin su kira mutane zuwa ga bautarsa *Subhanahu wa Ta'ala* shi kaɗai, da kuma nisantar bautar wani abu wanda ba shi ba. Ya kuma aiko su ne: ***"Domin bushara,"*** da samun Aljanna ga waɗanda suka kaɗaita Allah: ***"Da,"*** kuma: ***"Gargaɗi,"*** da tsoratarwa ga waɗanda suka yi wa Allah Maɗaukakin Sarki kishiya, da cewa, lalle Wuta ce madauwamarsu. ***"Dalili a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki, da ya ce: "Mazanni ne,"*** da muka aiko su zuwa ga mutane suna: ***"Masu bushara,"*** da tukuici da gidan Aljanna ga waɗanda suka yi wa Allah biyayya, ta hanyar kiyaye alfarmar mafi girman matakin ɗa'a gare shi, wato, Tauhidi. ***"Da,"*** kuma: ***"Gargaɗi,"*** ga waɗanda suka saɓa masa daga cikin *Mushrikai*, da waɗanda suka saba da sabgar ɓarna, cewa, gidan Wuta yana jiraye da su. Na'am! Wuta ce makomarsu

tunda babu wani saɓo ga Allah *Subhanahu wa Ta'ala* wanda ya kai kamar yi masa kishiya. Domin kauce wa irin wannan haɗari ne, Allah Maɗaukakin Sarki, ya aiko ma duniya da Manzanni, domin su kama hannayensu, su ɗora su a kan tafarkin gane Mahaliccinsu; bai bar su haka nan ba su yi ta hauma-haumar neman gane gaskiya. Babu kuma wani abu da Buwayayyen Sarki ya nema daga mutane baya ga biyayya zuwa gare shi. Waɗannan Annabawa da Mazanni kuma sun haɗu da manya-manyan wahalhalu da miyagun matsaloli da jarabawoyi a kan wannan tafarki na isar da saƙon Allah. Amma suka yi haƙuri har aka wayi gari haƙarsu ta cim ma ruwa.

Cewar kuma da Maɗaukakin Sarki ya yi: ***"Domin kada mutane su samu wata hujja a kan Allah bayan zuwan Manzannin."*** Yana nufin ya ɗauki wannan mataki ne, *Subhanahu wa Ta'ala* na aiko da Manzanni da annabawa domin yankan hujja ga mutane a ranar Alƙiyama. Domin kada su iya ce masa: *"Ai ba ka aiko mana da wani Manzo ba. Ba ka kuma saukar mana da wani littafi ba."* A haka sai aka yanke ma gaba ɗayan halitta hanzari, balle ɗaya daga cikinsu ya samu abin gaya ma Allah Makaɗaici; ya aiko musu da Manzanni, ya saukar musu da littattafai, ya kafa musu hujjoji, ya bayyana musu gaskiya, ya kuma tsatstsaga aƙidar Tauhidi a cikin tsarin halittarsu na azaliyya. Saboda haka babu sauran wani uzuri ga kowa. Tabbas babu, tunda ya aiko Manzanni wasu bayan wasu suna bayyana wa mutane addininsu, da sauran abubuwan da Mahaliccinsu yake so, yake kuma ƙauna. A hannu ɗaya kuma ya baje musu kolin duk abin da ke fusata shi, da hanyoyin Aljanna da na Wuta. Duk wanda ya kafirce daga cikinsu bayan haka, to, ya faɗa tafarkin rashin arziki, shantam.

***"Farkonsu,"*** waɗannan Manzanni shi ne Annabi: ***"Nuhu Alaihis Salam.*** Tsakaninsa kuwa da Annabi Adamu *Alaihis Salam* ƙarni goma ne. gaba ɗayan waɗannan Manzanni sun yi kira ne a kan tabbatar da aƙidar Musulunci. Bayan kuma da wuce wuri da azarɓaɓi a cikin girmama salihan bayi da ɗaukaka alkadarinsu, suka haifar da Shirka, sai Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko Annabi Nuhu *Alaihis Salam*; shi ne farkon Manzo a bayan ƙasa.

***"Na ƙarshensu kuwa shi ne Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam."*** Wannan abu ne da ya tabbata a cikin Alƙur'ani da Sunna, da kuma haɗuwar kan malamai. Abin kuma da yake tabbatar da zaman Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, annabin ƙarshe a cikin littafin Allah Maɗaukakin Sarki, shi ne faɗarsa: *"Kuma Muhammadu bai kasance uban ɗaya daga cikin mazajenku ba. Sai dai Manzon Allah ne, kuma cikamakin tsarin Annabawa."* Daga cikin Sunna kuma, akwai faɗar Ma'aiki *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: *"Ai yadda al'amarin yake; babu wani Annabi da zai sake zuwa a bayana."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[331]

***"Dalili kuma a kan kasancewar Nuhu Alaihis Salam farkon Manzanni,"*** daga cikin Alƙur'ani: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Lalle ne mu, mun yi wahayi a gare ka,"*** ya kai Annabi Muhammadu: ***"Kamar yadda muka yi wahayi ga,"*** farkon Manzanni, wato: ***"Nuhu,"*** *Alaihis Salam:* ***"Da Mazanni daga bayansa,"*** shi Nuhu ɗin. Shi ne Annabi na farko, wanda ya fara kira da gargaɗi a kan a nisanci Shirka. Dalili kuma daga cikin Sunna a kan cewa Annabi Nuhu shi ne farkon Manzanni, shi ne abin da ya tuzgo a cikin "Hadisin Ceto" cewa, wasu mutane a wannan rana za su zo wurin Annabi Adamu *Alaihis Salam,* suna neman ceto. Sai ya gaya musu cewa: *"Haƙiƙa Ubangijina ya yi fushi mai tsanani a wannan rana, irin wanda bai taɓa yi ba, ba kuma zai sake yi ba. Ya ƙara da cewa, idan ba ku manta ba ya hana ni cin wata itaciya, amma na saɓa. Saboda haka, ni ta kaina nake yi. Sai ku nemi wani wanda ba ni ba. Kai! ku ma dai tafi ku iske Nuhu. Sai mutane su ɗunguma su iske Nuhu, su gaya masa cewa: Ya kai Nuhu! Kai ne farkon Manzannin da Allah ya aiko zuwa kan doron ƙasa…."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[332]

Shi kuwa adadin Annabawa, Abu Zarri *Radhiiyallahu Anhu* yana cewa a kan sa: *"Na taɓa cewa, ya Manzon Allah! Shin adadin Annabawa nawa ne? Sai*

---

[331] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (3267) 3/1273, daga Hadisin Muslimu Hadisi na (1842) 3/1471 daga Hadisin Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

[332] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (3162) 3/1215, da Hadisin Muslimu Hadisi na (194) 4/1471 daga Hadisin Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

*ya karɓa mani da cewa: Dubu ɗari da dubu ashirin da dubu huɗu. Na ce: To, nawa ne adadin Manzanni? Sai ya karɓa da cewa: Ɗari uku da goma sha uku; lalle taro ya yi taro."* Ibnu Hibban ne ya riwaito shi.[333] Daga cikinsu akwai waɗanda Allah Maɗaukakin Sarki ya ba mu labari game da su, akwai kuma waɗanda bai ba mu ba. Tabbacin wannan kuwa shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Kuma wasu Manzanni lalle mun ba ka labari game da su, tun daga gabani. Wasu Manzannin kuma ba mu ba ka labari game da su ba."* Aiko waɗannan Manzanni kuwa da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi, ya kuma saukar da littattafai tare da su, hujja ce da yanke hanzari ga mutane.*

***"Babu kuwa wata al'umma,"*** da take ƙunshe da wani rukuni na jama'a: ***"Da Allah bai aika wa Manzo ba,"*** wanda zai kira su zuwa ga kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki, da yi musu kashedi da Shirka. Wannan kuma tun daga: ***"Tsakanin Nuhu Alaihis Salam,*** Manzo na farko a bayan ƙasa: ***"Zuwa Muhammadu Sallallahu Alaihi wa Sallam,"*** wanda shi ne na ƙarshen Manzanni, cikamakin tsarinsu kuma mafi daraja da ɗaukaka daga cikin su, mafi kuma yawan mabiya. Wato, a taƙaice dai babu wata al'umma, wadda Allah Maɗaukakin Sarki bai aika wa Manzo ba, domin yankan hanzari da kafa hujja a kan bayinsa. A hannu ɗaya kuma domin hakan ta zama wata hanya da zai bayyana wa bayinsa hanya madaidaiciya. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa a kan haka: *"Kuma babu wata al'umma face wani mai gargaɗi ya shuɗa a cikinta."*

Ya kuma aika Manzon ne *Subhanahu wa Ta'ala*: ***"Domin ya umurce su da bautar Allah shi kaɗai."*** Wannan shi ne abin da kowane Manzo yake kiran mutanensa zuwa gare shi, a matsayinsa na wani ɗayaɗayan saƙon da aka aiko su da shi. A haka sai aka wayi gari abin da kiran nasu ya ƙunsa a jumlace, shi ne bauta wa Allah shi kaɗai. Bayan haka: ***"Ya hana su bautar Ɗagutu;"*** a wayi gari sun yi musu tawaye, su da gaba ɗayan ma'abutansu. Ashe kenan da za a yi

[333] *Sahih Ibn Hibban,* Hadisi na (361) 2/76-79 daga Hadisin Abu Harri *Radhiyallahu Anhu.*

wa gaba ɗayan saƙonnin waɗannan Annabawa kallon tsaf, za a fahimci cewa, abu ɗaya ne suka zo da shi, wato, Tauhidi da tsoratarwa daga Shirka.

***"Dalili kuwa a kan haka shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Kuma haƙiƙa mun aika Manzo a cikin kowace al'umma,"*** da kowane jinsi na mutane, wanda zai hore su da Tauhidi yana mai gaya musu cewa: ***"Su bauta wa Allah,"*** shi kaɗai da zuciya ɗaya. Sa'annan: ***"Kuma su nisanci Ɗagutu,"*** ta hanyar kafirce musu. Da wannan ta tabbata cewa, Tauhidi shi ne farkon abin da Annabawa suka kira mutanensu zuwa gare shi. Tabbacin wannan shi ne labarin da Allah Maɗaukakin Sarki ya bayar cewa, farkon abin da Nuhu da Hudu da Salihu da Luɗu da Shu'aibu da sauran Manzanni suka gaya wa mutanensu, shi ne: *"Ku bauta wa Allah, ba ku da wani Ubangiji bayansa."* A wata ayar kuma Maɗaukakin Sarkin yake cewa: *"Kuma ba mu aika da wani Manzo ba, daga gabaninka, face mun yi masa wahayi cewa, babu abin bauta sai ni, saboda haka, ku bauta mani."*

Ko shakka kuwa babu, idan aka wayi gari mutum ya fahimci ƙabli da ba'adin Tauhidi, ta hanyar sanin girman Allah. Hakan za ta sa ya mayar da gaba ɗayan himmarsa a kansa; neman sani da aiki da shi iyakar zarafi. Haka kuma zai yi ƙoƙarin gane kishiyarsa. Amma dai, *ala ayyi halin*, abin da yake wajaba a kan kowane bawa na Allah, shi ne mayar da hankali, matuƙar mayarwa a kan sanin tuwasun addini kafin rassansa, waɗanda suka haɗa da salla, da zakka, da matara kama da su. Duk irin yadda mutum zai tsare alfarmar salla ko zakka, misali. Ba yadda za a yi ya samu ladarsu a wurin Allah, idan asalin addininsa na da tasgaro, ma'ana, idan Tauhidinsa ya ɓaci.

Ashe kenan wajibi na farko, shi ne sanin asalin addini, sa'annan a yi zancen rassa. Tabbacin wannan ƙauli kuwa shi ne, hadisin Mu'azu ɗan Jabalu a daidai lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya tura shi a ƙasar Yaman a matsayin wakilinsa, inda kafin ya kama hanya yake gaya ma sa cewa: *"Ka sani! Mutanen da za ka yi hulɗa da su, ma'abuta littafi ne. Saboda haka, farkon abin da za ka kira su zuwa gare shi, shi ne Kalimar Shahada. Idan sun karɓa wannan kira naka, sai ka karantar da su cewa fa, Allah ya wajabta musu*

*salloli biyar a cikin kowane dare da wuni."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[334]

Wannan yana nuna cewa, idan waɗannan mutane ba su gane Tauhidi ba, balle su yi aiki da shi, to, ba bukatar kiran su zuwa ga sallah, tunda ba su riga sun yarda da shi, sun shiga Musulunci ba. Saboda sallah, da sauran ayyukan ibada, ba su da wani amfani ga bawa, matuƙar ba shi da ingantaccen Tauhidi. Tauhidi matsayin fandisho yake ga gini. Ka kuwa san babu yadda za a yi shigifa ta tsaya da ƙafafunta, matuƙar ba a kan nagartaccen fandisho a ka ɗora ta ba. Haka, duk wani reshe da ka raba da asalinsa, babu abin da zai hana ya yanƙwane, ya bushe, ya kakkaɓe, ƙarshe kuma ya faɗi. To, ba kuwa komai ne asalin addini da tushensa ba, illa Tauhidi. A sane nake cewa, salla tana da babban matsayi a addinin Musulunci, wanda yake ma, ita ce ginshiƙinsa. Amma, ai tattare da haka. Tarihi ya tabbatar da cewa, sai da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya share shekaru goma cur yana kira da yekuwa a kan Tauhidi, sa'annan daga bisani aka farlanta Sallah.

Wani abu kuma da yake tabbatar da matsayin Tauhidi, na ginshiƙin Musulunci, shi ne irin yadda ake samun wanda zai shiga Aljanna ba tare da ya taɓa yin ko raka'a ɗaya ba a rayuwarsa. Lasisinsa kuwa ga wannan ƙofa duk, bai wuce imani da ya yi da cewa babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, ya kuma furta hakan ba. Sa'annan kuma ya riƙe ƙaƙam har Allah ya karɓi rayuwarsa a kan haka. Wato, ina nufin kamar mutum ya karɓi Musulunci yanzu-yanzu. Kafin kuma lokacin Sallah ya yi, kwaram sai a kira yaƙin jihadi. Shi kuma a matsayinsa na wanda ya musulunta, sai ya naɗe ƙafar wando ya ƙunduma cikin runduna. A can kuma sai aka kashe shi. Ka ga ya yi shahada.

Tabbacin wannan kuwa shi ne, Hadisin Bara'u ɗan Azibu *Radhiyallahu Anhu* da yake cewa: *"Wani mutum ya zo wurin Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam ɗauke da kansakalin ƙarfe, ya ce: Ya Manzon Allah! Zan je wurin yaƙi idan na dawo in karɓi Kalimar Shahada. Manzon Allah ya ce masa:*

---

[334] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (1395) 1/430, da *Sahih Muslim,* Hadisi na (19) 1/50.

*A'a, ka dai karɓi kalimar, sa'annan ka tafi yaƙin. Nan take kuwa ba tare da wata gardama ba, sai ya karɓi kalima, ya kuma faɗa cikin runduna. Ana shaya daga kuwa sai aka kashe shi. Sai Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ce: Kun gani ko! Ya yi aiki ɗan taƙaitacce, amma ya samu gagarumin sakamako."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.

Tabbas, Sallah ko da an yi mata rakiya da Zakka da Azumi, matuƙar ba a yi musu shimfiɗa da masaniyar Tauhidi da aiki da shi ba, tare da ƙudurce hakan a cikin zuciya, ba su da wani amfani ga mai su. Da su da babu, duk ɗaya. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Kuma mun gabata zuwa ga abin da suka aikata na aiki, sai muka sanya shi, toka abin watsarwa."* Wannan aya ita take nuna mana irin matuƙar girma da muhimmacin da kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki a cikin bauta yake da su, wato Tauhidi. Wannan ya sa kusan duk waɗanda suka halaka, ba komai ya ja musu haka ba, illa yin ko oho da Tauhidi, da kuma aiki da shi. Kofar kuwa da Shaiɗan ya samu ya shigar wa ire-iren waɗannan mutane, waɗanda suka samu kansu a cikin farfajiyar Shirka, ita ce, mummunar maganar da suke yamaɗiɗi da ita cewa, ai da zarar mutum ya furta kalimar shahada, to, ya gama komai, idan ana zancen Musulunci. Ko alama kuwa, ba haka wannan lamari yake ba. Wajibi ne a kan kowane musulmi ya san cewa, sanin kalimar shahada kawai, tare da furuci da kuma ƙudurta ta a zuci, ba tare da sani da kuma aiki da abin da take nufi ba. Kari a kan haka ya zamana ba a yi kaffa-kaffa da abubuwan da suke warware ta ba. Irin wannan matsayi, har abada ba zai haifa wa mai shi ɗa mai ido ba.

Kuma ko da mutane suke zaton ilimin Tauhidi, da Shirka a hannu ɗaya, wani abu ne mai wuya. Ba haka al'amarin yake ba. Hasali ma idan ana zancen ilimi, babu abu mai sauƙin ganewa, ga asali kamar su. Tabbas! A dunƙule, sanin waɗannan fannona guda biyu ya fi komai sauƙi. Ai ka ga a daidai zamanin da aka aiko Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, mutanen Makka sun san abin da Tauhidi da Shirka suke nufi. Saboda haka ne duk wanda Allah ya tarfa wa garinsa nono, ya iya furta kalimar *la'ilaha illalah,* sai ka taras ba tare da wani ɓata lokaci ba, ya kwashe nasa ya nasa, ya bar Shirka. Dalili kuwa ya

san cewa, ita da Tauhidin da ya runguma a yanzu, ba su ga maciji; hanyar jirgi daban da ta mota. Bisa wannan dalili ne, a lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ba su goron gayyata zuwa ga Tauhidi, sai suka mayar masa da martani cewa: *"Yanzu ashe, zai mayar da allola su koma alla ɗaya! Lalle, haƙiƙa wannan wani abu ne mai ban mamaki."*

Amma daga baya, da aka samu shubuha ta yawaita, sai gane Tauhidi da abin da ya ƙunsa, da kuma sanin irin yadda za a kauce wa kishiyarsa, ya wuyata. Hakan kuwa ta faru ne saboda irin yadda munafucci ya ci zukatan mutane ya kuma cinye. Aka wayi gari mafi yawan masu furta wannan kalima ta shahada, suna bauta ma waɗansu abubuwa ne ba Allah ba a lokaci ɗaya. Ba kuwa komai ya haifar da haka ba, illa irin yadda aka jahilci ma'anar kalimar ta Tauhidi. Wato, mafi yawan mutane a waɗannan kwanuka zaton suke yi, bauta wa Allah Maɗaukakin Sarki shi kaɗai ba tare da kafirce ma ɗagutu ba, shi ne kawai abin nema. Ko kuwa idan mutum ya furta kalimar kawai, ba tare da tabbatar da manufofinta ba, da kuma aiki da abin da take ƙunshe da shi, ya gama komai.*

# KAFIRCE MA ƊAGUTU NA CIKIN IMANI

*Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:*

*"Kuma Allah ya wajabta wa gaba ɗayan bayinsa kafirce ma Ɗagutu da imani da Allah. Malam Ibn Al-Kayyim Rahimahullahu yana cewa: "Ɗagutu shi ne duk abin da bawa ya wuce wuri a cikin tabbatar masa da haƙƙinsa, daɗa abin bauta ne, ko na yi wa biyayya ko ɗa'a." Ɗagutoci kuma suna da yawa. Sai dai manya-manya daga cikinsu biyar ne: Iblisu, la'antaccen Allah, da wanda aka bauta wa cikin yardarsa, da wanda ya kira mutane zuwa ga bauta masa, da wanda ya yi iƙrarin sanin wani abu na ilimin gaibi, da kuma wanda ya yi hukunci ba da abin da Allah ya saukar ba."*

*"Kuma Allah ya wajabta wa gaba ɗayan bayinsa,"* mutane da aljannu, maza da mata, Larabawa da bobayi, bayi da 'ya'ya, su: *"Kafirce ma Ɗagutu,"* da raba gari da duk wani abin bauta, da ma'abutansa, da yin imani da zamansu ba bakin komai ba; ba su iya amfanin kowa balle cutar da shi. *"Da,"* kuma *"Imani da Allah,"* ta hanyar kaɗaita shi da bauta, ba tare da yi masa kishiya ba.

Duk kuwa wanda ya yi imani da Allah, amma a hannu ɗaya bai kafirce ma Ɗagutu ba, ba za a kira shi *muwahhidi* ba. *Muwahhidi,* wato, wanda ya kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki, kaɗaitawa ta haƙiƙa, shi ne wanda ya haɗa hancin rukunan Tauhidi guda biyu, wato, kafirce ma Ɗagutu da kuma imani da Allah. Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah *Subhanahu wa Ta'ala*: *"Duk wanda ya kafirce ma Ɗagutu, ya kuma yi imani da Allah, to, lalle haƙiƙa, ya yi riƙo da igiya mai ƙwari wadda ba ta tsinkewa."* Wato, a taƙaice mutum ba zai cika mai imani ba, sai lokacin da ya yi baran-baran da duk wani abu da ake bauta wanda ba Allah ba. A lokaci ɗaya kuma ya bayar da gaskiya da Allah.

***"Malam,"*** Abu Abdullahi, Muhammadu ɗan Abubakar, wanda aka fi sani da: ***"Ibn Kayyim,"*** *Al-Jauziyyah:*[335] Allah ya yi masa rahama mayalwaciya, ya kuma saka shi Aljanna mafi girma da ɗaukaka: ***"Yana cewa,"*** game da fassarar kalimar: ***"Ɗagutu:"*** [336] ***"Shi ne duk abin da bawa ya wuce wuri a cikin tabbatar masa da haƙƙinsa."*** Yana nufin matsayin shi wannan abu, ko ma mene ne, wanda Shari'a ta tanadar masa. Da zarar haka ta faru, to, wannan wuce wuri da ya yi masa, ya sa sunansa a wannan rana ya tashi daga yadda aka san shi ya koma Ɗagutu, a wurinsa. Wannan wuce wuri da ya yi: ***"Daɗa,"*** ya shafi wani: ***"Abin bauta ne,"*** tare da Allah, ta hanyar kowace irin bauta. ***"Ko"*** ya shafi wani abu ne: ***"Na yi wa biyayya,"*** a cikin saɓon Allah, duka ɗaya. Wannan hukunci ya shafi duk masu kira zuwa ga kafirci da ɓata. Haka kuma ya shafi bokaye da matsibbata, waɗanda ake yi ma ɗa'a da biyayya a cikin abin da suka faɗa. ***"Ko,"*** wani abu ne da ake yi ma: ***"Ɗa'a,"*** wanda ba Allah ba, a cikin haramta halas, ko halasta haram. Bayan haka sai Ibn Al-Kayyin *Rahimahullahu* ya ci gaba da cewa: *"Da za ka yi wa Ɗagutocin duniya kallon tsaf, za ka ga ba yadda za a yi su wuce waɗannan kashe-kashe guda uku."*[337]

Idan ka fahimci wannan bayani na Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullahu* da kyau, dangane da ma'anar Ɗagutu. To, za ka fahimci cewa: ***"Ɗagutoci,"*** daga cikin halitta: ***"Suna da yawa,"*** ƙwarai da gaske. Dalili kuwa shi ne, duk wanda ya wuce iyakar da Shari'a ta shata masa na matsayi. To, hakan ta saka shi sahun ɗagutai. ***"Sai dai manya-manya daga cikinsu;"*** kuma jagorori, waɗanda aka tabbatar ta hanyar bibiya da nazari: ***"Biyar ne.*** Na farkonsu shi ne: ***"Iblisu;"*** Ɗan-lisu, jefaffe. Shi ne babban limaminsu. Ya kuma samu wannan matsayi ne sakamakon irin yadda ya wuce wuri, ta hanyar ƙin yin biyayya ga umurnin da Allah Maɗaukakin Sarki ya ba shi, da aikata abin da ya hane shi. Saboda haka duk wanda ya bauta ma wanin Allah, Ɗanlisu yana da

335 Ya rasu a shekara ta 751*Hijiriyyah*

336 *I'ilam Al-Muwaƙƙi'in* 1/50

337 Duba Littafin da ya gabata.

kamisho domin shi ne ya buɗe wannan ƙofa. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *"Ashe ban yi muku umurni na alƙawali ba, ya ɗiyan Adamu? Cewa kada ku bauta wa Shaiɗan, lalle shi, maƙiyi ne a gare ku bayyananne."* Saboda haka ne ya shahara da sunan: ***"La'antaccen Allah,"*** wanda aka kora aka kuma nisantar daga rahamar Allah. Tabbacin wannan kuwa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Kuma lalle, haƙiƙa, la'anata tana kanka har zuwa ranar sakamako."*

Na biyu kuma shi ne: ***"Wanda aka bauta wa cikin yardarsa."*** Wannan ibada koma wacce iri ce, ta tabbatar da zamansa ɗaya daga cikin manya-manyan Ɗagutai, jiga-jigai. Daɗa kuwa an bauta masa ne yana raye ko bayan mutuwarsa. Matuƙar dai ya aminta da hakan, to, magana ta ƙare. Ga abin da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa a kan haka: *"Kuma wanda ya ce daga cikinsu: Lalle ni abin bautawa ne baicinsa, to, wannan muna saka masa da wutar Jahannama. Kamar haka muke saka wa azzalumai."*

A lissafi sai ka haɗa: ***"Da wanda ya kira mutane zuwa ga bauta masa."*** Shi ne na uku daga cikin layin manya-manyan Ɗagutai, kamar Fir'auna, da sauran ma'abuta ɓarna, waɗanda ba su da wani guri a cikin ƙasa, sai dasa ɓarna da ririta ta. A ƙarshe kuma su danƙara wa mutane ƙangin bauta musu, koma bayan Allah Maɗaukakin Sarki. Ko kuwa su ɗora su a kan godaben bauta musu tare da Allah. A lokacin da suke raye ko bayan sun mutu. Misalin wannan shi ne labarin da Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yake bayar wa game da Fir'auna, da cewar da ya yi wa mutanensa: *"Ban san kuna da wani abin bauta ba bayan ni."* Bisa wannan dalili, duk wanda ya kira mutane zuwa ga bauta masa, ko da kuwa ba su bauta masa ɗin ba. To, ya zama ɗaya daga cikin Ɗagutai. Zancen sun karɓa wannan gayyata tasa, ko ba su karɓa ta ba, bai taso ba. Tunda dai har ya yi ƙarfin halin neman wani haƙƙi wanda ba nasa ba ai magana ta ƙare. Da ma ƙa'idar ita ce, duk wanda ya karkatar da wata bauta daga Allah zuwa ga kansa, to, ya yi shisshigi, ya kuma taho da gagarumar ƙarya.

Haka: ***"Kuma wanda ya yi iƙrarin sanin wani abu na ilimin gaibi,"*** kamar yadda bokaye da makamatansu, suke yi, to, shi ma ya zama wani marga-

margan dutse a duniyar Ɗagutai; shi ne kuma na huɗunsu. Duk kuma abin da yake gaya wa gamagarin mutane, ba komai ba ne illah ƙarya da yaudara. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa : *"Kuma a wurinsa a kwai mabuɗan gaibi; babu wanda ya san su sai shi."* Tabbas! Baya ga Allah Maɗaukakin Sarki, babu wani Mala'ika ko Annabi da ya san ilimin gaibi, balle daɗa wanda ba su ba daga cikin aljanu ko mutane ko masihirta ko kuma bokaye. Wannan kuwa yana daga cikin abubuwan da suke daɗa tabbatar da buwayar Allah Maɗaukakin Sarki, da ƙarfin *rububiyyarsa.* Tabbacin wannan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Ka ce: Duk wanda yake a cikin sammai da ƙasa bai san gaibi ba, sai Allah."* A wata ayar kuma yake cewa: *"Masanin gaibi da bayyane. Saboda haka ya girmama daga shirkin da kuke yi masa."*

Na biyar: ***"Kuma,"*** daga cikin waɗannan Ɗagutai, shi ne ***"Wanda ya yi hukunci ba da abin da Allah ya saukar ba."*** Wato, kamar wanda ya yi hukunci da dokokin Jahiliyyah, ko wani abu da ɗan adamu ya tsara, wanda babu shi a cikin Shari'ar Allah. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana cewa: *"Ashe ba ka gani ba zuwa ga waɗannan, da suke raya cewa, sun yi imani da abin da aka saukar zuwa gare ka, da abin da aka saukar a gabaninka, suna son su kai hukunci zuwa ga Ɗagutu, alhali, haƙiƙa, an umurce su da su kafirce masa."* A wata ayar kuma mai girma da ɗaukaka yana cewa: *"Kuma duk wanda bai yi hukunci da abin da Allah ya saukar ba, to, waɗannan su ne kafirai."* Allah Maɗaukakin Sarki shi ne wanda ya samar da gaba ɗayan halitta, saboda haka ya fi kowa sanin yanayi ya halaye da kuma ayyukansu. Shi ne kuma wanda ya saukar da hukunce-hukunce na adalci, waɗanda ya kamata a ce ana hukunci da su a kotunan musulmi. Da wannan kuma sai ya zama farilla a kan gaba ɗayan halitta su yi hukunci da abin Allah ya saukar.*

## BABU TILASTAWA A ADDINI

***Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ci gaba da cewa:***

***"Dalili kuma shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Babu tilastawa a cikin Addini. Haƙiƙa shiriya ta bayyana daga ɓata. Duk wanda ya kafirce ma Ɗagutu, ya kuma yi imani da Allah. To, haƙiƙa, ya yi riƙo da wata igiya mai ƙwari, wadda ba ta tsinkewa." Wannan shi ne ma'anar La'ilaha illallah. A cikin Hadisi kuma: "Kan al'amari shi ne Musulunci. Jijjigensa kuma shi ne sallah. Tsororuwar tozonsa kuma shi ne jihadi saboda Allah. Allah shi ne mafi sani. Tsira da amincin Allah su tabbata a kan Muhammadu da alayensa da sahabbansa."***

***"Dalili kuma,"*** a kan cewa Allah Maɗaukakin Sarki ya wajabta wa gaba ɗayan bayinsa, kafirce ma Ɗagutai, da kuma ba da gaskiya da shi: ***"Shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: "Babu tilastawa a cikin Addini."*** Yana nufin ba ya halasta a tilasta wani mahaluki ya shiga addinin Musulunci. Dalili kuwa shi ne, addini ne shi kammalalle, da yake tafiya kafaɗa da kafaɗa da tsarin halittar mutum na azaliyya. Da kuma kasancewar sa bayananne, mai sauƙin ganewa idan aka yi la'akari da dalilai da kuma hujjojinsa. Saboda haka ba ya bukatar a tilasta wani domin ya karɓe shi. Amma, duk wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya haskaka zuciyarsa, ya kuma faɗaɗa ƙirjinsa. A lokaci ɗaya kuma ya buɗe idanunsa, sai kawai a wayi gari ya samu kansa a cikin wannan addini a zaɓin kansa. Wanda kuma Allah ya makantar da zuciyarsa, ya kuma kife ƙofofin kunnuwa da idanunsa. Irin wannan babu yadda za a yi shiga Musulunci ya amfane shi da wani abu, matuƙar da ƙarfi a ka saka shi a ciki.

Sai dai yana da kyau a kula ƙwarai da gaske, wannan aya, babu cin karo tsakanin ta da waccan, wadda take magana a kan wajabcin jihadi. Dalili kuwa shi ne, jihadi an shar'anta shi ne saboda a kawar da duk wanda ya ce addinin Musulunci ba zai yaɗu ba. Amma, idan aka ce a yi amfani da shi domin a

tilasta wani mahaluki shiga addinin, to, an taho da wani abu sabo. Dalili kuwa shi ne, ai mun riga mun faɗa a baya kaɗan cewa: *"Tabbas, shiriya ta bayyana daga ɓata."* Wannan kalami kuwa yana nufin ne, gaskiya ta riga ta fito fili; an gane banbacin da yake akwai tsakaninta da ɓata. haka kuma imani, shi ma ya bayyana ƙarara; an iya tantancewa tsakanin shi da kafirci. *Kazalika* shiriya, mutum ko makaho ne, ba shi da bukatar wani dogon lokaci kafin ya gane cewa, wannan shiriya ce wannan kuma ɓata ne. Saboda hujjoji da dalilai, masu nuni a kan haka. Tunda kuwa har gaskiyar nan da kuma ɓata, kowanne daga cikinsu ya kama wurinsa ya yi tama-tela, babu abin da zai hana kowane irin mutum mai cikakken hankali, zaɓar gaskiya.

***"Duk,"*** kuwa: ***"Wanda ya kafirce ma Ɗagutu,"*** ta hanyar ƙaurace ma duk wani abu da ake bauta koma bayan Allah, da ma'abutansu; ya yi baran-baran da su. To, ya tabbatar da rukuni na farko daga cikin rukunan Tauhidi guda biyu. Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab ya ƙara da cewa: *"Yadda ake kafirce ma Ɗagutu shi ne, ka ƙudurce cewa bautar da ake yi ma duk wani abu, wanda ba Allah ba, aikin banza ce. Sa'annan a nisance ta, a kuma ƙyamace ta a zuci. Bayan haka kuma duk wanda yake da wata alaƙa da ita, a jefa masa gatarin kaulasan, a kuma shaya fagen gaba da ƙiyayya da shi."* [338] Tabbas! Kafirce ma Ɗagutu wani babban sharaɗi ne, wanda sai idan ya tabbata sa'annan ibadar mutum za ta samu karɓuwa a wurin Allah. Malam Ibn Al-Kayyim *Rahimahullahu* yana cewa: *"Bauta ma Allah da nuna masa soyayya da ƙauna, da kuma dogara gare shi, sa'annan a laɓe a inuwarsa, a kuma ji tsoron sa, a kuma yi fatan alhairi daga gare shi, abubuwa ne da ba su wadatarwa, har sai an wayi gari bawa ya nisanci bautar wanin Allah Maɗaukakin Sarki, da dogaro a kan sa, da laɓewa a inuwarsa, da tsoron sa, da kuma fatar samun alhairi daga wurinsa. Ya kuma ƙyamaci haka iyakar ƙyama."* [339]

Wanda kuma duk: ***"Ya yi imani da Allah. "*** ta hanyar bauta masa shi kaɗai, ya kuma wayi gari babu abin da zai aikata, face saboda Allah. To,

---

[338] *Majmu'at At-Tauhid,* shafi na 260.
[339] *Shifa' Al-Alil,* shafi na 346.

tabbas, wannan ya tabbatar da samuwar rukuni ɗaya na Tauhidi. Sheikh Muhammad bn Abdilwahhab *Rahimahullahu* ya ƙara da cewa: *"Ma'anar imani da Allah ita ce: Ka ƙudurce a ranka cewa, lalle Allah, babu abin bautawa bisa cancanta sai shi, shi kaɗai ba tare da yi masa kishiya ba. Bayan haka ka tsayar da niyyarka a cikin gaba ɗayan ayyukan ibada, su zama saboda shi, bayan ka haramta ta ga duk wani mahaluki wanda ba shi ba. Bayan haka kuma ka so ma'abuta tsoron Allah, ka kuma riƙe su madogara. Su kuwa ma'abuta Shirka, ka nuna musu iyakar ƙi da ƙyama da ƙiyayya."*

Duk wanda ya yi sa'a, waɗannan rukunai biyu na Tauhidi, suka samu gare shi, wato kafirce ma Ɗagutu, da kuma imani da Allah: ***"To, haƙiƙa, ya yi riƙo da wata igiya mai ƙwari, wadda ba ta tsinkewa"*** ita ce Tauhidi. Wato, ƙafafunsa sun riga sun kama ƙasa a kan tafarki madaidaici. Ko shakka babu kuwa, duk wanda ya riƙi igiyar Tauhidi, to, duk irin yadda ta yi gaji-gaji, babu abin da zai hana shi shiga Aljanna.

***"Wannan shi ne ma'anar La'ilaha illallah."*** Ai ba komai kalimar *la'ilaha,* take nufi ba, illa kafirce ma Ɗagutai. A yayin da ita kuma ta *illallah,* take nufin imani da Allah, tare da miƙa wuya ga al'amarinsa da kuma shari'arsa. Kalimar kuma ta Tauhidi ta fara da zancen kafirce ma Ɗagutai ne, kafin bayar da gaskiya da Allah, saboda babu yadda za a yi abu ya cika ya kuma kammala, matuƙar ba a gusar da ababen da ke iya kawo masa cikas ba.*

***" A cikin,"*** wani dogon: ***"Hadisi kuma,"*** wanda Turmizi ya riwaito daga Mu'azu ɗan Jabalu *Radhiiyallahu Anhu,* ya ce: Na ce: Ya Manzon Allah! Ka ba ni labari game da wani aiki, wanda zai shigar da ni Aljanna, ya kuma nisantar da ni daga Wuta. Sai ya ce: Wo! Lalle ka yi tambaya game da babban abu. Duk da yake mai sauƙi ne ga wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya sauwaƙe wa. Na farko, ka bauta wa Allah. Kada kuma ka haɗa shi da kowa a cikin bauta. Ka kuma tsayar da Sallah, ka bayar da Zakkah, ka yi Azumin watan Ramadhan, ka kuma ziyarci ɗakin Allah. Sa'annan ya ce: Ko kana so in ɗora hannunka a kan ƙofofin alhairi? Ka ga dai Azumi garkuwa ne. ita kuwa sadaƙa tana wanke zunubai kamar yadda ruwa ke wanke ɗatti. Da sallar mutum cikin

tsakiyar dare. Har ya karanta ayar nan da ta ce: *"Sasannin jikinsu suna nisantar shimfiɗar baccinsu, suna kiran Ubangijinsu a cikin tsoro da kwaɗayi, kuma daga cikin abin da muka arzuta su, suke ciyarwa. Ba wani mai rai da ya san iyakar abin da aka ɓoye mai sanyaya idanu dominsu, sakamako ga abin da suka kasance suna aikatawa."* Sa'annan ya ce: *"Ko kana son in ba ka labari game da kan al'amari dukansa, da ginshiƙinsa, da kuma tsororuwar tozonsa?* Na ce: Eh! Ya Manzon Allah. Sai ya ce: Kan al'amari shi ne Musulunci, ginshiƙinsa kuwa shi ne sallah. Tsororuwar tozonsa kuwa shi ne jihadi. Sa'annan ya ce: Ko kana son in ba ka labari game da abin da ya mallake su duka? Sai na ce: Eh! Ya Manzon Allah. Sai ya kama harshensa, ya ce: Ka kiyayi wannan ga kanka. Sai na ce: Ya Manzon Allah! Ashe ana kama mu da laifin maganar da muke yi? Sai ya ce: Kaiconka ya Mu'azu! Ko akwai abin da yake kife mutane a cikin wuta, a kan fuskokinsu. Ko ya ce: A kan hantunansu in ba girbe-girben harsunansu ba."

***"Kan al'amari,"*** wato, addini, wanda Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya zo da shi: ***"Shi ne Musulunci."*** Musulunci kuwa ba komai yake nufi ba illa: *shaidar babu wanda ya cancanci bauta daga wurin bayi sai Allah mahaliccinsu. Kuma Annabi Muhammadu Manzon Allah ne. Duk wanda ya kiyaye alfarmar wannan kalima, tabbas, zai shiga Aljanna.*

Mawallafin *Rahimahullahu* yana nufin ne ya kafa hujja da wannan hadisi a kan cewa, kowane al'amari yana da kai. To, kan al'amarin da Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya zo da shi, shi ne Musulunci. Saboda haka duk wanda ya yi iƙirarin cewa, ya karɓa kiran Allah, da na Manzonsa, amma a haƙiƙanin gaskiya bai riƙi abin tsakani da Allah ba, bai kuma kama hanyar addini gadan-gadan ba. To, duk wanda hakan ne halinsa, ya tabbata maƙaryaci.

***"Jijjigensa kuma,"*** shi, wannan addini: ***"Shi ne sallah."*** Wannan magana kuwa tattare take da cikakken bayani a kan maɗaukakin matsayin da Sallah take da shi a cikin addini. Wato, matsayin da take da shi, daidai yake da

na ginshiƙi[340] ga ɗaki ko shigifa. Ka kuwa san da zarar ginshiƙi ya kare, to, babu abin da zai hana shigifar faɗuwa. To, haka abin yake; da zaran aka rasa Sallah ga mutum to, addininsa ya rushe. Malam Ibnu Rajab *Rahimahullahu* yana cewa: *"Shi kuwa ƙashin bayan addini, wanda ba yadda za a yi ya tsayu ba tare da shi ba, kamar yadda shigifa ba ta tsayawa sai a kan ginshiƙi. To, shi ne Sallah."* [341] Dalilin wannan kamance kuwa shi ne, zaman barin sallah kawai kafirci, wanda yake fitar da mutum daga Musulunci.

Wannan Hadisi ya isa dalili a kan cewa, duk wanda kasala kawai ta sa ya bar Sallah, to, ya zama kafiri. Wani dalili kuma da yake tabbatar da wannan hukunci, shi ne, faɗar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, cewa: *"Abin da yake tsakanin mutum da Shirka, da kuma kafirci, shi ne barin sallah."* Muslim ne ya riwaito shi.[342] Haka kuma Umar ɗan Khaɗɗabi *Radhiyallahu Anhu* ya ce: *"Babu wani rabo a cikin Musulunci, ga wanda ya bar Sallah."* Maliku da Daraƙuɗni suka riwaito shi.[343] Haka kuma sallah tana ɗaya daga cikin ayyukan da Allah Maɗaukakin Sarki yake so da ƙauna. Saboda haka ne farkon abin da za a ayi wa ɗan Adam hisabin sa, a ranar ƙiyama shi ne Salla. Ita ce kuma kawai ibada ƙwara ɗaya taya tal, wadda Allah Maɗaukakin Sarki ya farlanta wa al'umma da kansa a daren *Mi'iraji;* bai sanya wani Manzo tsakaninsa da Annabi ba a cikin wannan lamari na Salla. An kuma riwaito cewa, saboda muhimmancin salla a cikin wannan addini, Khalifa Umar ɗan Khaɗɗabi yake rubuta ma Gwamnoninsa wasiƙa cewa: *"Babban aikin da nake son ku tsare shi ne Sallah. Duk wanda ya kiyaye alfarmarta, ya kuma tsare yin ta, to, ya tsare addininsa. Wanda kuma duk ya tozarta ta, to, babu abin da fa ba zai tozarta ba."* Maliku ne ya riwaito shi.[344]

---

[340] Kalimar ginshiƙi, mun fassaro ta ne daga kalimar *"alfusɗaɗ"* ta Larabci. Fusɗaɗ kuma a harshen Larabci yana nufin 'baitin waƙa.' An samo wannan fassara ne daga littafin *Lisan Al-Arab* 9/126, da kuma *Mukhtar As-Sihah* shafi na 211.

[341] *Jami' Al-Ulum wa Al-hikam,* 1/274.

[342] *Sahih Muslim,* Hadisi na (82) 1/88 daga Jabiru ɗan Abdulahi *Radhiyallahu Anhu.*

[343] *Muwaɗɗa' Malik* 1/39-40, da *Sunan Ad-Daraƙuɗni* 2/52.

[344] *Muwaɗɗa' Malik,* Hadisi na (6) 1/ 6

Karewa da ƙarau ma, sallah aba ce wadda take hani daga alfasha da mugun aiki, take kuma gadar da ƙanƙan da kai da tsoron Allah."*

*"Tsororuwar tozonsa,"* shi Musulunci, kamar yadda tsororuwar komai ita ce, muhalli mafi ɗaukaka da bayyana a cikinsa. Shi ne jihadi. An kamanta shi da tozon raƙumi ne, wanda shi ne ma'anar kalimar *sanaamu* ta Larabci. Shi kuwa tsororuwar tozon raƙumi, kowa ya san shi ne abu mafi ɗaukakar muhalli a cikin jikinsa. To, haka addini shi ma yana da tozo, yana kuma da tsororuwarsa. Waɗannan muhalli kuma shi ne jihadi *fi sabilillahi.* Jihadi shi ne abin da yake ɗaga darajar wannan addini tare da fitowa da martabarsa a fili. Malam Ibnu Rajab *Rahimahullahu* yana cewa: *"Wannan yana nuna cewa jihadi shi ne mafi girman ayyuka a cikin Musulunci bayan sauran farillai."* [345] Jihadi ya samu wannan matsayi ne, saboda irin yadda yake kare wa addinin Musulunci martaba da daraja. Hanya ce kuma shi, wadda ake kiran mutane zuwa ga shiga addinin Allah da ita, tare da ɗora su a kan tafarkin gaskiya ɗorawa ta har abada. Saboda haka aka ba shi wannan matsayi na zama tsororuwar addini, sakamakon kariyar da yake ba shi, yake kuma ba wa harkar Da'awah.

Jihadi shi ne aiki mafi maɗaukaka a cikin addini. Malam Ibnu Daƙiƙ Al-Id *Rahimahullahu* yana cewa: *"Babu wani aiki da yake iya ja-in-ja da jihadi."* [346] An kuma riwaito cewa, wani mutum ya zo wurin Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, ya ce masa: *"Ka karantar da ni wani aiki, wanda yake daidai da jihadi." Sai Annabi Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ce: Ban san shi ba." Sai ya sake cewa: To, ko kana iya idan mujahidai suka fita fagen fama, kai kuma ka shige masallaci ka yi ta sallah ba tsayawa. Ka kuma ɗauki Azumi babu shan ruwa ba? Sai ya ce, wa zai iya haka?"* Buhari ne ya riwaito shi.[347] Ba kuwa komai ya sa jihadi ya samu wannan matsayi ba, illa irin sadaukarwar da babu ita a cikin wani abu wanda ba shi ba. A cikin jihadi ne kawai mutum yake

---

[345] *Jami' Al-Ulum wa Al-Hikam,* 2/146
[346] *Sharh Al-Arba'in,* na Ibn Daƙiƙil-Id shafi na 169
[347] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (2633) 3/1026.

bayar da rayuwa, da dukiya, da kuma gaba ɗayan goyon bayansa domin ɗaukaka addinin Allah. A hannu ɗaya kuma ga irin gwagwarmayar da takan kasance tsakanin muminai da kafirai da munafukai. Waɗannan abubuwa ne suka taru, suka ba wa jihadi wannan matsayi. Tabbacin hakan shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Ya ku waɗanda suka yi imani! Ko kuna so in shiryar da ku a kan wani kasuwanci, wanda zai tserar da ku daga azaba mai raɗaɗi? Ku yi imani da Allah da Manzonsa, ku kuma yi jihadi saboda Allah, da dukiya da kuma rayukanku. Wancan shi ne mafi alhairi a gare ku idan kun kasance kun sani."* A wata ayar kuma Maɗaukakin Sarkin ya ce: *"Ku fita yaƙi kuna masu sauƙaƙan kaya da masu nauyi, kuma ku yi jihadi da dukiyoyinku, da kuma rayukanku a cikin hanyar Allah. Wancan ne mafi alhairi a gare ku, idan kun kasance kun sani."* Bayan haka kuma an samu nassosa da dama, da suka zo suna magana a kan falalar jihadi da kuma irin ladar da Allah Maɗaukakin Sarki ya tanada domin mujahidai. Misalin wannan shi ne faɗar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: *"Abin da yake shi ne kwatancin mai jihadi saboda Allah, tattare da Allah ne kawai ya san wanda yake jihadi saboda shi, shi ne misalin mai Azumi, mai kuma tsayuwar ibada. Ga shi kuma Allah Maɗaukakin Sarki ya yi alƙawalin shigar da masu jihadi saboda shi Aljanna idan an kashe su can. Ko ya dawo da su gida suna lafiyayyu masu kuma tarin lada ko ganima."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[348] A wani hadisin kuma mai tsira da amincin Allah ya ce: *"Tafiya ko dawowa wurin jihadi saboda Allah ya fi alhairi a kan duniya da abin da ke cikin ta."* Buhari da Muslim ne suka riwaito shi.[349]

Shaihul-Islam *Rahimahullahu* yana cewa: *"Jihadi aiki ne da ko shakka babu, ake yaba wa mai shi a zahiri. Idan kuma niyyarsa kyakkyawa ce, zai samu yabo zahiri da baɗini. Sai dai abin da zai sa ya samu wannan yabo shi ne,*

---

[348] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (2635) 3/1027, da *Sahih Muslim,* Hadisi na (1878) 3/1498 daga Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu.*

[349] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (6199) 5/240, daga Abu Ayyubal-Ansari *Radhiyallahu Anhu* da *Sahih Muslim,* Hadisi na (1883) 3/1500 daga Ummu Harisata *Radhiyallahu anha.*

*yin sa saboda taimakon Sunna da addini.”* [350] Haka kuma ta tabbata cewa, Allah Maɗaukakin Sarki ya tanadar wa masu jihadi darajoji a cikin Aljanna; gidan ni’ima. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce: *“Tabbas haƙiƙa, a cikin Aljanna akwai darajoji guda ɗari, waɗanda Allah ya yi tanadi domin masu jihadi saboda shi. Tsakanin kowace daraja da ‘yar’uwarta kamar abin da yake tsakanin sama da ƙasa.”* Buhari ne ya riwaito shi [351]

Haka kuma jihadi wani ginshiƙi ne daga cikin ginshiƙan addini. Shaikhul-Islami *Rahimahullahu* ya ce: *“Cikar Musulunci tana kasancewa ne da horo da alhairi da hani da abin ƙi. Hakan kuma ba ta samuwa sai tare da jihadi saboda Allah.”* [352] Jihadi kuma dalili ne da ake gane cikar imanin bawa; idan na Allah da Annabi ne shi. Shaikhul-Islami *Rahimahullahu* yana cewa: *“Jihadi wata hanya ce da ake gane ingancin imanin mutum da ita.”* [353]

Daga nan kuma sai mawallafin *Rahimahullahu* ya kammala wannan gagarumin aiki nasa da mayar da ilimi ga wanda ya kewaye da sanin komai, ya ce: ***“Allah shi ne mafi sani.”*** Sa’annan ya yi salati da sallama ga fiyayyen halitta, yana mai roƙon Allah da ya tabbatar masa da: ***“Tsira da amincinsa”*** shi ***“Da alayensa;”*** gaba ɗaya waɗanda suka bi addininsa: ***“Da sahabbansa,”*** masu girman daraja. Amincin Allah ya daɗa tabbata ga waɗannan rukunai na jama’ar Amada su samu katangar dutse tsakanin su da kowane irin sharri da ababen ƙi da ƙyama.

Da wannan kuma muke roƙon Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya mu daga cikin bayinsa masu bin tafarkin Tauhidi. Ya kuma tayar da mu tare da Annabawa, da Siddiƙai, da Shahidai, da Salihai; bayin da kowa ya tashi tare da su, ba zai yi nadama ba. Allah shi ne mafi sani.

---

[350] *Al-Fatawa* 4/9

[351] *Sahih Al-Bukhari,* Hadisi na (2137) 3/1038, daga Hadisin Abu Hurairata *Radhiyallahu Anhu*

[352] *Al-Fatawa*10/300

[353] *Al-Fatawa* 3/212

*Wa sallallahu ala nabiyyina muhammadin, wa ala alihi wa sahbihi wa sallama tasliman kathiran.*

Alhamdu Lillah.[354]

[354] Mun kammala Fassara a yau Laraba 11 ga Safar 1436H – 3 ga Disamba 2014M. Allah ya yi mana muwafaƙa, ya karɓi wannan aiki, ya sanya ma sa karɓuwa, ya sa mu yi tarayyar lada da asalin mawallafinsa a cikin sa.

Masu Fassara